[5/11, 17:15] ~fatieshak: *HALIN YAU*!

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

Bismillahir Rahmanir Rahim

Ina farawa da sunan Allah, ina neman tsari da rubuta 'Barna! Ina rokon na yi rubutun da za'a 'karu , ayi amfani da shi.Tsira da aminci ga shugaba Annabi(S.A.W.).

GARGADI

A kiyayi taba min labari na ta kowacce siga, Hakkin mallakar tawa ce ni ka'dai, Dole sai da izinina kafin a karanta shi a kowacce irin kafar sadarwa, wadda ya shiga hakkin mallaka kuma ubangiji ya isar mini.

JAN KUNNE

Gaba'daya Wannan labarin kirkirarsa aka yi(Fiction)!haka sunaye da garuruwan da ke ciki bana kowa bane, na zabe sune kawai dan 'kawata labarin, dan haka duk wadda yaci karo da abin da ya yi kamacanceceniya da rayuwar sa bada shi ake ba, arashi ne kawai

JINJINA

GA MARUBUCIYA

FADILA LAMIDO

SUGARI BA KI YI FARIN BANZA BA.

SADAUKARWA

Tun daga farkon labarin har zuwa karshen sa gaba'daya sadaukawa ne ga shugaban kungiyar *LAFAZEE WRITERS*

SADIQ ABUBAKAR.

1-2

Harabar makarantar kwana ta Gwamnatin Tarayya da ke garin Kiyawa (FGC Kiyawa), cike take mak'il da motoci da jama'a kama daga iyayen yara, da su kansu daliban rukuni-rukuni, gungu-gungu, cike da walwala sai ciye-ciye ake yi kasancewar yau ake ziyarar dalibai (visiting day).

Daga can gefen lambun makarantar, wata matashiyar uwa ce da a 'kalla ba za ta wuce shekaru talatin da biyu ba. Zaune take kan lallausar darduma wacce da alamu da ita ta zo, gefenta kulolin abinci ne da kuma ledoji masu dauke da tambarin *Sahad Store.*

Zaune take tana baza ido ta ga ta ina tilon dan'ta zai bullo, ba ta ankara ba ta ji an rungume ta tare da ambaton "Mamiii!"

Cike da dariya ta dago kai.

"Jawad wai ba ka san ka girma ba ne? ba don a zaune nake ba ai da ka kayar da ni."

Ya sake komawa ya kwanta a jikinta tare da cewa,

"Nayi kewarki Mami! Ina Inna?".

"Ta ce, a gaishe ka, shekaranjiya ta tafi Gamawa biki"

"Ki ce ba ta yi mini girebar ba kenan?" Ya fada cikin turo baki irin na sakalan yara.

"Wace ita? Ai ranar Laraba yini ta yi tana hidimar girebarka, bata samu sukuni ba sai da ta kammala."

Sai a lokacin ya saki fuskar yana cewa,

"Allah Sarki Innata!" Ya tashi a jikinta ya ci gaba da cewa,

"Ina yini?"

Ta amsa tana bin sa da kallon mamakin irin girman da ya 'kara cikin lokaci 'kalilan da ba ta gan shi ba, tana mamakin inda ya sami girman jiki tun da dai daga ita har mahaifinsa ba wani girma ne da su na a zo a gani ba, hasalima in ba ka sani ba cewa za ka yi 'kaninta ne.

"Kai Mami sai kin gano munina!".

Ya fada yana rufe idonsa da hannuwansa. Ta yi murmushi,

"Girmanka ne yake ba ni mamaki Jawad ka kerewa tsawona fa!"

"To, Mami aike tsayinki kadan ne, ni kuma irin tsayin Babana na yi."

"A'a, kai kam sai ka fi shi tsayi duka-duka fa watan jiya ka yi sha uku amma ka zan'kale haka!"

Cikin shagwaba ya fara fadin "Haba mana Mami ki daina fada, kar ajiyo. I am 15 fa!"

Ta kwashe da dariya tare da cewa

"Mantawa na yi ashe ka fi ni sanin ranar haihuwarka?".

Daidai lokacin ya zuge Jakarta ya dauko tsaleliyar wayarta ya mik'a mata, ''Bude mini na kira malam na ji ko ya dawo."

Ba ta ce uffan ba, ta karba ta bude masa kamar yadda ya bukata. Lambobi ya shiga daddanawa har ya jera lambar da ke adane a 'kwa'kwalwarsa a cikin wayar ya danna kira ya kara a kunne, tamkar da ma jiran kiran ya shiga ake yi, ya ji an dauka ba tare da ba ta lokaci ba, sallama ya yi tare da fadin,

"Malam!"

Daga cikin wayar aka amsa da,

"Jawad kana lafiya? Ka gan ni nan ina kan hanyar zuwa wurinka."

Cike da murna yace. "Ka dawo daga Bauchin ke nan?"

"A'a ban dawo ba yanzu dai nake kan hanyar dawowa na iso Babaldu zan biyo ta Dutse na iso Kiyawa."

Dadi ya kama Jawad, ya shiga masa addu'ar isowa lafiya, tare da cewa, "Ina wajen da muka zauna a waccan ziyarar."

Ya kashe wayar yana cewa "Oh! Allah ya so ni, jiya fa da na yi masa waya ha'kuri ya ba ni akan ba zai sami zuwa ba sai satin sama, saboda yana Bauchi, ko don bai ji na amsa masa na ha'kura ba ne, shi yasa ya bar komai ya taho?"

Ita dai ba ta sa masa baki ba har ya kammala maganarsa.

tana nazarin lokaci a agogon hannunta daya nuna 'karfe biyu har da mintuna talatin da biyar. "Ko ina ne Babaldu kuma? Ko har zai iya isowa kafin hukumar makaranta ta rufe shigowa?"

Tabe baki ta yi tana ji a ranta to ina ma ruwanta? Amma wani sashi na zuciyarta na fada mata saboda Jawad ne, ina mama ba wadda ya zo mini? Ya katse mata tunani,

"Baban Khalifa ne ba lafiya yana asibiti ka ga ai bai kamata na yi maganar mu taho tare da wani cikinsu ba."

"Me ya same shi?" Ya tambaye ta cike da nuna damuwa.

"Malaria yake ta yi har ta kada shi."

"Muma Mami ita ake ta yi anan, Allah ya sauwa'ke ya bashi lafiya, to yanzun a tasha kika sauka?"

Ta girgiza kai tana cewa, "Shatar mota muka dauko ni da iyalan gidan Ma'aji. Ka ci abincin sai mu je ku gaisa, suna can gefen mata."

Bayan La'asar ba da jimawa ba, ya iso cikin makarantar sanye yake cikin tsadadden yadi fari 'kal! 'Kafar shi dauke da takalmi cover ba'ki, kansa cike da gashi, ya dora hular zanna-bukar wadda ba ta rufe gashin ba, 'kamshin turaren Versace ke tashi a jikinsa.

A hankali yake tafiya cikin nutsuwa, matsakaicin jiki ne dashi, amma dogo ne yanayinsa daya da tauraron wasan kwaikwaiyon nan Yakubu Muhd, ba yadda za ka yi ka kalle shi ka ce shi ya haifi Jawad, sai dan tsananin kamar da Jawad ke yi da shi.

Tun kafin ya'karaso Jawad ya hango shi, don haka ya kwasa da gudu ya nufe shi.

Ga mamakin Sa'adah, sai ta ga ya 'daga Jawad cak ya yi juyi da shi tamkar yadda yake masa yana yaro.

Ya dire shi, ya ru'ko shi ta gefen shi suka doso ta, wadda duk ilahirin mutanen dake wajen sai da suka bi su da ido suna sha'awar Jawad da Babansa.

Kujera ya samo masa ya zauna daga gefe, amma ba wani tazara da inda Sa'ada ke zaune, ta juya musu baya. Hira suke cike da doki.

"Amma anya Jawad kana karatu kuwa? Ina *C.A* Result dinka?" Ya zura hannu a aljihun wandon shi ya zaro takarda ya mika masa ya karba ya bude yana dubawa, fara'arsa na 'kara fadada, ya ninke ya kalli dan nasa ya ce, "That is my boy weldone! Ka ci gaba da dagewa."

"Ni da zan zama direban jirgin sama, ai dole sai na yi karatu Malam, ko ka manta?"

"Murmushi kawai Malam din ya yi yana satar kallon gefen da Sa'adah ke zaune kamar ko yaushe ta ci kwalliya ta burgewa cikin tsadadden leshi doguwar riga(bubu), hannayen ta sun ci jan lalle da zobunan Dubai Gold, 'kamshinta na dindin na turaran Escada sentiment, turare na mussaman mai sau'kar da nutsuwa ga duk wadda yake shakar shi, sai kai wa hancinsa ziyara yake yi.

Ta sake zamowa yar yarinya, ta fi kama da 'yan shekaru ashirin da biyar ba wadda ta ba wa talatin baya ba.

Jawad ya mi'ke yana cewa, "Malam Ina zuwa.''

Kai kawai ya kada masa, kai tsaye uwarsa ya nufa, gabanta ya tsugunna ya ru'ko dukkan hannayenta,

"Mami ki zo ku gaisa da Malam mana"

Kai ta girgiza masa alamun ba za ta ba.

"Haba Mami gaisuwa kawai?"

Kan ta sake girgizawa a karo na biyu, tana ci gaba da latsa wayarta a cikin manhajar WhatsApp inda abokan tafiyarta suka ce mata ya kamata su ta fi haka nan, kar su yi dare. dan haka ta fara tattare warmers din da ta zo da su, tare da mi'ka masa ledojin siyayyar da ta kawo masa, tana sake jaddada masa ya kula da karatu ya kuma kula da ibada, muryarsa na rawa alamun zai yi kuka ya ce mata, "Ba fa ki gai da Malam ba".

A dan tunzure ta ce "Dole ne?"

Ganin kwalla a idonsa sai jikinta ya yi sanyi ta dauki handbag din ta tare da basket mai dauke da kulolin ta ce "mu je to."

Karbar basket din ya yi suka nufi Malam din da tazarar su bai fi taku biyar ba, don haka a kan kunnen shi duk yake jin tattaunawarsu.

Ba ta isa daf da shi kamar yadda Jawad ya yi ba, ta tsaya daga dan nesa ta ce, "Ina yini?"

ji ya yi kamar ba zai amsa ba tunda a wulakance ta yi gaisuwar, Irin gaisuwar je ka na yi ka, amma ganin Jawad ya zuba musu ido, sai ya amsa har ya na tambayar Inna, wanda ta ji shi, amma sai ta yi kamar ba da ita yake ba. Hannu ta mikawa Jawad akan ya ba ta basket din, no'ke kafada ya yi tare da cewa!

"Mami, Malam fa Kano zai wuce, don Allah ki bari ku wuce tare."

Wani malolon ba'kin ciki ya sa ke turnuketa, bayan ya tilasta ta, ta gaishe shi, ya kuma sake baro wata magana.

Ba ta ce masa komai ba ta fincike basket din tana cewa,

"Na gode ba sai ka kara gani na zo ba bare ka yi mini wannan iya shegen!"

Ta juya ta fara tafiyarta mai cike da nutsuwa, da sauri Jawad ya bi bayanta, yana cewa, "Haba mana Mami kar mu yi haka da ke!"

Kawai sai ta saki basket din hannunta da jakarta ta riko shi ta ringa zuba masa rankwashi tare da dundu, a sukwane Uban ya taso ya karbe shi yana jin takaicin ta na sake kama shi, wai a makaranta ma cikin jama'a ba za ta fasa halinta ba? Sa'arsa daya ma, wajen ba mutane kusan duk an watse sai tsirarru.

Ta sunkuya ta debi kayanta ta tafi tana huci, ganin haka Jawad ya fincike daga hannunsa ya bi ta yana fadin,"Ina zuwa Malam!"

Da gudu ya cim mata ta baya ya rungeme ta yana fadin,

"Am sorry Mami, very sorry!"

"Ai ni kuma ba ruwana da kai Jawad, tun da dai kai ba ka jin magana, na hana ka wannan manyancen naka, na hana ka shiga abin da bai shafe ka ba, amma ka 'ki, to ka je ka yi ta yi."

Ya marairaice yana ba ta ha'kuri har dai ya samu ta ha'kura ya ga murmushinta.

Malam yana zaune yana kallon su har suka ba ce ma ganinsa, a ransa yana mugun tausaya wa Jawad, tun da shi burinsa a ce Mamansa na tare da su, wadda faruwar hakan sai ikon Allah.

Yana zaune, ya dawo ya tarar da shi yana ta tunani, "Ni ma ai zuwa zan yi na tafi. Mu je mota ka kwaso kayanka."

Daidai lokacin wayarsa ta dauki ruri, yana dubawa yaga matarsa ce Farida ya amsa, tambayar Jawad ta yi, wayar ya mi'ka ma yaron tare da cewa, "Karbi!"

Ba wani karsashi ya karbi wayar har ita ma ta ji babu dadi tana tambayar shi ko lafiya ya ce mata, "Lafiya lau!" Bana son Malam ya tafi ya tafi nee, sannan baku zo ba ke da Hajiyan Bichi".

ta shiga bashi hakuri cike da murna ganin ya fara dawo mata tamkar farkon zamansu.

Suna tafe yana masa nasiha tare da nuna masa ba ayina uwa ba a yin musu da ita, dole a bi ta yadda take so, sannan ya daina shiga matsalar da ba tashi ba, hawaye yake gogewa tare da cewa,

"Ni dai Malam ka dawo da ita gidanmu ni ma in dinga ganin Mamana a gidanmu, kamar yadda nake ganin na friends dina, kowa Mamansa da Babansa tare suke zuwa masa amma banda ni!"

Ya 'karasa cikin kuka sosai, janyo shi jikinsa ya yi yana dan bubbuga bayansa alamun rarrashi yana cewa

"Ina ce ni ma tare da Antinka nake zuwa maka?"

"Amma ai ba da Mamana kuke zuwa ba!"

"To ka kwantar da hankalinka, ka dinga mana adddu'a sai ka ga very soon ta dawo har ma ka zama Yaya Jawad kana so?"

Ya daga kansa tare da sa hannu yana goge hawayen da ya'ki tsayawa.

"To in dai kana son haka, ka daina damuwa ka kuma daina yiwa Mami maganar bare ta dake ka, kawai addu'a za ka na yi, ni kuma ka dinga tuna mini, wataran sai dai ka dawo hutu ka ganta a gidanmu."

"Malam da gaske?" ya tambaya cike da zumudi.

"E Mana indai ka daina kuka, ka daina damuwa, ka daina damunta, kana addu'a to ina tabbatar maka ba abin da ya fi addu'a juya lamura!"

Murmushi ya shiga yi yana goge hawaye da handkerchief din hannunsa yana 'fadin,

"Ai ko Malam ban san murnar da zan yi ba,, kuma har da kai zan 'dauka a jirgin nawa".

Dariya Mk ya yi tare da cewa "Ai kuwa dai nima naji dadi tunda albakacin Mami zan shiga jirgin Jawad"

Kunya ta kama yaron yace "Ai dan ita bata taba shiga bane"

Ya sake cewa, "Malam ka gai da Hajiya, kuma ina zuba idon zuwanta, tunda ba ta zo yau ba, ina bin ta bashi!"

Alkalamin

Surayya Dahiru ✍

[5/11, 17:15] ~fatieshak: *HALIN YAU*!

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

Tukuici ga

FADILA LAMIDO

BINTA UMAR ABBALE

ZAINAB MAZAWAJE

Nagode da Shawarwarinku da 'karfafa guiwa, Allah Ya saka muku da alheri, Ya 'kara daukaka.

GODIYA GA MAKARANTA

Na gode da yadda kuka 'karbin wannan labarin, ha'kika jiya na ga ruwan masoya, ban yi zaton a 'kankanin lokaci littafin zai 'karade duniyar karatu haka ba, na gode muku sosai, in sha Allah ba za ku yi NADAMAR bibiyar wannan labarin ba!Heart U all

A sanyaye ya fito wa da Jawad kayayyakin provisions din da ya kawo mishi, tamkar wanda zai yi rabin shekara bai je gida ba, yana sake jaddada mishi ya daina damuwa ya kuma ci gaba da karatunshi.

Ya shiga mota Jawad na 'daga mishi hannu har ya fice, bai yi nisa sosai ba don kuwa bai gama barin garin Kiyawa ba, ya hango su Sa'adah da wasu matan a waje, gefe kuma an bude motar bakanike sai tabe-tabe yake, ga dukkan alamu motar ce ta lalace musu, kamar ya wuce sai kuma ya kasa.

Don haka sai ya tsaya a gabansu, bai fito ba, sai ya lalubo lambar da Jawad ya kira shi da ita dazu, ya san tabbas layinta ne duk kuwa da ba ainihin layin ta ba ne daya santa da shi.

Ya danna alamar kira, yana hango ta tana ta kici-kici da jakarta wurin lalubo wayar, amma abin mamaki ya ga ta fito da wayar amma ba ta dauka ba har ta katse, mamaki ya kama shi wai yaushe Sa'adah ta ko yi jarumta akan lamarinsa ne?

Ya yi jim yana tunanin rabon da Sa'adah ta shiga harkarsa, ba shakka ba lokaci ne Mai tsayi, ba ta sake neman shi ba, ba ta sake duba dukkan lamarin sa ba, ta yi fatali da shi da dukkan soyayyarshi, abin da ya dade yana mamakinsa. bai daddaraba, ya sake 'kira tana gab da tsinkewa ta daga ba ta yi magana ba, amma dai ta kara a kunnen ta, sanin halinta da ya yi na ba za ta fara magana ba, yasa shi cewa,

"Ke na gani a titi a na muku gyaran mota?".

Cikin rashin nuna damuwa ta ce "A a ba ni ba ce."

Bai yi mamakin amsarta ba ya ce. "Amma ba ke ce nake hangowa a tsaye kina amsa wayar nan daidai jikin Alheri bread ba?"

Shiru ta masa sai ji ya yi ta ma ka'tse wayar gaba'daya.

Shiru ya yi ranshi na suya ya na sake jaddada halayyarta a jininta ne ba za ta sauya ba.

Har ya ta da motar da niyyar barin wajen ta je ta 'karata, sai kuma ya tuna uwar Jawad ce tilon 'dansa, ya tabbatar da tare yake da Jawad din, ba zai yarda su tafi su bar Maminshi a bayan gari jejin Allah ba, ga yamma ta yi likis sosai, sanyin da ake 'dan busawa ya sake taimaka wa garin ya yi dan duhu, don haka sai ya fito bayan ya kulle motar ya nufe su.

Yana zuwa ya ga har da Zainab Ma'aji da wasu mata biyu da bai gane su ba.

Ita ko Zainab tana ganin shi ta saki fuska."Lah! Uncle kai ne ashe."

Ta gaishe shi irin gaisuwar da dalibi ke yi idan ya ga malamin da ya koyar da shi a baya. Shi ma ya amsa da jin dadin girmama shi da Zainab ke yi tun fil azal.

Hannu ya mi'ka ya dauki yaronta Walid ya masa wasa sannan ya ce, "Motar taku lalacewa ta yi ne?".

"E wallahi ga mu nan dai ana ta faman gyara".

"To ku zo mana mu wuce tun da ba tabbacin za ta gyaru yanzu".

Kallo ta kai ga Sa'adah da ta koma baya ta yi kamar ba ta gan shi ba, ta kuma cika ta yi fam kamar kububuwa.

Zainab ta ce "To uncle bari na yi wa abokan tafiyar tamu magana."

"Okay"

Kawai ya ce, yana ci gaba da wasa da Walid dake ta bingila mishi dariya tamkar ya san shi.

Bayani Zainab ta musu kamar yadda ya bu'kata, dukkan su sun amince, su bi shi, amma ban da Sa'ada. Don haka Zainab da 'yan uwanta su ma suka janye tun da dai ai sun san saboda ita ya tsaya har ya nemi ya taimake su, to kuwa ta ya ya za su ce za su bi shi alhalin ita ta yi rantsuwar gara ta kwana a nan da ta shiga motarsa!

A matu'kar kunyace Zainab take ba shi ha'kuri tare da ba shi uzirin direban ba zai ji dadi ba, ya san sarai Sa'ada ce ta'ki amincewa, amma sai ya ce ai zan sallame shi ku zo mu tafi kawai.

Nan ma sai ta sake dora wa 'yan uwanta laifi akan yayarsu tace ba zasu sab'awa direban al'kawari ba. Ya jinjina hankali da Zainab ke da shi, duk da ya san 'kawar ta ce ta'ki amincewa, amma ba ta fadi hakan ba, sai kariya take ta bayarwa, ina ma tun farko Sa'ada ita ta ri'ka a matsayin 'kawa, ba bara gurbi irin su Halima da Safina ba?

Wanda 'kawacenta da su bai amfane ta da komi ba sai muguwar asara da nadama, tunda sun mata ingiza mai kantu ta yarda har ta tsinke igiyar aurenta, a yanzu kuma sun bar ta sun koma suna zunden ta.

Don haka sai yace "To shi kenan ba damuwa ya matsa ga bakaniken dake ta iyakar kokarin shi don ya ga motar ta tashi.

magana suke yi da direba, cikin ikon Allah ba a wani dauki lokaci sosai ba motar ta gyaru, amma har an yi sallar Maghriba, dan haka malam da direban suka yi jam'i suka yi sallarsu, yayin da matan suka shiga wani kewaye su ka yi ta su.

Bai yarda ya tafi ba sai da ya ga tashin su sannan ya taka ya isa inda motarsa take shi ma ya bi su a baya.

A cikin motar kuwa yayyen Zainab sai caccakar Sa'ada suke da rashin kirkinta, "A haka kike son komawa gidan nasa? Ba kya girmama shi, a gaban kowa za ki iya keta shi?"

Cikin turo baki ta ce "Ni fa Anty da ne na yi haukan banza na son sai ya mayar da ni, yanzu kuwa ko ni da shi muka rage ba na sonsa ba zan koma ba"

Cikin fushi ita ma Anty Asiya wadda ita Zainab ke bi, kuma da ita duk a ka yi gwagwarmayar su Sa'adah, ta ce, "Ai shima ba son naki yake ba, shashasha da ba ta san me ya kamata ba."

Dattijon dake jan motar ya ce, "Um'um fa! Ba'a shiga lamarin mace da namiji, ai koni da yau na fara ganin su na hango soyayyarta mai yawa a idonsa da gangar jikinsa, ita ma kuma duk wannan kumburin da take yi da fiffi'ka duk soyayyar ce, da alama dai kishi ne ke dawainiya da ita a kansa, dan na ga fishi take mai tsanani da shi!"

Dukkan motar a kasa dariya a na cewa Baba ashe duk ka gano su?

Yace , "Haba yara mu da muka ga jiya muka yau, ku duba fa duk iya shegen da ta yi akan ba za ku bi shi ba, bai fa iya tafiya ba har sai da ya ga tashinmu, wannan kadai ya isa kowa yasa lunzami a bakinshi akan lamarinsu, suna da yara ne?"

Zainab ce ta ce "Yaro ne daya har ya fara girma, shi suka jewa visiting"

 Ya ce, "Ai shike nan magana ta 'kare, ko kowa bai musu sulhu ba, yaron zai zama tsanin afuwa a tsakaninsu, mu yi musu addu'ar fatan alheri, amma soyayya akwai ta"

Aka sake sa dariya ban da Sa'ada da ta yi kicin-kicin da fuska.

Tsohon ya sake cewa, "Ina cewa da za mu zo ita ce a gaban motar nan haka da za mu dawo,har muka zo inda motar ta lalace ita ce a gaban?amma ina ganinsu da za ta shiga gaba ya galla mata harara sai kawai naga ta shige baya."

Gabadaya aka sake dariya har da Sa'ada wadda ita ta karfin halin wannan bawan Allah ne, ita ba ta ga harara ba, ta san kuma tabbas bai yi 'karya ba, kaifin idon Malam ne yasa ta kasa shiga gaban motar wani akan idonsa, sai ta bige da cewa "Lallai Baba ba komi na gode" da haka ta sace ta daina fishi.

Shi ko Malam yana tafe yana ayyana abubuwa masu girma game da lamarin ta, komai nata burgeshi yake, bai ta ba ganin halittar da ke daukan hankalinsa irin surar ta ba, kawai wasu daga cikin halayyarta ke 'dimauta tunaninshi su hana shi zaman lafiya amma duk sanda zai dora idonshi a kanta sai ya ji bai ganin komai da kowa sai ita.

Har yau har gobe yana son ta, amma ta riga ta shayar da shi bakin cikin da zaman aure zai yi wuya tare da su. Har suka iso Kano tunaninta yake idan ya tuna *happy moments* dinsu yayi murmushi, idan ya tuna *though times* dinsu sai ya ja tsaki ko ya furta ya *Salam* ko *SubhanAllah.*

Ba su rabu ba sai da suka zo Gandu ya yi wa direbansu fitila ya wuce, a nan ma sai da Baba ya tsokaneta da cewa

"To Sa'adatu wannan fitilar fa da ya yi bata kowa bace, taki ce!"

Suka hada baki wurin fadin, "Ai kuwa dai Baba!" suna kuma dariya.

```Alkalamin

SURAYYA DAHIRU``` ✍✍

□ *HALIN YAU*! □

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

`

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

*SADAUKARWA GABA'DAYA GA*

*SADIQ ABUBAKAR*

5-6

Har 'kofar gidan yayarta Sumayya suka kaita dake kan titin  Kwankwaso Gandun Albasa, sannan suka juya,

Baba direba, nata jaddada mata ta daina saurin fushi mabudin fitina ne, ta yi godiya, tana cewa su Zainab sai nan da kwana uku za ta dawo unguwar tasu lokacin innarta ta dawo daga tafiyar da ta yi.

Da sallamarta ta isa cikin katafaren falon Sumayya, ba kowa sai TV da take ta babatu hadi da dan dirin AC da ke tashi a hankali, ga 'kamshin *Air Freshner* dake tashi sannu a hankali, take ta ji duk gajiyar da ta kwaso ta taso mata gabadaya.

Dan haka sai kawai ta zube a Kan doguwar kujera ta yi kwanciyar ta ba ta jima da kwanciyar ba, barci mai nauyi ya yi gaba da ita.

Sumayya fitowa tayi daga bangaren maigidan, da a yammacin yau aka sallamosu daga asibiti, ta ganta tana ta barci. Murmushi ta yi tare da cewa, "Oh a 'yar wannan tafiyar ne kika gaji har haka?" Ta gyara mata rigarta da ta 'dage, ta shige kicin don hada tea.

Hayaniyar yaran gidan ne da suka taso da ga lesson wadda takanas aka dauki malamin da zai zo har gida yana musu bita, yasa ta tashi musamman da 'karamar cikinsu ta fada kanta tana fadin, "Mami yaushe kika dawo?"

"Khairat kin san yadda na gaji!" Ta 'daga ta, tana cewa "Ina Yaya Jawad?"

"Ya na lafiya, ya ce duk yana gaishe ku"

Ta sake cewa, "Mami bai ba da komai ki bani ba?"

Daga Sumayya har Sa'adah dariya suka yi yadda Khairat din ta yi.

Jakarta ta bude ta dauko wani dan abu a nade da wrapping paper ta ce, "ga shi nan ni kaina sai da ya ro'ke ni kar na bude tunda ban san ma ya saba, ya dai ce mini zan ga abin Khairat don Allah kar na bude."

Yayansu Ayman wanda shi ma yana da yayu Abba da Khalifa suna Egypt suna karatu, ta nufa tana cewa, "Bude mini yaya!" Nan da nan ko ya hau warwarewa sai ga Lush Cookies Biscuit har guda biyar sai Teddy Bear  'yar 'karama mai kyau da yar 'karamar takarda an rubuta little Khairat.

Da murna soasai tace "Yaushe to zai dawo Mami?"

Anis ne ya ce, "Sai nan da  6 weeks."

Ta galla mishi harara, "Na tambaye ka ne?" Da yake sa'kuwar shi ce ba su cika jituwa ba. Ta juya ga yayansu,"Yaya Ayman kwana nawa ne a 6 weeks?"

Kai tsaye ya ce mata, "42 days." Da sauri ta ce, "Gobe zan samo stones 42, kullum na dinga minus, ranar da suka 'kare to ranar zai dawo saboda na soya mishi wainar fulawa."

Dukkan su dariya ta ba su, amma Sa'adah mamakin wayonta take, tana kallon Anis tana tuna daidai lokacin haihuwar sa ta shiga matsaloli masu yawa da Malam.

Shekarunta biyar a duniya amma wayonta da azancinta ya zarce na 'yan shekaru bakwai.

mutumiyar Jawad ce sosai ta fi shiri da shi fiye da yayyenta.

Shi ma kuma haka yake ji da ita musamman da shi ba shi da 'kani ko 'kanwa sai ya tattara dukkan 'kaunar da yaya yake yi wa 'kanwarshi a kanta.

*Bayan kwanaki uku*

" Iya Iya dai, na san tabbas daga shigarki ba za ki ce mini wai har kin yi barci mai nauyin da za ki kasa jin kuwwar da wayar ke faman yi ba."

Da kanta ta tashi ta leka, ganinta ta yi tana kwance ta 'kudundune ta rufe fuskarta da dukkan hannayenta,

"Kin san Allah? Idan kika bari na shigo ba ki tashi ba sai na ci mutuncinki, ai na san sarai kina ji na"

Tashin ta yi tana murtsika idanuwanta "Ni fa Inna barci nake yi!" Kafin Innar ta yi magana wayar ta sake daukan ruri a karo na uku dan haka ta kafeta da idanuwa, akan dole Sa'adah ta sa hannu ta amsa wayar.

Sannan Inna ta juya ta fita tana fadin, "Shashasha haka ki ke tunanin za mu bar ki ki yi ta zama? Ai tunda kin gama karatun to kuwa wallahi sai dai ki fito da miji cikin jerin wadanda suke son ki dan ba zan yarda da wannan zaman ba. Haka kawai kowa ya zo ki ce bai yi miki ba, kowa bai miki ba, wanda ya yi mikin kuma bai shirya sake zama dake ba. Amma kin kasa gane gaskiya, kin kasa gane ita mace lokacin ta 'kan'kani ne! Bari Baffan naku ya dawo na gaji da halinki!"

Sa'adah kuwa da alatilas ta dauki wayar Alh. Mamman wanda dan majalisar tarayya ne mai ci a yanzu, ya so ta tun tana budurwa, a lokacin yana dan majalisar dokoki na jaha, shi ne har yau yake ta bibiya, tun lokacin budurcinta ta san komai game da shi.

Mutum ne mai yawan kyauta da kyautatawa, ta tabbatar da hakan, ita kanta ta san ya mata 'barin kudi. Tun a lokacin yana da mata biyu da yara takwas wanda wannan dalilin yana cikin dalilin da ya sa ba tayi marmarin ma auren shi ba, Illa dan ta sami rabonta kawai, to yanzu kuma amaryar ce ta rasu shekaru biyu da suka wuce a wurin haihuwa, shi ne yake ta bin kanta ta maye mishi gurbinta, tunda ya riga ya saba da mace biyu ga kuma tsananin 'kaunarta da yake.

A nata bangaren kuwa ba ta fatan 'kaddara ta 'kaddaro ya zamo miji a gareta shi yasa tun watanni shida da suka shude ta yakice shi a dukkan lamarinta, tunda dai kam ai ta riga da samun rabonta.

Ta yi amfani da alfarmar shi ta cimma burinta, da kuma mallakar kayan 'kawa na alfarma, idan ko hakane dole ta yi gaggawan wullar da shi tun kafin reshe ya juye da mujiya.

Uzirin tana aiki ta ba shi akan za ta 'kira shi anjima, murmushi ya yi ya ce, "Ranar da na ga 'kiran ki a wayata Sa'adah tabbas rana ce mai muhimmanci a raina!"

Ya'ke ta yi tare da fadin, "Aiko idan hakane zan baka mamaki, ka saurare ni zuwa anjima"..

Ba ta jira cewar shi ba ta daste kiran, ta yi wulli da wayar ta na neman tsari da 'kaddarar da za ta hada su zaman aure da wannan mai tulelen ciki.

Kanta ta ji ya cushe musamman yadda Inna ta fara matsa mata a cikin kwanakin nan akan lalle sai ta tsayar da miji cikin manemanta, har zuwa yanzu ba ta jin akwai wani da za ta yi zaman aure da shi kamar Mukhtar Kabir Bichi.

Amma ko shi da ta tabbatar da abu 'daya, ta ha'kura da shi ba dan ba ta so ba sai dan ha'kurin shi yafi.

Ta kuma gamsu ita ke da laifi da kaso mai yawa na 'kaddarar rabuwar su da Abban Jawad, ta tabbatar ya so ta, son da ba algus amma *HALIN YAU* da rudin 'kawaye ya jefa ta cikin kogin nadama.

Irin wanda ake cewa tsalle daya mai jefa mutum rijiya, ya yi dubu bai fito ba! A hankali ta koma ta kwanta tana tariyo rayuwar ta, ta baya, tun kafin haduwarta da Mk Bichi. haduwarsu, aurensu, rabuwarsu, har zuwa yau da take jin duniyar ta yi mata daurin goro.

Ashe 'dan Adam baya rabuwa da matsala? Ashe duk matsalar da mace za ta fuskanta indai tana zaune a dakin aurenta matsalar da sauki, akan matsalar rashin auren, da rabuwa da 'ya'yanta? Wanne tabbas mace keda shi a wannan halin na yau, za ta sake samun damar aure a karo na biyu? Idan ta samu din ma ba za ta kauce wa matsalar *HALIN YAU* ba, ko kuma ta tabbata tana aure-aure.

Ta nisa ta tuna wata maganar gyara kayanka, da fasihiyar marubuciya, Fadila lamido inda take fadin, *"Uwa da sadaukarwa aka san ta, domin rayuwarta da ta 'ya'yanta, ta inganta.*'

To shin ita me ta yi ne dan ganin ta SADAUKAR da komi dan inganta kanta da tilo 'danta? Tabbas ba ta yi ko mai ba, sai rusa farincikin kanta dana 'danta Jawad! Ta yi dalilin da yake rayuwa ba a tsakanin uwa da uba ba, hawaye ya gangaro mata na takaici da kaico iri iri.

Ta tuna wani darensu a Abuja, ya dinga rarrashinta akan ta kwantar da hankalinta su zauna lafiya, komai take so zai dinga yi mata a hankali, a lokacin ita kuma tana ganin tamkar  idan ba ita, ba zai iya rayuwa ba, saboda yadda yake tsananin sonta da kulafacin son zama da ita, duk yadda take ganin aibun su Halima, a yanzu da take fuskantar NADAMAR biyewa Halayyar yau, ta fi ganin aibun kanta da kanta, tabbas zuciyarta da tunanin ta basu  mata adalci ba, domin tunda ta taso take jin ana azanci da cewa idan mafa'din magana wawane majiyinta ba zai zama wawa ba, amma ita sai ta zama mahaukaciya ma.

Zuciyarta ta sake ba'ki wani irin numfarfashi take yi tamkar mai fama da cutar Asma, hakanan hawayen ba'kin ciki ya kwace mata tamkar mai yin Takaba.

```Alkalamin

SURAYYA DAHIRU ```✍✍
```

 HALIN YAU!

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

SADAUKARWA GA

SADIQ ABUBAKAR.

7-8

HAWAYEN nadama marar amfani ya ci gaba da zuba da ga kyawawan idanuwanta ba 'ka'kkautawa, a hankali ta koma ta kwanta, zuciya na suya, rabon da ta shiga irin wannan yanayin tun shekarun baya da suka shude.

Shekarun da suka fi kowanne tsauri da tsanani a rayuwarta, a lokacin da ta dinga yun'kurin gyara kuskurenta amma MK bai ba ta wannan damar ba.

Duk da ta san ita ke da kaso mai yawa na lalacewar aurensu, tunda ba irin 'kabali da ba'adin da bai mata ba, ba kalar rarrashin da bai yi mata ba. amma tasa hannu har da 'kafafu ta tankwabar da dukkan ha'kurinsa, ta tabbatar akan dole ya rabu da ita, ita kanta ta shaida hakan.

Tissue tasa ta goge hawayen da ya 'ki yankewa, take kuma zuciyarta ta yi tsalle ta hasko mata irin kyaun da ya yi cikin tufafin da take matu'kar son ganin sa a ciki wato farin kaya, sam ba ya girma, ba wanda zai kalle shi yace ya kai shekaru arba'in har da biyu.

Dan kuwa idan ya ce bai yi auren fari ba, ba wanda zai 'karyata shi, Ubangiji ya mishi kyakkawan jiki matu'ka gaya.

Murmushi mai hade da hawaye take yi lokaci guda, saboda yadda ta ji a ranta da zuciyarta domin ita ya yi shigar tare da fatan ko Allah zai sa su hadu, a hankali ta fara jin sau'kin 'kullewar da 'kirjinta ya yi yana raguwa, a dalilin tabbacin da ta sake samu na har yau shi ma yana son ta, dama idan akwai abin data yarda dashi to son da ya ke mata ne. Amma kuma me yasa bai yarda da ita ba?

Nan da nan 'kuncin 'kirjinta da ya fara warwarewa ya dawo ya 'kulle fiye da farko idan akwai abin da yake 'daga mata hankali bai wuce rashin amincin daya jefe ta da shi ba, alhalin shine mutum na farko daya kamata ya shede ta,

ta kuma zama amintacciya a idonsa, kuka ya 'kwace mata sosai, da sauri tasa hannu ta rufe bakinta dan kar Inna ta jiyo.

Haka ta danna kanta a pillow ta yi kuka mai nuna tsantsar bakin ciki da takaicin da mai yinsa ke ciki, duk yadda zuciyarta ta yi zafi, kanta take 'kalubalanta, ta san ko mai Malam ya yi ko ya ce mata, ba shakka ita ce sila, ita ta janyo.

Istigifari ta dinga ambato dan ta sami sau'kin zuciyarta, tsawon lokaci kafin ta ji ta fara samun nutsuwa sai ajiyar zuciya take saukewa.

Wayarta ta dauko tana nazarin shin a littafi zata rubuta ne ko a waya? A littafin tafi gamusuwa da ta rubuta tarihin rayuwarta dan ya zama izna ga sauran mata. Idan ta sami halin buga shi, za ta buga dan ya zama gargadi ga duk wacce son zuciya da *HALIN YAU* ke dawainiya da ita.

Mi'kewa ta yi tana laluben littafi da biro a cikin jakar karatunta, amma cikin rashin sa'a ba ta samu ba, kowanne ta yi rubutu mai yawa a ciki.

Tsaki ta ja, ta rike 'kugu kafin ta yi wani yun'kurin abin yi, ta ji sallamar almajirinsu yana fadin na dawo.

Da sauri ta iso ga katifarta, ta 'daga pillow ta dauki gudar dari biyar ta fita ta ba shi, ya siyo mata littafi na rubutu mai shafi tamanin (80 leaves).

Daga nan ba ta dawo dakin ba, buta ta dauka dan tayi alwalar la'asar tunda yan mintina ka'dan ne su ka rage.

*****

Kwance ya ke kan sofa a dakin barcinsa, ya lumshe ido tamkar mai barci amma a zahiri ba barcin yake yi ba.

Tun ranar da ya ga Sa'adah nutsuwa ta masa tutsu duk yadda ya kai ga daurewa har abin ya bayyana a fuskarsa da gangar jikinsa gaba'daya.

Wata irin nutsuwa ya gani a tare da ita, wadda bai taba gani a tare da ita ba, gaba'daya ta canja, ilimi da hankali sun matu'kar ratsa ta. ba kamar lokacin da suka rayu tare ba. ko dan ya dauki lokaci mai yawa bai ganta ba ne?

Farida ce ta shiga dakin, kusa da 'kafafuwansa ta zauna tana mai jan yatsun 'kafarshi, a hankali cikin sanyin murya da halittarta ce, ta 'kira shi "Abban Jawad!"

Bai amsa ba, amma ya bude idanuwanshi da suka yi ja alamun ko barci bai ishe su ba ko kuma ana cikin damuwa.

Ta sake nazartar shi a hankali ta ce, "Tunda ka dawo na kasa gane maka, na san akwai abin da ke damun ka amma ka'ki fada mini, ni kuma na san matsalar! Idan na yi rantsuwa cewar Sa'adah ke da ala'ka da wannan damuwar da kake ciki ba zan yi kaffara ba, mai yasa ba za ka yafe mata ba, mai yasa ba zaka daina wahalar da zukatanku ba, me yasa kake gudun gaskiya da gangan? Ni dai na san ', kullaci, da rashin yafiya ba halayyarka ba ce!

Ban san me yasa ka aro ka yafa akan Sa'adah ba! yau shekaru kusan bakwai kana ta wahalar da zukatanku, sai yaushe za ka hutar da ku? ko makaho ya ji halin da kake ciki yasan kana sonta, balle ni da nake tare da kai, na ro'ke ka ka gaggauta gyara tsakaninku, tun kawaicina bai 'kare ba, tun ban fara kishi da ita kamar yadda take yi dani ba, na tabbatar idan hakan ta faru ba zaka samu nutsuwa ba!"

Sai a lokacin ya bu'de baki murya ba amo ya ce, "Kece kike ganin haka duk yadda kike tunanin lamarin ba haka ba ne, kinsan kuma ban taba 'karyar ba zan dawo da ita ba, saboda Ubangiji ne ke jujjuya lamura, idan ya 'kaddara sake zama a tsakaninmu zan dawo da ita."

"Zuwa yaushe za ka dawo da ita din? Ka fi shekaru uku kana wannan maganar, ba irin girman kanta da ba ta ajiye ta baka ha'kuri ba, ni kaina na sha ganin ta tsugunne a gabanka. haba Abban Jawad! Wanne irin abu ne haka da ba zai wuce ba?"

Ta fada muryar ta na karyewa.

Shi kansa bai san mai yasa ya shiga ru'du a dalilin halin ko in kular da Sa'adah ta mishi ba, da kuma yadda ta daki 'dansa a gabansa, alhalin kuma tun tuni ta san baya son ta masa haka a gabansa. Amma saboda da ta nuna masa ba shi da sauran gurbi a zuciyarta, ba shi da mutunci a idonta ta rufe Jawad da duka akan idonsa.

Sannan a gaban jama'a ya tsaya dan ya taimake su amma ta wula'kanta shi, ta nuna masa iyakarsa, idan ya tuna wadannan abubuwan sai ya ji har zazzabi ne ke neman kama shi, hakan na nufin Sa'adah ta daina son sa, ta ha'kura da shi ke nan? Zuciyarsa na bugawa idan ta hasaso masa cewar ta samu wanda take so, ko kuma za ta sabunta soyayyarta da Khalil Ibrahim wanda yake jin komai na iya faruwa da shi idan hakan ta faru.

Ya nisa ya ce, "Ke fa duk yadda kike tunanin lamarin Sa'adah ya kerewa tunaninki, yanzu bata so na, ba ta da burin sake zama da ni"

A yadda ya yi maganar ta san akwai abin da ya gani a tare da ita da ya jefa shi cikin wannan yanayin.

Wata'kila ta gaji da bin kansa, ta tattara ta jefa shi a kwandon shara, kamar yadda ya mata, shine kuma dan son kai irin na namiji zai ji an masa rashin kyautatawa, su dai sun fi son mace ta yi ta bin su, suna jan ta a 'kasa.

"A hankali cikin son 'karfafa masa guiwa ta ce, "To ina ruwanka da soyayyarta? Ina tabbatar maka son da kake mata ya isa ya ri'ke auranku, muhimmin da za ka damu da shi mutuncinka a idonta, balle ma nasan nan duniya ba namijin da take so sama da kai, ba kuma wanda zai zarce ka a gunta. Wata'kila ta gaji da yadda kake tamaula da ita ne, ko ba ta ci albarkacin so ba, taci albarkacin Jawad! ko ka san Jawad, komai zan yi masa ba zai gamsu ba, matu'kar ba uwarshi ya gani a tare da kai ba"

Idonta ya dan ciko, ta dan tsahirta sannan ta ci gaba da magana, "nan gaba Jawad zai tattara dukkan tsana ya dora mini, zai ga saboda ni ka 'ki zama da uwarsa, kai ma kasan tunda muka dawo 'kasar nan ya canja, na ro'keka dear kar ka ruguza farinciki da kwanciyar hankalinka da na 'danka"

Janyo ta jikinsa sosai ya yi, ya ri'ke hannunta ya kalleta sosai ya ce ,"Farida ke din mai kirki ce, mai ha'kuri ce, mai sanin ya kamata ce, kina sona kina son kwanciyar hankalina, ina yaba miki, ina kuma fatan Allah ya fi ni yabawa, Allah ya ba mu zuria dayyiba!"

Hawayen da take ma'kalewa ya zubo a kan fuskarta ta ce, "Ni da ban da lafiya ne zan haihu?"

Cikin kulawa mai yawa ya ce, "To menene ya gagari Ubangiji? Son da nake miki wallahi ko ban taba haihuwa ba, zan zauna dake a haka domin ke nake so ba wani abin da zan samu a gareki ba, sannan rashin haihuwarki kullum ke sa na ji son ki da tausayinki na sake cika mini dukkan zuciyata, ina son ki da ke da dukkan lalurarki Farida!"

Sai kawai ta fada jikinsa tasa mishi kuka, shi kuma yana dan bubbuga bayanta, yana jin ina ma zai iya bude mata 'kirjinsa dan taga 'kololuwar matsayinta a zuciyarsa?.

Ya tabbatar bata san yadda yake jin ta a Zuciyarsa ba ne.

```Alkalamin

SURAYYA DAHIRU```✍✍

[5/14, 11:03] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•

*_LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ®_* ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏
```

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

GAISUWAR GIRMA GA

HAJ HAFSAT SODANGI

(MIJIN TACE)

9-10.

Tsawon lokaci suna wannan halin har ya samu nasarar dawo mata da walwalarta,

"To kawo mini abincin nan mu ci don nasan ke ma ba ki ci ba".

Ta yun'kura tana cewa, "Ina zan iya ci alhalin mijina bai ci ba!" Kicin ta nufa ta hada komi a kan faranti ta kinkima ta yi dakin nashi kamar yadda ya ba ta umarni, Sai da ta shimfida ledar cin abinci sannan ta zuba musu abincin a faffadan plate, shinkafa da miyar kifi ne, sai hadin Salad, gefe kuma zobo ne wanda ta sarrafa da tsurar sugar da cocomber sai flavour.

Ba ka jin komai sai karo tsakanin cokali da plate kasancewar shi ba ya magana idan yana cin abinci.

Suna gamawa ta kwashe komai ta gyara wajen sannan ta hada masa ruwan wanka ya shiga. Ta fice zuwa nata dakin, ta fito falo sukayi kicibus da shi, ya fito cikin lallausan yadi mai kalar sararin samaniya,(Skye blue) bai dora hula ba, amma ya taje sumar nan da ta cika kan fam! Ya dora farin glass a idanuwanshi, sai tsadden kamshin turaren Versace ne ke tashi a jikinsa.

Kugu ta rike ta zuba mishi ido tana murmushi ta ce, "Na san mijina gwanin iya wanka ne, amma irin wannan kwalliya haka da La'asariyar nan! Sai ina? ko wurin Iya Basiru za a?"

Ya fashe da dariyar tuna baya, sai ya ce, "Kinsan fa har yau fadanta na nan lalle idan ta ji wannan sunan kin san 'yan kallo zaku kwasa."

Ita ma cikin dariya sosai ta ce, "Ai na san yanzu ta girma da fada, ka san me?"

Ya girgiza kanshi, "Ada idan mun hadu sai na faki idon mutane naga ba kowa, sai na ce mata Sa'ade ko na ce Iya Basiru, sai na ga ta fara sababi, kawai sai na sulale na bar ta a wajen."

Ya sake sakin dariya "Ashe ke ce kike tsokanar ta duk mu hadu a ba ta rashin gaskiya?"

"E to ai haushi nake a lokacin, ta dauke maka hankali, har sai da ta kwace mini kai!"

Ya nuna ta da yatsa, "ke ko! kin san irin su Sa'adah suna dadewa kafin a gane cutar su da ake yi, saboda hayaniyarsu sai sun dade kafin a gane a fahimci gaskiyarsu. yau kwana biyu ban je gidan Hajiya ba can na nufa idan kuma za ki dauko mayafinki, Bismillah".

Kai ta girgiza alamar a'a tare da cewa, "Na fi son na je na wuni, ka gaishe ta da kyau!"

Ya fice ita kuma ta bi shi da addu'ar dawowa lafiya.

Da sallama ya shiga gidan, a tsakar gidan ya same ta zaune kan tabarma tana jin radio, kusa da ita ya zauna. suka gaisa tana tambayar Farida, daga nan kuma tayi shiru da bakinta.

"Hajiya wai har yau fishin rashin zuwanki wurin Jawad din ne? Ni ma fa ban ji da wuri ba, ina Bauchi ya yi mini waya daga can na zarce amma ki yi mini uziri, kiyi hakuri."

"Ni abin da ya dame ni, ba a kai masa abinci da 'yar miya ba!"

Dariya ya yi sannan ya ce, "Ai yanzu ba a barin su su tafi da shi hostel, iya wanda suka ci a wajen shike nan, saboda kwalara sannan kuma a can na tarar da uwarshi ta je masa da abincin".

Shiru Hajiyar ta yi tana jin takaici rashin Sa'adah cikin ahalinta, ba karamar asara ba ce. Tunda ita kam a iya zamanta da yarinyar ba za ta ce ga ta'kamaiman laifinta ba, sai yan 'kananun kura-kurai da ko 'danka na cikinka wani lokacin zai yi maka.

Duk artabun da ake yi tsakanin uwar miji da surukan zamani ita ba ta san shi a zamanin zaman Sa'adah ba, yarinyar ta iya zama da manya.

Komin fa'da da rashin ha'kurinta, ita dai ba ta ganin su, tunda dai mafi yawa akan kishi take fadan. duk mace kuwa ba a raba ta da kishi, sai dai wata ta iya dannewa wata kuma nata mai zafi ne.

Sannan abu mafi dadi a halayen Sa'adah yadda ta yarda ta isa da ita, duk yadda ta murde, da zarar tasa baki za ta ha'kura ta bar maganar. Amma ga shi nan, shi da ta haifa ta kasa sarrafa shi, akan komen yarinyar, shi yasa take jin kunyarta, take jin nauyin iyayenta, duk da aure rai ne da shi, Ubangiji idan ya 'karar da zama ba yadda za ayi.

Ta kalle shi, "Kuma kun gaisa da ita?"

Tausayin uwarsa ya tsirga mishi ya san babban burinta Sa'adah ta sake zama surukarta a karo na biyu, ya yi 'dan murmushi "Hajiya ai da ma muna gaisawa"

Harara ta galla mishi tare da cewa, "Ina ce nan da ta zo duba Jawad akan idona ba ku gaisa ba?"

"An yi haka Hajiya amma ai ba ni zan gaishe ta ba ko?"

"Kai ne namiji, Kai ne zaka fara magana tunda gidanku ta zo, kuma uwar dan ka ce!"

"To ni Hajiya ba uban 'dan nata ba ne?"

Kwafa ta yi, "Wallahi ba ka ta ba bata mini rai na ji zafinka sosai ba sai akan Sa'adatu."

Kai tsaye ya ce, "Na ba ki ha'kuri Hajiya! yanzu ma shi zan ba ki, ki yi ha'kuri ki yi mana adddu'a."

"To tun yaushe nake adduar?" Niyya ce dai da ba ka yi ba!"

Ya katse mata fadan nata ta hanyar cewa, "Da kyar fa Jawad ya sa ta gaishe ni, kuma na taho a hanya na ga motarsu ta lalace, wai ni da abin arziki, na tsaya na ce su zo mu taho amma yarinyar nan a gaban jama'a ta tsinka ni! Ko kallon tsiya ba ta mini ba, bare na arziki."

Ya nisa sannan ya ci gaba da fadin, "Amma kullum sai ki yi ta dora mini laifi, ki yi ta ganin ni ne marar kirki, alhalin tsiyarta tafi ta tsohuwar mota. Inda tana son sake zama da ni ai lallaba ni za ta ci gaba da yi, tunda dai ta san ba na son rashin kunya."

Tunda ya fara magana ta zuba masa ido tana nazarta shi, tsawon shekaru bakwai da rabuwarsu, yau ne ya bude baki yake magana mai tsayi a kanta. Ta kuma lura

da sassauci da afuwa mai yawa akan lamuranta a yau, ta tuno farkon rabuwarsu da ta nuna iko irin na uwa, akan sai ya mayar da ita tilas, yasa mata kuka riris lamarin da yasa ta janye takunkumin dolen da ta mishi.

Yana rufe baki ta ce, "To saboda Allah wanne irin ha'kuri ne bata ba ka ba? So kake ta tabbata tana bin ka kana walagigi da ita? kuma ko don ka nuna na isa da kai, ka ji abin da na ke fada maka, saboda rayuwar 'danku ta inganta, yau yaro ba abu mai dadi a wajensa irin ya bude ido ya gan shi a tsakanin uwa da uba. Amma ku iyayen yanzu ba ku cika duba wannan matsalar ba."

Ajiyar zuciya ya saki, "To shike nan Hajiya In sha Allah zan je na yi istikara ba za ta gagara ba!"

Nan da nan Hajiya ta hau murna har da hawaye take sharewa tana kuma fadin, "Na gode, Allah ya tabbatar da alheri, da ikon Allah akwai alheri tsakaninku. Duk ba'kin cikin da na kwashe shekarun nan a cikinsa, wannan maganar kadai ta sanyaya min zuciyata, Allah ya yi maka albarka."

Ta mi'ka hannu ta dauko wayarta, "Kira mini Yayar ku".

Ya karbi wayar yana cewa, "Me za ki ce mata?"

"Na shaida mata wannan abin arz'kin mana, duk wannan bacin ran ai da ita muke yinsa!"

Ya kalle ta, "Amma Hajiya na ce sai na yi istikara fa, idan kuma ban sami nutsuwa da abin ba, a zo a ce na yi baki biyu? Ni dai na ro'keki, ki yi shiru da bakinki, mu yi addu'a nan da kwana uku muga mai Ubangiji zai rinjayar mana a zuciya."

Ajiyar zuciya ta yi ta ce, "Da ikon Allah ma alheri ne, jiya mun gaisa da Ahmad."

Ta fada cikin jin dadi,"Ai ni tun ina Bauchi rabon da mu gaisa ya ce mini wai satin sama zai zo."

Addu'a ta bi shi da ita kamar kullum, ya mi'ke, "Hajiya bari na tafi Magariba ta kawo kai"

"To ka gaida Farida, ya jikin nata dai?"

"Da sauki da na ce ta zo mu taho tare, ta ce yini ta ke so ta zo ta yi miki."

"Ina zuba ido Allah Ya kawota lafiya."

Ya amsa da "Amin!" Ya fice yana fadin, "Allah Ya tashe mu lafiya."

Ta bi shi da kallon 'kauna zuciyarta fes! Tamkar wacce aka mayar da aurensa da uwar dansa haka take ji. Ta san shi kansa sai ya fi samun nutsuwa idan yana tare da Sa'adah saboda ita shaida ce na tsananin son da yake mata.

ta tuna jinyar da ya yi a dakinta a dalilin rabuwarsu.

Abin kuma da ke ba ta mamaki yadda har yau bai ta ba bude baki ya ce ga sanadin rabuwar tasu ba, ita ma Sa'adah ba yadda ba a yi ba ta'ki fada, lamarin da kowa ya kyale su aka bi su da addu'ar alheri.

Duk irin sha'kuwa da aminci da ke tsakanin Sa'adah da Baffanta, ko shi ta'ki fada masa dalili. Haka ma Mk duk yadda yake jin nauyin surukin nasa bai iya fada masa dalilin rabuwar tasu ba, illa ya ro'ke shi, akan kar ya yi fushi ko ya ga laifinsa, ko rashin kirkinsa akan sun rabu da Sa'adah. 'Kadarrar su ce haka, shi ma kuma Baffan bai zafafa ba, bai kuma takura sai ya ji dalilin ba, ya yi ammana tunda suke boye sirrinsu da alamun za su iya yi wa junansu afuwa a gaba, duk kuwa da a farkon mutuwar auren hana Sa'adah zaman gidansa yayi.

****

Bayan yaron ya kawo mata littafin, ta dauko al'kalami ta fara, ta yi layi kamar uku ta goge tana ganin bai tsaru ba, ta ina za ta fara ne?

Daga haihuwarta har zuwa girmanta, ko kuwa daga rayuwar makaranta inda nan ne mafari tsakaninta da MK Bichi, ko kuwa ta rayuwar aurensu za ta fara?

Ashe rubuta labari da tsarawa ma iyawa ne? Lalle a gaida marubutanmu.

Sau uku tana yi tana sokewa, ta tabbatar dai ba za ta iya ba, tunda ba ta taba ba, ai ko za ta ne mi wata cikin fasihan marubuta, ta bata labarin ita kuma ta fasashi ya zama littafi. Ta tabbatar ba za a rasa darasi da jan kunne cikin rayuwarta ba.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍

[5/14, 15:55] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

*SADAUKARWA GA*

*SADIQ ABUBAKAR*.

11-12

A cikin wannan yanayin Zainab ta yi sallama a tsakar gidansu, sai da ta fara shiga gurin Inna ta gaishe ta, ta bar mata Khalifa, ta yi dakin Sa'adah.

Zaune ta same ta kan katifarta hannunta ri'ke da littafi da biro.

Gefenta ta zauna tana fadin

"Nazari kike ne haka?"

"A sanyaye tace

"Wai nan littafi zan rubuta amma na rasa ta inda zan fara."

Dariya Zainab ta yi tare da cewa, "Sa'adah manya, to wanne irin labari za ki rubuta?"

Kai tsaye ta ce "Akan rayuwata, wata'kila ba za a rasa matan da suke cikin rayuwar da na yi a baya ba!"

Ina fatan su ji labarina don su farka daga barcin makantar da suke, kafin su bude ido su gan su a *HALIN YAU* da nake fuskanta! Hawaye ya zubo mata ta sa gefen dan'kwalinta ta dauke a 'ko'karinta na kar Zainab ta gani.

Cikin sanyin murya da tausayawa Zainab ta ce,

"Amma kuma Sa'adah na dauka zuwa yanzu kin gane rayuwar nan bata da tabbas, bamu muke tsarawa kanmu rayuwa ba, da ace kowa shike sarrafa rayuwarsa da baku rabu da Uncle ba, da baki yi kukan rabuwar ba, Ni kaina ba irin kukan da ban taya ki ba,  ba irin walankeluwar da ba mu yi ba a waccan lokacin, amma da yake a lokacin ubangiji bai nufa zamu samu cikar burinmu ba mun hakura kan dole.  yanzu kuma Allah ya karkato da hankalinsa, maimakon ki yi wa Allah godiya, ki bishi sannu a hankali,har Allah ya taimake ki, ki koma dakinki, ki ri'ke 'danki, amma sai ki 'bullo da iya shege? Ni sai yanzu na gane ashe duk kuka da damuwar da kika yi ba har zuciya bane! Wallahi Sa'adah iskancinki ya fara damuna yanzu abin da kika mishi, da ya tsaya don ya taimake mu ya yi dai dai?"

Sai a lokacin ta bude baki ta ce "Idan dai taimakon daga gareshi ne ba na so, ya je ya rike dukkan taimakonsa, ke duk wani abu da ya shafe shi bana bu'kata. ya yi harkar shi na yi tawa, idan Allah ya so ma ba zan sake kuskuren bari mu hadu ba, ai wannan visiting 'din ma dole ne yasa na je, Inna bata nan, Anty Sumayya kuma tana da uzirin mijinta ba lafiya, dama su ne suke zuwa masa. Jawad ne yace, Malam ya ce masa baya gari ba zai sami zuwa masa ba, kin ji 'karfin zuwana." Ta ja majina ta ci gaba da cewa,

"Amma ban da haka ba zan je a ranar ba, balle mu hadu!

Zainab da ne na yi haukan banza na son na koma masa, amma a yanzu ko zan mutu ban yi aure ba, zan yi iyakar 'ko'kari na ga ko zaman mota bamu sake yi ba, balle zaman aure"

Muryarta ta karye alamun kukan da take ma'kalewa gaf yake da ya kubuce mata, ta ci gaba da cewa, "Ban taba dauka Mukhtar zai jefe ni, da abin da ya jefe ni da shi ba, in da tun farkon rabuwar mu na san kallon da yake mini ke nan da ko zan mutu ba zan bi shi ba, bare na ba shi ha'kuri, tunda na san shi ban huta ba.

Ban ga kuma da me na tsira a cikin zamana da shi ba, sai ko rabon Jawad da ya ratsa shi ma Ubangiji ne Ya 'kaddara ni ce uwarshi, amma a zuciyar MK, Farida yaso ta zamo uwarshi"

Sai lokacin Zainab ta katse ta da cewa, "Wallahi karya kike yi, ina ce ba dole aka mishi ya zabe ki a farko ya barta ba? kin dai san namiji ba a mishi dole, kuma ke da kanki kin tabbatar ke ce kike da alhakin mutuwar aurenki?"

"Tabbas ina da laifi amma ai shi ma ba za a rasa nashi ba, sannan kuma bi-ta-da-'kullin da ya bi ni da shi a idonshi da zuciyarsa ya sa na ji ko son shi ne ajalina sai dai na mutu da na koma masa, balle ma ba abin da hakuri ya bari"

"Ko za ki kwana kina rantsuwar ba kya son sa, ko ba kya son ki koma, ba yarda zan yi ba don kuwa 'karya ne tsagwaronta, don kuturun munafunci kun 'ki fa'dan mussababin rabuwar taku ai wannan ka'dai ya isa a san kuna son junanku tunda ba ku yarda aji sirrinku ba. Amma ban sani ba ko kin fa'da wa Halima tunda 'kanwar Inna ce ko kuma madadin Anty Sumayya"

'Kin tanka mata Sa'adah ta yi dan ta san magana ta fada mata a fakaice. Ganin haka yasa Zainab canja magana don tasan idan ta ci gaba da zungurarta yanzun nan Inna za ta shigo ta raba su don ba 'karamin aikin Sa'adah ba ne ta rufe ta da sababin da duk wanda ke gidan sai ya san an ta'ba ta.

Sai ta bige da lallashi, "Haba Maman Jawad na san ki da fa'da amma ba ki da ri'ko sam, na ro'keki kar fishi yasa ki yanke hukuncin da za ki yi kukan da ya zarce wanda kika yi a baya".

Ta nisa ta kalli Sa'adah, ta sake cewa  "Idan ma wani Abu ya ce miki da ya miki ciwo wata'kila ya fada ne a lokacin da yake cikin fishi, ko kuma ya fada ne don ya 'kuntata miki, ki ji yadda shi ma yake ji. Amma shi ba abin a ranshi yanzu, tunda akan kunnenki Baba direba ya tabbatar da shi kanshi ya fahimci irin son da yake miki, ke ma kuma ya lura kina son shi, haba Sa'adah!"

Kukan da Sa'adah ke ma'kalewa ya kwace mata sosai, har Zainab ta ji to ko akwai wata magana data fada cikin kuskure wacce tasa ta kuka haka?

Amma da ta tuna Sa'adah sarkin kuka ce ko ba dalili, yasa ta samin nutsuwa.

Shiru ta yi, ba ta yi yunkurin hana ta kukan ba, ta san ko ba komai dai za ta sami salama a zuciyarta, sai da ta tabbatar ta yi ya ishe ta sannan ta ruko hannunta tana fadin ya isa haka, ki yi hakuri komai zai wuce ya zama tarihi, ki yi addu'ar zabin alheri, bawai  zabin ranki ba."

Ta mike tana cewa, "Kin ji har ana kiran Maghrib bari na tafi sai na sake shigowa, ko kuma sai na gan ki."

Sa'adah ba ta ce mata uffan ba, ita ma Zainab din sanin halin 'kawarta tun fil'azal yasa ba ta damu ba. Ta juya ta fita, a tsakar gida ta tarar da Inna ta goya Khalifa ya nata barci,

"Ah goyo ki kayi haka Inna? Ai sai yasa miki ciwon baya."

Murmushi Inna ta yi tare da cewa, "Ku dai yaran yau da bakwa son goyo ne kuke kallon zai sa ciwon baya, alhalin shakuwa da tausayi ke 'karawa a tsakanin uwa da danta, amma ku boko da gayu ya hana ku goyo sai dai a hannu"

Dariya Zainab ta yi tana fadin

"Inna Allah ina 'ko'kartawa."

"Allah Ya sa!" Inna ta fada tana kunto shi, yaro yasa kuka, wai shi an saukko da shi, ai ko Inna ta ce, "Juyo na sa miki shi a bayan." Cike da kunya da girmamawa tace, "To"

Ta sunkuya ta sa mata shi har zanin Inna ce ta daura mata, sannan ta bar ta ita kuma ta hau kiciniyar gyara goyon.

A gurguje suka yi sallama ta tafi ita kuma Inna ta yi bandaki da buta a hannunta.

Ta idar da sallar Maghrib tana zaune kan sallayar tana jan carbi, wayarta ta hau 'kuwwa, hannu tasa ta janyo ta ganin sunan Hajiyar Bichi, yasa gabanta ya fadi, duk da suna waya lokaci zuwa lokaci, amma ba tasan dalilin faduwar gaban da ta ji a yau ba. katsewa ta yi sai ta kira ta, Hajiya ta ambata sai kuma tace, "Assalamu alaikum!" Ciki-ciki Hajiyar ta amsa. Sai jikin Sa'adah ya yi sanyi ta ce, "Lafiya kuwa Hajiya?"

"Ba lafiya ba Sa'a, yanzu a ce za ki tafi wurin Jawad amma ki kasa fada mini? Na san kuma kinsan ubansa baya nan?"

"Hajiya ni ban sani ba".

"kin sani mana ai ba zuwa kike ranar da ake taron ba, amma wannan karon kin je saboda wanda kike gujewa haduwar ta ki da shi ba zai jeba,

sai kuma Allah ya yi nufin haduwar taku wanda shi kadai ya san manufar hakan.

Ban ga kuma laifinki don kin kame kanki ba. Laifinki daya da kika san dukkan ahalinki ba za su sami zuwa ba, sai ki fada mini mu tafi bibbiyu, wannan abu da kika mini sai nake ganin kamar ni ma fushin da kika dauka ya shafe ni ganewa ne ban yi ba sai yanzu."

Cikin son kare kai da kuma iyakacin gaskiyarta tace, "Wallahi ko ka'dan Hajiya ba haka ba ne, ba abin da za ki mini nan duniya na yi fishi da ke, har gobe ke uwa ce. Tunani na bai ba ni na yi hakan ba, na ma yi tunanin direba zai kai ku tare da Antinsa, amma ki yi ha'kuri Hajiya"

Take ko Hajiyar ta ce, "Na huce dama rashin fahimta ne, ki gaida Innar taki, kuma In sha Allah ina nan tafe cikin satin nan"

"Allah ya kawo ki Hajiya!"

Ta ajiye wayar tana jin idan akwai asarar da ta yi cikin rabuwa da MK to kuwa rashin nagartatciyar suruka irin Hajiya na kan gaba, jin kanta ya mata nauyi ne yasa ta ci gaba da ambaton Allah.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍

[5/15, 19:03] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```
```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

*SADAUKARWA GA*

*SADIQ ABUBAKAR*.

*ALLAH KA JIIKAN*

_HAUWA M. HASSAN_

*(FINE GIRL)*

_UBANGIJI KA ALBARKACI SU FA'EEZA_.

13-14

Tsawon kwanaki addu'ar za'bin alheri ya dinga yi tsakaninshi da Sa'adah ba 'kak'kautawa, kuma ALHAMDULILLAH, ya ji takurar da yake ji akan zama da ita ta kau, ya sami sau'kin nauyin da zuciyarshi ta yi akan ta.

Ranar Juma'a bayan an sau'ko Masallaci kai tsaye gidan su ya zarce kamar yadda ya saba a falo ya tarar da Hajiya zaune kan sallaya, tana lazimi. Ya jima yana zaune kafin ta shafa addu'arta ta juyo ta kalleshi, a nutse ya shiga gaishe ta tare da
```

tambayar jikinta kasancewar kwanaki biyun nan fama take ta yi da zazzabin cizon sauro.

"Jiki kam na ji sau'ki sai rashin 'karfin jiki wanda sai a hankali."

Ta fada tana daddanna 'kafarta.

"Hajiya 'kafar ciwo take miki ne?" Ya fada cike da kulawa.

Ta ce, "Ba wani ciwo kawai kasala ce!"

"Sannu idan kin gama shan maganin ba ki ji daidai ba, sai na mayar da ke wajen likita."

Da sauri ta ce "Kai raba ni da zancen Likitan nan na ji sauki."

Dariya ya yi! dama tsokanace wannan zazzabin ma da 'kyar ta yarda ta je asibitin bare ta yarda ta koma.

"Har yau ba ka ce mini komai akan maganar Sa'a ba?"

Murmushi ya yi "Oh! Hajiya ai na ga ba ki da lafiya ne."

"A a

na ji sauki "

Gyara zama ya yi sosai ya fuskance ta, "Hajiya!" Ya kira sunanta.

"Na'am!" Ita ma ta amsa tare da mi'ka dukkan natsuwarta gare shi.

"Kamar yadda na ce miki zan yi addu'a, to na yi! kuma na ji tsoro da razanin da nake ji a tattare da zama da yarinyar nan ya gushe daga zuciyata, amma..." Sai kawai jin ta ya yi tana ambaton Alhamdulillah! tausayinta ya kama shi na ganin tsananin murnar da take yi akan abin da ba tabbacin yi yuwar faruwar shi.

Ya san Sa'adah, ta kyautata mata matu'ka. Lamarin da Hajiya ta tattara dukkan kaunar da take mishi ta mi'ka mata, duk irin laifin da za ta mishi tofa a idon Hajiya ba laifi ba ne sai ta ce ai yarinya ce, 'kuruciya ce ba kuma hankalinsu 'daya ba.

Har ya fara yi wa Sa'adah kallon macijiya ta sare shi, ta kuma koma gefe ta lullube uwarshi da alheri, haka nan hatta 'yan uwansa, mussaman Samira da Hafsatu basu dauki lamarin Sa'adah da wasa ba, saboda yadda ta kyautata musu iyaka, ya san ba ta da rowa, tana da saurin sabo, ba ta kuma sa ido a lamarinsa da 'yan uwanshi, komai zai musu kuwa, wani lokacin ma ita take ankarar da shi.

Shi har mamakin ta yake yi yadda duk wani rikicinta, fa'danta, rashin kirkinta, da kuma rashin ha'kuri duk akan shi ya 'kare.

Ta 'dago tana kuma ambaton ALHAMDULILLAH.

"Hajiya abin da nake so ki gane yarinyar nan fa yanzu gaba'daya ba yadda kike zaton ta ba ne, na tana son dawowa 'dakinta, don haka kar ki sa a ranki cewar za ta dawo, azo kuma abu bai yiwu ba, ki zo ki sake shiga damuwa kinsan dai kullum girma 'kara kama ki yake"

Shiru ta yi can ta nisa, "Shin kai a wurinka magana ta wuce ta 'bacin rai ba tashin tashina?"

Ya yi jim, yasan dole sai sun sake baje tashin hankalin da ya gitta a tsakaninsu, kafin a manta shi gaba'daya! Amma sai ya amsa mata da cewa

"Babu Hajiya! amma wallahi bazan ta bin kanta ta amince ba, don na lura yanzu wani iya shege ta ke ji"

Da sauri Hajiya ta 'daga mishi hannu,"Kai da'dina da kai ba ka fahimci yarinyar nan ba, kishi ne ke 'dawainiya da ita, ka duba mana kafin ka yi auren nan wanne irin bibiya ne ba ta maka ba? har kowa ya gane ita ce mai laifi a tsakaninku, duk da ba ku cewa kowa ga yadda abin yake ba".

Ta yi 'kasa da murya, "Yanzu fa duk girman laifinta, kama ta hukuncin da yanzu kai ne mai laifi a tsakaninku tunda ka mata kishiya, abin da nake so da kai, kar ka yarda wani borinta yasa ka yi 'kasa a guiwa, ka lallaba ta ka'dan, ni kuma sai na lalla'ba mana ita da yawa"

Dariya ya dinga yi,"Oh Hajiya saboda Allah ni da Sa'adah wa kika fi so?"

"Ai kai ma kasan ita na fi so! nan kusa za a dade ba'a samu mai girmama uwar miji da 'yan uwanshi irin ta ba. Ina fa ji ina kuma ganin yadda she'danun yaran yau suke wa iyayen mazan su iyashege kala-kala, har sunaye suka la'kaba musu, wai uwar miji ce Ulcer, BP, ciwon kai, da sauran sunaye na tsiya, amma Sa'a bata a cikin wannan layin".

Dariyar ya sake yi tare da cewa, "kun yi dace ne kawai ke da ita wasu laifin iyayen mijin ne ai, da basa 'dauke kai ga harkar gidan ya'yan su maza, sannan basa jan surukan nasu a jiki, basa kuma yi musu sassaci da uzziri.

Wasu kuma tabbas laifin *Matan Yau* ne da suke ganin uwar miji tamkar wata 'yar katsalandan ga rayuwar su sai afara zaman Allah ya kawo maraba. Allah dai ya rufa asiri kawai, amma Hajiya ita Farida fa?"

Da sauri ta ce, "Ita ma ba ta da laifi tana da irin nata alherin, amma..." Ya katse ta da cewa "Ba kamar Sa'a ba ko??"

Dariya ta yi tana cewa "Yaushe zaka je gun nata?"

"Zan je In sha Allah!" Jin yadda ya sau'ko ya kuma amince da maganar Sa'adah a karon farko tun bayan rabuwarsu, yasa bata matsa mishi da yawa ba, sai ta ce, "To ka mayar da hankali don Allah, a yi a gama komai cikin 'kan'kanin lokaci ku dai yanzu ba yara ba ne"

Mi'kewa ya yi yana gyara sakun hularsa tare da cewa, "Ke da kika ce za ki lallaba mana ita, ai ni ba sai na yi komai ba."

Cikin sauri ta furta, "Ai ko tilas kai ne mai magana a farko"

Murmushi ya saki tare da yi mata sallama ya fita yana fadin, "Sa'a ta same ki sosai Hajiya"

Gidansa ya nufa, a falo ya tarar da Farida cikin kwalliya ta burgewa tana zaman jiran shi, ta hau hidimar kawo mishi abinci, da abin sha, sai daya kammala, ta kwashe komai sannan ta dawo ta zauna tana tambayar Hajiya. ya amsa da cewa "Tana lafiya! ta ce a gaishe ki."

Murmushi ta yi tare da fadin "Na gode!"

Hannunta ya riko ya janyota sosai kusa dashi, "Ina son mu yi magana mai mihimmanci, ki nutsu ki ji me zance miki, ki kuma fahimce ni"

Idanuwanta masu sheki ta zuba masa tana jin a jikinta abin da ta dade tana jiran ya tabbata ne yake neman faruwa a wannan karon, kai ta gyada tare da cewa, "Ina jin ka."

Sai kuma ya kasa cewa komai tsawon lokaci, ita kuwa da ke ba mai gaggawa ba ce ba ta ce masa uffan ba.

Har ya gaji ya nisa don kanshi sannan ya ce, "Ba sabuwar magana ba ce mun sha yin ta, sai dai ta yau 'din ta sha banban!"

Nan ma cewa ta yi, "Ina sauraron ka!"

Abin mamaki sai ya ji shakkar furta maganar yake. Cikin dauriya ya ce, "Maganar Sa'adah ce zan fara magana da ita, idan Ubangiji bai 'karar da zaman namu baki 'daya ba, zata dawo "

Gabanta ya fadi duk da a kullum cikin tsammanin faruwar hakan take, amma sai da ta kadu matu'ka da gaske, amma da yake tana cikin jerin matan da Ubangiji ya ba su ha'kuri mai yawa da sanyin hali, da kuma ha'diye damuwa sai ta ce!

"Ai da ma ka sha fada mini a kowanne lokaci idan 'kaddarar zamanku ba ta 'kare ba za ka dawo da matarka, ni kuma na sha fada maka cewa ba zan baka matsala ba hakane?"

Ta tambaye shi, kai ya 'daga mata, "To a yau ma ina tabbatar maka baka da matsala da ni. amma zan ro'ke ka abu daya, na san kana son ta sosai, ni kuma ina son ka sosai, don Allah ka yi mini adalci"

Wani abu ya ji ya tsirga mishi tun daga kanshi har zuwa 'kafarshi. Gaba'daya ya janyota jikinshi yana jin tausayin ta na tsirga mishi a zuci da gangar jikinsa gabadaya.

Cikin murya marar amo ya ce, "Farida a tsayin zamana da ke kin san ina son Sa'adah amma abin mamaki ba ki san ina son ki ba?"

Luf ta yi ba ta amsa ba, saboda yadda take kokawa da zuciyarta da numfashin ta.

"Kai, kishi, bala'i!" Ta fa'da a zuciyarta, ban da haka abin da take da tabbacin zai faru ne, don yana neman faruwa kuma sai ya dame ta? kamar ba ita ce take ta mishi kau'din ya dawo da matarsa ba?

Amma a yau da ya amsa, har ya zauna yana fa'da mata da bakinshi akan zai dawo ita sai ta ji kishin da ba ta yi tunanin zai taso mata ba, ya taso da wani irin 'karfi mai gigitarwa.

Jin ta yi shiru yasa shi fadin, "Ban aure ki akan wani dalili ba sai don ina son ki, ina zaune da ke saboda ina son ki, ina kuma jin dadin zama dake, don haka ba wani abin dazai raba ni da ke matu'kar ba ke ce kika bijire mini ba. Ina son ki Farida irin son da zan iya sadaukar miki da komai, ba abu mai da'di a soyayya irin a so ka da kai da dukkan matsalarka, a mutuntunta ka, a kuma yarda ka isa koda kuwa a zahiri baka isan ba.

Ba abin da baki mini na kyautatawa ba, ba kuma zan manta ba, kar ki yarda ki sa a ranki wai zan juya miki baya akan Sa'adah, kar ki ji a ranki na fi son ta akan ki, ni ban san wacce na fi so ba, wacce duk ta kiyaye mini 'bacin Raina, ta zauna da ni lafiya cikin aminci, ta yarda bazan musguna mata da gangan ba, ba shakka itace zata jagoranci zuciya ta. Idan kuma kina da matsala akan dawowarta fada mini zan iya fasawa, idan har hakan zai fi zama masalaha."

Rungume shi ta yi sosai ta na jin wata irin nutsuwa ta na shigar ta.

Ashe har haka matsayinta yake, ashe darajarta ta kai haka? kai ta hau girgizawa, ta ce, "A a ban da matsalar komai wallahi, kawai dai fargaba nake kar ka canja mini kar ka juya mini baya".

Murmushi ya yi yasan tana da hujjarta tunda an yi hakan a baya, don haka sai ya ce, "Aure ya wuce wasa ba na fatan kuma na rabu da matar aure na akan wata matar, ki cire wannan tunanin don yanzu ke ce matata, zan iya ha'kura da ita, matu'kar ta ce ba za ta zauna da ke ba, ke ko ba zan iya rabuwa da ke akan ta ba"

Sai kawai ta saki kukan da take ta haniniya da shi akan kar ya zubo, ya 'dago ta ya shiga lashe hawayen nata, wanda na tsananin murnar maganganunsa ne ko da ba haka ba ne a zuciyarsa ya nuna mata girmamawa tare da karramawa, ta kuma gamsu yana son ta sosai.

"Ubangiji Ya sanya alheri ya zaunar da mu lafiya, Allah ya 'kara maka lafiya, da bu'din arziki ya kuma hore maka ikon yin adalci"

Amin ya ke ta fa'di tare da jin ba abu mai dadi a duniya irin mace ta gari, mai fahimta, mai kuma ilimi da aiki da shi, don sau tari shedanun matan masu ilimin ne, kawai aiki da shi ne ba sa yi. A fili ya ce, "Ubangiji Ya miki albarka My Feri-Feri, Allah Ya ba ki rabo mai amfani."

Zuciyarta ta yi fes ta na jin dadin wannan addu'ar da yake yawaita yi mata na albarka da samun zuri'a mai albarka.

Suna haka har aka kira La'asar sannan suka mike shi ya yi Alwala ya yi masallaci ita kuma ta yi a 'dakinta.

Bayan ya dawo Masallaci bai shiga gidan ba a 'kofar gidan ya samu gefe ya zauna ya ciro wayarshi ya fara lalubo lambarta, karon farko bayan shudewar lokaci mai yawa, daf da za ta tsinke ya ji ta dauka, Sallama ta yi, ya amsa, sai kuma ta ja bakinta ta tsuke, shi kansa sai al'amarin ya zo mishi a bai bai, cikin 'karfin halin da aka san namiji da shi ya ce, "Ke ba ki iya gaisuwa ba ne?"

Cike da son ta nuna mishi ba shi da sauran matsayi a zuciyarta ta ce, "Waye?"

Bai yi mamaki ba, dan haka sai ya nufin 'kunsa mata takaici shima.

"Wadda ki ke ta sallar dare ne akansa".

Yana rufe baki ta ce, "Babu wannan halittar"

tare da kashe wayarta.

Zuciyarta na bugawa wai yau mafarki take ne ko kuwa da gaske Malam ne ya kira ta taka nas? Wacce iriin sa'a yau ta tashi da ita? tana tuna kalaminshi na 'karshen maganar su a wani lokaci da ya shu'de, sai ta ji murnarta ta koma ciki, ba za ta

saurare shi ba har sai ya janye kalamunshi, da kallon da yake mata, idan ko ba haka ba, to tabbas ba za ta sake mu'amala da shi ba, bare babbar mu'amala irin ta aure, ko da hakan na nufin mutuwarta ne.

Al'kalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍✍

[5/16, 13:26] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

SADAUKARWA GA

SADIQ ABUBAKAR

Fatan Alheri ga

DANDALIN MUM KHADY.

□□

15-16

Mamakin ta ne ya yi matu'kar kama shi wai yau shi ta kashe ma waya? Anya Sa'adah za ta canja hali kuwa?

Sake 'kiran ta ya yi a karo na biyu, amma ga mamakin sa har 'kiran ya katse ba ta 'daga ba.

Ya ri'ke wayar ya yi jim cikin sanyin jiki da tunani iri iri.

Ya san kirkinta ya fi sharrinta yawa, har yau kuma, shi dai a idanuwanshi bai ga wacce ta iya tsara kwalliya da gayu irin Sa'adah ba, ma'abociyar son 'kyale-'kyale

ce, kusan wannan dabi'ar tata na son kayan 'kawa masu tsadar gaske ya taimaka wurin sake jefa aurensu cikin garari.

Lambar amininshi ya lalubo Dr. Mahmoud Karfi, ba ta dade tana dokawa ba, ya ji an 'dauka, tare da sallama, kai tsaye MK ya ce, "Kana Ina?" Daga can bangaren ya amsa da cewa, "Ina makaranta, lafiya?"

"Lafiya Lau jira ni gani nan zuwa"

Ya katse wayar ya mi'ke ya shiga gida, ya dauki mukullin motarshi, tare da yi wa matarshi sallamar ya fita, ta bi shi da addu'ar dawowa lafiya.

"Kai tsaye sabuwar Jami'ar Bayaro ya nufa, bai bi takan ofishin saba, ya zarce ofis din Dr. Mahmoud Karfi.

Da sallama ya shiga shi ka'dai ya tarar yana dakon isowarsa, musabaha suka yi, Dr. Karfi ya dube shi, "Ka sa ni tunani iri iri fa"

Jim MK ya yi tare da cewa, "Wallahi ru'dani na shiga, ka san Hajiya ta matsa akan maganar na dawo da yarinyar nan, to dai yanzu na amsa mata akan na amince bayan na yi addua na kuma ji na aminta da lamarin. Wai yau na 'kira ta a waya da farko ce mini ta yi waye?"

Dariya ta so subuce wa Dr. 'Karfi, amma ya kirne, shi kuma ya zarce da cewa,

"Karshe kuma sai ta kashe mini waya"

"Alhamdulillah!"

'Karfi ya furta a fili tare da cewa "Ni na da'de ina ji a jikina idan dai ba mutuwa ce ta sure dayanku ba, to kuwa za ku sake ha'dewa. Shi yasa na kyale ka ka sami nutsuwa, ka san dai Sa'adah ta bi ka iyakar bi akan ka yafe mata, amma ba ka yi

ba, ka zo ka yi aure dole ta gaji ta yi fishi, amma na san fishin ba mai yawa ba ne, tunda tana son ka."

A sanyaye ya ce, "Anya kuwa? ba ku san ta ba ne, a makarantar su Jawad fa baka ga iya shegen da ta mini a bainar nasi ba"

Dariyar da Dr. 'Karfi ya ke ri'kewa ta subuce, ya hau yi sosai, har ta sha'kar da MK, don haka sai ya mike ya ce, "Na gode"

Da sauri 'Karfi ya ruko shi ya na fadin, "Yi hakuri ka zauna ai ba mu gama ba"

Cikin fushi ya ce, "Ya zan zo maka da matsalar da ta dame ni, ka sani gaba kana mini dariya ka mayar da ni mahauka ci!"

"Wane ni Allah ya huci zuciyarka zauna mu gama"

'Karfi ya fada bayan ya shanye dariyarshi. Komawa ya yi ya zauna amma fuskar nan a ha'de.

"Yanzu ka san me? Zan je na same ta mu yi magana, idan ya so sai mu koma tare, daga nan kuma shike nan sanda za ka je ma ba zan sani ba"

Cikin cin magani ya ce "Ni wallahi bazan ta zarya a wajenta ta na mini iya shege ba, yanzun ma Hajiya ce ta matsa amma banda haka ta je can ta 'karaci tsiyarta"

Mahmoud ya ce, "Yanzu ma damuwar da na gani a fuskarka, akan ta kashe maka waya, Hajiya ce ta matsa ka fada mini?"

Tsaki ya ja, ya san sha'kiyanci zai masa, tunda idan akwai wanda ya san yadda yake son Sa'adah to kuwa Mahmoud ne.

Sai kawai ya mi'ke ya fice yana fadin, "Sai ka yi kai ka'dai."

Shi kuwa ya ci gaba da dariyar shi a sake yadda yake so.

Ta idar da sallar Maghrib ke nan tana zaune tana tasbihi, zuciyarta cike da farin cikin fara gyaruwar al'amuranta, wayarta ta hau kuwwa, ganin sunan Baban dady yasa ta jin wani farin ciki ya 'kara kama ta, ba ta yi azarbabin 'dagawa ba har ta katse.

Kafin ta yi wani yun'kurin, ya sake 'kira, haka ta gama yau'kinta, ta dauka hadi da yin sallama,"Ranki ya dade ai na zaci ba za ki dauka ba ne"

'Yar dariya ta yi, "Akan me? Sallah na idar."

"Ya mutanen gidan to?" Ya tambaya, ta amsa mishi da, "Duka lafiya Lau"

"Ina son ganin ki wanne lokaci zan same ki?"

sanin mutuncinsa da karamcinsa ya sa ta fadin ko yaushe "Ina gida!"

"To ki saurare ni anjima kadan zan iso."

"Sai ka zo." Ta fada tana jin wani irin nisha'di na tsirga mata.

Wanka ta shiga ta fito ta shirya cikin lallausan yadi ruwan hoda, mai shegen tsada ba shi da adon komai haka yake plane sai yauki yake da 'daukar ido. Doguwar riga ne aka 'kawata da shudin stones masu sheki matu'ka, don haka ta yane jikinta da matsakaicin mayafi blue,

mai da roll on kawai ta shafa, kasancewar turarukanta sun kama kayanta sosai kuma ma'abociyar yin turaren kaya ne irin na barebari (garam). Duk da dare ne, sai da ta shafa powder ta kuma zagaye le'banta da jan baki ruwan hoda.

Yanayin jikinta irin tauraruwar wasan kwaikwayon nan ce Hafsat Barauniya, duk da Hafsar ta fi ta shekaru, ta kuma fita hasken fata, kasancewar Sa'adah mai duhu ce, ba kuma ta yarda ta shafa man da zai canja mata launin kalarta ba,

illa tana 'batar da kud'a'de masu yawa wurin siyan tsadadden man dake fitowa da ainihin kalarta, ta goge ta yi tas da ita, ta yadda ko mace sai kin yi sha'awar launinta shi yasa idan akwai tambayar da a rana ana mata ya kai sau biyar, ita ce wanne mai ki ke shafawa, wanne mai ki ke amfani da shi? wani lokacin ta fa'da, wani lokacin kuma ta yi murmushi wushiryarta ta sake 'kawata ta tace "Vaseline"

Tana tsaye jikin Shoe Rack (ma'adanar takalman)ta ta fito da wani Tom's blue, Innarta ta shigo ta kalle ta ta ce, "To 'dawisu sarkin ado a wannan daren kike wannan kwallliyar anya Iya baza ki rage wannan 'kyale-'kyalen ba? Shi yasa ai da yawa mazan suna son zuwa gunki amma gani suke kin fi 'karfin su"

"Inna tunda ba ni na fa'da ba ai shi kenan, idan mutum da gaske son nawa yake ya zo mana idan mun daidaita ai zan aure shi ne"

"Yanzun kuma mai za ki yi da takalmi, da na ga kina gogewa? Na san dabi'ar ki ce ca'ba kwalliya ba sai za ki fita ba, amma wannan takalmi ai na fita ne, kuma kin san ba inda za ki a wannan daren"

"Kai Inna don Allah!" Ta fa'da cike da shagwaba, "Ni fa ba fita zan yi ba, ba'ko zan yi"

"Kin fa'da wa Baffanku za ki yi Ba'ko?"

Kai tsaye ta ce, "Na fada masa kafin ya tafi sallar Isha"

"Shi kenan amma don Allah Iya ki daina bata wa mutum lokaci kina kuma karbe mishi abin hannunsa alhalin kin san ba auren sa za ki yi ba,

yaudara ba kyau. Alhaji Mamman din nan ni ban ga laifinsa ba, mutum mai mutunci mai nagarta ga shi babba ne ya mallaki hankalinsa amma kina tasa 'kafa kina shure shi, kuma kina kar'be mai dukiya"

"In sha Allah, Inna ko mai ya kusa zuwa 'karshe, ki 'kara 'kaimi wurin yi mini addua"

Dadi ya kama uwar tata kusan yau ne Sa'adah ta bude baki ta yi magana mai kyau akan aure.

Nan da nan ta hau fa'din,

"Addu'a kam ai kullum yin ta nake, mantawa na ke da ko mai sai ke idan ina addu'a, Allah ya miki zabin alheri"

Ta fita tana sake cewa, "Ba abin da ke raina irin in gan ki a 'dakinki kin nutsu wuri daya"

Har sai da ta yi sallar Isha sannan ya mata waya ya iso. Fararen kujerun da ta tanada saboda zuwan wanda tabawa izini, ta 'diba ta fita dasu zauren gidan nasu da ke da yalwar fili, tana zuwa shi ma yana 'karasa shigowa, da sauri ya karbe kujerun yana cewa "Ai da kin sani kin jira na zo na 'debo, wannan ba aikin uwargidanmu ba ne"

Dariya ta yi, "Za ka fara ko?"

Shi ma dariyar ya yi, "Zan fara fa'din gaskiya ba"

komawa ta yi ta ha'do mishi ruwa (pure water) da kuma kunun ayan da Inna ke yi akan faranti tare da Tumbler, ta ajiye mishi tare da cewa "Ga ruwa"

Ya yi godiya ita kuma ta hau gaishe shi tare da tambayar iyalinshi, ya ba ta amsa da cewa, "Ai ta yi fishi da ke tace rabon da ki taka mata tun barkan haihuwar Kausar,

ga Kausar tana gudu ko Ina."

Ta ce, "Hidimar makaranta ce ta 'boye ni amma yanzu kam na gama za ta gan ni, a ba ta ha'kuri"

Sai da ya bude ruwa ya sha sannan ya yi gyaran murya ya ce, "Zuwan fa na mussaman ne, tare da albishir din abin da muka dade muna nema ya samu, takanas MK ya same ni ya ce mini ya kira ki, amma kin kashe mishi waya haka ne?"

Kai tsaye ta ce "E ai ban san shi ba ne"

"Ban gane ba ki san shi ba ne"?

"To bai gabatar da kansa ba,

ya fara maganganun da ban fahimce su ba".

Shiru ya yi tare da cewa

"Amma ba ki da lambarsa ne?"

"Ban da ita"

"Ba ki da ita?" Ya tambaye ta cike da mamaki.

"E!" Kawai tace ta ja bakinta ta tsuke.

Kamar zai bar maganar sai kuma ya ce, "Amma aikin haddace a kanki"

Nan ma ta ce, "Na manta"

Ya yi dariya, "Sa'adah wai yaushe kika cire mu a ranki har haka ne?"

Murmushi ta yi ta ce, "A lokacin da na fahimci ba komai ne idan ka rasa yake dawo maka ba, ba kuma komai ne kake so yake zama alheri ba"

Da sauri Dr. 'Karfi ya ce, "To mu dai alheri ne kuma mun dawo mu sake daukar ki a karo na biyu."

"Amma bai kama ta, ya manta cewar aure ya 'kare a tsakanin mu ba?"

Ta fa'da cikin 'daure fuska.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·

matsalar ba. ko wani sabon auren kipka yi komai jin da'din da za ki riska sai kin tarar da matsala"

Ya nisa sannan ya sake fa'din,

"Ina tabbatar miki kuma a yanzu ne ya fi dacewa ki koma dakinki, ba a wancan lokacin da ke kadai kike son komawar ba, yanzu da shi ya bukaci hakan da kansa za ki fi 'kima, ki fi daraja"

Sunkuyar da kai 'kasa ta yi hawaye na cika idonta, amma ba ta ce komai ba, ganin yadda jikinta ya yi sanyi, hakan ya 'kwarara guiwar 'Karfi.

Ya sake kur'bar ruwa ya ce, "Kar ki bari wannan damar ta kubuce miki, ina tabbatar miki, MK bai so wata mace kamar ki ba, kar ki bari rudin 'kawaye da zuciya su sake rudar ki a karo na biyu, wai ya yi aure, ko kaza da kaza, da duk abin da zai sake dagula miki lissafi.

Ki sa a ranki cewar ko kuna tare zai auri Farida! tunda an rubuta a cikin littafin 'kaddararshi cewar matarshi ce, mu gode Allah da ya kasance rabuwa ku ka yi, ba mutuwa kika yi ba, kin san akwai rabon da ke kashe mutum".

Hawayen da ta ke tattalawa ya zubo akan lallausar fuskarta, ta ce, "Ai ni sai daga baya na gano dama auren ya 'kallafa rai zai yi shi yasa ya yi ta zungurata, komai 'kankantar laifi sai ya juya shi ya zama garma, ashe dama akwai abin da ya 'kudure, to ya aureta hankalinshi ya kwanta, ni ma kuma ai bai jini a gadon asibitin mahaukata ba, bai kuma ji labarin auren nashi ya zama ajalina ba"

Kuka ya so kubuce mata saboda haka ta yi shiru sai rishin kukan kawai. Sai da ta nisa sannan ta sake dorawa da cewa, "Ni kuma nan duniya ban ga mai zai mini na ga farin shi ba"

Ta fada cikin dakewa da shanye kukan dake son kunyata ta. Jikin Mahmoud ya sake yin sanyi, ya yi shiru cikin rashin abin cewa.

Tsawon mintuna biyar kowa ya yi shiru a tsakaninsu sai fama suke da tunanin zuci.

Shudewar yan mintuna kafin ya ce, "Ni fa ba tone-tone za mu yi da ke ba, dukkanku, kowa da irin nashi laifin amma kin sani, laifin ki ya fi yawa"

Cikin takaici ta ce, "Baban Dadi tunda laifina yafi yawa, ai ya sake ni ya auro wacce ba za ta yi kuskure ba, wacce son da ake mata zai sa ayi ta mata uzirin ri'ke igiyar aurenta da kyau, sai dai a nuna mata kurenta cikin ladaftarwar da shari'a ta tanadar, shi yasa ni ma da na gane ba son nawa ake ba, kuma duk ni ce mai laifin sai na dau hukuncin da macen da ta san ciwon kanta za ta dauka don ta tsira daga ba'kin cikin namiji".

Shiru Mahmoud ya yi mata ya lura kishin Farida ne ya ke cinta shi yasa take ta furzar da magana, don haka ya 'kyale ta, at least dai za ta sami sau'kin ciwon dake addabar zuciyarta.

Sai da ta yi shiru don kanta, sannan yace"Ki yi ha'kuri, ki bi komai a sannu, ban hana ki nuna bacin ranki ba, amma kar ki wuce gona da iri, saboda kin san kema kin mishi laifin da sai da ya yi jinya bayan rabuwarku, tunda har ya sau'ko, to fa kar ki wuce makadi, ina fada miki wannan maganar ne a matsayin yayanki"

Ya dan numfasa, kana ya zarce da fadin, "Lamarin aure yanzu sai ha'kuri ba Perfect Marriage, kowanne aure da irin nashi 'kalubalen, duk abin da aka ce ibada ne, to fa sai an yi hakuri".

Ya mi'ke yana cewa, "Zan wuce, ki saurari zuwanmu!"

Hannu yasa a aljihunsa ya fito da yan dari biyar guda ashirin ya zuba kan kujerar daya tashi, da sauri ta ce, "Don Allah ka bar su, kullum a cikin hidima kake "

Murmushi ya yi yana cewa,

"Wannan kudin zance ne, ina fatan dai za a karbe mu da dukkannin raunin mu, kasancewar mu Malaman makaranta masu sadaukarwa, ba ma su satar kudin jama'a ba"

Ta san sarai inda maganar shi ta dosa, da Alhaji Mamman ya ke, tunda ya sha ganin ta da shi, wanda 'karara yake taya amininsa kishi.

Dariya ta yi tana kuma godiya amma ta ci alwashin bashi ya ci, dole sai an baje maganar nan ai ya san tun farko ta zabe su tabar Alhaji Mamman din da dukkan abin da yake da shi.

Tun a mota yake 'kiran lambar MK amma bai dauka ba, har ya gaji ya mayar da wayarshi caji a jikin motar. Mintuna kusan ashirin har ya shiga layin gidansa yaji 'karan wayar shi, ganin sunan MK yasa shi dauka da sauri, tare da cewa, "Wai ina ka shiga ne?"

Daga can ya amsa mishi da cewa, "Wallahi ina tare da Farida ne ba zan so ka yi mini maganar Sa'adah a gabanta ba"

Shiru Dr Mahmoud ya yi yana jin shi kam bai san wani namiji da ke gudun 'bata wa matarshi da gangan irin MK ba, ya tuna lokaci da dama da yake zaunar dashi yana caccakar shi akan tsoron Sa'adah ya ke yi, ashe ba tsoro ba ne tunda ga Farida ma hakan ya ke mata.

Mutum ne mai martaba abin da yake so, ko wadda yake son sa, ya sake tuna ko a abotarsu, MK ke ha'kuri da shi, shi ke masa hidima ba tare da tunanin ai yasan yawan albashinsu 'daya ba, samun irin Mukhtar Kabir Bichi zai yi wuya a wannan lokacin.

Amma duk da hakan sai da ya tsokane shi da cewa, "Dadi na da kai mijin ta ce ne kai, ni ban san me ya sa kake jin tsoron mata ba, ai na 'dauka Sa'adah ce kawai dodon taka, ashe wa lnnan alankosar ma murza ka take yi".

Shi ma cikin 'kosawa da shakiyancin da ba ya gajiya da mishi ya ce, "Kai ai ba za ka gane karatun ba ne ni kadai na san mai suke jiyar da ni, ka ga kuwa ai dole na yi tattalin farincikinsu, kar ni ma a hana ni nawa farin cikin"

Dariya sosai 'Karfi yake yi yana cewa, "Ashe haka karatun yake ganewa ne ban yi ba? amma da dukkan alamu karatun naka na daban ne"

"Idan kagama iya shegen naka, ina sauraranka don waje na fito, idan kuma ba ka gama ba, to zan koma, ma hadu gobe"

'Karfi ya gintse dariyarsa hadi da cewa, "Kai MK wallahi da alama 'yar darun taka, ta shiryawa daru kala-kala, amma dai na san kishi ke 'dawainiya da ita, ka san tunda ka yi auren nan bata bude baki ta ce 'kala ba, yana ta cin ranta, na ga soyayyarka mai yawa a idanuwanta duk da bakinta na 'kirarin rashin son"

Shiru MK ya yi har Mahmoud ya yi tsammanin ko wayar ce ta katse. Amma da ya ce,

"Kana ji na kuwa?"

MK ya amsa da cewa

"Ina jin ka. Mamakin ta ne ya ke ta kama ni".

"Ai ba mamaki a lamarin mace." A cewar 'Karfi.

"Ka shirya gobe muje mu same ta, kada Hajiya ta tambaya ta ji ba ka fara kafa tubalin kome ba ta yi fishi"

Ya 'karasa maganar cikin zolaya.

"Hmmm!" Kawai MK ya yi tare da cewa "Na gode sosai sai mun hadu gobe idan Allah yaso"

*

Sa'adah tana shiga a dakin mahaifiyarta ta ci burki, "Inna na dawo"

"Zo ki zauna magana zamu yi"

Ba ta musa ba ta shiga ta zauna daf da ita,"Waye ya zo?"

"Ba wani daban ba ne Baban Dadi ne"

Tabe baki ta yi tare da cewa "Waye hakan, kar ki ce mini Mahmoud abokin Muutar?

Cikin shagwaba ta rungumo uwar tata ta ce "Shi fa mene ne Inna?"

Ture ta ta yi tana cewa

"Ashe baki daina bibiyar yaron nan ba ko? 'dazu amsar da ki ka bani na komai ya kusan 'karewa akan maganar aure, ashe kina nan kina zawarcin Muutar ne? Wannan shi ne al'kawarin da ki ka mini?

Tunda kin zabi son ranki sama da nawa to ki je ki ta yi,

amma ki sani ba da yawuna ba, ba kuma da son raina ba, sai don kin fi 'karfina, don kin san zaki samu goyon bayan mahaifin ki ne"

Ta nisa sannan ta ci gaba da cewa, "Tunda na ga kina ta hanzarin shiryawa tare da 'doki na tabbatar ba kowa kike wa wannan rawan jikin ba sai shi"

"Inna ba fa yadda kike zaton lamarin ba ne wallahi ban karya al'kawarinmu ba, amma don Allah ki yi hakuri ki gafarce ni ba na son kina damun kan ki akan wannan maganar"

"Ai dole na damu tunda na gane ke da Baffanku, ba ku da burin da ya wuce ki koma gidan Muutar, ni kadai na san ba'kin ciki da wahalar da na sha kafin na samo ki a

dalilinsa. kuma yanzu da komai ya wuce sai ya lallabo ya sake dama miki lissafi, saboda ya mai da ke marar zuciya, wacce ba ta san ciwon kanta ba"

Cike da tausasa murya Sa'adah ta ce, "In sha Allah Inna ba zan sake shiga halin da kike jin tsoro ba, ni ma nasan abin da kike guje mini, tuni na cire shi a raina."

"To idan dai haka ne ki ba wa Alh Mamman ko yaron nan Anwar dama wani cikinsu ya fito, ki yi aurenki idan ba haka ba, hankalina ba zai kwanta ba."

Ta fada tana goge hawaye da hannun zaninta.

Jikin Sa'adah ya yi sanyi ashe dai da gaske Inna take akan ba za ta koma wa Malam ba? Ashe haka ta zafafa lamarin?

Wannan wacce irin ba'kar 'kaddara ce ke bibiyar ta ne? Bayan doguwar wahalar da ta sha akan komawarta 'dakinta, sai da abu ya zo a lokacin da ba ta yi tsammanin zuwansa ba, kuma mahaifiyarta ta yi bara'a da lamarin, hankalinta idan ya kai dubu to ya tashi.

Wai mene ne ke faruwa a tsakanin ma'auran biyu? Mene ne ainihin labarinsu? Mene ne ya raba su duk da matsananciyar soyayyar da ke tsakaninsu? Mu je ga mafari don jin wacce irin waina suka toya?

Al'kalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

19-20.

MAFARI

Malam Basiru Ado Gogel, haifaffen garin Gogel ne, wani gari a 'karamar hukumar Warawa. Karatun Allo ne ya kawo shi cikin garin Kano, ya sa himma har Allah ya taimake shi, ya haddace al'kur'ani, sannu a hankali kuma ya fara sana'ar tura kura a kasuwar Singa

Da damina zai tafi gida yayi aikin gona gadan-gadan kasancewar al'ummar garin Gogel manoma ne, duk da ya ta so ba uba, domin ya na da 'karancin shekaru mahaifinsa ya rasu, dan haka ya yi birgimar ta shi fa'din rayuwa a tsakanin mahaifiyarshi da 'yan uwan mahaifinsa.

Da haka ya hada jarin sa ya bude 'yar tireda a cikin unguwar da ya ke hayar 'daki, a unguwa uku, a shekarar kuma aka masa aure da Salamatu 'diyar 'kanin mahaifiyarsa wadda asalin mahaifiyar ta shi 'Yar asalin gamawa ce ta jahar Bauchin Yakubu, aure da rabon haihuwar sa ne ya kawo ta Gogel, kenan Salamatu ma, da ga Gamawa aka ba shi ita.

Ya taho da ita cikin kano, suna zaune lafiya, cikin rufin asiri.

Yarinyar su ta farko da suka haifa bayan shekaru uku da aure, sunan ta Sumayya, ba sunan kowa taci ba, illa sunan Nana Sumayya, macen farko da ta yi shahada a musulunci. tare da fatan yarinyar ta sami albarkacin mai sunan.

Haka sukaci gaba da rayuwar su cikin rufin asirin Allah, dukkansu sun da ce da juna, masu ha'kuri ne, masu kuma wadatar zuci ne.

Sai da Sumayya ta yi shekaru takwas sannan aka haifi Sa'adah wadda sunan mahaifiyarsa ta ci (Sa'adatu). Daga shi har Innar su Salamatu su ke kiran ta Iyah, kamar yadda ake kiran mai sunan nata. A shekarar kuma mahaifiyarshi ta rasu, shi yasa ya tattara ko mai da ya ke dashi a Gogel ya siyar illah gona 'daya da ya bari, wadda zai dinga noma wa, sai kuma 'dakin mahaifiyarsa da yake cikin gidansu ya rufe shi saboda idan ya je Yana da gurin zama. ya zo kano ya si yi madaidai cin gida anan cikin unguwar gidan akan titine a kuma babban layin na Unguwa Uku.

Haka rayuwar su ta ci gaba da tafiya cikin ha'kuri da godiyar Allah, har Sumayya ta kammala 'Karamar sakandire manema suka mata ca kasancewar ta doguwar mace fara sol irin fulanin Gamawa.

Idris shi yafi kwanciya a ran Malam Basiru dan haka ya ce ya bashi, ba kuma ya bu'katar komai a gunsa sai sadaki da musulunci ya wajabta, komai zai ma ta idan ta je gidan shi sai ya yi.

Wannan karamcin da iyayen Idris suka ga ni ya faranta ransu ba ka'dan ba, suka girmama lamarin Sumayya da iyayen ta, kullum cikin jan kunnen shi su ke, akan ya ri'keta cikin aminci.

Haka aka yi auranta ba wani hidima, ya 'dauke ta zuwa ogshobo ta jihar osun inda yake aiki da babban bankin Nigeria (CBN) reshen jahar osun.

Dan haka Sa'adatu ita kadai ta taso a gidansu domin kuwa, ba ta wuce shekaru takwas ba, aka aurar da yayarta kasancewar mahaifinsu bai wani damu da karatun boko ba, muhimmi dai a gunshi a haddace alkur'ani.

Tun kuma akanta basu sake samun haihuwa ba, shi yasa sha'kuwa mai yawa ce tsakanin ta da iyayenta biyu har tana rasa gane waye yafi sonta a cikin su.

Yau da gobe aka ce ba ta bar komai ba, Iyah ta kammala 'karamar sakandire, amma ganin yadda ta k'wallafa rai a boko da kuma yadda ba ta sauraren ko wanne saurayi yasa Malam Basiru barin ta ta tafi babbar sakandire, kamar wasa aka zabe su, su biyar a makarantar su, ta GGC U/Uku, su rubuta jarrabawar shiga sakandire ta gwamnatin tarayya ta Kano (FGC KANO). jarrabawar na fitowa kuwa sunanta ya fito cikin mutum uku da suka yi nasara, ita kanta ta yi mamaki tunda duk ragowan da suka fa'di sun fita 'ko'kari.

Ganin ku'di tsululu da za'a kashe a hidimar makarantar Malam Basiru ya tabbatar ba makarantar dan talaka ba ne, da bashi da ko mai da kowa sai Allah, shiyasa ya zaunar da ita yace, "Iyah kin san ni ba mai kudi ba ne, bani da halin sa ki a wannan makarantar, ki ci gaba da wadda ki ke yi, kin san dai, ko yanzu idan kin samu mijin da na yarda da nagartar shi auren ki zan yi.

Shuru tayi amma a ranta tana jin ba 'karamin abin kunya ba ne ace ta sami damar shiga babbar makaranta irin wannan, amma ace ba ta tafi ba, ba ta san ma da wanne ida za ta kalli 'yan ajin na su ba, mussaman Zainab Salisu Ma'aji da su ke kusan unguwa 'daya, kuma ita ma taci makarantar tana da tabbacin za'a kai ta tunda ta na da yayye ma'aikata.

Kasancewar ta mai tsananin tsabta da gayu sai ake mata kallon tamkar ta fito ne a gidan wadata, ita kuma ganin haka yasa ta yin alfahari mussaman da ba ta da makusa a halittar ta.

'Karfe takwas na dare ta dauki wayar innarta, ta shige 'dakin da ya ke mallakin ta ne, Yar uwarta Sumayya da a yanzu suke zaune a Jos babban birnin jahar Plateau da yaran su biyu Abba da Khalifa, ta shiga yi wa flashing, cikin 'kan'kanin lokaci ta biyo baya, tana 'daga kiran, ta sa mata kukan da ta kasa yi a gaban mahaifan nasu, jin kukanta ya matu'kar tada hankalin Sumayya, ta shiga tambayar ta menene, me ya same ki? jin yadda Sumayya ta 'daga murya a gigice ya janyo hankalin mijinta wadda ya ke kur'bar shayin da ta hada masa, cikin kukan ta fa'da mata yadda ta ci makaranta irin FGC KANO, amma kuma Baffan su ya ce ba shi da kudin sa ta a wannan makaran ta.

Jim sumayya ta yi kafin ta ce "To ban da abin ki Iyah! Ba sai ki yi ha'kuri ba, kinsan dai nan duniya idan Baffa bai mi ki abu ba, bashi da hali ne, da girman ki da komai ki zauna ki na kuka, akan abin da ki ka san ba da gan gan aka 'ki miki ba?"

Shesshkar kukan ta cigaba da yi, Sumayya ta sake cewa "kukan shagwaba ki ke yi Iyah! ni da ba a barni na gama ba fa?

Turo baki ta yi kamar ta na ganin ta, tace "To ai ke yanzu maganar ki ta wuce, kuma gaskiya Aunty, ki dena cemin Iyah". da sauri Sumayya ta furta "Yi hakuri Anty Sa'adatu"

'Dan murmushi ta yi hade da jan majina, sannan ta ce"Ina su Abba? Sumayya ta ce "gasu can sun yi barci sun gaji"

A haka Sumayya ta lalla'ba 'kanwar ta har sai da ta yi dariya sannan su ka yi sallama, amma Sumayya ta dinga jin jina halin kanwarta na yadda ta ke kai kanta inda Allah bai kai ta ba.

Mijin Sumayya da ya fahimci maganar su, sai ya 'kudure abu a ranshi amma bai mata maganar ba, kamar yadda bata sa shi cikin maganar su ba, idan akwai abin da ya ke 'kara mata 'kima to rashin hayaniyar ta da 'karancin buri ne, da wahalar gaske ta bude baki ta ro'ke shi wani abu kai shi zai iya cewa bata ta'ba ba.

Abin da ya mata shike nan, sai shi ne da ya fahimci halin ta, sai yake yawan kyautata wa iyayenta, mussaman da ya fahimci suna bu'katar taimakon amma halin su, na wadatar zuci da rik'e girma, basu ta'ba nunawa ba, bare a gane.

Kwanaki uku a 'tsakani ya tura ku'di masu yawa ta hannun amintaccen amininshi akan ya je ya kai wa surakin nasa, ayi wa Sa'adatu hidimar makaranta, wadda da 'kyar Malam Basiru ya karba.

Ya 'kira Sumayya ya ma ta fa'da akan mai za ta 'dorawa mijin ta nauyin da ba nashi ba?

Rantsuwa ta dinga yi akan ita bata fa'da masa ba, sai dai idan ya ji sadda suka yi waya da Iyah ne, sannan kuma bai fa'da mata, zai yi wani abin ba.

Yace to " Ki masa godiya kudi masu yawa ya aiko, ki kuma 'kara masa biyayya, ki 'kara ha'kuri dashi"

Shikenan sai aka fara shirye shiryen shigar ta makarantar har komai ya kammala.

Ana cikin Shirye shiryen sai ga Baffa yazo da dimemiyar katifar yan makaranta har da filo dukkan su(Vitafoam)ne,da kuma bargo duniyar kule amma 'karamin size, sabo dal a cikin jakar shi.

Da mamaki Inna ta hau duba katifar ta na fadin "wannan katifar ai ta yan makaranta ce".

Sai da ya zauna akan tabarmar da aka shimfida domin shi sannan yace "Wallahi Salamatu wani yaro ne muke gaisawa da shi,tun ba yanzu ba, 'dan gaban tireda ta yake da shago, kullum yazo sai ya gaishe ni, a haka muka yi sabo na gaske. Yau kwanaki uku na fada mishi yarinyar waje na ta ci babbar makarantar gwamnatin tarayya. Bawan Allah sai ya zaci ta kwana ce, ashe wai akwai bangaren ta kwana (boarding), akwai ta je ka ka dawo(day)".

Ya numfasa ya dauki kofin ruwan da aka ajiye mishi ya sha, sannan ya 'dora da cewa

"Sai ganinsa na yi 'dazu da katifar nan, wai ya kawowa 'yar makaranta, nace kai ma ka na fama da kan ka, ya za ka takura kanka"?

Tunda dalibi ne a jami'ar Bayaro, yace min yana shekarar 'karshe, na'ki karba tare da nuna masa ita ba ta kwana ta ci ba, dan haka ya mayar ya amshi kudinsa, nan ya rantse ba zai koma da ita ba, tunda ya riga ya siya, ya kuma yi niyya, abata ta dinga kwana a kai.

Kuma abin mamaki har da ku'di wai a siyi littafai"

Sai lokacin Inna tace "oh mukam mun gode Allah, Allah ya saka masa da alheri, Allah ya sanya alheri da farin ciki a rayuwarsa".

Take kuma ya ce "Iya zo ki dauki katifar nan da bargon nan naki ne, wani yaron arzi'ki ne ya baki, sai ki sa shi cikin adu'oi'n ki".

Da murna ta ja katifar tana fadin Nagode Allah ya saka da alheri.

"Ya sunansa Baffah?"

"Sunansa Muuktar amma ni Mutari na ke ce mishi ya kuma amsa ci ke da girmamawa".

Inna ma ta bi sahun Iyah a wurin murna tana sake dauko sabbin addu'a, "Madallah da wannan yaro, Allah ya bashi ilimi mai amfani,ya bashi mace ta gari".

Da ga Iyah har Baffan suka hau rige rigen amsawa da Amin.

Inna ta sake cewa "sunan shi mai da'di amma ka ke ce masa Mutari? Ni kam Muutar zance" Suka sa mata dariya, Sa'adah na cewa ai ko dai Inna gara ma ki ce Mutarin.

A daren ranar ta fito da yar tsohuwar katifar ta, da ta zama tamkar tsumma, ta shimfi'da sabuwa cike da zumudi, a ranta tana ta kwararawa wadda ya siyi katifar fatan alheri.

Shigar ta makarantar sai ya 'kara mata girman buri, saboda yadda ta hadu da 'kawaye fe'kak'ku wadda suka fita rawar kai da waye wa.

Kusan dukkan daliban makarantar ya'yan masu dashi ne, ko kuma na ma'aikatan gwamnatin da suke daraja ilimi.

Arts Class ta zaba a burinta na son zama Barista, ba'a kammala farkon zangon karatu ba (first term) sai da sabo da sha'kuwa ta shiga tsakanin ta da Halima mu'az Matazu, Safina Usman Bunkure, da Humaira Suraj wadda dukkan su iyayen su masu 'kumbar susa ne, itace kadai yar talaka, ko Halima da ba wani kudi ke gare suba, sun wuce matsayin su Sa'adatu, tunda Baban ta ma, aikaci ne a ma'aikatar Revenue yayin da mahaifiyar ta take principal a wata makarantar 'yan mata ta gwamnatin jaha(GGC).

Ita Sa'adatu kawai kwalliya da gayu ne ya janyo mata 'kawaye tunda tana samun abubuwa masu tsada daga yar uwar ta Sumayya.

Tunda suka hada group basu cika mai da hankali kan karatun su ba, illa kwalliya da kuma soyayya tunda kowa ya san FGC KANO co-education ake yi, ma'ana makarantar maza da mata ne a ha'de.

Dukkan su suna da samari a ajin, inka dauke Halima da ta ce ta fi 'karfin soyayya da yara 'kananu, kasancewar tana da saurayi na gaske a gida, wadda ya kasance 'Dan 'kawar maman ta ne.

Khalil Ibrahim na cikin wadda su ke son Sa'adatu Bashir, mahaifinsa ne kwamishinan ilimi na Kano a wanccan lokacin, ita ma kuma ya fi kwanta ma ta a rai, dan haka tana kula shi, dukkan kudaden shi na kashewa a makaranta a kanta ya ke 'karewa.

Wani lokacin ma har fakar idon mahaifiyar shi ya ke ya debo mata kudi kasancewar ta shahararriyar yar kasuwa domin Dubai take fita ta shigo da kayayyakin mata na alfarma, wani lokacin har da Abaya da lace yake daukowa dan ya bawa Sa'a

Suna da 'kokari amma da yake basu mai da hankali kan karatun ba sai suka sha mugun kaye.

Halima da ta kasance ogar su saboda duk tafi su 'kokari ta kuma fi su izza da buri, ita ce kawai ta yi ta shida, amma kowacce a cikinsu ta wuce ta ashirin.

Sa'adatu ita ce kashin baya ta kai ta talatin tunda duk sun fita background din makaranta mai kyau.

Dukkan su jikin su yayi sanyi da ganin sakamakon su, amma Sa'adatu ba ta wani damu ba, tunda dai ta san daga Inna har Baffa sun san tana da 'ko'kari a makarantar da ta baro. zai yi wahalar gaske ma a wani tuhume ta in dai ba Sumayya ce ta zo garin ba.

A cikin wannan yanayin suka kammala SS1, suka shiga aji biyar, budurci sosai, ya bayyana a jikinsu, duk wadda ke FGC KANO ya san da zaman 4stars.

Barin Sa'adatu Gogel, ba wai kyau ta fi su ba, a a kawai ita ma'abociyar kwalliya ce kusan kowanne term sai tasan yadda ta yi, tsakanin 'karya da gaskiya an sabun ta mata uniform, sannan ko mai na ta mai tsada ne tunda ga kan sandal, da school bag, Sumayya ta tsaya ma ta a wannan bangaren, duk kuwa da tana mamakin yadda kowanne hutu sai ta canja komai. Hakan yasa ta saje cikin Ya'yan ma su wadata har ma ta fi su daukar ido, mussaman saboda 'kirar jikin ta.

Zangon karatu na biyu, a aji biyar din su, a ka turo sabbin 'yan hidimar 'kasa (COPPERS)

Cikin su har da Mukhtar Kabir Bichi (MK Bichi).

[5/19, 18:52] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•·•·

Sannan ta yi firgit ta mi'ke, ba tare da ta rufe takardar da ta ke rubuta reply din ba, cike da yanga da iyayyi tace ,"I am Sa'adatu Bashir Gogel" daidai lokacin ya 'karaso jikin desk din na ta,

Yasa hannu ya na nazarin rubutun da ya 'dauke mata hankali, baice uffan ba ya dauki takarda ya zira a aljihun sa.

Wucewa ya yi yana fadin "next"

har aka kammala ya cinye period dinshi ya fice tare da takardar.

Takaici ya kama ta, ta fara tunanin mai ta rubuta ne?

Nagode da kulawa Khalil komai ka ga ni indai ya burgeka, ni ma zai burgeni, Sa'a luvs you.

Abin da ta rubuta kenan, haka kawai ta ji takaicin wannan Malamin da ya kira kanshi Mukhtar ya kama ta, Ina ruwan shi da ita daga zuwan shi?

Washa gari da ya shiga, karatu sosai ya zazzaga musu cikin turancin da ya kama bakin shi tamkar a 'kasar ingila ya girma.

Ya yi tambayar an fahimta ko da akwai mai tambaya?

Serious student din cikin su ne, su ka shiga tambayar abin da basu fahimta ba, shi kuma ya sake bayani a hankali dalla dalla, har kowa ya ce ya fahimta, sai yace zai yi tambaya.

Ba zato yayi pointing Sa'adatu Bashir ta tashi ta yi masa bayanin yadda ta fahimci topic din da ya gama bayanin sa.

Nan da nan taji ta muzan ta, saboda ba wani fahimta ta yi sosai ba, ta mi'ke ta na rarraba ido ta kasa furta kalma ko guda cikin tambayoyin da ya ke mata, da 'kyar tace "ban gane explanation din ba dama"

Ido ya zuba ma ta yace

"We're not talking in Hausa but we're in English"

kunya ta kama ta, wato har ya gane ba ta iya mayar da magana da turanci? ya sake cewa "I ask all of you who didn't understand, but you mutter"!

Ita dai ba baki, sai ido tana jin wata kunya na kama ta. ya dade yana nazarin ta, sannan yace ta zauna ya sake bayani sosai, a lokacin kuma ta mai da hankali ta na sauraro tunda tana jin maganar, wurin mayar wa ne ke mata tasga'do.

Cikin 'kankanin lokaci ya fahimci ita da 'yan group din su, ba abin da suka sa gaba irin kwalliya da soyayya, mussaman idan class ba teacher to hirar kenan.

Transfer ta baza ta ce ta sami malaman makarantar, ciki har da class master din B class, na ss2 ajin su Sa'adatu, nan take kuma akasa Mukhtar Kabir Bichi a mastayin Class master din nasu.

Wannan damar da yasa mu ne ya 'kudure a ran shi sai ya canja wa'dannan daliban, abu na farko da ya yi musu ya rarraba musu gurin zama ya cillasu ta yadda sai dai hange a tsakanin su.

Haka kawai ya ji duk yafi jin haushin Sa'adatu saboda yadda ya lura wadda ta hada kai dasu din sun fita dama, kullum sai ya ga an kawo su a motoci masu kyau, an kuma zo an dauke su, sa'banin ita da ta ke zuwa da kanta cikin adaidaita sahu ko mashin,'kawarta da ya ke ganin suna zuwa tare Zainab Ma'aji sam ba halinsu 'daya ba, ba ta da hayaniya ta na kuma maida hankali wurin karatu duk da ita tana c class, ajin commercial.

Amma yayi nazarin sa ya gane buri da ra'ayin Sa'adatu ya kerewa mu'amala da irin su Zainab.

Saboda haka sai yafi matsa mata, kullum da kalar tambayar da zai mata, wadda kesa ta muzan ta.

Abin da ya lura dashi bawai 'ko'kari ne Sa'adatu ba ta da shi ba, illah mai da hankali ne ba ta yi.

sannan kuma tana da (infiority complex). ma'ana rashin 'kwarin guiwa akan kanka, tunda ya gane tsoron kar a mata dariya yasa ba ta son yin magana da turanci.

Wannan matsin da ya mata sai ya janyo tsanar shi a ranta, ta shiga fargaban zuwan period 'din shi,

a haka har akayi jarrabawar gwaji(Test). ganin a kowanne darasi bata ta'buka ko mai ba sai shiririta, sai ya canja salo ya fara disgata a gaban aji, ta hanyar 'kiran ta da sunaye kala kala, da suke nuni da ba abin da ta sani sai dai ta wanke uniform, ta yi yanga, amma empty brain, har cema ta yake bata dace da wannan makarantar ba.

Sannan kullum cikin bada misali da za'kwa'kuran dalibai masu azama yake, takaicin ta 'daya, yadda kullum misalin sa ba ya wuce da Farida Nasir Torodi , tun fil'azal ita jinin ta bai hadu da Farida ba, duk kuwa da ba ajin su 'daya ba,

Farida a A, science class kenan,

doguwa, siririya sosai, fara 'kal buzaye ne, gashin ta har gadon baya, farkon zuwan ta makaranta har nuna ta ake, na yadda ta ke tuma a cuci a kanta saboda idan ta tufke gashin yake girma, sai a hankali aka gane gashin ta ne.

Mai sanyin hali ce ko kadan ba ta da kwarafniya, bata kuma harkar 'kawaye.

'Kawar ta 'daya wadda kullum zaka gansu tare Ru'kayya mustapha.

Ga ilimi kamar me, dan kuwa tana cikin 'yan gaba gaba na 'dalibai masu haza'ka a duk fadin makarantar.

Sannan iyayen ta ma su wadata ne, domin mahaifin ta ambasadan Niger ne a Nigeria.

Wadannan abubuwan da Farida ta hada sai wasu cikin dalibai su ke mata kallon mai girman kai, da 'daukar ita wata ce yasa take ganin ta wuce kula su, shiyasa suma basa wani harka da ita ba ta da farin jini a tsakanin set dinta. barin ma da 4stars da suke ganin sai dai ta nuna musu kyan fuska amma ba dai na jiki ba😀.

Yawan misalin da yake yi da Farida ya 'kara tsanar ta a zuciyar Sa'adatu.

Cikin abubuwan da ba zata manta suba indan har za ta tuna rayuwar ta a FGC KANO, shine ranar da ya musu dictation wato yana fa'da suna rubutawa, ita kuma slow writer ce, kafin ta kammala rubuta wata kalmar, ya fadi ta gaba, kan dole ta ha'kura da bin, ashe yana lura da ita.

Sai da ya gama ta ji ya kira sunanta"Sa'adatu Bashir where's your note?"

Cikin daburcewa da tsoron yadda zai kunyata ta, murya na rawa ta tattaro kalaman da zai fahimce ta a gajarce ta ce

"My pen stop"

kafin ya yi magana anyi attishawa mai 'karfin gaske wadda ta iya shege ce, ba kowa bane illah Fahad Auwal! wadda shima haushin yadda ta za'bi Khalil ta barshi ne yasa yake jin da'din dizgin da ake mata.

Hannu ya mi'ka yana cewa "let me see"

zuciyarta ta buga amma hakan nan ta mi'ka mishi biron, ya duba ya ga lafiyar biro 'kalau ya watsa mata kallo tare da cewa "out of my class! I am tied of your manners" ta mi'ke sai kuma ta tsaya tace "Am sorry" cikin tsawa yace "don't sorry me, say sorry to ur parents who are keep westing their money".

Jin haka yasa ta fita, hawaye ya cika idonta, a baranda ta tsaya amma sai ya le'ka yace mata "on your kneels" kuka sosai ya kwace mata .

A ranta ta na tambayar kanta me ta mishi ne ya ke wula'kanta ta? mai yasa ya matsa mata? saboda ba ta da 'kokari ne dalilin? ta ke ta ji in dai 'ko'kari zai sa ta tsira da mutunci a idon wannan mutumin da ya yankewa tozarci cibiya to kuwa za ta nemo shi a ko'ina yake.

Sai da ya kammala darasinsa sannan ya fito ya kalleta yace "I want you to borrow your boyfriend's note, and copy what you can't write by urself, if not u will be in.." ya girgiza kan shi ba tare da ya fadi mai zai biyo baya ba .

Ya wuce ta yana sa ke fadin "useless girl, you can go back to ur class".

Tsawon lokaci ta shafe a gun tana kuka tsabar ba'kin ciki zuciyarta Kamar ta fashe, har sai da ta hango Mr uche's wadda ya ke 'daukan su darasin tsumi da tanadi(economics). sannan ta mik'e ta na kar ka'de jikin ta, ta shige ajin ta na ganin wa'danda dama su na jin haushin su, ita da 'yan group din su, su na bin ta da wani irin kallo, mai kama da madallah.

AL'KALAMIN

SURAYYA DAHIRU

✍✍.

[5/20, 16:04] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

•·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•·•·

Kullum tana ri'ke da littafan koyon turanci, ire-iren su Teach ur self.

Ta sake mannewa Safina Bunkure. kasancewar Safeena girman Lagos ce, mafi yawan maganarta turanci ne, dan haka ba ta yarda su yi magana da hausa tare da safina, itama kuma Safina ba ta gajiya da gyara mata a inda ta ji ta yi kuskure.

Ba'a dauki lokaci mai tsayi ba,ta fara rage tsoron kar ta yi turanci a mata dariya, ganin ta na iya mayar da magana cikin harshen da ke mata nauyi, sai kuma ta mai da hankali akan ragowan darussan gaba 'daya.

Ta matu'kar rage shiririta, yanga, da hirar soyayya, da duk wata sharholiyar da su ke, abu 'daya ne ba ta bari ba, kwalliya, wadda wannan kam a jinin ta ne.

Su Halima cewa su ke basu ga Malamin da zai uzzura mu su, babu dalili basu yi maganin sa ba.

Ita ko tsaki take ja a fili, ta yi shiru.

A zuciyarta ko cewa take ai ku ya ga kun iya turanci, kuma yana ganin yadda ake zuwa 'daukan ku a motoci na garari,

ni kuwa ya ga ba ko 'daya, ba dole kowacce shara ya debo ya juye a kaina ba.

Tabbas tana takaicin yadda ita kadai ya ke gallazawa.

Shikuma ganin yadda ta yi laushi ta kuma maida hankali kan karatun ta, sai ya sassauta mata, duk kuwa da zai yi wahalar gaske ya yi darasi bai ce ta tashi tayi bayanin yadda ta fahimci darasin ba, kawai dai kyara da disgin ya rage.

A haka har suka yi jarrabawar mock wadda duk 'dalibi ya ke tsoro da fargaban kar ya fa'di.

Ana yin hutu da kwana biyu mijin Sumayya ya turo takanas a dauki kannen shi 'yan mata guda biyu da yar autar dakin su, da kuma wadda suka hada uba yar amaryar

Baban su, sai ya ro'ki Baffah! akan ya basu Sa'adah ta yi musu hutu tare da 'kannen shi. ba musu ya amince, har gida suka zo suka dauke ta, sannan suka dauki hanyar jos kwata, ta yamma da Bauchi😀.

Wannan hutun yana cikin abubuwan da Sa'a bata Mantawa da shi, domin kuwa ta yi matu'kar jin dadin zama da 'kannen Idris yadda suka kasance yara kamammu, marasa hayaniya amma kuma yan kwalliya ne na sosai, shiyasa abotar su ta yi da'di.

Sumayya kuwa ba ta matsa musu, hatta abinci wadda suke so shi zata ce su yi, mai gidan kuma kusan kullum sai yasa direbansu ya zaga dasu, sunga gari, da wuraren sha'katawa , sannan kuma duk fita sai ya basu kudin kashewa, wadda ba abin da suke siya sai kayan kwalliya ko dai abin da ya shafi sutura.

Ba abin da ya dame su illah tunanin mock exam din da suke fargaban fitowar ta, tunda dukkan su set daya suke Amma makaranta daban daban.

Haka suka 'kare hutunsu cikin jin Dadi da mutunta juna, da kanshi Idris ya kawo su har gida tare da kayan tsarabar ni'ki ni'ki, barin ma dankalin turawa da dangin su cabbage da Kara's, harta atile kamar wadda za'a ci a tsawon wata.

Baffa da Inna sai godiya suke,tare da sake godiya ga Allah, na yadda Sumayya ta sami mijin daya San alheri yake kuma rama alherin da kyautatawa da mutunci.

Barinma idan ta zauna tana bawa Inna labarin daular da Anti Sumayya ke ciki, sai dai ta yi murmushi mai nuna yadda zuciyar ta ke cikin farin ciki.

Ba zata yi magana ba sai dai ta bige da cewa kema Allah ya ba ki mijin rufin asiri, yasa ki dace kamar na yar'uwarki.

Ita kuwa kai tsaye take cewa

"Amma fa Inna gaskiya ni bana son irin tsarinsa, ace mutum duk inda matarka zata fita kace sai ta zumbula hijabi har 'kasa, kuma wai dole sai ansa safa? ko 'dan wanne mazahaba ne?"

Cikin mamaki Innar ta zuba mata ido, tare da tafa hannu tana sallallami tace

"ke kuwa Iyah wannan tsarin da yake yi na martaba shari'a ne bai Miki ba?

Na mijin kwarai shi ke kishin matarsa, ya 'dora ta akan ka'idojin shari'a, wadda zasu gudu tare su kuma tsira tare!

"Daular da ya sanyata a ciki ta burge ki, kina kuma fatan ki samu irinta, amma abin mamaki, hijabin da Ubangiji ne yace a saka shine bai miki ba?

Anya Iyah, Baffan ku bai yi kuskuren barinki shiga wannan makarantar da ta ke sake girmama burinki ba?"

Da sauri tace

"Haba mana Inna! ni fa ba cewa nayi kar asa hijabi ba, gani na yi tana da tsala tsala dogayen riguna tunda ga kan yan 'kasashen Oman, Qatar, Saudi, Dubai, masu tsadar gaske masu kauri, amma wai dan 'kauyanci kuma sai akawo hijabi a maka, bayan su karan kansu hijaban ne".

Ta fa'da tana fashe wa da dariya.

Allah ya shirye ki kawai, Inna ta fada tare da mi'kewa ta yi tsakar gida, tana fadin wannan dogon burin na ki yana ban mamaki Iyah.

Ban da 'karya da fariya, da kai kanka inda Allah bai kai ka ba, gidan uban wa kika san 'kasashen da suke sarrafa riguna masu tsada?

Naga dai ke kam baki da halin samun su, ban da Allah ya miki gata ya baki yar'uwa mai halin girma tana baki kuncen su, wasu ma ko saka su bata yi, ta ke baki, amma har ki zauna ki karkace baki kina min lissafin inda ake sarrafa su?".

Ta cika fam saura 'kiris ta fashe cikin turo baki tace

"Amma Inna abin har da gori?"

Da sauri tace

"Eh dole na goranta miki, dan na ga nema kike ki manta cewa ke'din ba yar kowa bace, face malam Basiru mai 'yar tireda😀wadda ko hanyar inda jirgi ya ke sauka ba ki ta'ba zuwa ba,

Amma kina bada labarin 'kasashen duniya, wallahi Iyah ki canja wadannan halayen da nake ganin kina sake arowa kina yafawa".

Shiru Sa'a tayi amma takaici ke cin ta shikenan sai mutum ba zai fadi ra'ayin sa ba?

Sai a hau mishi gore-gore, har a nemi cewa ya raina shari'a?

Hawaye ya siraron mata, ta goge ta tashi ta yi 'dakinta, tana fatan Allah ya bata miji mai kula da iyali kamar Idris, amma ba mai a'kidunsa na asalin bahaushen arewa ba.

Kayanta na makaranta ta shiga fitowa dasu tunda ga kan uniform, sandal, school bag dukkan su sabbi ne, ta shiga shirya su ta yadda gobe sai dai ta dauka a kammale.

Ba tasan meyasa ta ke 'dokin komawa makarantar ba wannan karon? domin kuwa tunda Mk Bichi yaje makarantar ko hutun weekend ne fargaban zuwan Monday take yi.

Wata'kila kuma dan ta sami sau'kin kunyata ta da yake yi ne.

Amma Kuma duk da sau'kin da ta Sami a bangaren shi, haushin shi da tsanar shi na nan cike a zuciyar ta.

kwanukan abincin su ta wanke su tas kafin ta kammala wanke wanken har gawayin ya fara kamawa, dan haka ta cika tukunya ta dora ruwan wanka, tana gama wanke

kwanukan, sai kuma ta hau share tsakar gidan hadi da wanke dan matsakaicin bandankinsu, kafin wannan lokaci kuma ruwanta yayi zafi, ta juye ta shiga wanka! bayan ta maida ruwan kunu da ta jefa mishi tsamiya kan wutar.

Tana fitowa a wanka innarta ma ta fito tsakar gida, tana ganin yadda Sa'a ta gyare mata gida tsab.

Da'di ya kamata na yadda ko kadan Iyah bata da son jiki.

Ba zato ta ji anrungumeta tare da cewa

"morning Innah"

Ture ta tayi tare da cewa

"oh ni kam Ina kallo a gun ki".

Dariya tayi tare da fadin "Inna gaisuwar kawai shine abin kallon"?

Wuceta ta yi tana bude ruwan dake Kan gawayi, ganin yana shirin tafasa yasa ta fara shirin dama kunun, ita kuma sa'a tayi 'daki tana shiryawa.

Cikin 'kankanin lokaci da dama kunun, ta kuma dauko fulawar data kwaba a 'karshen dare dan yin fanke, ganin ta tashi sosai yasa ta maida mai kan wutar tana shirin suya, tana kwashe kaskon farko Sa'adatu na fitowa ta shirya amma bata sanya uniform ba.

Ganin yadda innarta ke kwaso fanke yayi brown ya tashi sosai, da'di ya kama Sa'adatu.

Sai kawai tafara rawa tana juyi tana wa'kar

"Mamana, mamana! mai sona, mai tattalin zuciyata".

Kwafa Inna ta yi tana fadin "zanga sadda za ki girma Iya"

"Idan Kinga na girma sai kin haifa min 'kani ko 'kanwa".

Ta wuce ta dauko, kofi da plate tana fadin "Allah Inna Ina son 'kanne gashi Anti Sumayya tayi min nisa bare na dinga debo su Khalifa".

Ta fa'da cikin muryar tausayi tamkar hakan zaisa innar ta haihu yanzu yanzu.

Numfasawa Inna ta yi sannan tace

"Ai kin kusa samun 'ya'ya ma indai kina da rabo, ba'di iyanzu ai kina dakin ki ".

Daure fuska tayi, sannan tace

"Nifa sai na fara karatu".

Da sauri Inna tace "Inma karatun za ki zama sai dai a dakin ki, tun yanzu kina ruwan ido kowa ya zo kice ba kya sonsa, amma kuma kina son duk wani abu da zai 'kullo ya baki".

Mi'kewa ta yi bayan ta debi kunu da fanken tana cewa

"To Inna ai ba ro'konsu nake yi ba, Kuma Annabi yace ba kyau mai da hannun kyauta baya"

"Wannan maganar dai kin fi ri'keta a duk maganganun Annabi. saboda ta dace da ra'ayin ki, amma saka hijabi da ke yaci karo da tsarin ki, ai jiyan nan a gabana kika ce 'kauyanci ne"

Kasa magana tayi kawai ta shige 'dakinta, ta fara cin abincin ta, tana ayyanawa a zuciya duk saurayin da yayi gigin yi mata kyauta, ita ko ba zata 'ki amsa ba, tunda dai ba ro'kon su take yi ba.

Tana gama karyawa ta fita da kayan sannan ta sake yin brush wadda sau biyu take yi a kullum safiya tun Inna na mitar barnar makilin har ta gaji, ganin hakan yasa Baffa ya ware mata makilin din ta yana cewa uwar masu gida dole a bata komai, indai ba wadda ya wuce ka'ida bane.

Sai da ta shirya tsaf ta fito tana fadin Inna zan tafi, kallo daya ta mata taga yadda ta yi kyau tamkar ba uniform tasa ba, tasan 'yarta mai kyau ce fiye ma da Sumayya dan dai kawai ita duhun fatar mahaifin su ta kwaso amma Ubangiji ya mata cikkaken diri.

Ta nisa tace

"Iya! wannan turaren na ki bana zuwa makaranta bane,'kamshin sa bana shiga cikin maza bane".

"To Inna" ta fada a gajarce ba dan ta gamsu ba.

" 'Daga can ki dauki kudin makarantar,yau Baffan ku jana'iza ya tafi tun sallar asuba bai dawo ba".

Turus tayi dan kuwa ba yadda za'ayi tasa hannun ta a wurin sana'ar Inna tunda ta riga ta shirya.

Ganin yadda taja ta coke tasan ta'bawa ne baza ta yi ba, kwafa tayi sannan ta mi'ke ta 'daga daron kayan, ta 'kirga kudin ta mi'ka mata, maimakon ta karba sai ta mi'ka mata pos din akan ta sa mata a ciki, hakanan tasa mata tana mata adduar shiriya, tun tana yar 'karamarta, bata son daddawa da kuka, da kubewa bushasshiya, da Inna ke 'kullawa tana siyarwa.

A bakin titi suka hadu da Zainab kamar kullum,suka rankaya suka tafi.

Suna Isa makarantar suka tarar da dodon na ta on duty, yana sizing kayan da makaranta ba ta yarda dasu ba.

Kowa yazo sai ya gaishe shi, hatta Zainab Ma'aji sai da ta risina ta gaida shi cike da girmama wa, amma ita banda kirne fuska ba abin da ta yi. kallo ya bi ta dashi yana raya wadda duk ke mata gugar kaya, ya kamata a bashi sarautar shugaban masu guga.

Ita ko sanin ba wani abu na karya doka a tare da ita yasa bata ji 'dar ba.

Har sun wuce sai yasa baki yace "Gogel"

Zuciyarta ta buga tare suka juyo da Zainab, amma sai yace Zainab ta tafi, itakuma ta dawo, tsaye ta yi mishi 'kerere fuskar nan tamkar gobara, ta gefen idonshi ya ke 'kare mata kallo baisan mai yasa kyaun da ta yi cikin sabon uniform 'dinta ya mintsine shi ba.

Sassanyan 'kamshin da ke tashi a jikin ta ya matu'kar ta'ba shi, ta na zuwa gaba daya gun ya cika da 'kamshi. ita kanta bata san tsadadden turare bane dan kuwa na Sumayya ne ta dauko mata.

Ba tare da ya kalle ta ba yace

"On ur kneels"

Nan da nan hawaye ya cika idon ta wanne irin mugun mutum ne wannan? mai ta mishi zai wula'kantata daga dawowa? haka ta zube cikin 'kasa da ciyayi bai sallame ta ba, sai da ya tabbatar ta shiga sahun 'yan late comer's(makararru).

bayan ya mata bulala biyar a hannu masu zafin gaske, yana ce mata

" for ur indispline manners, u are not here only to learn, but da tarbiya in ganeral".

Haka nan dai aka sake mata punishment (horo)na latti. a wannan rana haka ta yini da ba'kinciki, murna da ake na shigar su aji shidda ita kuka ne ya maye gurbin, hankalin Khalil dana 'kawayen ta ya yi matu'kar tashi sai lallashinta suke.

dukkan su tsanar Mk ta cika 'kalbin su mussaman ma Khalil da ya ke jin tamkar ya yi hayar yara a bishi unguwar su a mishi dukan kawo wu'ka.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍

`Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍

[5/22, 12:02] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*!□

.•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•.•

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

25_26.

Kwanci tashi har jarrabawar mock ta fito cikin ikon Allah Sa'adatu ba ta sami matsalar komai ba tasan kuma MK ya taka muhimmiyar rawa ga samun nasararta, tunda a sanadin matsin da yake mata yasa ta zama cikin jerin daliban da suke nacin karatu.

A wannan term din kuma ta tsinci kanta da jin haushi idan ta gan shi da Farida, gashi dai ta tsane shi, amma ko yaya ta gan shi da ita, musamman da ya kasance Farida Prepect ce, kuma mafi yawa idan shi ne Duty Master, to kuwa za ta kasance Duty Prefect, sai ta ji ranta ya mugun 'baci.

A yanzu tafi jin takaicin 'kokarin da Farida take da shi fiye da komai cikin FGC.

Kasancewar Farida na cikin daliban da suke wakiltar makarantar gaba'daya, dan yanzu ma shirin tafiya Lagos gasar Cowbell Competition suke yi, tunda sun cinye na jahar Kano, yanzu matakin 'kasa zasu tafi, kuma Uncle MK din na cikin tawagar Malaman da za suyi masu rakiya zuwa birnin na Ikko.

Wannan dalilin sai ta sake zama so mute, ita kadai ta san mai ta ke going through a zuciyarta.

Kullum idan ta zauna ta dinga bincikar kanta, me yasa ilimin Monica Paul bai dame ta ba?me yasa Khalil Ibrahim da yake da 'kokarin shima bai dameta ba, tunda har da shi za'ayi ma tafiyar?

Kanta har zafi yake dauka akan wannan tunanin.

Kyashi take mata ko kuwa hassada ne?.

Kullum kuma indai ta ga Farida, a ranta sai tace, oh ance mutum tara yake bai cika goma ba, komi da ake so Farida ta hadasu, doguwar mace, Fara tas, mai dogon gashi, mai ha'kuri, mai tarin ilimi gashi ta yi sa'ar fitowa a gidan wadata, kawai dai ba ta da dirin jiki, sai tsananin kyaun fuska.

siririyace ta sosai, shiyasa komi na jikinta 'karami ne.

Sannan kuma ta lura bata da cikakkiyar lafiya wadda takan shafe sati idan ciwon ya tashi ba tazo ba. wannan ciwon da rashin cika irin ta cikkakun mata, shine tawayar da tasa bata cike goma cif cif ba.

Tauraron Farida ya sake haskawa ne bayan sun yi nasarar zuwa na 'daya a gasar da suka yi, wadda itace tafi bada amsa a tsakanin Monica da Khalil.

Kowa nan nan yake da ita tunda ga kan principal da sauran teachers, dama student gaba daya.

Wannan ya sake sa tsanar ta a zuciyar 4stars da suke jin su din isassu ne.

A kuma wannan term din Sa'a ta dage, ta 'kure malejin jarumta, ta dau ki 8th position, wadda shine sakamakon farko mafi kyau a tarihin rayuwarta, dan ko a makarantar da ta baro, double lamba take dauka, bare wannan makarantar da ta ha'da za'kwa'kuran 'dalibai.

Wannan sakamakon shine mafarin dai na 'yar tsamar su da Uncle Mukhtar, duk 'karshen zangon karatu ya wajabta wa kanshi bawa daliban ajin nasa daga na daya

zuwa na uku kyautar 'karfafa guiwa, a matsayin sa na class master dinsu, a A class ya bawa Farida.

A wannan karon har Sa'adatu ya bawa kyautar the most hardworking student in the class, Kamar kullum Khalil Ibrahim ke daukan 1st position, shi ya 'Kira a 'karshe bayan ya bawa Sa'a. da monicca as 2nd, da wani Abdulrashid da ya zo na uku.amma da yaje karba sai yasa left hand ya Kuma juya fuskar shi, wannan rashin 'da'a da ya nuna ya hassala Mk ya fasa bashi kyautar ya kuma hukunta shi ta hanyar sa shi, sharar school area.

Tunda ga nan aka fara cece kucen son Gogel yake banda haka, ta yaya ga Halima ta zo ta hudu bai bata ba, ga na biyar, duk ya tsallake ya tafi Kan 8? asalima sai da wannan kyautar ya kawo mata matsala tsakanin ta da Khalil da kuma Halima.

Na Halima kyashi ne, shikuma Khalil kishi ne, gani ya ke kawai soyayya suke yi amma ai kowa yasan yadda ya takura mata, menene dalilin gift din? alhalin akwai wadda suka fita cancanta amma bai basu ba.

Kusan wannan ta'kardamar ne dalilin afkuwar soyayyar ta su dan ta dade tana jin kishinsa akan Farida bata gane kishi bane sai a wannan lokacin daya sake da ita, ya gamsu tana karatu kamar yadda ya kamata.

Ranar juma'ar da akayi hutu, tana cikin ranakun da bata Mantawa cikin rayuwar ta a makaranta, a ranar ne ta nutsu ta 'kare mishi kallo na tsanaki, a lokacin da ya shigo dan ya musu bankwana sai kuma bayan hutu.

Dogon saurayi mai matsakaicin jiki, ma'ana siriri ne, amma kuma bashi da rama ko kadan kai tsaye za'ace mishi fari, duk da idan irin su Farida na gun, duhunsa za'a gani, doguwar fuska mai dauke da dogon hanci, da madaidaitan idanuwa, farare tas, da zagayayyen 'karamin baki mai dauke da 'kananun ha'kora jerraru, ya kuma zagaye bakin da gemu. yanayin sa tamkar 'kani ne ga tauraron wasan kwaikwaiyon nan Yakubu muhd saboda yadda suke yanayi.

sanye yake cikin shadda fara 'kal, ma'abocin tara suma, mai kuma yawan gyarata dan kullum comb din shi na aljihunsa, hular yan bautar 'kasa ya saka, kafar sa dauke da open takalmi ba'ki, hannunsa daure da agogon silver samfurin (D&G). tun

kuma a lokacin yake amfani da turaren Versace,'kamshin sa na cikin abubuwan da dalibai ke magana akai.

A wannan kallon da ta mishi na 'kurillah ta janyo wa kanta, domin bata dauke idon ta akan shi ba, sai da son shi ya cika zuciyar ta dam, irin son nan da yake shiga ba tare da an ankaraba, lokacin da za'a ankare din ya riga da yayi illar da ba yadda za'ayi dashi.

Da kanta ta dinga cewa Madallah da 'ka'idojin musulunci, sai da akace kallon shari'a 'daya ne tak, amma ni na mishi kallon 'kwal uwar 'daka.

Nasiha ya musu, akan ko a gida su dinga bitar karatunsu, su kuma zama yara masu tarbiya, ta yadda duk inda aka ga 'dalibin FGC KANO aga ya banbanta da na kowacce makaranta soboda ladabi.

'karshe ya kulle bayanin shi da lallai su kyautata wa iyayen su, su musu biyayya, su kuma taimake su akan sha'anin ayyukan gida.

Ya kalli side din maza yace

"wadda kuke tu'ki, ku bi a hankali kusa nutsuwa".

Banda kallon shi ba abin da Sa'a keyi tana jin turancin sa tamkar Baturen da yanke wa yaren cibiya.

Yana kammala wa yayi waving hannun shi alamar bye, ya fice da sauri.

Basu bar class din ba sai da Safina ta yi sulhu a tsakanin Halima matazu da Sa'adatu Gogel, dan haka rabuwa suka yi ta salin alin a tsakanin su tare da al'kawarin zasu hadu a gidan su Humaira asabar din sama, bata gobe ba.

Tafe suke ita da Zainab da Asiya wadda yayar Zainab din ce.

kamar ance ta juya ta hango Uncle Mk da Farida a tsaye jikin wata bishiya da dukkan alamu ba a zo 'daukar ta ba, hira suke hankali kwance.

Take ta ji tamkar ta mutu, zuciyarta ta daure,'kirjin ta yayi nauyi ainun, tafiya kawai take amma bata sanin inda take jefa 'kafarta.

Suna tsaye a bakin gate din makarantar suna jiran abin hawa ta ga yazo ya wuce su akan mashin 'dinsa da a wancan lokacin ake mishi la'kabi da tsuntsun soyayya.

Hannu ya daga musu amma sai ta juyar da fuskar ta, tayi kamar bata ganshi ba, Zainab ce kawai tayi waving 'din shi.

Tana isa gida 'dakin ta, ta wuce ta fa'da kan katifarta wani kuka ya kwace mata, tayi abinta ta 'koshi kasan cewar Innar ta na wanka, daga kukan barci yayi gaba da ita, sanin da mahaifiyar ta yi na fashin salla take yasa bata tashe ta ba.

Haka ta yi hutun nan su ku ku, ciwon so na wahalar da ita, a tunaninta tasan so akan khalil, Ashe ba son sa take ba, kawai shakuwa ne da kuma yadda yake mata hidima, a yanzu ne take dandana azabar soyayya, yanzu ne take jin so tun daga zuciyarta, idanuwanta, da gangar jikinta gaba'daya.

Idan ta tuna Farida yake so, sai taji tamkar za ta sume.

A yadda ta ji ciwon ganinsa da Farida a tsaye yana mata magana cikin walwala komi yana iya faruwa da ita idan ya kasance kullum zata na ganinsa tare da ita.

Zaune ta ke tana fargaban komawar ta makaranta wani satin, a da ta dauka zullimin zuwa makaranta ya 'kare tunda yanzu ta tsira daga tozarcin Uncle Mk! ashe tsugunne bata 'kare mata ba?.

Agogon bango ta kalla taga 2:30pm da sauri ta 'mike ta shiga wanka ta fito ta shirya cikin lallausar atamfar quali-wax mai kalar samaniya(Skye blue)da ratsin ja, Riga da skirt ne, dinkin yayi matuqar zama a jikinta,'katon jan 'dan kunne mai round tasa, a lokacin yayin kwalliya irin ta wannan zamanin ba tazo ba, amma duk da hakan ta she'kawa fuskar ta kwallliyar da ta dace da ita.

Mayafi jah ta ya fa, sumfurin(internet). ta sanya takalmi half-cover amma hills. da yar mitsitsiyar jakarsa wadda zuwanta jos ta siyo su masu Jan duhu. ta fesa turare ta fita zuwa 'dakin Inna.

Inna na shirya, mi'ke wa tayi daga kishingidar da ta yi, hannun ta ri'ke da carbi tunda ta idar da sallar azahar bata tashi ba.

"Yanzu Iyah ba za ki daina zabga turaren nan idan zaki fita ba?

Ba kyau fa, ki kiyayi taba shari'a wallahi"

A hankali tace

"Allah Inna 'dan ka'dan ne, kawai 'kamshi ne dashi".

"To tunda kin san yadda yake dole ne, idan zaki fita sai kin saka?

Ki fa dinga jin tsoron ubangijin ki, kina kiyaaye ka'idojin shari'a".

Kafin tayi magana, ta sake cewa

"A gabana kika ce da Baffan ku, bayan la'asar za ku dawo, ki sani idan kika wuce wannan lokacin ba zan 'ki fada mishi ba"

"In sha Allah bazan kai maghrib ba Innah"

"Sannan kuma kiji tsoron Allah idan mu bama kallon ki, shi yana kallon ki.

inda kika tambaya nan kawai aka lamince miki zuwa.

Sai kin martaba kanki, kafin wani ya martaba ki, sannan kuma

duk saurayin da ya tsayar da ke kice mishi yazo gidan ku, ya nemi izinin magana dake a wurin mahaifin ki."

A sanyaya ta amsa da

"Zan kiyaye Inna"

Sannan ta juya ta tafi, tana rayawa ko sai yaushe Inna za ta dena mata bitar wannan nasihar a duk sadda zata fita?

Jikin ta yayi sanyi, nasihar ta matu'kar ratsata.

take ta ji ta fasa zuwa inda ta yi niyya, tunda gidan su Halima zata je su hadu da Khalil dake duk kusan unguwar su daya.

Tunda akayi hutu basu hadu ba, a dalilin fushin da yake yi da ita, yana zargin soyayya suke ita da Uncle Mukhtar.

Baisan gidan su ba, kullum cewa take ba a barinta yin zance, sannan indai aka ganshi yaje gun ta za ta Sami matsala babba, nan kuwa gani ta ke da kunya yazo ya ga gidansu.

Nasihar Inna tasa ta canja shawara gara kawai yau ta kaiwa Zainab Ma'aji ziyara ta huta da gorin da ta ke mata na ba ta zuwa gidansu, tunda dama nan ta cewa iyayen ta za ta.

Tana fita yar tafiya tayi 'kadan, tana jiran ta tsallaka, kamar ance 'daga kanki kawai sai idanuwan ta ya fada cikin na shi yana fitowa daga wani shagon aski da ke gaban gidansu kadan.

Mamaki ne ya kamashi ya tsallako ya same ta, tuna nasihar da ya musu na nuna ladabi yasa ta risina tare da fadin

"Barka da rana"

Maimakon ya amsa da hausa sai ya juya harshe, yace

"Sa'adah how are you"? how ur parents and everything?"

A hankali tace"very fine"

Ya sake fadin "are you living here?"

Kai kawai ta 'daga tare da nuna mishi gidansu "this is our house"

bata san mai yasa shi bata ji, kunyar nuna masa gidan nasu ba, kamar yadda ta ke jin kunyar su Halima da Khalil su ga gidan. duk kuwa da bashi da makusa tunda ginin bulon siminti ne, a shafe yake da filasta, 'kyauren 'kofar shiga lafiyeyye ne mai aminci, sabanin gidajen su 'kawayen nata manyan gates ne dasu, masu zubin mahadi ka ture mussaman gidan su Safina da Humaira Suraj, nasu Halima ne dai ba wani shararren gida bane amma darajar unguwar ma kadai ta kerewa tasu unguwar.

Yayi murmushi tare da fadin "wonderful I know ur father since"

Da mamaki ta kalle shi tace 'Realy"?

"Sosai kuwa for over 5 years, is he around?"

"No yaje Gogel 'dazu"

"Said it in English"

Ta tura baki alamun ya fara son 'kureta wadda shikuma hakan da tayi drives him crazy.

Tace, "He went to our Home town" ta tsuke bakinta ta yi shiru in ma bata yi dai dai ba 'karshen dagewar ta kenan.

Murmushi yayi ya sake cewa "oh rude Sa'adah!"

Har cikin ranta take jin dadin yadda ya yanke sunan yake fadin Sa'adah!

Bashine farkon fa'da mata hakan ba, amma shine farkon wadda ya iya fadin sunan, shinea farkon wadda yasa mata son sunan.

Ba zato ta ji yace "where's is ur loverboy"?

Kunyar duniya ta kamata ta yi 'kasa da kai tana jin kamar 'kasa ta tsage ta shige,

Ganin yadda ya kunyata ta, yasa shi tambayar inda zata,

Kai tsaye tace

"Gidan su Zainab Ma'aji".

Sai ya mata sallama, ya tsallaka ya hau mashin dinsa.

ganin haka yasa ta wuce ta nufi gidan su Zainab.

Cike da shauki ta isa gidan su Zainab din, a dakin dake mallakin tane da yayarta Asiya suka zauna, suna hira, tare da Anty Asiya gaba'daya, cike da farinciki take basu labarin haduwarsu da Uncle Mk yanzun nan.

Asiya ta ri'ke baki tana kallon yadda Sa'adatu ke bada labarin shi cike da 'doki da farin ciki, kasa 'boye mamakinta ta tayi, tace

"Sa'adatu da wuri haka?"

Cike da rashin fahimta tace

Kamar "Yaya da wuri haka, ban fahimce ki ba?"

Cike da iya shege Asiya tace "Ato na ga a duniya kin washi ayi maganar bawan Allah nan, abin mamakin kuma sai gashi yau da kanki kina hirar shi cike da shauki da jin dadi, shine nace da wuri haka har 'kiyayyar ta 'kare?"

Kunya ta kamata sai cewa tayi "Ni fa ba gun ki nazo ba, kuma bada ke nake zance na ba".

Dariya suka sa mata daga Zainab har yayar tata, take kuwa takaicin su ya kamata sai kawai ta fashe musu da kuka.

Nan da nan kuma jikin su yayi sanyi, suka gintse dariyar, suka hau bata ha'kuri, barin ma Asiya da ta ke ta fadin "daga wasa, nifa tsokanar ki nake, to yi ha'kuri ba zan sake ba"

da ga haka ta mi'ke ta bar musu dakin cike da mamakin shagwaba irin ta Sa'adah.

Da 'kyar Zainab ta shawo kanta ta huce, ta shiga bata labarin tunda akayi hutu basu hadu da Khalil ba, saboda yana fushi da ita akan Mk.

Tabe baki Zainab ta yi tana fadin jimin yaro da 'karfin hali, to shi da nufin sa baza ki kula wani ba? bama shi da hankali.

Sanin da Sa'a ta yi Zainab ba ta yin Khalil, ya sata tsuke bakin ta, har sai da ta gama caccakar shi ta 'kosa dan kanta, ta bar maganar.

Wai a Ina kika ga Uncle Mk din? Zainab ta tambaya cike da son jin 'karshen maganar da Asiya ta so watsawa.

Bata rai ta yi tace inace dariya ku ke min?"

"Ni ba ke na yiwa dariya ba, Yaya Asiya ce ta bani dariya da ta shiga zancen da ba na ta ba".

Numfasawa ta yi tace

"A 'kofar gidan mu ya fito a wannan shagon na The Boss barbing shop".

Amma dai kin gaishe shi, Zainab ta tambaya da sauri.

"Ah sosai ma har hira mun yi"

Murmushi Zainab tayi tare da fadin

"In sha Allah wannan ne mafarin hirar taku, ba 'karshe ba"

Da sauri Sa'adah ta dube ta, tace

"saboda me kika ce haka?"

Kai tsaye ta bata amsa da cewa "saboda kuna son junan ku"

Sunkuyar da kai Sa'adah ta yi tana mamakin yadda ta hasko tana son Mk, sanin Zainab akwai ta da sa ido sai ba tayi mamakin gano ta da ta yi ba.

Kamar zata yi shiru sai ta kasa tace

"Zainab shi ba ya sona, Farida ya ke so", ta fada cikin muryar kuka.

Hannunta Zainab ta ru'ko cikin lallashi tace

"Wallahi yana son ki, ke duk wannan takurar daya miki a banza ce? kin ta'ba tunanin mai yasa ke kadai ya damu ki maida hankali a kan karatun ki?

Ni na dade da gane yana sonki amma irin mutanan ne masu kiyaye doka da oda. kinga ai bai dace ya nuna miki soyayya alhalin aikata hakan laifi ne babba da hukumar makaranta ba za ta amince da shi ba,

Sannan Farida 'daliba ce mai haza'ka irin su farin jini ne da su a gun dukkan malami ba wai Uncle Mk ba kawai. gaskiya ba sonta ya ke, so irin na soyayyar saurayi da budurwa ba, illa 'kaunar da malami yake yiwa dalibarsa mai ladabi da haza'ka".

Cike da gamsuwa Sa'adah ta sake cewa

"Ba kya ganin 'kaunar da ya ke mata zai iya juyewa zuwa irin son dana ke jin tsoro?"

Shiru ta yi na 'dan lokaci,sannan ta nisa tace

"Sa'adah gaskiya zai iya juyewa amma idan kin cigaba da bada 'kofar faruwar hakan".

Alkalamin Surayya Dee

✍✍

[5/22, 12:02] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

.•.•.•.•.•.•.•.•.•.••.•.•.•.•.•.•.••.•.•.•.•.•.•.•.•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•.•.•.•.•.•.•.•.•.••.•.•.•.•.•.•.••.•.•.•.•.•.•.•.•

SADAUKARWA GA *SADIK ABUBAKAR*.

Gaisuwar fatan alheri ga Zauren Fadila lamido!

BA LABARI FANS 2

MK DA SA'ADAH NA GAISUWA.

27_28.

Cike da fargaba ta zuba wa Zainab ido, zuciyarta na bugawa ta ce, "Ban gane ba?"

Muskutawa Zainab din ta yi sannan ta ce "Ina nufin ki toshe dukkan 'kofofin da kika bude na rashin 'da'a a gabanshi, kinga

yanzu ya gamsu kin canja, kin shiga sahun 'dalibai masu dagewa, to ki tattaro dukkan ladabi da nutsuwa ki sanya su a fuskarki da dukkan ayyukanki, ba iya haka ba har a zuciya, ina tabbatar miki idan kika yi haka kin rufe 'kofar da zai dinga miki ganin mai 'karancin tarbiya. Sannan ki yi addu'a, ki bar wa Allah za'bi, idan alheri ne kuma an 'kaddara mijin ki ne, kina zaune Allah zai turo miki shi".

Shiru ta yi tana nazarin maganganun Zainab, wanda ta tabbatar iyakar gaskiya ta fa'da mata.

Ta nisa sannan ta 'dago ta ri'ke hannun Zainab ta ce

Na fahimce ki, na kuma gode da shawarar ki, amma don Allah ki ri'ke mini sirrina."

Murmushi Zainab ta yi tare da cewa, "Ki sa a ranki amana mu

ka yi wannan maganganun, kuma mutum amintacce ne mai 'rike amana. Ina tabbatar miki da ikon Allah baki da matsala da ni"

Haka suka ci gaba da hirarsu, bayan sun yi sallar La'asar ba da jimawa ba, ta musu sallama ta tafi, Zainab ta raka ta har kusan gidansu.

Tunda suka koma makaranta gaba'daya ta mayar da hankali kan karatu, sannan ta bi shawarar Zainab, don haka gaisuwar girmamawa tare da mutuntawa take wa

Uncle MK, har ya ji cewa lallai wannan ita ce Sa'adah 'diyar Malam Basiru, waccan da ta gabata ta aro ce. don haka ya daina duk wani gallazawa da yake mata, sai ma wani shiri da yake da ita.

Wanda hakan ya janyo hankalin 'dalibai aka fara gaskata ra'de radin da ake yi cewar son ta yake yi. Wani abin mamakin kuma ita ma Farida sai ta fara jin haushin Sa'adah, tana ganin ta tamkar wata 'yar fashi a soyayya ko mai barazana a rayuwarta. ta san duk yadda take da 'kyaun da ya kai ya kawo, ba ta yaudari kanta ba, ta tabbatar ba za ta nuna wa Sa'adah komai ba, sai fari da gashi da kuma tsayi. Amma batun cikar halitta da kuma boyeyyen kyau da sai an nutsu ake gane shi ta sani Sa'a ta kere mata.

Wata rana sun hadu a Biology Lab, kawai Sa'adah sai ji ta yi Farida ta ce "Iyah Basiru" Ranta ya yi mugun 'baci, tunda da izgilanci ta fada mata, take ko ta 'daga murya ta fara mata sababi, saboda Sa'adah mafadaciya ce ta gaske, sai dai kuma ita wacce ta yi tsokanar ta si'dade ta barta a gun. Wanda hakan da ta yi har ya fi wa Sa'a ciwo fiye da tsokanar da ta mata.

Shike nan sai Farida ta mayar da tsokanar ta zame mata 'ka'ida sai dai idan ba su hadu guri 'daya ba, ranar kuma a shop suka hadu ta faki ido ta galla mata harara tace, "Sa'ade gwalli"

Abinka da wanda aka dade ana tsokana kuma mai 'karancin ha'kuri sai kawai ta zabura ta kai mata wawura, ta sha'ke ta da 'karfin gaske, nan da nan hankalin mutanan gun ya kai kansu, aka taru aka karbe Farida a hannunta, tana mayar da numfashin wahala dan ba 'karamin sha'ka ta sha ba, musamman da ke ba ta da da kuzari saboda rashin cikakkiyar lafiya.

Aunty Ngozi malamar (Mathematics) ce ta zo wucewa ta tsaya tana tambayar ba'asi, bayani aka mata wanda kusan duk gurin shaida aka wa Farida cewa tana tsaye kawai aka ga Sa'adatu ta kama ta da kokawa.

Saboda haka sai ta tattara su ta tafi da su Staffroom wanda a can aka yi shari'a. Kusan dukkan staff din bayan Farida suka bi, saboda rashin hayaniyarta, ga ta kuma hazi'ka ce, haka aka yi punished din Sa'adah ta hanyar sa ta shara da kuma gargadi mai tsanani, akan komai za a mata ba ta da ikon daukar doka a hannunta.

Hatta Uncle MK, Sa'adah ya jawa kunne akan zai yi wahalar gaske Farida ta tsokane ta wanda hakan da yayi yasa ta jin wani takaici ya kama ta fiye da yadda aka ba ta horo bayan kuma ita ce da gaskiya. Wannan abin ya yi matu'kar tsaya wa Sa'adah a ranta, shi yasa ta ji gaba'daya makarantar ta fita akanta musamman ko yaya idan ta ga gilmawarshi da Farida sai ta ji dukkan walwalarta ta kau, duk da dai ba ta da tabbacin abin da take zargi a tsakanin su.

Tunda ga nan kuma Farida ba ta sake marmarin tsokanar Gogel ba dan kuwa ta ji 'kamshin mutuwa a hannunta.

Ana cikin haka aka fara register din JAMB, tana fada wa Baffan su maganar kai tsaye ya ce mata ba wata jarrabawar shiga Jami'ar da za ta yi don kuwa aure zai mata idan mijin ya yarda sai ya siya mata ta yi a 'dakinta.

Wannan ma na cikin damuwar da ta sake sa mata tsanar FGC KANO. Dukkan 'yan ajinsu za su yi wannan jarrabawar sai ita kadai ce a ajin za a ce ba za ta yi ba. Wanne irin koma baya ne wannan? Wannan ba da kai har ina? Kamarta ace ita ce koma baya a komai? Sa'adah ke nan!

Wadannan damuwowin sai suka sa ta ji gara ta koma asalin makarantar da ta bari a baya ta zana jarrabawar kammala sakandire, nan ma da ta gabatar da maganar gaban Baffa tare da ba shi uzirin ai ba sosai ake cin jarrabawa a wannan makarantar ba, kai tsaye ya ce mata bazai yiwu ba, tunda anriga an biya mata kudin jarrabawar ba, ba za a yi asarar su ba, wannan shi ne karon farko da Baffan bai goya mata baya akan wani abu ba.

Ganin ba ta sami goyon baya ba, ga kuma ba'kin cikin da za ta kwasa a FGC KANO, sai kawai ta daina zuwa makarantar gaba'daya, wanda hakan bai damu Baffanta ba, sai cewa ya yi to ta fito da miji, ai Sumayya ma ba ta sami hakan ba ya aurar da ita ga shi nan kuma tana zaune lafiya cikin rufin asiri mai yawa, fiye ma da wanda suka yi karatun.

Inna kuwa uffan ba tace mata ba saboda yadda take ganin take-taken Sa'adah nan gaba fin 'karfinsu za ta yi, garama a aurar da ita ya fi mata kwanciyar hankali.

Tsawon sati tana gida ba ta je makarantar ba, rannan da yamma tana kwance a dakinta, tunda yanzu Inna fushi take da ita sosai, don haka ba ta jin da'din zaman gidan gaba'daya, ta ji murya Baffa na fadin"Iyah"

Da sauri ta amsa ta fita tsakar gida inda yake tsaye, ta tsugunna tare da cewa "Gani Baffa"

Ya kalle tay ya ga duk ta lalace tsabar fitinar da ta sawa ranta.

ya ce, "Da ma yaron nan Mutari ashe a makarantarku ya ke koyarwa?"

Shiru ta yi tana nazarin sunan, kafin ta ce, "Wani abu ya sake cewa?"

"Dazu ya same ni a inda nake zama shima nan ne wajen zamansa ya tambaya an tabbatar masa nan ne gidan ku, ya yi mamakin yadda, bai gane ke yarinyar wajena ba ce sai a kwanakin nan, kuma ya ga ba kya zuwa makaranta shine ya tambaya lafiya kuwa?"

Ya nisa sannan ya ci gaba da fadin, "Na fada masa kawai makarantar ne ba kya so, ni kuma ban takura miki sai kin ci gaba da zuwa akan dole ba, amma ba zan zauna na zuba miki ido ba, aure zan miki!

Ya ro'ke ni alfarmar yana son ya zo ya ganki ya ji dalilinki na gudun makarantar alhalin aski ya zo gaban goshi, na amince masa ya zo ba dan komai ba, sai don mutuntani da yake yi, katifar ma da kike kwana a kai shi ya kawo miki ita, don haka idan an yi sallama da ke bayan La'asar na miki izinin ku tsaya a zaure"

Kai ta 'daga tare da cewa

"To"

ya juya ya fice ita kuma ta koma daki tana jin faduwar gaba.

'Karfe hudu da rabi 4:30pm yaro ya shigo ya ce, "Wai ana sallama da Sa'adatu" Daidai lokacin ta fito a ban'daki dan haka ta ce, "Je kace tana zuwa".

A gurguje ta shirya cikin tsadaddiyar doguwar riga Coffee Colour ta yi roling da mayafin rigar, ta fesa turare bayan ta shafa powder da wet lips, ba ta cikin walwala don haka ba ta sami sukunin yin kwalliya sosai ba, duk da hakan rigar ta karbe ta, ta yi mata kyau.

Dakin Inna ta le'ka ta ce mata, za ta fita." Kai ta 'daga mata ita kuma ta dauki 'yar 'karamar tabarmar da take jingine a dakin ta fita.

A jingine ta same shi, ya yi shigar 'kananun kaya, wandon jeans ne mai kalar ba'ki, sai T-shirt fara 'kal an rubuta *PYRAMID* da manyan ba'ki a gaban rigar, zanen dutsen pyramid 'din kuma ta bayan rigar, 'kafarsa dauke da boot farare sai zabga 'kamshinsa na dindin yake yi, sumarshi tasha gyara sai she'ki take yi, yau har farin glass ya saka wanda ba kasafai yake amfani da shi ba, ba ta yi mamakin shi ne Mutarin da Baffa yake bayanin sa ba, saboda ai ya taba ce mata yasan Baffan shi ma.

Ba 'karamin kyau ya mata ba, amma da yake haushin sa take ji sai bai wani burge ta ba, sai da ta shimfida tabarma ta ce "Bismillah!" Ta juya ta dauko ruwa, a zaune ta same shi a farkon tabarma ita kuma ta sai ta zauna a 'karshen tabarmar.

Da 'kyar ta bude baki ta gaishe shi, ya amsa yana nazarin yadda ta zabge lokaci guda.

Kai tsaye ya ce, "Mai ya hana ki zuwa makaranta tsawon sati guda?"

Shiru ta yi amma a zuciyarta fadi take na bar muku makarantar sai ku tabbata kai da Farida da sauran staff masu shaidar zur, har Mahdi ya bayyana.

Sau biyu yana tambayar ta, ba ta 'dago kanta ba, bare ta amsa mishi. A karo na uku ya yi magana a kausashe tare da cewa "I will not repeat myself!"

Cikin turo baki ta ce "Ni ban son makarantar ne na gaji"

Mamaki ya kama shi wacce irin yarinya ce wannan? Ka zo shekarar 'karshe a karatunka kuma rana daya ka ce wai ka gaji?

Ya zuba mata ido yana nazarinta matsakaicin tsayi gare ta, ba'ka ce amma ba sosai ba, irin su ake cewa wankan tarwa'da, zagayayyiyar fuska ce da ita, mai dauke da manyan idanuwa dara-dara, gashin girar ta a cike, sannan hancinta ya dace da fuskar sai dan 'karamin baki irin na Baby Girl, mai dauke da wushiryar da take 'kawata murmushinta, ga ta kuma da dimples a dukkan kumatunta ko motsa bakin ta yi sai sun lotsa, ba siririya ce ba amma kuma bata da jiki na sosai, sai dai a cike take, 'kasanta ne mai fadi, amma ta sama a tsuke take musamman da ta yi sa'a ba ta da tumbi sai hakan ya taimaka wurin fito da cikakkiyar sura mai birgewa. Shi yasa uniform ke mata kyau tunda sai sun mishi shape sannan kuma hijabin su 'dan mitsil ne.

Ya nisa yana kokawa da zuciyarshi, ya ce, "Ban gane kin gaji ba"?

Shiru ta yi ba ta ce 'kala ba.

Ganin yadda ta rame ya san dole akwai wani abu daya sata wannan borin sai ya tausasa murya ya ce,

"Sa'adah what's your problem, mai yasa haka? Ba za ki ji tausayin iyayenki ba, duk wahalar da suka yi sai da abu ya zo gaf, kice ke ba za ki yi ba, ko auran kike so wata nawa ya rage ki kammala sai a miki"

Wani malolon ba'kin ciki ya tokare mata wuya, tasan Baffa ne ya ce mishi haka, ta kasa magana amma ranta in ya kai dubu to ya baci.

Sai shi ne ya gaji da shirun ya ce, "Tunda gajiya ce kawai dalilinki ai yanzu kin huta tunda kin fi sati kina hutawa, kuma gobe Monday lallai ki shirya ki zo makaranta.

Kai tsaye ta ce, "Idan har FGC ne sai dai a kai gawata!"

Ta fada kuka na kwace mata, ta sunkuyar da kai tana danne kukan.

Shiru ya yi tare da tunanin dalilin 'kin makarantar haka farat 'daya, murya ba amo ya ce "Listen, idan aka canja miki wata makarantar za ki je"?

Kai ta 'daga mishi.

Ya ce "it's ok but let's talk the reality. Fada mini dalilinki na son barin makarantar ni kuma idan na ji kina da hujja da kaina zan nemo miki wata makarantar na kawo wa Baffa"

Ta yi shiru sai shesshe'kar kuka take yi, jikinsa ya yi sanyi zuciyarsa sai kisima mishi abubuwa take yi.

Ya dade yana lallashinta da kalmomi masu dad'i har ya samu ta bude baki ta ce, "Akan me zata dinga tsokana ta sannan duk a hadu a ba ni rashin gaskiya? Saboda ita Babanta mai kudi ne, ni kuma nawa talaka? Saboda ita mai haza'ka ce, ni kuma ba ita ba ce? Duk staff kowa ita ya gasgata! amma ni da nake yar class 'dinka, ka kasa kare mini hakkina, saboda ita Bebinka ce, ni kuma ka tsane ni? To na bar mata makarantar ta tabbata a ciki kar ta fita"

Mamaki ya yi matu'kar kama shi amma ganin ta hau dokin fushi mai yawa, sai ya tattaro dukkan alhini ya ya'ba a fuska da gangar jikinsa.

Ya kira ta, ta amsa ba tare da ta 'dago kanta ba, cikin muryar lallashi ya ce, " Have I ever said I hated you?"

Ta girgiza kai alamun a'a sai kuma ta ce. "No, but actions speak louder than words!"

A thick silence sweeps the atmosphere! Ya zama speechless, bai yi tunanin irin kallon da take masa ba kenan. Cike da ta'ajibi ya ce,

"Kar fa ki zama cikin jerin mutanen da idan an musu gyara yake zama gaba, tunda haka ne na miki al'kawarin ba zan sake shiga cikin case 'dinki ba, wannan bai kai dalilin da za ki bar karatu ba, sai dai idan da gaske auran kike so, ko kuma ba gaskiyar maganar kika fada mini ba."

Ta yi shiru ya ce, "Yanzu kin ha'kura za ki koma?"

"Amma ai cewa ka yi idan na fada maka dalilina za ka samo mini wata makarantar."

"E na fadi hakan! €amma nima sai da nace idan na ji kina da dalili, to ban gamsu da wannan dalilin ba."

Ta yi 'kasa da kanta,"Ai dama na san ba zaka mini adalci ba, tunda abin ya shafe ta."

Ido ya zuba matat kamar kishi take da Farida, amma kuma ai shi ba wacce ya ce yana so a cikinsu, daga Ubangiji sai shi sai zuciyarshi su kasan me yake ciki.

"Wai ta ina ta zama Bebina?"

Da sauri ta ce, "Saboda kullum bakinka baya gajiya da ambaton ta, duk fadin makarantar nan da ita kake misali, alhalin ba ita ce kawai daliba mai 'kwazo ba, sannan za ta tsokane ni, amma har da kai a masu gaskata ta, ni kuma a 'karyata ni" Ta fada cike da takaici kwarai da gaske.

Ya nisa, "To ai nace ba zan sake shiga case din ki ba"

Ya sake sassauta murya ya ce "Sa'adah!" Har cikin jikinta sai da 'kiran ya ratsa, jikinta ya yi sanyi, ya sake kiran a karo na biyu. "Sa'adah!"

Ba ta amsa ba amma ta dago ta zuba mishi manyan idanuwanta da sukayi ja saboda kuka.

"Idan na ce ke ce Bebin nawa fa?"

Da sauri ta yi 'kasa da kanta saboda yadda maganar ta dirar mata a ba zata! kuma yanayin sa ya matu'kar sa kunya ta kama ta.

"Ki dago ki amsa mini." Ya fada murya ba amo.

Ganin ta kasa magana, ya fara gaskata zarginsa na ita ma tana son sa, ya nisa tare da cewa. "Ban so na fada miki sirrin zuciyata yanzu ba, na so sai kin kammala karatunki, sai na zo na nemi aurenki a gidanku, amma ke na lura gaba'daya kallon wani 'dan ta'adda kike mini, idan za ki yarda da ni, ni ba son Farida nake yi ba, amma na san ina tausayin ta, sannan idan ke ba ki amince mini ba, to tabbas zan iya maye gurbinki da ita"

Wani takaicin ya sake kama ta akwai alamun tausayin nan zai iya rikidewa zuwa soyayya kamar yadda Zainab Ma'aji ta hasaso, abin da take ayyanawa a ranta ke nan.

Ya gaji da jiran amsarta ya ce, "Kin yi shiru?"

'Kasa ta sake yi da kanta cikin fushi ta amsa, "Tunda har za ka iya maye gurbina da ita, kawai ka ri'ke ta tun yanzu ai dama ita ce a ranka."

Ta fada murya na rawa.

"Wai ke kam wacce irin yarinya ce mai 'karyata na gaba da ita? Kin sa na fada miki sirrin zuciya ta, amma kina 'karyata ni. zan maimata miki a karon 'karshe, ke ce

Bebina ba Farida ba, da gaske auren ki nake son yi, don nan ba gidan da zan yi wasa ba ne".

Ya mi'ke yana sa takalmi, yana ci gaba da fadin,

"Idan kin amince kin kuma gaskata ni, to lallai gobe na gan ki a makaranta, zan kuma fada miki wata magana. Rashin zuwan ki amsa ne na baki amince da soyayya ta ba, ba kuma ki gaskata ni ba, kin ga ba zancen ki ji ma maganar da zamu yi, zan tafi sai yadda hali ya yi ki gaida Inna!"

Ya juya ya fice.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU.

✍✍

[5/26, 20:33] Aminan Ibrahim: □ *HALIN YAU*! □

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•.•

Dan Allah masu son Halin Yau! Daga farko, ku dinga tambaya a group, a kullum nakan turawa mutane daban daban sama da sau goma, nasan soyayyar labarin ne ta kawo hakan, amma abin yana mini yawa mussaman da kullum'kara yin nisa muke yi! Idan anturo ku dinga tarawa, idan antambaya ku yi sharing, yanzu aka fara, labari na gaba, JAZAKUMULLAHI KHAIR.

Comments din ku na sani nisha'di na gode sosai fans Allah ya fini yabawa

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

29.

Ta jima zaune a gun, tana jin wani irin nisha'di tare da shauki yana ratsa zuciyarta da gangar jikinta gaba'daya, tana tuno yadda ya lankwashe murya yana fadin,

"Ke ce Bebina ba Farida ba"

Cike da farin-ciki ta na'de tabarma ta shiga gida, dakin Inna ta fara shiga ta shaida mata ta dawo sannan ta jigine mata tabarma inda ta dauka.

'Dakinta ta shiga, ta fara tattara uniform din da ba ta wanke su ba, ta fita tsakar gida ta hau wanki, hatta sandal sai da ta wanke ta shanya, tana gamawa ana kiran Maghrib. Koda Inna ta fito ta ga shanyar uniform uffan ba ta ce mata ba.

Sai da Baffa ya shigo bayan sallar Isha ta je ta durkusa gabansu, ta shaida musu gobe za ta je makaranta, Inna dai ba ta tanka ba, Baffa ne ya ce,

"Allah ya kai mu"

Ta dade a tsugunne tana jinta wani iri, ta san fushi suke da ita dukkansu musamman Inna. don haka sai ta sanyaya murya ta ce,

"Don Allah ku yi ha'kuri na san ban kyautata muku ba, na yi musu da ku, ku yi mini afuwa"

Ta fada cikin muryar kuka, kasancewar Baffa ya fi mata sassauci, shi ne ya fara tankawa da cewa,

"Ni ban san inda kika samo dabi'ar yin musu da iyaye ba Iyah? Ni da kaina na rarrashe ki akan wannan maganar kika kafe, kika nuna mini ni ne zan bi ki ba ke za ki bi ni ba".

Jikinta ya yi mugun sanyi ta shiga kuka na sosai tana jin kunyar maganganunsa na matu'kar ratsata, musamman yadda komai take so yana kokarin yi mata duk kuwa da wani abin don ya faranta mata yake yi, ba don yana so ko yana da karfin yi ba. Cikin kuka sosai ta ce, "Don Allah ka yi ha'kuri Baffa In Sha Allah ba zan sake ba."

Ya nisa ya ce, "Shike nan na yafe miki, amma ki kiyaye, wannan ba dabi'ar kwarai bace, musamman kasancewar ki mace, ko wani daban wanda kika san ya girme miki ya ce miki kar ki yi kaza, ai kin mutunta shi ki bar abin kasancewar ya fi ki hangen nesa, bare kuma ni mahaifinki da ba zan cutar da ke ba ta kowacce fuska".

A hankali ta ce, "In Sha Allah zan kiyaye, na gode Allah ya kara lafiya da nisan kwana Baffa".

Cike da tarin soyayya mai yawa ya amsa mata da,

"Amin Mamana!"

Sai kuma ta juya ga Inna da ba ta tsoma musu baki ba ta ce, "Don Allah Inna ke ma ki yi ha'kuri da bacin ran da na saku".

"Ni ba ki yi mini komai ba Iyah, amma tabbas inda ta ra'ayina za a bi kin gama yin boko tunda ke naki karatun na raini ne, haka siddan ana wahala da ke rana tsaka ki hau iyashegen ke ba kya son makarantar sai an canja miki, alhalin tun farkon samun wannan makarantar kin san ta fi karfinmu, amma kika kafe sai ita, kina kallon yadda yar'uwarki da mijinta suke 'dawainiya da ke, mu ma muna irin namu kokarin tunda wahalhalun makarantar yawa ne da su, sai kuma don kin raina mu ki ce lallai sai kin bar makarantar kin koma wata saboda ki nuna duk wahalar da ake yi akan makarantar ba karatun da'a kike koya ba, na raini ne da iyashege."

Jikin Sa'adah ya sake yin tubus ta san Innarsu mai zafi ce amma a yau yadda take furzar da magana ta san ba karamin fishi ta yi da ita ba. don haka sai ta sake yin kasa da kai ta ce, "Ki yi ha'kuri Inna"

Ta nisa ta ce, "Ke ce da ha'kuri Iyah, domin ina lura da take-takenki, kwatakwata ba ki ajiye kanki kusa ba, ina jiye miki kar ki jefa kanki a *HALIN YAU* na nadama marar amfani".

Sai da Baffa ya sa baki sannan ta ha'kura ta ce ta huce magana ta wuce, Sa'adah da kyar ta mik'e bayan ta musu godiya tare da tabbacin ba za ta sake 'ba ta musu ba.

Kasancewar sanyi ake kadawa yasa uniform din, nan da nan suka bushe, kafin ta kwanta barci sai da ta goge su tas! Sai da ta kammala komai ta kwanta ta fara tunanin yadda za ta kaya a tsakaninsu, anya ma ba zai ga rashin ajinta ba? daga magana daya sai ta hau bare-bare, kodai ta ki zuwa makarantar ne a iya gobe ta yadda idan ta koma zai gane ba saboda shi ta koma ba, tunda yanzu kam ta gane, ba karamar wauta ta yi na barin karatunta saboda wani dalili marar kangado ba?

Da sassafe ta tashi ta yi ayyukan da ta saba yin su, ta karya sannan ta shirya, ta yi wa iyayenta sallama ta karbi kudin makaranta ta tafi bayan sun bi ta da addu'ar albarka da dacewa.

Kai tsaye makarantar ta yi saboda ta san Zainab ta riga ta tafi, tunda ta sha biyo mata, tana cewa ba za ta je ba. Ba irin banbakin da Zainab ba ta mata ba, har ta gaji ta fusata ta daina biyo mata.

Tana shiga class dinsu aka hau ihun murna tare da fadin "Gogel is back!".

Ba su sarara ba sai da Uncle MK ya shiga don yin attendance, ya shiga rarraba ido, ya hango ta zaune kan desk dinta sanye cikin uniform sai daukar ido take yi, ga mamakin ta sai ta ga ya yi kamar bai gan ta ba, bare ya nuna wata alamar ya ji dadin ganin ta.

Ya shiga kiran sunayensu, har aka zo kanta, tana amsawa kuwa ya ba ta umarnin ta mike tsaye, sai da ya kammala gaba'daya sannan ya tambaye ta dalilin rashin zuwanta makaranta tsawon sati biyu, cikin rawar murya ta ce, "Am sick!"

Ya daure fuska sosai, cikin harshen turanci ya ce, "Waye ya zo ya fadi cewar ba ki da lafiya? Ina kuma shaida daga asibiti da makaranta za ta gamsu da gaske rashin lafiya kika yi? Ta rasa me za ta ce, sai ta yi shiru tana mamakinsa, ganin haka yasa ya ce ta fito, ta bi shi zuwa Staffroom.

Bai dake ta ba amma ya yi punished din ta, ta hanyar sata wankin staff toilet wanda duk dalibi ya tsani a sashi wannan aikin. Tana gamawa ya sake cewa ta wanke window glass din Staffroom wanda duk malamin da ya zo wucewa sai ya gan lta, wani ya tambayi me ta yi, wani kuma ya wuce. Mrs Ngozi, Maths Teacher dinsu kuwa sababi ta yi ta mata, tana cewa, "You again? You're rude student." saboda yadda kwanaki ta musu case da Farida.

Zuciyar Sa'adatu kamar ta fashe don bakin ciki, tana aikin tana kuka tana raya ashe da ma so yake ta zo ya ci ubanta shi yasa ya yi tattaki har gidansu ya mata kalamai wanda duk karya ne tsagwaronsu?.

Har aka tashi, tana wannan aikin, kuka ta yi shi kamar idanuwanta su fado kasa.

Koda aka tashin, da kyar Mr. Charles (Chemistry Teacher) ya ro'ki MK akan ya mata afuwa, ya bar ta haka nan, wanda ita a lokacin ta riga da ta fusata ba ma ta bu'katar ya mata afuwar, ai duk tsananinsa dai ba zai raba ta da numfashi ba, sai da aka gama watsewa sannan ya ce ta tafi. Tana kuka sosai ta wuce shi ya ce, "Sa'adah dawo, ba za ki gode mini ba? Takaicinsa ya sha'ke mata wuya, amma sanin halinsa na zai iya janye afuwar da ya yi mata sai ta ce,

"Thank you!" Cikin kuka.

Zuciyarsa ta yi rauni amma sai ya dake ya kalle ta tana tsugunne cikin kasa, ya tuna yadda ta zo cikin tsabta tana daukar ido amma yanzu ta yi futu-futu ta fita a hayyacinta. Sai ya ce ta jira shi a gate, wajen makarantar ke nan.

Takaicinsa ya sake kamata, amma sai ta amsa da to ba don za ta jira shi 'din ba.

Tana tafiya ita ka'dai kasancewar duk 'daliban sun tafi, tana rayawa ita kuwa mai zai ce mata? Ai kuma ba zai sake yaudararta a karo na biyu ba.

Makaranta dai za ta ci gaba da zuwan ko don zaman lafiyarta da iyayenta, amma In Sha Allah za ta yi iyakar 'ko'kari ta cire MK a ranta, tana shirin tsayar da abin hawa ya cimma ta kusa da ita ya tsayar da mashin dinsa.

Ta dauke kai tamkar ba ta gan shi ba ya ce, "Hau na kai ki".

Fur ta 'ki, don haka ya sauko ya kafe mashin din, suka gangara inda ba wucewar ababen hawa sannan ya tsaya ya dube ta ya ga yadda ta hade rai tamkar hadari.

Ya nisa ya ce, "Sa'adah are you angry with me?"

Hawayen ba'kin ciki ya ziraro ta ce, "A a, Am happy with you".

Ya san inda ta dosa, don haka sai ya ce, "Saboda Allah kinga ya kamata, ki yi laifi na kasa hukunta ki alhalin dokar makaranta kika karya? Kin san fa, if you want to show an example, you have to start it from your section for them to know you are not a selfish.

Ke yanzu na san dauka zaki yi da gayya na miki hakan, Ni kuma na rantse miki, ba zan yi son zuciya a cikin aikina ba, don haka ki ri'ke, ki kuma kiyaye".

Ta tura baki irin na sakarci da nuna takaici ba tare da ta ce uffan ba.

Ya nisa ya ce, "Ba za ki daina wannan fishin ba?"

Sake daure fuska ta yi tare da 'kin tankawa.

"Amma kin san na yi farin cikin zuwan ki makaranta yau?"

Sai a lokacin ta fashe, cikin kuka ta ce, "Ni kuma ban yi farin-ciki ko ka'dan ba, sai tarin ba'kin ciki da nadama."

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU.

✍✍

[5/26, 20:33] Aminan Ibrahim: □ *HALIN YAU*! □

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•·•·

Kuka sosai ya kwace mata, wanda ya yi matu'kar taba shi, tun a wannan ranar kuma ta gane rauninsa yana motsawa ne idan ya ga tana kuka.

A ki'dime ya shiga tattaro duk wata kalmar sanyaya zuciya, da nuna kololuwar kulawa, duk da ba ha'kuri yake bata ba, tunda shi ya san akan 'ka'idojin makaranta ya hukunta ta, ba ya kuma fatan ya ci amanar aikinsa.

Tsawon lokaci tana kuka, ta koma ajiyar zuciya tunda dama tun safe take yinsa.

Da kyar ya shawo kanta ta yi shiru, sai da ya ga ta nutsu sosai, sannan ya samu sukuni a zuciyarsa, yana mamakin yadda yake jin matsananciyar soyayyarta na ratsa dukkan jikinsa gaba'daya.

Cikin murya marar amo saboda shauki ya ce, "Jiya na ce miki zan zamu yi magana ko?"

Bai jira amsarta ba ya ci gaba da fadin, "Ban yarda ki fada wa wani ko wata cikin makarantar nan abin da ke faruwa a tsakaninmu ba, wannan sirrinmu ne ni da ke da ba zan so ya shiga kunnuwan students ba."

"Sannan bana bu'katar, ki nuna wata alama da students za su fahimci akwai wani abu a tsakaninmu, lastly ki rabu da fitunannen yaron nan (Khalil), ki fita harkarsa in dai kina bu'katar kwanciyar hankalina".

Ta yi shiru tana nazari maimakon ta fahimci inda ya nufa sai ta karkace, zuciyarta ta shiga kissima mata ai saboda Farida ne yasa zai ce bai son aji yana sonta banda haka mene ne na boyewa tunda dai aure za su yi ba wata 'barna ba.

Ya gaji da shirunta, ya ce,

"Kina tare da ni kuwa?"

Nan ma shiru ta yi, bai ji dadin shariyar da ta mishi ba, amma sai ya waske, ya san dama haka take, bare kuma yau ya ta'bo ta.

'Kasa ya yi da murya sosai ya sake cewa, "Magana fa nake miki, amma kin yi mini shiru".

Cike da fishi sosai ta ce

"To ni me zance?"

Zuba mata ido ya yi, yana kallon yadda take ta cika tana batsewa har wani huci take yi, jikinsa ya yi sanyi bai cika son mace mai fusata sosai irin haka ba, sai dai son da yake mata ya riga ya yi bunkasar jurewa duk wani kalubale daga gare ta.

Wannan karon ido ya zuba mata, tare da bude murya sosai ya ce, "Ina ta miki magana amma kina jina kin mini shiru, kar ki bari na ji a zuciyata son da na ce ina yi miki shi ne dalilin da za ki fara raina ni".

Kawai sai ganin hawaye ya yi yana tsere a kan kuncinta, tana ta yunkurin bude baki don ta yi magana amma ta kasa.

A ransa yake fadin akwai aiki a gabana, a kankanin lokaci ya gane shagwababbiya ce ta gaske, banda haka mene ne kuma abin kuka a maganar da ya yi? kan dole ya yi ta rarrashi akan ta fada masa abin da yasa ta kuka cikin maganganun da ya yi.

Cike da kukan kuwa ta hau cewa, "Ai an sha fada mini duk saurayin da yake boye kanshi kar a san yana son mace, to ba da gaske yake ba, yaudarar ta zai yi".

Ta 'karasa maganar cike da gunjin kuka, mamakin ta ya kama shi sosai ya ce, "Amma na sha fada miki gidanku ba gidan da zan yi wasa ba ne, tunda kina shakku a kaina a satin nan zan gabatar da kaina a gaban Baffa shike nan?"

Ta goge Hawayen da ya'ki tsaya mata, a hankali ta ce

"To saboda kar Farida ta sani ne kake son a boye?"

Takaicinta ya kama shi, amma kuma ya kasa yi mata jan ido, sai ma lallaba ta da ya shiga yi, ta hanyar fadin. "Sa'adah ya kamata ki dinga fahimta ta, inda Farida nake so, nake burin aure ba abin da zai kawo ni gunki tunda ba dole aka mini ba! Ribar me zan ci idan na zo don na miki karyar ina son ki? Mahaifinki mutumin kirki ne, na san shi, tun kafin na san ki, akan me zan yaudari yarsa? Ina son ki yarda da ni, yarda ita ce matakin farko a soyayyar gaskiya, abin da yasa nake son mu bar maganar a tsakaninmu ba komai ba ne illa don na kiyaye dokar makaranta!

Ba makarantar da ta yarda malami ya yi soyayya da 'daliba, ni kuma zan yi iyakar'ko'kari na kiyaye kowacce irin dokar makaranta, ta kowacce fuska wannan shi ne gaskiyar magana".

Ta yi kasa da kanta, tana jin nutsuwa da maganganunsa.

Ya nisa ya ce, "Kin yarda da manufata?"

Kai kawai ta 'daga mishi alamar eh, sai ya ce "To ba ki ce komai akan wancan yaron ba"

Ta sake yin kasa da kanta ta ce,

"Ai ni ba saurayina ba ne".

Da sauri ya ce "Magana muke ta gaskiya fa Sa'adah! kin san har letter da kika masa wacce na dauka tana nan, kawai idan kin amince kina sona, to ki fita harkarsa, kin

san dai yaro ne karami, da ba zan iya hada soyayyarki da shi ba, ga shi dama ba tarbiya ce ta wadace shi ba".

Kanta tsaye ta ce " To! na ji zan rabu da shi, kai ma kuma ban yarda na dinga ganinta tare da kai ba, kodayaushe tana hanyar staffroom saboda kai, kai ma da ka motsa sunanta ne a bakinka, to ba ita kadai ba ce mai 'kokari ba, ire irenta suna nan, wasu da yawa ma a cikin makarantar sun fita kokarin, ita zubin Sadakar Yallah da kuke gani a tare da ita yasa kuke ga kamar ta fi kowa".

Mamaki da dariya suka kamashi lokaci guda, amma ya dake bai bari dariyar ta fito ba, ya ce, "Amma ai na tabbatar miki ba son ta nake ba, sannan kin san dole wani abin zai hada mu tunda dai ni malaminta ne, abin da za ki yarda da shi shine wallahi ba budurwa ta ba ce, ba ni kuma da niyyar auren ta".

"Amma da bakinka kace mini za ka iya maye gurbina da ita".

"Tabbas na fadi hakan amma ki sa a ranki sai idan ke ce kika so faruwar hakan, ina nufin kika juya mini baya, sai na yi maleji da ita a rashin ki, kin san Bahaushe ya ce a rashin uwa, akan yi uwar'daki".

Da'di ya kamata har murmushi ya subuce mata, shi ma ya taya ta murmushin tare da cewa,

"Na rantse miki ban taba ganin wacce ta fi ki kyau a duniyata ba, musamman idan kika murmusa".

Kunya ta kamata tasa dukkan hannunwata ta rufe ido tana jin kamar su tabbata a haka.

Ganin sun dan fahimci juna ka'dan ya ce "To muje ki tafi gida kar aga kin dade da yawa, tunda ba za ki yarda na kai ki ba".

Sai da ya sa ta cikin Adaidaita Sahu ya biya kudin, sai da ya ga sun tafi sannan ya koma ya hau mashin dinsa yana jin shauki na shigarsa, yana kuma jinjina kishin Sa'adah.

WAYE MK BICHI?

Haifaffen karamar hukumar Bichi ne, a jahar Kano. Mahaifinsa Alhaji Kabiru Wadata, Bafulatanin Bichi ne, mai arziki ne a lokacinsa, don zai shiga cikin jerin attajiran Bichi shi yasa ake masa la'kabi da Wadata. 'Dan kasuwa ne mai sana'ar fata, yana fataucin ta zuwa jahohin Arewa.

Mukhtar shi ne babban dansa na namiji, shi ne kuma na biyar a dukka gidan, an haifi mata hudu kafin shi.

Matan gidan biyu ne Hajiya Babba (Indo), tana da yara bakwai wadda ukun farko dukkan su mata ne, Zainab, Khadija, Amina, kuma duk sun girmi MK, sannan Abbas, Akil, Sameera, da auta Bilkisu.

Sai dakin amaryar gidan wacce ita ce mahaifiyar MK, Hajiya Rabi yaranta uku kacal, Hafsatu ce Babba, sai Mukhtar sannan auta Ahamad, da Mk ya girme masa da shekaru kusan goma

Mahaifin MK mutum ne mai sau'kin kai, mai kokarin wadata iyalinsa da komai na bukatar rayuwa, dukkan su, sunyi karatu, matan dai suna kammala sakandire yake aurar da su, yayin da mazan ke zurfafa karatunsu a jami'o'i daban-daban a cikin kasar nan.

Gidansu akwai zaman lafiya, duk da ba a rasa yan kananun gutsuri tsoma irin na gidan Polygamy Family, amma dai nasu da sauki ainun kasancewar iyayensu matan ba su cika samun sabani ba. Idan ma sun samu to suna bari a tsakaninsu ba tare da sun bari yaransu sun shiga rigimar da ba tasu ba.

Wannan dabi'ar tasu, tasa hankalin mijinsu ya kwanta da su, inda yake musu hidima su da ya'yansu kan jiki kan karfi.

Mahaifinsu a tsaye yake kan sha'anin tarbiya, sannan ya dace da mata na-gari da suke taya shi, dora yaran akan kyakkawar turba, domin kuwa duk yadda namiji ya kai da kula da tarbiyar yara in bai yi dace da mace ta-gari ba, to da wahalar gaske yaran su bi tsarinsa.

Mukhtar ya fara karatunsa a kwalejin ilimi ta tarayya dake garin Bichi, bayan ya kammala sakandiren hadaka ta gwamnatin jaha (Unity Boys Karaye). Sai da ya kammala NCE, sannan ya yi JAMB ta D.E, ya yi sa'a ya samu level 200 a jami'ar Bayero, inda ya karanta harshen turanci (English Language), yana shekara ta biyu ne Allah Ya yi wa mahaifinsu rasuwa a hadarin mota ya je dauko Bilkisu a makarantar kwana, wacce tare suka rasu da Bilkin.

Wannan mutuwa ta matu'kar taba ahalin wannan gidan, dole suka tattara suka ha'kura suka bi su da adduar samun rahamar Ubangiji.

Haka iyayensu mata suka ci gaba da zama suna ci gaba da kula da ragowar yaran da ke gabansu wanda Sameera ce kawai ta rage ba a aurar ba sai maza su kuma suna ta karatunsu cikin nutsuwa.

Da ma can suna da sana'oinsu, sai suka samu sau'kin tafiyar da gidan da kuma tallafin 'ya'yansu maza da mata, musamman MK da ya kasance shi ne babba, kuma shi ya debo kusan halin mahaifinsu, na hakuri da yawan kula da lamarin gidan.

Yana da sau'kin kai ta yadda duk yan'uwanshi suna jin da'din mu'amala da shi, kafin ya fusata yana jimawa, amma fa idan ya yi fishin wuyar sauka ne da shi.

Abu mafi kyau cikin halayyar MK Bichi, ma'abocin addini, mai kokarin kiyaye dokoki ne na gaske, sannan duk layin da ba gaskiya, ba za ka same shi a ciki ba. Akidar son bokon da ya taso da ita bai sa ya yi watsi da kyawawan al'adun Malam Bahaushe ba.

Sannan MK ma'abocin 'kamshi ne tun yana Secondary, da kamshinsa ake gane ya zo guri, bayan haka kuma He is Frank and friendly to all.

Wannan ke nan.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

KAR KU BARI A BARKU A BAYA WURIN KARANTA LABARIN HAZI'KAR MARUBUCIYA.

⚜BUƊAƊƊIYAR SOYAYYA⚜

Jameey yar'mutan kankia.

Promo *Promo* *Promo*

Daga yau 21/5/2022 promo dinmu zai fara,har zuwa 30/5/2022 inshaa Allah,ga yanda promo din yake.

#300-sau biyu a rana

#500 -sau ukku a rana

#700 -sau hudu a rana

Kiyi man wanann number magana danjin ynda zaki biya 08160508316.

MASU SON A TALLATAH MUSU HAJARSU 'KOFA A BUDE TAKE

TUNTUBI

08032773332.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

32-33.

Tana isa kofar gida ana kiran La'asar, sai da gabanta ya fadi saboda yadda za ta sha tuhumar inda ta tsaya har zuwa wannan lokacin a wurin mahaifiyarta.

Ilai kuwa a tsakar gidan ta tarar da ita sai safa da marwa take yi, jin sallamar ta yasa ta tsaya cak, tare da zuba mata ido, amma ganin ta futu-futu kuma idanuwanta a kumbure sai ta sami sau'kin tashin

hankalin da ta shiga, don ta tabbatar Iyah ba za ta iya biyawa wani wajen a haka dukun-dukun ba, amma duk da hakan sai da ta ce "A ina kika tsaya har zuwa wannan lokacin?"

Fuska daure ta ce "kwanakin da na yi ban je makarantar ba shine suka ci zalina."

Ajiyar zuciya Innar ta sauke sai kuma ta ce "Madalla da wannan cin zalin."

Sannan ta dauki buta ta zaga ban'daki.

Sa'adah daki ta yi tana tube kayanta, zuciyar ta fes ,tana tuno hirar su da MK da ya mantar da ita takaicin da ya kunsa mata a safiyar yau.

Tana idar da sallah ta wanke uniform din da ya baci da 'kura sannan ta zuba abinci, kai tsaye falonsu ta shiga wanda ba komai sai leda a shimfide da labulaye, sai yar karamar talabijin kirar (sharp) a kan dan karamin tebur, kusa da mahaifiyarta ta zauna da ta ke kulla bushasshiyar kubewa.

Ganin Innar ba ta 'daga kai ta kalle ta ba yasa ta fadin, "Inna ko ki tambaye ni, ko na ji ciwo a cin zalin da aka mini?"

Cike da rashin kulawa ta ce "Tsuntsun da ya ja ruwa shi ruwa kan doka, tunda kin yi girman da za ki zabawa kanki abin da ya dace da ke ai magana ta 'kare"

Jikinta ya mutu ta ce "Inna kin ce magana ta wuce, amma kina ta share ni kina nuna ko oho da ni" Ta ture abincin tare da fashewa da kuka.

Da farko share ta ta yi, amma jin yadda take ta sauke ajiyar zuciya, ga kuma hawaye nata tsere a fuskarta, sai ji ta yi raunin da bata son ta nuna mata ya kubce mata cike da tarin soyayya irin ta uwa ta tausasa murya ta ce "Share hawayen kin san dai ba na son kukan ki ko?"

Ta tura baki cike da shagwaba ta ce "Inna ai da ne ba kya son kukan nawa, yanzu sau nawa za ki ga ina kuka amma ko ki nuna kin gani bare ki rarrashe ni?"

Murmushi ta yi ta ajiye ledar da take hannunta ta zuba mata ido sannan ta ce "Iya bawai kukan naki bai dame ni ba ne. Ni kadai na san yadda zuciyata ke zafi idan na gan ki cikin rashin sukuni, halayen da nake gani a tare da ke ne ba su mini ba, ina matu'kar kaduwa da yadda kike kokarin jefa kanki a rayuwar da ba za ta bulle da ke ba"

Sa'adah da jikinta ya yi laushi amma sai ta yi karfin halin cewa, "Don Allah Inna wai mene ne nake yi wadda bai miki ba?".

Muskutawa ta yi sannan ta ce "Iyah kin san dai ke din nan ba 'yar kowa ba ce, mu iyayenki ba wasu ba ne illa masu neman abin da asirinmu zai rufu, amma ke kina daukar ra'ayin ya'yan masu wadata, ba kya duba idan ba yawan gashinku daya ba, yawan kitson ku ba zai daidaita ba! Watanni kadan ya rage ki kammala makarantarki, kin san kuma aure za a miki amma duk saurayin da zai zo gidan nan da maganar aure za ki yi tsalle ki ce bai miki ba, amma kina son abin hannunsu saboda kawai kin 'dorawa kanki sai kin daura abin da kike gani a jikin yaran da 'karfin iyayenku ba 'daya ba"

Ta nisa tana jiran ko Sa'adah za ta yi magana sai taji sabanin hakan, duk da dai ta lura jikinta ya sake yin laushi fiye da 'dazu, don haka sai ta sake cewa, "Ki ajiye wannan dabi'ar, sannu a hankali idan kina da rabon yin arzikin za ki yi shi ne. Yanzu dai babban misalin da zan miki da yayarki ne, duk da cewa lokacin da aka aurar da ita ba ki da wayon da za ki gane komai, mijinta ko mashin din da kika raina mai hawansa ba shi da shi, amma a yau mene ne bai mallaka ba? A saninki 'kasashe nawa ya debi iyalinsa suka fita? Wace irin hidima da karamci ne ba ya mana ke ma shaida ce tunda dai ko wannan makarantar da kike yi ba don shi ba, da ba ki yi ta ba, da ace farko ta raina matsayinsa da yanzu ta cim ma wannan jin dadin da kowa

ke mata kallon tana ciki? Tsakanin ki da Allah ba don ta sau'ka'ka buri ba ta kai wannan matsayin?"

Kai Sa'adah ta girgiza wa mahaifiyarta don kuwa harshenta ya mata nauyi, amma a ranta tana raya in dai akan zaben miji ne an wuce wannan babin, zuciyarta ta riga da ta aminta da MK Bichi kuma shi ma ai talaka ne tunda ko mota ba shi da ita. Jin da'di da son kayan 'kawa kuwa ba mahalukin da ba ya so sai idan bai samu ba, ita a jininta ne son gayu ba wai fariya ko 'karya ta sa a ranta ba. 😀 Don haka ba ta dauki maganar ajiye dogon buri da aka mata nasiha da wani muhimmanci ba.

"Kullum addu'a ta Allah ya ba ki miji nagari wanda zai kula da ke da amana, ke ma irin adduar da za ki rike ke nan. Dauki abinci maza ki ci kar ya gama hucewa, Allah ya miki albarka."

Ajiyar zuciya ta sauke ta ce "Amin na gode?" Sannan ta ja abincin ta hau ci, danwaken fulawa ne da yaji mai da'din gaske, tana ci tana yaba yadda Innarsu ta iya sarrafa abincin gargajiya masu da'di, kawai dai abincin zamani ne ba ta yin su ko kuma don za su ja kudi ne?

Sai ta tsinci kanta da cewa "Allah Inna na kusa daina cin abinci mai nauyi."

Cike da mamaki ta ce "Me za ki dinga ci to?"

Murmushi ta yi, ta ce "Chips, chicken, sai dangin su pizza, da indomie da kwai, sai na bi bayansu da ababen ruwa irin su juices da yougurt ko hadadden shayi hadin kauri."

Salatin da Inna ta 'dauka ne ya sa ta dakatawa tare da tunanin ta yi subutar baki.

"Ashe duk togaciyar da na gama yi miki bai shiga kunnenki ba? A gidan uwarki kika san wadannan kayan, wadda ba ta alfahari da abin da ta bude ido ta gani a gidansu, sai hangen kayan wani da ba ya rufa maka asiri!

Nasan kina nufin idan kin je gidan miji ne kike tunanin wannan rayuwar za ki yi"

Ta kafe ta da ido tana mata kallo mai tsanani sannan ta ci gaba da cewa, "To saurare ni da kyau aure ya wuce wasa tun wuri ki cire wannan tunanin a ranki, gabadaya aure ibada ne, duk abin da akace ibada ne, to ba son ranka za ka yi ko zaka gani ba, sannan ba abin da ke ri'ke da aure gabadaya sai ha'kuri don haka ki cire wannan tunanin a ranki. ki yi fatan Allah ya ba ki miji nagari, da hankalinki zai kwanta, domin komai za ki samu idan ba kwanciyar hankali ina tabbatar miki ba za ki ji dadinsa ba Allah ya shirye ki, adduar da zan dinga miki ke nan."

Ta fada da iyakacin gaskiyarta, domin ta lura addu'a ce kawai za ta canja mata Iyah ba hantara ko nuna fishi ba.

***

MK yana isa gida ya tarar da Hajiyar Bichi ta zo, a falo ya tarar da su ita da Hajiya Babba suna cin makani wanda ba ya tantamar daga Bichi ta taho da shi, da murna ya hau fadin,

"Hajiya ashe da gaske kike da wuri za ki dawo?"

Dariya ta yi ta ce "Allah Ya yarda ban dade ba".

Suka ci gaba da hirarsu har su Abbas da Ahamad suka dawo aka ci gaba da hirar da su, Maghriba ce ta dakatar da su.

Bayan sallar Isha MK ya tarar da Hajiya Babba a dakinta, ya gama kame-kame da soshe-soshen 'keya, sannan ya ce "Hajiya so nake aje a tambayar mini izinin magana da wata yarinya a wajen mahaifinta."

Dadi ya kama ta, ta shiga fadin "Alhamdulillah! Allah Ya sa abokiyar arziki ce, ina ne gidan nasu?"

Sake kasa ya yi da kansa da kyar ya ce "A babban layin Unguwa Uku suke mahaifinta mai karamin karfi ne amma mutumin kirki ne, na san shi tun kafin nasan yarinyar."

Farin ciki ya bayyana a fuskar Hajiiya Babba ta ce, "Yanzun nan za mu tattauna da Hajiyar Bichi tunda Allah ya sa ta zo garin, gobe In Sha Allah zan je har gidan Babanku Alhaji Isa (Aminin mahaifinsu ne) na shaida masa. Sai ya je ya tambayar maka, tunda ka kammala karatun kuma ka iya harkar kasuwanci ba za mu ji tsoron aurenka ba, bare da ikon Allah da wuri za ka sami aikin yi ka ci gaba da rike mu gabadaya."

Koda ta sami Hajiyar Bichi da maganar fatan alheri kawai ta yi tare da cewa, "Hajiya Babba ai ke ce uwarsa, ni 'yar addua ce!"

Wannan biyayyar da tun fil'azal Hajiyar Bichi ke yi wa Hajiya Babba ta taimaka kwarai wurin samun zaman lafiya a tsakaninsu, tare da saukaka kishin junansu matu'ka da gaske.

A satin aka tambayo masa izinin magana da Sa'adah, a take kuma Baffa ya ce ya bashi damar ya nemi yardarta ba don yana jin tsoron halin dan yau ba, da a take zai ce ya ba shi ita, to tsoron kar ta ce ba ta sonsa ta kunya ta shi yasa ya ce idan har sun daidai ta kansu to ya ba shi, aka yi murna aka rabu ana addu'ar Allah Ya sa hadin Allah ne.

A ranar Baffa ya zaunar da Sa'adah tare da mahaifiyarta ya ce, "Bakin da suka bakunce ni a yammacin yau, zuwan Iyah ne. Yaron nan Mutari ne ya turo a ba shi iznin neman amincewarki, ni kuma na ba shi dama ya nemi yardarki ba don Ina jin tsoron kada ki yi mini *HALIN YAU* ba, da kai tsaye zan ce na ba shi su zo ayi maganar aure. Saboda yaron nutsatstse ne , ya san mutuncin manya mai kokarin neman na kansa ne, kullum ya zo shagon askinsa sai ya zo ya gaishe ni, ban kuma taba jin hayaniyarsa da wani ba, kiga dai yadda shagon yake cika dam da matasa amma ban taba jin an ce ana fada da shi ba.

Da shi muke sallar Magariba da Isha kullum yana sahun gaba, ba zan miki dole ba amma da a ce zan miki zabi ki karba, to da ba zan tsallake shi ba. Idan kuma kin

kafe shi ma bai miki to lallai ki tsayar da wanda ya miki da zarar kin kammala makaranta zan aurar da ke, ki ri'ke wannan!"

Alkalamin

SURAYYA GWARAM

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•·•·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•·•·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

TALLAH *TALLAH*!

KAR KU BARI A BARKU A BAYA WURIN KARANTA DADDAN LABARIN NAN

⚜BUƊADƊIYAR SOYAYYA⚜

_NA_

Jameey yar'mutan kankia.

Promo *Promo* *Promo*

Daga yau 21/5/2022 promo dinmu zai fara,har zuwa 30/5/2022 inshaa Allah,ga yanda promo din yake.

#300-sau biyu a rana

#500 -sau ukku a rana

#700 -sau hudu a rana

Kiyi ma wanann number magana danjin yanda zaki biya 08160508316.

MASU SON A TALLATAH MUSU HAJARSU KOFA A BUDE TAKE

TUNTUBI

08032773332.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

34-35.

Baffa na rufe baki, Inna ta yi caraf ta ce "Gara ka jaddada mata don ni a halin da nake ciki da ita, ban ki ka kawar mini da ita a cikin wannan watan ba."

'Dan murmushi ya yi mai sauti tare da cewa, "Anya Salamatu ba gaskiyar Iyah ba ne da take cewa kin fi nan nan da Sumayya?"

Da sauri ta ce "Hmm Ni yaushe ma na ga yayar tata bare har na nuna son kan da take korafi? Mafi yawa ai karamin 'da ya fi shiga rai, sai idan halinsa ne marar kyau ko ba ya jin magana".

Ya sake fadada fara'arsa ya ce "Ato ni ma dai na ce ban taba ganin wacce ba ta ririta autarta ba sai ke".

Da sauri Sa'adah ta ce, "Ai ni Baffa Inna ba ta dauke ni a auta ba, ALLAH ne ya mayar mata da ni auta akan dole."

"To ki dinga jin maganar da ake fada miki, ki rage dogon buri, sannan ina sake jan hankalinki akan yaron nan kar ki bari ya kubuce miki."

Ta yi kasa da kanta, nuna alamun kunya, a ranta fadi take "Son sa nake sosai Baffa daina jan hankalina" 😀

Sa'ade ke nan.

Daga haka ya sallame ta ta mike tana fadin "Sai da safe."

Tana zuwa, ta zube kan katifa tana jin wani irin nisha'di na tsirga mata, idonta a rufe wani irin shauki yana mamayar ta.

Can kuma ta fara tunanin maganar Baffa in da ya ce, "Shagon aski! Kar dai The Boss barbing shop?" Duk titin ba katon shago irinsa, shago ne da ya samu karbuwa wurin samari yan kwalisa da kullum suke dafifin zuwa gyaran suma ko yin aski. Ashe shi yasa kwanaki ta gan shi agun? A fili ta ce, "Hadadden guy dan boko da yin aski?"

A take wani sashi na zuciyarta ya ce mata ai ya huce takaicin bani-bani a wurin iyaye da dangi, ya kuma kere sa'a a tsakanin abokai masu jiran gwamnati ta ba su abin yi.

Maimakon ta ji abin alfahari ya yi, ta yabawa kokarinsa na dogaro da kafafunsa, sai ta ji tana jin kunyar ace saurayinta wanzami ne 😁.

Washegari da wurwuri ta shirya ta biya wa Zainab Ma'aji, a hanya ta ba ta labarin yadda ta kaya tsakaninta da MK, murna sosai Zainab ta yi tare da cewa "To ki kiyaye abin da ya ce baya so, sannan ki kama bakinki."

Duk sa idon su Halima ba su iya gano soyayyar da ke tsakaninta da Malamin nasu ba, saboda yadda suka rufe kofar da za a gane akwai wata alaka a tsakaninsu da ta wuce Malami da dalibarsa.

Khalil ne kawai ya kasa gamsuwa musamman yadda ya lura Sa'adah ta yi matu'kar sauya masa, sannan ta toshe duk kofar da suke samu su yi hira, zai mata letter sau goma bai fi ta ba shi amsa daya ba a dukunle. Wannan sauyin da yake gani a tare da ita yasa ya sake kullatar MK yana ganin tun zuwansa makarantar ya canja masa Sa'arsa. Saboda haka ya sake daukar samfurin nuna rashin da'a a gaban Uncle MK, duk lokacin da ya zo ajin sai Khalil ya yi abin da zai harzuka zuciyarsa, wanda hakan ya janyo kiyayya mai tsananin gaske a tsakaninsu, wata rana an fita break ya samu ya yi magana da ita a dalilin ya sa Halima ta tsayar masa da ita, duk tambayar da ya mata idan laifi ya mata ta yafe masa.

Ta ba shi amsa da cewa, "Khalil ba ka mini komai ba, kawai ganin jarrabawarmu ta gabato akwai bukatar mu fuskanci karatunmu ne."

Kai tsaye ya ce, "Zan so wannan dalilin ya zama shi ne gaskiyar magana, amma na san idan na rantse ba zan yi kaffara ba, cewar akwai wani dalilin ba wannan ba. Ni koma mene ne zan yi ha'kurinsa amma idan wannan mugun Malamin is behind your changes, to ba zan yafe masa ba!" Ya fada cike da 'bacin rai.

A tunanin Sa'adah tunda ya turo a ba shi iznin neman amincewarta, an kuma bashi ai zai dinga zuwa zance, sai ta ga an kwashe kwanaki kusan goma bai zo ba, bai kuma sake waiwayar ta ba ko a makaranta, wannan abu na ci mata tuwo a kwarya musamman da a safiyar yau 'yan ajin nasu suka yi laifin da gaba'daya ya zane su, amma da ya zo kanta sai ta ga ya dage iya karfinsa ya zabga mata bulala har hudu maimakon bibiyu da ya yi wa kowa.

Abin ya tsaya mata a rai sosai, sai kawai ta tsiri fishi da shi, ya lura da fishin da take yi amma sai ya share, tun ranar da ya gan ta tana hira da Khalil ya ji gabadaya ya rasa inda zai sa ransa shi yasa da ya samu damar dukan yan class din ya ninka nata dukan!

Ranar wata Juma'a da yamma Sa'adah na zaune a tsakar gida tana yanke farce ta yi kwalliya da daguwar riga ta shadda purple (Mai ruwan Shanshanbale) a lokacin surfani aikin sama ake ya yi, dinkin ya yi kyau sosai!

Innarta sai mita take yi, akan har yau Muutar bai zo ba, ganin Sa'adah ta yi shiru ba tare da ta ce komai ba, sai ya harzuka ta, ta zuba mata ido ta ce, "Iyah ba magana nake yi ba ne kika mini kunnen uwar shegu?"

Tura baki ta yi da ya zame mata jiki cikin yanayin tabara ta ce, "Ayya Inna ni ma ban sani ba fa!"

A tunzure ta ce, "Kin sani Iyah kawai dai kin nuna masa halin naki ne"

"To ni a ina zan nuna masa halin nawa tunda ko a makaranta ma ba kula ni yake yi ba, ni wallahi na fara tantamar shi ya aiko yana so na? Shekaranjiya ba ki ga dukan da ya mini ba."

Jikin Inna ya yi sanyi ta fara wasiwasi tana fatan Allah ya sa lafiya, amma sai ta ce, "Allah ya sa dai ba wani abin ba ne."

Tana rufe baki yaro ya yi sallama ya ce, "Wai ana sallama da Sa'adatu" Da sauri Innar ta ce, "Je ka ce Wai waye?"

Ba a jima ba ya dawo ya ce, "Wai Mukhtar ne." Dadi ya kamata da sauri ta ce, "Je ka ce ta na zuwa."

Ta juya ta ga hakimar ko motsawa ba ta yi ba tana ci gaba da yankan farcenta, kamar za ta yi magana sai kuma ta shanye, tana mai son ganin iya gudun ruwanta.

Fiye da shudewar mintina goma tana zaune ta gama yankewar. Amma sai ta tsiri kankarewa, zuciyar Inna ta hau ba tare da Iyah ta ankaraba, kawai ta ji saukar duka

da mafici a zabure ta mike tana dire-diren shagwaba tana cewa, "Me na yi kuma na duka Inna?"

Dakuwa ta mata da hannunta na dama tare da cewa, "Za ki wuce ki dauko mayafinki ko kuwa?"

Ta shige dakinta tana cewa "Daga zuwansa zan debi jiki na fita, ba jan aji ba komai, salon ya ga arhata."

Mahaifiyarta bin ta yi da kallo, jiki a sanyaye ta rasa bakin magana, ta shiga dakinta ta fito da lemon kwalba guda biyu, da Swan roba biyu, da tuni Baffa ya tanada saboda zuwansa, ta zuba mata a kan faranti mai kyau ta ajiye.

Kan dole ta bi ta dakin a zaune ta same ta ta sake gyara fuskar ta yi kyau sosai ga mayafin da ya dace da zaren surfanin dake jikin rigar, kamshin tsadadden turaren Escada sai tashi yake a dukkan dakin! Sassautawa ta yi ta ce, "Yanzu zama ki ka sake yi Iyah? ko ba komai ai malaminki ne, malami kuwa ai kamar uba ne, ki duba fa tsawon lokacin da kika shanya shi yana faman jiran ki?"

Bata ce komai ba ta mi'ke ta fice ta dauki tabarma, ganin ruwa da lemo a kusa da tabarmar yasa ta ganewar iyayenta sun fi ta kambama lamarin MK.

Tabarma kawai ta dauka ta nufi zauren, a tsaye ya jigina da bango ta same shi. Sanye yake da farar shadda kal (Bankole style) ya dora hula ba'ka, kafarsa dauke da bakaken cover shoe. Sallama ta yi tare da shimfida tabarma sai da ya zauna sannan ta zauna ta gaishe shi. Ya amsa ba yabo ba fallasa, kamshin turarensa na Versace da wanda ta yi amfani da shi Escada suka cakude suka cika zauren da wani irin lafiyayyen kamshi mai nutsar da zuciya.

Tsawon mintina suna zaune shiru, ita kanta a kasa yake tana ta wasa da yatsun hannunta da ta musu kwalliya da zobuna (fashion).

Shi kuma kawai kallon ta yake yi, yana nazarin yadda ta iya tsara simple kwalliya ta burgewa tamkar wacce take karantar fashion and design.

Gani ya yi ta mik'e tana cewa, Ina zuwa." Ba ta jima ba ta dawo dauke da faranti a hannunta ta ajiye a gabansa. Ta koma in da tashi ta zauna.

Can ya nisa ya ce, "Wai fishin ne har yanzu?"

Takaicin sa ya makure mata wuya, tunda ya zo ban da kallon ta bai ce komai ba, sai gaisuwar da ya amsa mata ba karsashi, shi ne yanzu zai ce wai fishi take yi, so yake ta saki baki ta masa hira bayan shi ya kame bakinsa ya tsuke, saboda yana jin isa?

Don haka sai kawai ta daure fuska sosai, sannan ta juyar da kanta gefe ba tare da ta ce ko mai ba.

Dariya ta kamashi ya murmusa, sannan ya ce, "Ke kullum a cikin fishi kike? Da kin san yadda murmushi yake sake kawata miki fuska da kullum kin kasance a cikinsa"

Ba ta ce komai ba, ya yi shiru yana nazarin mai zai ce da zai sa ta kula shi. Ya nisa ya ce, "Babana ya yaba da karbar da Baffa ya masa, ya yi murna sosai har cewa ya yi na iya zaben suruki, yana fatan a ce ke ma ki yo halin karamci irin na gidanku "

Ba ta ce komai ba amma ta sassauta daurewar fishin, yana kula da ita, don haka sai ya sake cewa, "Kin san kafin na zo raina a bace yake da ke amma kina fitowa na ga wannan kwallliyar da aka cancanda mini sai na ji na manta komai! Ke kawai nake gani kin cika ko ina fiye da duniyar gaba'daya!"

Dadi ya kamata ta murmusa kadan, amma ba ta ce uffan ba.

Ya dade yana rarrashi kafin ta ware su yi hirarsu, cikin dabara ya tabbatar mata ai ya gan ta da Khalil suna hira a class shi ne kuma dalilin da ya hana shi zuwa, don Allah ta kiyaye.

Ba ta musa ba, cike da dariya ta ce, "Shi ne dalilin da ya sa ka ninka dukan da ka mini?"

"E, saboda ki ji dan kadan cikin takaicin da nake kwana ina tashi a cikinsa."

Bai tafi ba sai da aka fara kiran sallar maghrib, ya mike yana cewa kawo mini buta na yi alwala.

Tana tsaye har ya yi alwalarsa ya mayar da agogon da ya cire ya zura hannu ya ciro sabbin yan dari-dari da suka sha turare guda ashirin ya mika mata da 'kyar ta karba wanda sai da ya rantse akan sai ta karba, sannan ta sa hannu biyu ta karba, ita kanta a ranta addu'a take Allah ya sa kar ya mayar da kudinsa! Ta ga samu ta ga rashi 😁 a wancan shekarun dubu biyu tana da daraja ba kamar yanzu ba.

Ta kalle shi a kunyace ta ce, "Ka tsaya sai ka rasa sahun gaba, Baffa yana ta cewa kullum a sahun gaba kake sallah."

Dadi ya kama shi tare da cewa, "Ashe har kamfen Baffa yake mini a gunki, lallai ki ce na kwantar da hankalina, na same ki na gama! Amma yanzu ba na iya zuwa wurin da yake yin sallah, kunyarsa nake ji."

"Ta yi dariya sosai ta ce, "To kuma a ina kake yi?"

Ya kalleta yana jin wani irin abu na tsirga masa da sauri ya fice yana cewa, Nan Masallacin bayan layi nake zuwa."

Ya tabbatar sai ya sake alwala saboda yadda ya tsinci kansa cikin yanayi na sha'awa sosai.

Bata lura da yanayinsa ba ta dauka kawai gaggawa yake yi tunda an tayar da sallah, shi yasa bai bari sun yi sallama ba.

Sai da ta yi sallah sannan ta je falo gun Inna ta mika mata kudin da ya ba ta, za ta fita ta ce "Zo ki zauna."

Kusa da ita ta zauna, a hankali ta ce, "Ina fatan dai ba shi da matsala ko Iyah!"

Dariya ta kama Sa'adah ta cije ba ta yi ba, amma sai ta yi nufin tsokanar Innar, don haka sai ta ce

"Ba shi da matsalar komai Inna amma gaskiya ni wanzancin da yake yi ne bai mini ba!" Ta fada a dake tamkar gaske.

Salati sosai Inna take yi tana karawa, amma sai ta taushi zuciyarta cikin lallashi ta ce, "Iyah mene ne laifin sana'arsa saboda Allah? Ai abin alfaharinmu ne duka ace matasanmu sun daina zaman banza, sun daina zaman jiran gwamnati ta basu abin yi, ke yanzu raina wanzancin kika yi? To bari ki ji tun a lokacin ma'aiki akwai wanzamai, sannan duk inda wanzamai suke mutane ne masu amana masu kuma tsananin zumunci, bare kawai don yana da shagon aski sai ki mayar da shi wanzami?"

Dariyar da take dannewa ta kubuce ganin yadda Inna ta kwantar da murya tana lallaba ta, tana cewa a ranta Inna ta koma lallashi.

A fili kuma ta ce

"To shikenan ki cigaba da addu'a Allah ya sa na ji ina son sa tunda na lura duk ya kwanta muku a rai"

"Ai ni tunda na ji Baffanku ya yabe shi na ji ya kwanta mini a rai, kinsan mijin yayarki ma shi ne ya zaba mata, halayensa da nagartarsa kawai ya auna, shi yasa kema nake so ki masa biyayya kar ki yarda ya kubuce miki".

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•·•·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•·•·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

KAR KU BARI A BARKU A BAYA WURIN KARANTA DADDAN LABARIN NAN!

⚜BUƊAƊƊIYAR SOYAYYA⚜

NA

Jameey yar'mutan kankia.

Promo *Promo* *Promo*

Daga yau 21/5/2022 promo dinmu zai fara,har zuwa 30/5/2022 inshaa Allah,ga yanda promo din yake.

#300-sau biyu a rana

#500 -sau ukku a rana

#700 -sau hudu a rana

Kiyi man wanann number magana danjin ynda zaki biya 08160508316.

MASU SON A TALLATAH MUSU HAJARSU KOFA A BUDE TAKE

TUNTUBI

08032773332.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

36-37.

Sannu a hankali cikin nutsuwa MK ke tafiyar da Sa'adah, a sati sau daya yake zuwa zance. Duk da ya karbi lambar wayar Inna tun da yanzu koyaushe wayar na hannunta amma ba kasafai yake kiran ba, duk a kokarinsa na ganin bai raba mata hankali ba, musamman da kullum jarrabawarsu kara kusantowa take yi.

A bangarenta kuma sai ta ke ganin kawai rashin daukar ta da muhimmamanci ne yasa yake nuna mata rashin kulawa, musamman yadda Khalil ke kiranta safe da yamma sannan su raba dare ana musayar kalamai, shi yasa ya daina damuwa da rashin saurarar shi da ba ta yi a makaranta.

A haka har aka rubuta jarrabawar JAMB, duk kokarin da MK ya yi na ganin Sa'adah ta samu rubuta jarrabawar abin ya ci tura! Saboda yadda Baffa ya ce masa "Ni sakandiren nan ma a dole na bar ta ta kammala ,yar uwarta aji uku kawai ta yi na aurar da ita, don haka ni ba zan barta ta tafi wata babbar makaranta ba, ta zo tafi karfina".

Ya dan tsahirta sannan ya rufe maganar da cewa, "Idan Allah ya sa ta zo hannunka komai ma sai ta yi, amma ni a yanzu babban burina shi ne na sauke nauyinta da ya yi saura a kaina, na aurar da ita a hannun da ko ba na numfashi ba za ta koka ba".

Kan dole MK ya ha'kura da maganar amma ya kudire a ransa Sa'adah za ta yi karatu har sai ta ce ya ishe ta.

Gab da za su fara rubata WAEC wa'adin da MK zai yi a makarantar FGC ya cika, amma saboda yajin aikin da jami'o'i suke yi, yasa hukumar makarantar ta roke shi ya ci gaba da zuwa kafin lokacin da ASUU za ta janye yajin aikin. Kasancewar MK da sakamako mai daraja ta daya (First Class) ya fita, yana cikin wadanda Jami'ar Bayero za ta dauka don yin koyarwa.

A haka suka ci gaba da tafiya a baibai tsakanin MK da Sa'adah, shi yana ganin ya ba ta lokacin da za ta yi karatu sosai, ita kuma tana masa kallon wanda bai girmama lamarinta ba, hakan ya sa take saurarar duk wanda ya nuna yana son ta ba tare da tunanin ai tana da wanda take so ba! Musamman da a lokacin damina Baffa ya fi zaman Gogel saboda kula da noman da yake yi, ita kuma Inna zuciyarta daya ta dauka MK ne yake zuwa.

A haka har ta kammala makaranta gaba'daya, cikin wannan yanayin ta hadu da Alhaji Mamman! Asibitin (Arewa Surgery) suka je duba Mahaifiyar Safina ita da Halima, sun fito harabar asibitin suka hadu da shi, ya nemi su shigo mota ya kai su, Sa'adah ta'ki amincewa amma da yake tare suke da Halima sai da ta rinjaye ta suka shiga motar, a hanya ya nuna ra'ayinsa akan Sa'adah, wanda sam-sam bai kwanta mata ba, musamman da yake ta gan shi dattijo da alamun yana da iyalai masu yawa a karkashinsa.

A lokacin wayar hannun ba ta da yawa sosai kamar yanzu, sannan mai madannai ce komai tsadar wayar. Ya tambayi lambar wayarta, Sa'adah ba ta ce komai ba sai da ya sake tambayar a karo na biyu sannan ta ce "Ba ni da waya."

Bai yi mamaki ba tunda a lokacin ba ta zama ruwan dare irin yanzu ba, ko iyayenta ma Sumayya ce ta sayo musu don ta ri'ka gaisawa da su tun da ita ba mazauniyar gari ba ce. Ita kuma ta gaje ta Inna.

Halima ta ce "Ba Inna na da waya ba?"

Shiru ta yi da alamun dai ba ta son ba da lambar ne, shi kuma sai ya ce "Yawwa 'kawarmu a taimaka a ba ni lambar Innarmu!"

Haka Halima ta bude wayarta ta karanto masa lambar Inna saboda ta ga alamun za su sami kudi a tare da mutumin.

Duk kokarinsa na son sai ya kai Sa'adah har kofar gidansu, amma hakan bai samu ba, saboda ta kafe akan idan aka gan ta cikin motar da ba a san mutumin ba, za ta fuskanci tashin hankali, wannan kalaman ya sake jin son ta sosai, ya san daga dukkan alamu da ga Babban gida ta fito ma'ana gidan tarbiyya.

Kan dole ya kai su gidan su Halima wanda ita ko dar ba ta ji ba, hakan ya sa yake ganin anya iyayen Sa'adah ba tufka suke wannan 'kawar tana musu warwarba? A dan haduwar nan tasu ya lura da kamewar Sa'adah, ya kuma gane rawar kan Halima, a ransa yana rayawa da zarar ya sami Sa'adah zai raba ta da wannan kawar da idan kawancesu ya ci gaba da wanzuwa, zai ta ba tarbiyar Sa'adatu.

Halima ta shige gida ta bar su, bai wani jima ba shi ma ya ce zai tafi don ya lura da Sa'adah kamar a tsorace take, kudi ya dauko har kimanin dubu talatin ya ba ta ya ce ta bawa kawarta goma a ciki. Ta tattaro dukkan kunya ta yaba a fuskarta tare da cewa, "Ka bar su ba zan karba ba!"

Shi kuma ya na ta fadin "Idan ba ki karba ba, ba zan ji dadi ba Sa'adatu."

Da kyar tasa hannu ta karba ta yi godiya bayan ya karbi address din gidansu, wanda kai tsaye address din gidansu Zainab Ma'aji ta bayar.

Jiki na rawa ta shige gidan su Halima ta tarar da ita a falo da kaninta suna kallo kasancewar mamansu tana wurin aikinta, haka suka shige dakinta, kudin ta ciro ta nuna mata suka hau ihun murna! Halima na cewa "Ai tunda na gan shi na san akwai rodina tare da shi sannan ba matsolo ba ne."

Dariya Sa'adah ta yi tare da cewa, "Kin ga kuwa takanas ya ba da naki sakon."

Dadi ya cika zuciyar Halima da ta ji yawan kudaden da ya ba ta, haka ta sake jan Sa'adah zuwa Country Mall wanda a lokacin aka bude shi, suka kashe kudin nan tas a wurin siyan kayan kwalliya, da takalmi da jaka. daga Country Mall suka rabu kowa ya yi gidansu, Sa'adah zuciyarta sai wasiwasi take yi mai za ta cewa Inna akan wadannan kayan?

Ta tabbatar uwarta ba sakaryar uwa ba ce! Duk wani motsinta akan idonta ne, wa za ta ce ya ba ta wadannan kayan? A ina ta zubar da nasihar da kullum take yi mata idan za ta fita na kar ta tsaya da saurayi a hanya, ko dazu kafin ta fita sai da ta jaddada mata duk mai son ta ya zo gidansu ya same ta, kar ta yarda a tsayar da ita a hanya.

Ta gama tunaninta kaf ba ta sami kalaman da zai shiga zuciyar mahaifiyarta, ta fahimce ta ba, don haka kai tsaye gidan su Zainab ta sauka, ta ba ta ajiyar kayan tare da ce mata khalil ne ya ba ta, ba ta son a gani a gida, don ta san idan ta fada wa Zainab gaskiyar magana sai ta iya zuwa ta fada wa Inna tunda ta tsani abotarsu da Halima, kullum sai tace mata, "Sa'adah ki kiyayi kawance da Halima Mu'az ba wayewarku daya ba, ba kuma irin tarbiyarku daya ba"

Da kyar Zainab ta karbi kayan bayan ta gama mata mitar ita a rayuwa ba ta son shiga shirgin rashin gaskiya, ban da rashin gaskiya ina ke ina sauraran wasu mazan tunda dai kin san namiji daya za ki aura! Kuma kin tsayar da wanda kika aminta da shi.

Sa'adah da yake mafita ta ke nema sai ta yi mukus ta kasa tanka wa Zainab tamkar ba ita ce mafadaciyar nan ba.

Tana isa gida ta tarar da Baffa ya dawo daga Gogel, ta yi farincikin dawowarsa amma a gefe takaicin yadda za a ci gaba da yin tuwo ba kakkautawa take yi.

A kwanakin da baya nan hilatar Inna ta ke yi ba sa yin tuwo amma yanzu kam ba hilar da za ta mata ta yarda, tunda tafi girmama ra'ayin Baffa fiye da komai, sannan kuma ba za ta bari ta yi nata girkin ba, ce mata ta ke yi nan ba gidanki ba ne, ki bari idan kin yi naki gidan sai ki yi yadda kike so.

Kallo daya Inna ta mata ta gano rashin gaskiya a tare da ita, ba ta mata magana ba, sai da ta gama da hidimar Baffa ya fita waje. Sannan ta iske ta a daki tana game a waya, ta zauna kusa da ita ta kamo hannunta ta ce, "Iya na ga sauyi a tare da ke mai kike ciki ne da har ban cancanci na sani ba?"

Duk da yadda Sa'adah ta maze akan ita ba komai, bai gamsar da Innar ba, amma sai ta ce, shike nan Iyah! Ki sani tun kafin ki san kanki na san ki, tun kafin ki yi dabarar boye mini halin da ki ke ciki nake tattalin ki, don haka komai za ki yi, zan gane. Ki sani idan har mu ba mu san mai kika yi ba, Ubangiji ya sani! Shi ne kuma zai kama ki saboda ha'intar da kike kokarin yi Mana."

Ta fada tana kallon ta irin kallon nan mai tsanani.

Jikin Sa'adah ya yi sanyi sosai musamman kallon da uwar take mata mai kama da ban yarda da ke ba, sai ta ce,

"Ni fa Inna ban je ko ina ba."

"Iyah ai ban ce kin je wani gun ba amma fada mini ina kuka biya daga asibitin sannan bayan Zainab da wa ku ka hadu a tafiyar?"

"Yan makarantar mu ne kawai Inna"

"To wa ye kuma ya ce yana son Zainab?"

"Babu!"

Ta sake ri'ko hannun ta sosai sannan ta ce "Waye ya tsayar da Iyah?"

Kai tsaye ta ce "Kai Inna ni fa ban kula shi ba, wani mutum ne tsoho ne fa!"

"To tsohon ba namiji ba ne?"

Idan har nagari ne kuma kina son sa ai magana ta kare! Ba za mu miki dole ba, don haka ko waye ya tsayar da ke idan kin ga ya miki ki turo shi wurin mahaifinki, laifin da za ki mana shine ki yaudare mu, ki yi abin da kika san ba za ki iya yi akan idon mu ba, ina abin da ya ba ki?"

Dariya ta kwace wa Sa'a ta ce

" Ban karba ba Inna"

Ita ma Innar dariyar ta yi tare da cewa "Ban yarda ba Iyah! Na san ki da martaba kalmar nan ta ba kyau mayar da hannun kyauta baya, amma na san Iyah ba za ta boye mini duk wata kyauta da za ta samu ba.

Don ta san ba zan ki ta da alheri ba, sai dai na kiyaye ta daga fada wa hatsarin MAZAN YAU musamman da ba gidansu aka biyo ta ba."

Tana fadin haka sai ta mike ta fice ta bar Sa'adah da sanyin jiki da kunya iri-iri suna saukar mata a lokaci guda.

A ranta kuma fadi take, "Ko yara nawa ne irinta suka dace da samun tsayayyiyar uwa mai sa ido akan duk wani motsin 'ya'yanta?" A fili kuma ta furta "Madalla da uwa irin Inna!"

Tana Jin komai za ta yi In Sha Allah ba za ta tozarta tarbiyar da Inna ke yi a kanta ba gajiyawa ba, amma kuma ba ta jin, za ta ki karbar duk wata kyauta da za a mata kawai dai boyewa ne ba za ta sake yi ba. don haka da kanta ta fada wa Alhaji Mamman gaskiya cewa gidansu na gaba kadan da wancan da ta fada masa da farko, haka nan hatta Khalil ta ba shi damar zuwa, ta gaji da boye-boye tunda wanda take yi domin sa ba fin su son ta ya yi ba, ita ce dai tafi son sa.

Yawan wayar da Alhaji Mamman yake mata ba kakkautawa, sau tari ma gajiya take yi da amsa kiran nasa, ya sake sa ta raina kulawar MK, tunda dai yanzu ai ta gama karatun tunda ada uzurin kar ya raba mata hankali a karatu ya gabatar.

Amma har yau ya ki canjawa idan ya kira ta da safe ba zai kara kira ba sai da daddaare shi ma a ya dade su yi maganar mintina uku, sabanin Khalil da Alhaji Mamman sai su shafe fin awa akan waya suna neman saye zuciyarta tamkar ba kati suke sawa ba.

Tana yawan tambayar kanta shin Uncle MK soyayya ne bai iya ba, ko kuwa matsayinta ne a zuciyarsa bai kai ya mata yadda su Khalil ke mata ba?

Zuwan ma bai canja ba sau daya a sati, duk da kullum sai ya zo unguwar, sannan ba ya mata kyautar bajinta kololuwar kyautar sa dubu biyu, sai dai karshen wata ya kan hado mata shopping din kayan kwalliya masu matsakaicin kudi da tarkacen alawowi masu dadi da biscuit, wanda ba sa dadata da kasa saboda yadda Alhaji Mamman da khalil mai sato kudin iyayensa suke mata barin kudi.

Wani zuwa da Alhaji Mamman ya yi ya fa'da mata matansa biyu, da yara bakwai, bai boye mata shi dan majalisar jaha ba ne mai wakiltar karamar hukumar Gezawa, uwargidansa na can Gezawa yayin da amarya ke nan cikin Kano a kwatas din 'Yan Majalisu na Farawa.

Da daddare Sa'adah na kwance a daki tana hira da Khalil, cike da nishadi take amsa wayar don kuwa tabbas tana jin son Khalil, kawai sanin ba za a masa aure yanzu da kuma soyayyar MK da ta danne tasa ne! Amma tana son sa yana burge ta ya dace da tsarinta na Luxury Life.

Tana ganin kiran MK sai shigowa yake yi amma ba ta katse ba, tunda ta san shi ba wani lokaci mai yawa zai dauka yana lallabar ta ba, sai daga baya ta katse kiran Khalil bayan ta dauki excuse akan ya ba ta mintina biyar tana zuwa.

Tana kiran sa ya katse ya kira ta bai mata complain din da wa take waya ba, hakan ma yasa ta sake jin haushinsa, ya tambayi lafiyarta, ya kuma sanar mata cewa gobe zai zo abokinsa na son ganin ta, to kawai ta ce, a ranta kuma tana cewa abokinsa ne yake son ganina ba shi ba.

Washegarin kuwa suka zo shi da amininsa Mahmoud Karfi, wani abu mai kama da almara Mahmoud na dora ido a kan Sa'adah ya ji son ta ya cika zuciyarsa, ta zo masa a yadda yake burin samun matar aurensa ta kasance.

kwalliyarta, yangarta, shan kamshinta duk sun tafi da shi, amma sai ya yi yaki da zuciyarsa ya danne ta yana nanatawa kansa MK ya wuce ya hada soyayyar mace da shi, ya tabbatar idan MK ya gane yana son ta to tabbas zai bar masa.

Idan kuwa haka ne shi ne ya kamata ya haramta wa kansa wannan yarinyar da a yau ya dora ido a kanta, a daddafe aka yi hirar Mahmoud ya ba ta kyautar kudi dubu biyar suka tafi yana ta neman tsarin shaidan da zuciya da suke sake kawata masa Sa'adah.

Madalla da aboki irin Mahmoud wanda yake daraja abota da kuma sadaukarwa, ba wanda zai zagaye ya yi wa abokinsa kafar ungulu ba.

BAYAN WATA UKU.

Zuwa wannan lokacin Sa'adah ta canja sosai domin ba karamin kudi Alhaji Mamman ke sakar mata ba, ta mallaki zobunan Dubai Gold a boye har guda biyu. Ta mallaki waya mai kyau Sliding 'kirar Nokia da SIM a ciki, wayar dai Inna ta sani amma zobuna ta kife ta musamman da Innar ba ta san Gold ba.

Tun MK bai lura da canjawar Sa'adah ba har ya fara ankara da yadda kwallliyarta ta karu, ta daina dokin amsa masa waya, ta daina mitar rashin zuwansa, sannan dan flashing din da take masa ta daina idan zai kwana ya yini bai kira ta ba, baya taba ganin text ko flashing dinta.

Duk da bai san tana da waya ba har zuwa wannan lokacin shi da layin Inna ya ke kiran ta, so yake ya mata bazata jiran fitowar results dinsu yake yi, idan har ya yi kyau, waya zai siya mata, idan ma bai yi ba dai zai siya mata. Ashe shi bai san ta kerewa rike kananun wayoyi irin wanda yake harin siya mata ba.

Jikinsa ya fara sanyi don haka ranar wata Laraba ya kasa jiran Juma'a ta zo, ya shirya ya nufi gidansu da yamma.

Sai dai yana zuwa ya tarar da Alhaji Mamman zaune a kan tabarma, yana tsayawa a bakin zauren ita kuma ta fito daga cikin gidan ba ta 'karasa isowa zaure ba, amma idanuwansu sun sarke da juna, bai ce kala ba ganin Alhaji Mamman bai ganshi ba sai kawai ya yi murmushin da babu nisha'di a cikinsa ya juya abin sa.

Sai ta tsinci kanta da diriricewa, ta ji tamkar ta ruga da gudu ta ce masa ka dawo, kai nake fatan ace kai ne a zaune ba wannan mutumin ba, amma ba damar yin haka, a daddafe ta gaishe shi, ta gabatar masa da uzurin zazzabi take yi don kar ya ji ba dadi ne yasa ta daure ta fito. Ya gamsu a yadda ya ga duk jikinta ya saki ta yi wani iri, tashi guda, don haka ya fita ya je mota ya kwaso mata sayayyar da ya jido mata, bayan ya ajiye mata rafar yan 200 sabbi kal.

Tayi godiya ta shiga gidan zuciyarta daya tunda Inna ta je cikin Unguwa yinin biki don haka ta rage wasu kayan ta boye akan sai wani zuwan ta nuna mata.

Jikinta na rawa ta shiga lalubo lambar MK, amma har ta katse bai dauka ba, ta sake kira har sau uku nan ma bai dauka ba.

Alkalamin

SURAYYA GWARAM

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan, ba tare da iznin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

Fatan alheri ga

Asma'u Sani

Aisha Lagos

(Mrs Dan manya).

Shafin na ku ne ku yi yadda kuke so da shi.

38_39.

Haka ta ci gaba da kiran har ta gaji, tana 'kiyasta adadin kiran da ta yi masa ya kai ashirin, jikinta ya mutu tamkar marar laka, zuciyarta ta cunkushe da fargaba, tasan tana son MK sosai amma a yau ta sake sanin son da take masa marar adadi ne, duk da kasancewar ba lokacin zafi ba ne sosai, amma zufa sai karyo mata take yi. Waya kuma na hannunta, tana ci gaba da kiran sa.

Tunda ya bar gidansu Sa'adah Masallaci ya nufa da 'kyar ya karasa saboda yadda zuciyarsa ta daure, ba abin da yake bukata sai kadaici. Ya Jima a zaune yana ta ambaton Allah har ya sami sassauci sannan ya dauki Qur'ani ya fara karatu a fili, a hankali, duk kiran da Sa'adah ke yi masa yana gani, duk da a silent ya mayar da wayar.

Bai bar massalacin ba sai da aka yi Magariba zuwa wannan lokacin ya samu saukin daurewar da zuciyarsa ta yi a dalilin kishi, ya fito daga Massalacin ke nan kiran ta ya ci gaba da shigowa ba kakkautawa.

Gefe sosai ya samu ya zauna ya fito da wayar ya katse kiran nata sannan ya kira ta.

Jikinta har rawa yake yi wurin amsa kiran wanda ta dade ba ta ji zakuwa da dokin amsa kiran sa ba kamar a wannan lokaci.

Muryarsa ba amo sosai ya mata sallama tare da cewa, " Sorry Sa'adatu! Kin kira na bar wayar a caji ne tun dazu sai yanzu na ga tarin missed calls."

Wani nauyin jiki ya kara kama Sa'adah, ta rasa kalmar da za ta furta saboda abubuwa biyu, na farko bai nuna ta masa laifi ba tunda da ban ha'kuri ya bude maganarsa bugu da kari ma katse kiran ta ya yi, ya Kira ta.

Na biyu ya ambace ta da Sa'adatu rabon da ya kira ta da hakan tun lokacin suna yar tsama, ita kam ya binneta, ha'kuri za ta ba shi ko kawai sharewa za ta yi kamar yadda ya yi?

Da kyar ta bude baki ta ce "Ai na dauka kana sane ka 'ki amsawa."

Tana rufe baki ya ce

"Ko daya to mai kika mini?"

Ta san sarai a cikin fishi yake, don haka sai ta lankwashe harshe ta ce "Ka yi ha'kuri don Allah!"

Da sauri ya cafe da cewa

"Ni fa ba ki mini komai ba, laifina ne da na zo kai tsaye ban sanar da ke ba, sannan ai yaudarar kai ne na yi tsammanin ni kadai kike kulawa, ke allura ce a cikin ruwa don haka feel free you did nothing."

Ta kasa gane inda ya dosa shin gatse ya ke mata ko kuwa da gaske hakan yake nufi a zuciyarsa?

Don haka sai ta ce "To ka dawo na ganka dama ai na kwana biyu ban gan ka ba"

Kai tsaye ya ce, "Ai ba na zuwa zance da daddaare"

Shiru ta yi sannan ta ce "To gobe za ka zo?"

Tana rufe baki ya ce "Ina da schedules masu muhimmamanci a gobe."

Kawai sai ji ta yi kuka ya zo mata, cikin rawar murya ta ce "Har sun fi ni muhimmamanci?"

Cike da rashin kulawa ya furta "Wadancan tabbas ne, ke kuwa gaibu ce."

Ta yi shiru amma kuka take yi, yana jin yadda ta ke jan majina da shassheka, amma ya yi burus da ita, yana fatan ta ji a ranta cewar ita ba wata tsiya ba ce a gunsa.

Cikin kuka ta ce "Ni ka ke kwatantawa da gaibu?"

Ko dar bai ji ba wurin ba ta amsa da cewa, "E!" A gajar ce.

Bai sani ba ko kishin dake cin zuciyarsa ne, ya sa bai ji kukanta ya taba shi sosai ba.

Yayin da ita kuma bakin cikin yadda yake nuna mata rashin kulawa yake dada addabar ta.

Duk da hakan sai ta daure ta ce "Jibi Juma'ar za ka zo?"

"Zan zo idan ina cikin masu rai da lafiya idan kuma uzuri ya taso ban sami zuwa ba, to sai satin sama."

Ta yi shiru tana jin ta rabu da wannan mutumin da yake nuna mata ita ba komai ba ce a idonsa, sanin ya gan ta da wani ta san dole zai ji ba dadi yasa ta ajiye komai ta neme shi.

Har ha'kuri ta ba shi amma shi ya nuna ma ba laifi ba ne bai yi fishi ba, anya kuwa yana son ta, anya ba ita ke bankaura akansa ba?

Jin ta yi shiru ya sa ya magantu da cewa, "Sai yadda ta yiwu." Ya katse wayar! Bakin ciki ya kama ta sai kawai ta kife kai a kan filo tana kuka.

Shi kuma ya mike ya mayar da wayar aljihunsa, yana sake jin sau'kin radadin da zuciyarsa ke yi masa, tunda dai ya tabbatar ita ma ta shaki takaici.

Washegari tun safe Sa'adah ke zuba idon kiran MK har aka yi sallar Isha bai kira ba, a lokacin ha'kurinta ya gaza, ta dauko wayar Inna ta shiga kiran sa, sai da ta gama ringing bai dauka ba, tana shirin sake kira sai ga kiransa ya shigo. Ba ta tsaya jan aji ba ta dauka da sauri sai kuma ta yi shiru ta ki yin magana.

Sai da ya yi sallama har sau biyu sannan ta amsa ciki-ciki, mamakin ta ya kama shi amma ya waske ya ce, "Mura ki ke yi ne?"

Nan ma ta yi shiru ya nisa ya ce, "Yau yini guda ban zauna ba, ina ta yunkurin kiran ki, sai wani al'amarin ya mantar da ni.

Yanzu kuma na dauko wayar da nufin na kira sai kika riga ni, Ina fatan kin yini lafiya?"

Haushin sa ya kama ta sosai ta kasa tanka masa, amma tana raya cewa wai ya manta da jin muryarta.

Jin ta sake masa shiru sai ya kashe wayarsa.

Ita ma ta ajiye wayar daga kunnenta, tana gaskata zarginta na zaton MK da gaske ba son ta yake yi ba.

Kafin ta yi yunkurin yin wani abu kiransa ya sake shigowa ta yi kamar ba za ta dauka ba sai kuma zuciyarta ta kasa jarumta. Haka ta sa hannu ta amsa, ba tare da ta yi magana ba.

"Kina jina?"

Abin da ya furta ke nan, ta sake yin shiru! takaici ya kama shi cikin fa'da fa'da ya ce, "Kin san ba za ki yi magana da ni ba mene ne zai sa ki kira ni?"

Sai kawai ta saka masa kuka mai tsananin gaske irin mai cin rai! Ya yi shiru yana jin kukan nata wanda yake rasta dukkan sassan jikinsa musamman yadda take yi tana ajiyar zuciya.

Jikinsa ya yi sanyi sosai sannan kuma hankalinsa ya tashi, duk da ya san ma'abociyar kuka ce ita din, amma wannan ba na zallan shagwaba ba ne, da alamun damuwa sosai a cikin kukan.

Ya yi kasa da muryarsa sosai ya ce, "Me ya faru, fada mini mene ne yasa ki kuka haka?"

Jin ya karya murya yana tambayar ta sai wani kukan ya sake kwace mata sosai wanda ya tayar da hankalin MK sosai.

A gigice ya dinga fadin "Don Allah ki yi shiru ki fada mini me ya faru, kin tayar mini da hankali."

Ta kasa magana saboda kukan ya ci karfinta ita kanta so take yi ta daina amma ta kasa sai shesshka da ajiyar zuciya ta ke yi.

Ya yi shiru yana jinta, yana jin shi ma tamkar ya rushe da kukan ko ya sami sau'kin yadda zuciyarsa ke bugawa.

Ya lankwashe murya ya ce, "Sa'adah! so ki ke ni ma na yi kukan ne? Don Allah ki taimake ni ki yi shiru haka nan , ko so ki ke kanki ya yi miki ciwo?"

Cikin kukan ta ce, "Ka damu da ni ne da har kake gudar mini jinya?"

Ya ce, "Haba Sa'adah wacce irin magana ce wannan! Ai ni gani nake yi Baffa da Inna ne kawai suka fi ni damuwa da ke "

Ta yi fit ta ce "A hakan?"

Ya nisa sannan ya ce, "Ke matsala ta da ke ba ki fahimce ni ba, har yanzu kin kasa gane manufata. Kowanne Dan adam yana da tsarinsa, don ina sonki ba zan miki karya ba, abin da nasan zan iya shi zan miki, amma tun ba mu je ko'ina ba, na gane kin raina kulawar da nake ba ki gaba'daya"

Ya dan yi shiru sannan ya nisa ya ci gaba da fadin, "A farko tsakanina da Allah kamar yadda na fada mikil saboda jarrabawar da za ki yi yasa ban cika yawaita zuwa da kuma kiran ki a waya ba, sai ke kuma hakan ya zama dalilin da kika mini kishiyoyi, alhalin kin san har a gidanku na bayyana kaina ina son auren ki"

Ya fada muryarsa da rauni sosai.

Yayin da ita kuma kukan ya tsaya mata cak, tana jin wani irin abu na taso mata da ta kasa tantace mene ne shi.

Ya sake cewa, "Sa'adah duk motsin ki akan idona kike yin sa, ta ya ya ki ke tsammanin zan saki jiki da ke alhalin na tabbatar zuciyarki tana rawa a kaina! Na dade da gane kin samu mai kudi, na dade da sanin kina tare da Khalil har yanzu, ba don ina son ki sosai ba ai kamata ya yi na janye kaina a cikin 'yan takara amma kullum ina karfafa wa kaina guiwa da cewa idan rabona ce ke zan same ki, duk da haka dole na yi kaffa-kaffa don ba ni da tabbacin kina so na bare nasa rai Sugar Daddy ba zai kada ni ba!"

Kunya ta lullube ta, da kyar ta iya cewa "Ba ka da tabbacin Ina son ka fa ka ce?"

Da sauri ya amsa da cewa, "E wallahi da kina so na ba za ki saurari kowa ba, kin ga ni namiji ne zan iya hada mata biyu ko sama da hakan a rana na aura, amma tunda ke nake so, ke na aminta ta zamo mini uwar 'ya'yana ban sake kula wata da sunan soyayya ba. da na lura ba ki ba ni irin wannan matsayin ba, shiyasa na ke janye jikina, musamman yadda kika ci gaba da kula fitanannen yaron nan."

Kalamansa sun sa mata kasala sosai bayan kunyata ta da suka yi.

Da kyar ta bude baki a hankali ta ce, " Na daina!"

Ya yi murmushin da ya iso har cikin kunnenta, ya ce, "Mai ki ka daina din?"

"Abin da nake yi da ba ka so! Sannan kai ma ka daina mini wulakanci, kana nuna mini ba ni da daraja a gunka"

Ya sake murmusawa ya ce, "Akwai darajar da ta wuce na aure ki, na killace ki a gidana?"

Kunya ta kama ta, ta yi shiru dadi na cika mata zuciya.

Ya lankwashe murya sosai ya ce, "Ke ba ki san idan na tsananta zuwa ina kallon ki, za a samu matsala ba? Ko fa waya mu ka yi mai tsayi sai wanka ya kama ni, ya kike ganin kuma idan kullum zan gan ki a kusa da ni?"

Kunya mai tsananin gaske ta kama ta ta kashe wayar tare da rufe idanuwanta tamkar yana tsaye a gabanta.

Ya kira tana gani har ta katse amma ta kasa dauka ya ci gaba da kira har sau uku ta kasa dauka saboda yadda ya ba ta kunya.

Sai ga text ya shigo ta bude ta karanta kamar haka

"Da gaske nake yi Sa'adah, don haka na roke ki, ki daina kallon rashin zuwana akai-akai da sunan rashin daraja ki, kokari nake yi mu kiyaye dokokin shari'a! zan zo gobe bayan Masallaci amma plz kisa hijabi ki 'boye wadannan abubuwan da suke karya mini alwala. Good night!"

Ta karanta yafi sau ashirin tana jin shauki mai dadi na fizgar ta, tana jin ta tamkar a gajimare take yawo tsabar dadin soyayya. Ta hakikance MK shi ne mabudin farincikinta, duk wata damuwar zuciyarta ya wanke mata tas.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

TALLAH

_Akwai ingantaccan maganin□□ gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number..... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana

gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.....*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

40.

Washegari tun safe Inna ta lura da yadda Iyah ta tashi da kuzari da walwala, duk ayyukan gidan cikin kuzari take yin su sabanin kwanakin biyun da suka gabata da ta ke sukuku.

Kafin La'asar ta shirya, sai dai ta rasa hijabin da za ta saka. Gabadaya hijaban ta guda uku ne, biyu na Islamiyya ne, dayan kuma sallah take yi da shi, ta yi shiru tana nazari sai ta zabura ta fita. 'Dakin mahaifiyar ta shiga ta lalubo wani hijabinta da ta sayo a Jos amma ba ta taba sawa ba, a tsakar gidan ta ware shi kalar fari da maroon fulawa a jikinsa ya yi kyau sosai, ta saka ta ga ya zarta guiwarta da kadan, ta isa kusa da Inna da take zaune ta na tsinkar zogale ta ce, "Inna na dauko Hijabin nan."

"To." Kawai ta ce mata ta bita da ido, tana mamakin yau Iyah ce za ta saka hijabi ba don zuwa makaranta ba? 'Dakinta ta koma ta gama shiri, ta fito sanye cikin riga da siket na wani yadin material mai laushi, maroon colour! Hijabin ya hau sosai, ba karamin karbar ta suka yi ba.

Tana fitowa Inna ta juyo ta zuba mata ido tana raya komai Iyah ta saka sai ya mata kyau, ta ce, "Da kin san yadda Hijabin nan ya miki kyau da kin daina saka mayafi kin koma ado da hijabai."

Dariya ta yi tare da cewa, "Allah Inna tsokana ta kike yi"

"Da gaske nake yi miki, ba ki gan ki ba tamkar bakar Balarabiyar Habasha."

Dariya Sa'adah ta dinga yi sosai tana cewa, "Ashe har haka autar ki take da kyau Inna?"

Can kuma ta katse dariyar ta ce, "Inna Uncle Mukhtar ne zai zo kuma ya ce zai shigo ya gaishe ki."

Dadi ya sake kamata da sauri ta ce, "To! Kamo mini Baffanku a waya na fada masa."

"Kai Inna don zai gaishe ki ne za ki ce a fada wa Baffa?"

"Dole na fada masa mana tunda dai bai san wani zai shigo masa gida ba, idan bai amince ba ai kin san kuwa ba yarda zan yi ya shigo ba."

Sa'adah ta tura baki gaba alamun maganar Inna ba ta mata dadi ba ta ce, "Inna Uncle din ne wani?"

"Wani ne mana tunda ba mu da alaka da shi, sai ya aure ki tukun, zai zama cikin ahalinmu, amma a yanzu kam dole yana da iyaka."

Hakan kuwa sai da ta sanar da mijin nata, ya ce ya shigo idan ya zo babu damuwa. Ta kalli Iyah ta ce, "Komai aka yi shi akan ka'idojin shari'a ba a nadama, ke ma ki yi koyi da hakan. Kar ki yarda ki yi wasarere da hakkin mijinki, ko da baya gidan ki kiyayi duk abin da kika san ba ya so."

Sa'adah ta amsa da "To!" Sannan ta sauya maganar da tambayar, "Inna na dauko juice din?"

Da sauri ta amsa mata da cewa "Dauko mana ki hado da ruwa, ai ba sai kin tambaya ba."

"To Inna ai shekaranjiya na ga kin hana ni dauka ne!"

Tana rufe baki ita ma ta ce "Ai ba don shi aka saya ba, saboda Muutar ya sayo ya ce a ajiye idan ya zo ki dinga ba shi. Kin ga kuwa idan har ba Muutar ba ne ai ni ba zan bayar ba."

Wucewa dakin Sa'adah ta yi tana dariya tare da cewa,"Oh Innah maganar Baffa tamkar hadisi take a gunki!"

"Aljannata nake nema kin san kuwa aljannar mace ta fi samuwa idan mijinta ya yarda da ita."

Cikin dariya sosai Sa'adah ta ce, "Sadaqati Inna! Kin yi gaskiya In Sha Allah har a aljanna ke ce uwargidan Baffah."

Dariyar ita ma ta shiga yi tana fadin, "Allah ya shirye ki Iyah"

Daidai lokacin kuma waya ta hau kuwwa tana dubawa ta ga MK ne, ta amsa, ya sanar mata ya iso.

Ta mikawa Inna wayar tana cewa, "Ya iso."

Daki ta koma ta sake gyara fuskarta sannan ta feso turare ta fito, ta dauki tabarma ta na fadin, "Ki tashi Inna ki kintsa, na ajiye miki Hijabin da za ki saka a kan gado."

Harara ta galla mata tare da cewa ba zan saka wanda kika ajiye din ba 'yar fariya! Kin yi shigarki ta burgewa, amma kin tashi kin fesa turare."

Ta yi kwafa tana ayyana dauke shi za ta yi ta boye.

Murmushi ta yi tare da cewa, "Take heart mom!" Sannan ta juya ta tafi.

Ta isa da sallama yana tsaye yana amsa waya, ya yi kwalliya da yadin kufta kalar ruwan kasa (brown), ya dora hular da ta dace da kayan. Sosai ya yi kyau, musamman yadda sumarsa da hula ba ta rufe ta gaba'daya ba tana ta sheki alamun ta sha gyara na musamman.

Ya katse kiran yana zuba mata ido sosai sai kuma ya hau murza dukkan idanuwansa, ya sake kallon ta soasai, ya bude baki alamun mamaki tsawon sakanni goma sannan ya nisa ya ce, "Sa'adah ce kuwa, ko idona ne ya ke mini gizo?"

Ta tura baki tana dan murmushi tare da shagwabe fuska.

Hakan da ta yi sai ta sake burge shi ya ce, "Kin canja fa! Ba ki ga yadda kika yi kyau ba, ganin ki na yi tamkar 'yanmatan Ethiopia."

Da'di ya kamata musamman yadda bakinsa ya yi daidai da na Innar ta, ya lura da yadda take murmushi, ya fahimci tana son a ce ita mai kyau ce, ko ta yi kyau.

Ya ce "Ki fa daina wannan shagwabar ita ma tana sani a wancan yanayin!"

Ta rufe fuskarta da gefen Hijabinta, ba tare da ta iya cewa komai ba.

Ya sake cewa, "Idan ba so kike na zama agwagwa ba, to ki daina yin ta a yanzu. Ki tara mini ita zuwa lokacin da za mu tsinci kanmu a dakinmu!"

Ta sake rufe ido sosai tana ayyana wai shi ba ya jin kunya ne?

Ganin yadda ta rufe ido ta makale a bango sai ta ba shi dariya sosai.

Ya dan juya dan ganin ba wanda zai ji shi, ya yi kasa da murya ya ce, "Ba ki ji yadda na ji ba, ina ma ni kika makale ba wannan bangon ba! Kunyar nan ma burge ni take yi, komai na ki is special!"

Shiru ta yi ta kasa juyowa, bare ta tanka masa, tana ji a jikinta yadda idanuwansa ke yawo a kanta.

Da kyar ta bar jikin bangon ta shimfida tabarma tana cewa, "Bismillah!" Ya yi kicin-kicin da fuska tamkar ba shi ne mai walwala yanzun nan ba.

Ya ce, "Ba zan zauna ba!"

Ta dago ta kalle shi a kunyace ta ga yadda ya hade fuska, gabanta ya fadi, tana tunanin me ya 'bata masa rai kuma?

A hankali ta ce," Tafiya za ka yi?"

Ya girgiza kai sannan ya ce, "Zaman ne ba zan yi ba, ki dinga shimfida wa Honorable."

Ta yi shiru tana jin fargaba na taso mata!

Ta nisa ta ce, "Amma dai ai na ba ka ha'kuri, magana sai ta wuce."

Da sauri ya ce, "In dai sai na zauna a inda yake zama to kuwa magana ba za ta wuce ba!"

Ya juyar da kansa gefe guda, ganin yana Shirin dawo mata da yanayinsa da ba ta so na nuna ko in kula ta kalle shi ta ce "Bari na dauko maka wani abin zaman to."

Bai ce komai ba, ta nade tabarmar ta shiga da ita, ta dawo da kiret din lemon kwalba mai kwari, ta ajiye ta dora sallaya a kai, kamar ba zai zauna ba sai kuma ya zauna din.

Ita kuma ta zauna a kan wani dutse da ya ke zauren. Ta kalle shi ta ga bai ware ba, ta daure ta ce, "Ba don fishinka na gigita zaman lafiya ta ba, da haka zan so ganin ka kullum. yadda ba yanmatan da za su ga fuskar tunkarar ka, saboda kwarjini da tsare gida."

Dariya ta kwace masa, ya nisa ya ce, "Kina da son kai Sa'adah! Ba kya son na kula yanmata amma ke ba ki kiyaye kula wasu mazan ba."

Ganin ta yi kasa da kai sai ya canja maganar da cewa, "Mahmoud ya na gaishe ki"

A hankali ta ce "Na gode!"

Sun jima suna hira bayan ya sha ruwa, suka shiga ya gaida Inna, ya ajiye mata kudi, sannan su ka koma zauren, ba su dade da zama ba Baffa ya dawo, ya tarar da su, a kunyace, MK ya sauko daga inda yake zaune ya tsugunna ya gaishe shi. Baffa ya

amsa cike da farinciki, har ya wuce sai ya dan tsaya ya ce, "Da ma kuwa ina son ganin ka, idan ka samu lokaci ka same ni."

Da girmamawa MK ya amsa da Fadin, " Koyaushe ina da lokaci."

Baffa ya ce "To bayan La'asar gobe idan ranmu ya kai."

Sai da ya shige sannan ya koma gun zamansa, Sa'adah na masa dariyar yadda ya takure.

Ya kalle ta ya ce, "Idan akwai abin da ya fi haka na kunya zan ji tunda yarsa nake so ya ba ni, ya kuma san abin da zan yi da ita!" Shike nan ya rufe bakinta ruf.

Ya zuba mata ido ganin yadda ta turo baki gaba alamun fishi-fishi.

Ya waske kamar bai gani ba, ya nisa ya kira ta da alamun seriousness "Sa'adah!"

Ta yi shiru, sanin halinta na shariya da sanin ta ji shi ya zarce da fadin, "Magana za mu yi ta gaskiya, ki nutsu ki ban hankalin ki."

"A kan kunnenki Baffa ya ce za mu yi magana, ga zatona mafi karfi ina ganin zai yi maganar idan mun shirya kanmu na turo da magabatana."

Nan ma ba ta ce kala ba.

Ya nisa ya sake cewa, "Kina ji na kuwa?"

Kai ta daga masa alamun tana tare da shi.

Ya ce, "Tsakaninki da Allah ki fada mini gaskiya don na san yadda zan tunkare shi. Mun kai lokacin da ya kamata a ce mun fahimci juna, maganar aure idan manya suka shiga ta kare fa! Ba maganar canjawa idan dai ba mayar da iyaye abokan wasa za a yi ba.

So nake yi, ki fada mini da bakinki idan Baffa ya tambayi mun shirya kanmu, me zan ce masa?"

Ta yi kasa da kanta ta kasa cewa komai, tsawon minti guda sannan ya dora da cewa, "Kar ki ji nauyin fadar gaskiya na yi miki al'kawarin zan fahimce ki, zan kuma fahimtar da Baffah yadda ba zai ga laifinki ba."

Ta kasa bude baki ta yi magana ita kanta ba ta san me yasa harshenta ya yi mata nauyi ainun ba? Tsawon mintuna yana dakon ta magantu amma shiru.

"Ina ta magana kin yi mini shiru kuma kin san ba na son ina magana kina ji amma ki yi kunnen uwar shegu."

Ta sake yin kasa da kai, da kyar kuma a hankali ta ce, "Ni to me zan ce?"

Bai ji dadin yadda ta ce ba amma sai ya ce, "kinsan me za ki fada mini da zai nuna kin aminta da Ni ko akasin hakan".

Ta kasa fadar ko daya, ya gaji da sauraronta ya ce "Shirunki yana nufin na yi hakuri, na sha kaye a hanun abokan takara".

Yana gani ta bude wayar dake hannunta wacce ta Inna ce ta fito da ita.

Ba zato ya ji wayarsa ta yi kara kadan, alamun shigowar sako (message) bai duba ba ga zaton sa MTN ne.

Ganin ta share ta hau daddana waya sai ya sake jin rashin dadi sosai, a tunzure ya ce,

"Silent again?"

A kunyace ta ce, "Ka duba wayarka!"

Bai yi musu ba ya dauko wayar sa ya shiga ma'adanar sakwanni (inbox) ya ga text din da ya shigo ita ta turo shi. Da sauri ya bude, harrufa uku kawai ya gani.

"*YES*"

Kawai ta rubuta wani irin dadi ya mamaye zuciyarsa da sauri ya ce, "Kin amince mini na turo Sa'adah da gaske?"

Kai kawai ta daga masa don ta sake ba shi tabbaci.

"Alhamdulillah!" Yake ta fadi tare da cewa "Na gode!" Ya bude murya sosai ya kira ta, bai jira amsawarta ba ya zarce da cewa, "Idan fa kin zabe ni har na turo aka nema mini aurenki, hakan na nufin kin rabu da Honorable, da wannan tabbataccen yaron! Da ma kowa da kowa, sai ni kawai.

Kin ga saboda na san kina da damar ki zabi wanda ya miki shi yasa nake danne kishina, amma tsakani da Allah idan har maganar aure ta kullu tsakanin manya dole ki rabu da kowa kin amince?"

Ba wani dogon Turanci ta ce, "E!"

Farincikinsa ya karu ya hau fadin, "In Sha Allah ba za ki yi nadamar zabe na a matsayin mijin aurenki ba."

Shauki ya debe su ba su ankara ba har aka fara kiran sallah sannan ya tafi yana cewa, "Duk yadda muka yi da Baffa za ki ji."

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

TALLAH!

Akwai ingantaccan maganin□□ gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number..... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.....*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah.

41-42

A Daren ranar Baffa ya sake zaunar da Sa'adah tare da mahaifiyarta, ya ce "Ina sane na bar ki kina sauraran wasu bayan Mutari.

Saboda na ba ki damar da shari'a ta ba ki, na kar na aurar da ke bisa dole, duk da shari'ar tace ni na fi cancanta na zaba miki mijin aure kasancewar ki budurwa.

Amma tunda muna wani irin zamani da 'ya'ya suke ganin sun fi iyayensu sanin abin da ya dace da su, ya sa na ba ki damarki, na sha fada miki aure zan miki, ba kuma zan miki auran dole ba, sai dai na dora ki akan shawara mai kyau. Alhamdulillah lokaci ya yi, don haka ki fada mini a cikin masu zuwa wajenki wa kika zaba? Ina son ya turo mini magabatansa a tsayar da magana guda daya."

Ta yi shiru kanta na kasa, Inna ce ta tanka , "Ai na ga alamar sun daidaita da Muutar din."

Hannu Baffa ya daga mata alamun ta yi shiru, ya bude murya ya ce, "Iyah tsakanin Alhaji Mamman da Mutari wa kike so?"

Ta sake yin shiru, ya nisa ya ce, "Dole fa ki yi mini magana saboda duk hukuncin da zan yanke, ya kasance da yardar ki, ba na so daga baya ki ba ni matsala, kwanakin baya da Alhaji Mamman ya same ni ban ba shi amanna ba, amma na ce ya nemi

yardar ki, saboda shi ma mutumin kirki ne, ya samu yabo a wurin mutanen da suke kewaye da shi. Yanzu kuma lokaci ya yi da zan sallami daya a cikinsu."

Inna da ta ke sauraran su ta ji tamkar ta ce Alh Mamman zai sallama amma ta yi shiru saboda bai ba ta damar yin magana ba.

Ya sake kiran ta a karo na biyu, "Iyah!"

Ta amsa murya a dakushe. "Wa zan sallama a tsakaninsu? Ko kuma dukkansu ba ku shirya ba?"

Ta jima kafin ta bude baki ta ce, "Dazu Inna ta fada ai."

Da'di ya kama dukkansu, ya ce, "Kina nufi da Mutari ku ka shirya?"

Kai ta sake yin kasa da shi ba tare da ta amsa ba, Inna ce ta yi fit ta ce "Ka san ba za ta iya amsawa ba, amma na lura da Muutar ne za'binta."

"ALHAMDULILLAH!" Baffa ya furta a fili. Ya zarce da fadin, "Shike nan da kaina zan ba wa Alhaji Mamman hakuri, Allah Ya sanya alkhairi a tsakaninku, ki yi ko yi da uwarki wurin biyayya, Allah Ya tabbatar da alherin da muke zaton sa tsakaninki da yaron nan."

Da haka ya sallame ta wanda da kyar ta iya tashi.

Washegari kuwa bayan La'asar MK ya samu Baffa, zatonsa ya tabbata domin kuwa maganar turo magabatansa ya yi bayan ya tabbatar masa ya yi magana da Sa'adah ta ce shi ne zabinta. Godiya sosai MK ya yi tare da cewa, "Za su zo ba da jimawa ba."

Baffa ya nisa ya ce, "Ka yi shirinka a hankali sannan zan fada maka ni ba a kawo mini lefe sannan ni ma bana yin kayan daki, don haka ka shirya dakin da za ka ajiye ta da iya abin da za ka iya, ni ma zan hado ta da yan tarkacen da zan iya.

Daurin aure kawai za a yi sai kuma uwarta za ta dan yi taron mata a gida, zuwa yammaci da kaina zan kai ta dakinta, Ban yarda da wani taron maza da mata da sunan fati ko wani abu na daban ba! Idan kun tare kuna da ra'ayi, da damar yin walima wannan sunna ce sai ku yi. idan har wannan tsarin ya yi, akan hakan za ka turo mini magabatanka, Saboda idan sun zo, zan sanar da su."

Godiya sosai Mk ya sake yi tare da fadin, "In Sha Allah yadda duk ka ce haka zan yi Baffa, na gode sosai da karamci Allah ya saka da alheri."

Da haka suka rabu MK na jinjina halin wannan dattijon, ko irin su nawa ne suka yi saura a cikin al'ummar mu?

Gefe guda kuma tunanin yadda Sa'adah za ta karbi lamarin yake yi, ko ya ya za ta ji idan aka ce ba za a yi mata lefe ba? Sannan ya za ta yi idan ta gane cewa ita ma haka za a kai ta ba kayan daki, ba biki irin na zamani?😁

Da kansa ya ji dariya ta kufce masa haka ya samu gefe ya yi dariyarsa mai yawa, sai da ya gama a fili ya ce, "Sa'adah big girl ba lefe!" 😁

MK shiru ya yi bai fada wa Sa'adah tsarin Baffa ba, bai san mai yasa yake jin tsoron fada mata ba, ya ja bakinsa ya tsuke, ta ji maganar a bakin wanda ya tsara lamarin.

Takanas 'yan uwan mahaifin MK, Baba Umaru, da Baba Idi, suka taho Kano suka hadu da Alhaji Isa, suka rankaya gidan su Sa'adatu nema wa MK auranta. Kai tsaye ya ce ya ba su sannan sadaki kawai za su kawo masa. Bai boye musu tsarinsa na rashin yin hidima ba.

Dukkansu, sun yi farinciki, sun kuma yi amanna da tsarinsa, suna fadin ai mu ma da ga yau za mu yi koyi da kai don mu sami sauki a cikin zamantakewarmu, sannan

darajar aure za ta karu za a daina fargaban yin sa, saboda an kewaye shi da hidimomi masu wahalarwa.

Baffa ya sake cewa "Na baku wuka da nama duk lokacin yaron ya kammala shirinsa kusa ranar aure da kan ku, sai ku sanar da ni, ina kuma rokon ku fada masa iya abin da zai iya shi zai yi, fatana dai Ubangiji ya albarkaci auren."

Godiya sosai suka yi

suna yaba halin kwarai irin na mahaifin Sa'adah, suka jaddada masa ba da jimawa ba kuwa zai ji ranar da suke ganin ta dace da shirin MK, suka sake yi masa godiyar wannan girman da ya ba su. suka rabu cike da farinciki, a hanyar su ma tattauna karamcin da suka gani suke ta yi.

Alh Isa ya ce, "Ai ni tun zuwan da na yi a farko na gane Mukhtar ya nemo aure a gidan mutunci, sai dai mu yi fatan Allah ya zaunar da su lafiya."

Dukkan su, suka hada baki wurin fadin, "Ameen."

Baba Umaru ya nisa ya ce, "Saboda karamcin wannan Mutumin, bayan sadakin da zan biya wa Mutari har kudin da zai shirya wa yarinyar daki zan ba shi ya kara saboda iyayenta su san muma mun iya karamci."

Su Alh Isa su ma suka hau fadin, "Ai kuwa mu ma za mu sake sabon shiri."

Sai da suka je gidan su MK suka yi wa Hajiya Babba bayanin halin da ake ciki, sannan suka tafi.

Dukkan dangin MK sun karbi tsarin mahaifin Sa'adah, na ba zai yi kayan daki ba, musamman da bai nemi a ba shi wani kudi ba, illa ma lefen da ya ce su ma kar su yi.

Da daddare suna falon gidan gaba'dayansu har Hajiyar Bichi, kasancewar duk sun zo gidan saboda haihuwa da Sameera ta yi, yau kuma aka yi suna, shi ne suka zarto gidan su. Hafsatu ce kawai ba ta nan, saboda a Lagos take aure, Hajiya Babba ta sanar musu.

Ta kare maganar da cewa "Kayan da na fara tarawa na lefe kuwa tabbas zan ba ta, don da sunanta na ke sayan su."

Hayaniya ta cika falon na yadda suka ji dadin tsarin suka hau fadin, "Ai kuwa dai za mu dage mu yi kayan daki masu kyau."

Abbas ya dubi MK ya ce, "Amaryar taka tana da 'kanwa ne?"

Falo ya sake daukar hayaniya Akil ya ce, "Saboda ka ji ba lefe ba bidi'oi?"

Shi dai MK bai sa musu baki ba, suka yi shewarsu, suka gama. Haka ma Hajiyar Bichi uffan ba ta ce ba! Haj Babba ce da ragowan yaran suke ta dabdalarsu.

Kwanaki uku tsakanin zuwan iyayen MK, Alhaji Isa ya sake yin tattaki da kansa ya sanar da Baffa suna son a yi auren bayan karamar sallah watanni biyar masu zuwa. Bai musa ba ya ce, "Allah ya sa ranmu zai kai"

Baffa bai yi kasa a guiwa ba ya hakurkurtar da Alhaji Mamman, da ke ba yaro ba ne rabuwa aka yi irin ta salin alin, duk da bai so hakan ba, amma ya hakura, ya kuma roki Baffa ya ba shi damar ganinta, a karo na karshe. Baffah bai ki ba ya ce zai iya ganin ta. Maimakon ya jira a turo masa ita sai ya ce bari ya je ya dawo.

Ashe sayayya ya tafi lodowa, bayan ya dawo bai jima ba, ya ba wa Sa'adah manyan leda har biyu shake da kayayyaki, yana fadin, "Na gode da mutuntuwa, Ubangiji Ya sanya alheri a tsakanin ki da wanda za ki aura" Ya yi mata sallama ya tafi yana jin ciwon rasa ta don so yake mata na fisabilillahi.

Sai a lokacin Sa'adah ta ji sanyin jiki tana jin tausayin sa na ratsa ta. Tana shiga gida, ta zauna kusa da Inna ta fara bude ledar da ya kawo mata. Ta shiga dubawa, manyan leshi masu tsadar gaske guda biyu, da shadda getzna, ita ma biyu, da kuma atamfa Super Wax ita ma biyu, kowanne kuma da mayafinsa sai turaruka. 'Dayar ledar kuma takalmi da jaka ne har set shida masu tsananin kyau da tsada, da envelope wanda da dukkan alamu kudi ne, za ta ya ga ke nan,

Inna ta ce, "Kar ki bude ki bari Baffan ku ya gani".

Inna tana daga kaya tana fadin, "Wannan ya gane cewa aka yi ya yi ha'kuri? irin wannan kayan sai ka ce mai hada lefe?"

Sa'adah dariya ta yi sannan ta ce, "Kai Inna duk da dai kayan masu daraja ne amma ai ko an sayar da su sai dai a hada lefe irin local din nan."

Zuba mata ido Innar ta yi, sai kuma ta yi kwafa sannan ta ce, "ko ma yaya ne ai an yi 'ko'kari wata ai ba ma za a mata lefen ba, bare ta ga ya yi ka'dan."

Cikin dariya sosai Sa'adah ta ce, "Yo kuwa Inna wacce ba za a mata lefe ba ai sai bazawarar da ta sarayar don tana bu'katar auren, da kuma budurwar da ba ta da daraja ake neman kai da ita."

"Dariya ita ma Innar ta yi tana cewa "Ashe yayarki ma ba ta da daraja! don kuwa babu lefe aka aurar da ita, ba kuma neman kai mu ka yi da ita ba."

"Auran Anty Sumayya ai irin na zamanin jiya aka mata, kar ki ba da misali da auranta"

Ta nisa ta ce, "Iyah ba ki ga kuma saboda mijin natan ya san mutunci ya zame mata irin mijin da ba a cika samun su a Yau ba! Ke da kanki kin san mijinta irin mijin JIYA ne ba na YAU ba, ki yi fatan dacewa kawai, duk auran da aka ƙaranta wahala da bidi'a ya fi karko ya fi albarka".

Cike da rashin gamsuwa ta ce, "A'a Inna gara dai a yi maka din, mijin ma ai sai ya raina ka, danginsa su isheka da gorin sadakar ka aka ba shi."

Shiru Inna ta yi ta kyale ta, tana tunanin ashe akwai kallo ranar da tasan irin auran da za'a mata.

Baffa da ya ga kayan da Alh Mamman ya kawo bai yi fada ba, kamar yadda yake yi a baya, ya farke envelope din sai ga rafar dari biyar wato dubu hamsin wanda ta zarce darajar dubu darin yanzu.

Ya ajiye kudin, kayan kuma ya ce su dauka ta yi amfani da su, tunda dai sai da aka fada masa gaskiya sannan ya ba ta. shikenan rabuwar su da Alhaji Mamman.

Tunda aka tsayar da maganar aure Sa'adah ba ta sake tsayawa da saurayi a fili ba, sai ta waya wanda suke cika mata waya da kudi, sai kuma Khalil da ta kasa rabuwa da shi duk da ba ta yarda ya zo gidansu sai dai idan ta je gidan su Halima ko kuma idan ta je gidan su Zainab Ma'aji sai ya zo.

Soyayyarta da MK a gurinta za ta ce ba laifi, idan ya kira ta a waya yana dan jimawa su yi hira, haka nan yanzu sau biyu ya ke zuwa zance a sati, wani zubin ma har sau uku.

Amma dai ita ba sosai ta gamsu da kulawarsa ba, kawai dai tana bin sa da yadda yake yi, da fatan Allah Ya sa ba soyayyar ne bai iya ba ta bakin Halima da Safina, da suke kushe shi duk da sai yanzu da aka tsayar da maganar aure, suka san da gaske soyayya suke yi.

Kiri-kiri suka nuna mata me zai sa ta yi gangancin barin Alhaji Mamman inda za ta huta, ta bige da auran mai fama da alli da hidimar gidan su?

Ita dai Sa'adah sai dai ta ji su, ta yi shiru. Musamman da ta ta'ba ce musu ba son sa take yi ba Baffa ne ya mata dole, ai nan ma suka mata ca tare da cewa, "A wannan karnin na 21st century za a miki dole?"

Ta yi shiru tana jin yadda suke ta sakin maganganun rashin 'da'a tare da ingiza mai kantu, suna jaddada mata da dai ta auri mugun Malamin da ya gama tozarta ta a bainar nasi, gara ma ta auri Khalil Ibrahim sa'anta.

Shiru take yi, wani lokacin zuciyarta ta shiga wasiwasi akan MK Bichi, musamman yadda bai kai su Khalil nuna mata soyayya ba. Amma dai ta san ba ta isa ta koma ta ce wa Baffan ta ta fasa ba.

Alkalamin

Surayya Dee

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

TALLAH.

_Akwai ingantaccan maganin gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number..... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar

naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.....*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

43-44

A kwana a tashi ba wuya wurin Ubangiji. Watanni biyu suka zo suka shude tamkar walkiya, mai ya'ki da zuciyarsa kadai ke ribatar lokacin sa a cikin wannan zamanin da ababen shagala suka kewaye shi.

A wannan lokacin manhajar 2go ta bullo, matasanmu samari da yanmata suka yi tururuwar karban wannan sabuwar manhajar wanda hakan ya taimaka wurin sake ruguza tarbiya matasa da yawa, saboda yadda ake hira da musayen hotuna na rashin da'a ba tare da jin shakku ko nauyi ba.

Sa'adah na cikin jerin yan matan da suka yi tashen 2go da taimakon su Safina da Halima, yini take yi da waya a hannu har sai da Inna ta fahimci sabuwar rayuwar da ta shiga na yadda ta fi bawa waya muhimmanci fiye da komai.

Ada kafin Inna ta fito da safe Sa'adah ta kammala komai na gyaran gida, wani lokacin har abin karin kumallo za ta yi, musamman idan Baffa ba ya gari, amma a yanzu sai ta kai rana ba ta share gidan ba, ga wanke-wanke a gefe kudaje na bin su, ko karyawar ma sai Inna ta yi ta faman kiran ta sannan za ta fito, Nan ma tana cin abincin amma wayar na hannunta, tana ta latse-laste tana murmushi.

Wannan abin ya yi matu'kar damun Inna musamman yadda ta lura wanka ma Sa'adah sai ta kai la'asar ba ta yi ba, sabanin lokutan baya da sanyin safiya take wankanta da zarar ta kammala ayyukan gida, amma yanzu sai yamma likis ko ma dare.

Ranar wata Litinin aka tashi da rashin wuta a unguwar gabadaya, cikin rashin sa'a ta kwana da rashin caji a wayarta, don haka sai ta tashi sukuku da rashin karsashi. Tana kwance lamo a kan katifarta, ta kalli agogon bango dake jikin dakin, ta ga karfe 7 na safiya, sai ta ga lokacin ma baya gudu don haka sai ta yun'kura ta gyara dakinta, ta gangara tsakar gida. Kafin wani lokaci da ba shi da yawa ta gama komai har wanke-wanke, gefe kuma ta dora musu abin da za su ci.

Koda Inna ta fito ta gan ta, a tsakar gida sai mamaki ya kamata, musamman yadda ta gan ta ba waya a hannunta, ta gaishe ta ita ma ta amsa da walwala, sai da suka karya, ta yi wanka ta shirya ta yi fes da ita, ta fito tsakar gida ta sa tabarma ta zauna saboda lokacin zafi ne.

Sai lokacin Inna ta dube ta ta ce "Wannan ita ce Iyah da na rayu da ita, wannan ita ce Iyarmu, ta jiya da ragowar kwanakin da suka shude ba Iyar mu ba ce ma'abociyar aikin gida da kuma ado"!.

Kunya ta kama Sa'adah ta sa hannunwanta biyu ta rufe fuskarta, ita kanta ta san ta shagala, tana son ta tashi ta yi ayyukanta, amma sai ta kasa ajiye wayar tana ganin bari a dan jima, a haka har sai lokaci mai yawa ya tafi ba tare da ta an kara ba.

Cikin hikima Inna ta sake fadin, "Ko a mafarki idan aka nuna mini wai zai ki zama yadda kika zama Iyah zan karyata na kuma yi gaggawar neman miki tsari da wannan karko irin na kifi.

Ta ya ya za a ce kin rayu kina tafiyar da komai na aikin gida da tsaftar jikinki akan lokaci da kuma kuzari, amma sai da aurenki ya zo gaf kuma sai lalacewa ta zo miki? Wayar nan mai tsada ta zamani hatsarin dake cikinta ya fi alherin da ke tare da shi. Ki rabu da wannan shiriritar tun ba ki fada tarkon da za ki kasa fitowa ba!"

Jikin Sa'adah ya yi sanyi sosai tana gaskata mahaifiyarta, yau kadai da wayar take kashe ta samu rarar lokaci har sallar walaha ta yi. Ta kuma samu sukunin tattaunawa da uwarta, ta yi abin da ya dace na ayyukan yau da kullum.

Inna ta sake nisawa ta ce, "Ba namijin da za ki je kina masa wannan ba'kin dabi'un da kika fito da su, ku samu zaman lafiya da shi, duk son da yake miki kuwa. Ban hana ki amfani da waya ba, amma ki dinga ajiye ta sai kin kammala komai na aki, nauyi ne zai sake kama ki, shi namiji idan yana da mata komawa yake yi tamkar jariri komai sai an yi masa, ta ya ya za ki iya kula da miji da hidimar gida da wannan danne-dannen wayar da tun ana ganin na 'dokin wayar ne har kuma ya koma na kauyanci da asaranci ya zarce hankali da ka'ida."

A hankali Sa'adah ta ce, "Zan gyara Inna."

"Na ji za ki gyara, sai mai za ki ce mini kuma"? Inna ta fadi haka tare da zuba mata ido.

Cikin kunya "Sa'adah ta ce kai Inna don Allah, to ki yi hakuri."

Kai tsaye ta ce, "Tafiya za ki yi ki fara rayuwa da wani mutumin da ba ki saba da shi ba, ba shi kadai zaman zai kasance ba har da dukkan ahalinsa don haka ki koyi ba da hakuri idan kin yi laifi, ki kuma zama mai karbar gyara yayin da aka gyara miki laifinki, wannan shi ne mafi dadin zama a cikin mutane, na lura da ke ba da hakuri na miki nauyi, sai tura ta kai bango kike tuba wanda alamu ne na girman kai. idan mijinki ya gane kina da girman kai kuwa, wahalar ki zai yi don shi ma girman kan zai miki indai ya san ciwon kansa, sai dai idan solobiyo ne."

***

Bangaren MK yana ta Shirinsa musamman na gyran gidan da zai zauna, saukin da ya samu gidan mallkinsa ne da ya fado a gadonsa, tun lokacin yan haya suke ciki sai yanzu aka tashe su yake gyara, a unguwar Gadon Kaya gidan yake, ba wani babba ba ne amma tsarin gidan ya yi kyau, falo ne matsakaici mai dauke da manyan dakuna biyu da bandaki a cikin daki daya. Sai tsakar gida mai matsakaicin girma, daga gefe wani dakin ne shi ma da bandakinsa, sai daya gefen kuma kicin ne da wani bandakin karami, daga harabar gate kuma akwai karamin filin da zai dauki mota guda daya, ya shuka flowers sun fara fitowa wanda nan gaba za su 'kawata gurin.

Gini ne mai aminci amma ba tayals ba ne siminti ne a dakunan.

Shi kuwa a kokarinsa na son dadawa amarya Sa'adah yake son sanya mata tayals a falo da bandaki duk da a lokacin an fi saka carpet irin dan yankan nan.

Aka fara aikin gida sai lashe kudi yake yi sosai, wanda hakan ya sake mayar da MK ya zama very busy kullum aka tashi a makaranta yana gidan gurin masu aiki, ko wurin neman ku'dinsa ba shi da lokacin kansa wanda hakan ya sake karfafa

zaton Sa'adah na bai iya soyayya ba.

Shi yasa take kula Khalil har yanzu! take kuma shan soyayyar 2go, idan MK ya zo shike nan idan bai zo ba, huta roro ba ta kewarsa.

Sakamakonsu ya fito wanda WAEC din Sa'adah ta kasance ba yabo ba fallasa, amma NECO ta yi kyau sosai, a lokacin suka shirya bikin kammala makaranta da murnar sakamakonsu, ba laifi a shekarar an ci NECO sosai.

A *HANG OUT* suka shirya yin bikin, a lokacin gun ne yake tashe a wurin samari da 'yan-mata, da kyar Inna ta bar Sa'adah ta halarci taron.

Shi ma sai da ta yi karyar yayar Zainab ce ta haihu za su je, nan kuwa iya su 4stars ne, sai samarinsu na aji Irin su Khalil da kuma saurayin Halima Sagir.

Haka suka yi wannan bidirin. Sa'adah a takure saboda wannan ne karon farko da ta ta'ba zuwa wani guri da sunan party, kuma a cakude da maza sai abin ya zame mata bako, ga dai kayan kwalama cike da teburinta hatta ice ream da ta ke jarabar so bata iya 'dan'danawa a bakinta ba, Khalil sai kaffa-kaffa yake yi da ita don ta sake, ita kuma sai raya ina ma kulawa da iya soyayyar Khalil, MK ne ya iya su.

Tana cikin wannan tunanin wayarta, ta shiga ruri, tana dubawa taga MK ne, ta 'ki amsawa, tana tunanin idan ya ji wannan kidan sai ya ishe ta da tuhumar inda take.

Bai daina kiran ba har sai da ta yi shahadar amsawa, jin hayaniya da kade kade yasa shi tambayar inda take, ta karkace baki ta shirya karyar ta raka Zainab gidan suna, yayarta ce ta haihu, ya yi shiru ba don ya gamsu ba, saboda ki'dan music yake jiyowa ba dan ka'dan ba.

Ya nisa ya ce, "Son ganin ki nake yi, ya za a yi ke nan?"

A ki'dime ta ce, "Ai anjima za mu dawo na san dai zuwa magariba mun iso."

Da sauri ya ce, "Har Magariba za ki kai a waje? yanzu karfe 4, ki tabbatar biyar da rabi ta miki a gida, ina jiran ki."

Ya kashe wayarsa ba tare da ya jira mai za ta ce masa ba, saboda bai gamsu a gidan suna suke ba.

Ta yi shiru da waya a hannunta, tana tunanin yadda MK ya mata magana a gadarance tamkar ya zama mijinta, wani sashe na zuciyarta kuma so yake ta isa gida kafin lokacin da ya ce din.

Duk kokarin Sa'adah na son ta bar wurin da wuri ya ci tura, su Safina sun hana ta, kan dole ta kashe wayarta don kada MK ya sake samun ta.

Sai bayan Maghrib suka kawo ta gida, ita ce a gaban motar su Halima na baya, duk yadda ta so su ajiye ta a hanya Khalil kin yarda ya yi, don so yake mugun malaminsu ya ganta a motarsa tunda a unguwar yake sana'ar sa ta wanzanci, ya san kuma saboda shi take son su ajiye ta daga nesa.

Su Halima na sake zuga shi ta hanyar cewa, "Idan ka ajiye ta a hanya wallahi soyayyarka ba ta kai ba!"

Dai-dai lokacin MK yana kofar shagon kusa da jikin gidansu ana masa gyaran tayar mashin dinsa da ta yi faci, daf da shi Khalil ya tsaya, tsaleliyar mota(Continue Discussion) a wancan lokacin ita ce motar da take tashe ko'ina ka shiga maganar motar ake yi wanda shi ma ta mahaifiyarsa ce ya dauko, gaban Sa'adah ya sake tsananta bugawa musamman yadda hankalin mutanen wajen ya juyo kan motar, ga ta ita ce a gefen hannunsu, ma'ana tana bude kofa dole kowa ya gan ta.

A tsarin mahaifinta ba ma MK kawai ba, bai kamata mutanen gurin su gan ta ta fito a motar saurayi a irin wannan lokacin ba.

Ta rasa yadda za ta yi ta fita, musamman yadda kayan jikinta suka kamata sosai duk da mayafin babba ne. Sai dai shara-shara ne, hijabi ta saka da za ta fito, saboda Inna ba za ta barta ta fita da wannan dinkin ba wanda anko ne telan Safina ya dinka musu, da ma nufinta tana isa zaure ta maka Hijabinta baki alaikum.

Kunya da tozarci iri-iri suka dinga bin ilahirin jikinta, ganin yadda ta kasa fita a motar ya sanya Khalil fita ya zaga, ido biyu su ka yi da MK ya hura hanci ya dauke kai, ya bude gaban motar yana fadin fito, da kyar ta fito fuskarta a kasa ta kuma ja mayafin har kanta aka bita da ido, mazan da suke gun dukkansu a ransu yaba surarta suke yi har daya a cikin su wanda dan kwaya ne ya kasa hakuri, a fili ya furta "Kai waccan baby an zuba mata halitta Billahillazi da ina da kudi da na yi kerwa da ita."

Tun tsayuwar motar MK ya ji zuciyarsa ta tsinke musamman da ya ga mace a gaban motar ta kare fuskarta, haka kawai ya dinga fatan kar ta kasance Sa'adah ce, ya san zai yi wahalar gaske ta zama ita ce, amma sai ya kasa nutsuwa, a lokacin da ya ga Khalil ya fito da gadara sai ya tabbatar Sa'adatu ce, take ya ji wani irin matsanancin kishi ya kama shi, irin kishin da yake danne soyayya.

Maganar da wannan saurayin ya yi na yabon surar ta sai ya sake ninka bacin ransa wanda bai taba Jin irin sa a tsawon rayuwarsa ba.

Zuciyarsa ta yi zafi, take ya ji yawun bakinsa ya kafe makogaronsa ya bushe, kansa ya sara da wani irin ciwo mai tsananin gaske.

Ashe Sa'adah da Khalil ta fita, ashe shi yasa ta kashe wayarta, don ta nuna masa tana tare da wanda ya fi shi, ta kuma yarda ya kawo ta har titin da take da tabbacin zai iya ganin su a tare, karo na farko da ya ji ya yi kuskuren barin Farida saboda Sa'adah.

Ya tabbatar ta fi ta son sa kawai dai shi Sa'adah ce ta fi shiga zuciyarsa, kuma ta fi daukar hankalinsa.

Ko ta kan gyaran mashin din bai tsaya ba, ya tari abin hawa ya nufi gidansu, kafin ya isa wani irin zazzabi da azababben ciwon kai sun masa mugun kamu.

Alkalamin

SURAYYA DAHIRU

✍✍.

 HALIN YAU!

•·•·•·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·••·•·•·•·•·•·•·•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

TALLAH.

Akwai ingantaccan maganin gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number..... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.....*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah.

45-46

Tana shiga zauren gidan ta fito da hijab ta sanya, sukuku ta shiga gidan. A tsakar gidan ta sami iyayenta. Tsoron da ke cikin zuciyarta ya sake bayyana a fuskarta da jikinta.

Baffa ne kawai ya amsa sallamar, da 'kyar ta tsugunna ta gaishe shi, ya amsa ba sakin fuska, ya kalle ta fuska ba wasa ya ce, "Daga ina ki ke?"

Cikin rawar murya irin ta rashin gaskiya ta ce, "Zainab na raka gidan yayarta kuma sai da na tambayi Inna."

A kufule Inna ta ce, "Tabbas kin tambaye ni amma ce mini kika yi ba za ku dade ba, don haka na gode miki da cika al'kawari."

Ganin yadda ran Inna ya baci sosai sai shi kuma ya sassauta, ya mata nasiha tare da cewa, "yarinyar kirki in dai ta san kanta, killace kanta take yi a gida, bai kamata dare ya riske ta a waje ba."

Har ya sallame ta sai kuma ya ce, "Yawwa dama zan fada miki, aurenki bayan sallah za a yi, nan da wata uku kenan.

Bayan haka kuma na sanar da iyayen yaron cewar kar ya yi lefe, ni ma kuma ba zan wahalar da kaina wurin saya masa kayan daki ba, ke zan ba shi ina kuma da yakinin na miki tarbiyar da zai sami nutsuwa da ke. Uwarki kuma ta koya miki yadda zai yi alfahari da ke a matsayin uwar yayansa. Haka na yi wa Sumayya har yau din nan da ta kai shekaru goma a dakinta ban taba jin ance mini ga wani abu na kaico daga gare ta ba, mijinta kullum kara girmama mu yake yi, Ina fatan ki yi koyi da ita, Tashi ki je."

Ta mike ta wuce dakinta cikin wani irin yanayi, tana zuwa ta fadi kasa ta fara kuka kasa-kasa, tana jin karshen tozarci an yi mata.

Ta ya ya za a dinga hada Sumayya da ita, ai ba lokacin su daya ba, sannan ba iyayen mijinsu daya ba, a wannan zamanin ma an kai yarinya da kayan daki idan ba na alfarma ba ne, dangin miji suna yi wa yarinyar izgili da habaici, to ina kuma ita da za a kai ta tsurarta? Wanne irin raini da kaskanci za a janyo mata? Ba'kin cikinta ya ninku ta rasa inda za ta tsoma ranta.

Ashe shi yasa MK yake mata gadara da isa, saboda an nuna masa sadaka za a ba shi an dauke masa lefe? Shima kuma kar ya sa rai za a je a yi masa jere. Ba ta san lokacin da ta bude murya ta dinga zunduma ihu ba.

Daga Inna har Baffa a kidime suka mike suna rige-rigen isa dakinta a tuninsu wani abin tsoro ne a dakin, ko maciji ko kunama ta harbeta.

Sai dai ganin ta ras illah kukan da ta bare baki tana yin sa tamkar yarinya yar karama yasa suka yi cirko-cirko! Baffa ne ya ce, "Mene ne ya saki wannan ihun sai ka ce wacce ba ta zuwa Islamiyya, ba za ki ambaci Allah ba! Sai ki cika mana kunne da kuka har da ihu?"

Cikin kuka sosai ta ce, "Ka taimake ni Baffa! kar ka kai ni ba kayan daki wallahi gori za a yi mini, ko a yi ta zunden sadaka ta ka bayar." Ta karasa cikin gunjin kuka.

A zuciye Inna ta ce, "Watau ke ba za ki bi shi ba, sai shi ne zai bi ra'ayinki, ke kullum sai an yi artabu da ke? Kin taba ganin wanda ya bi iyayensa bai ci ribar rayuwarsa ba? Ashe ba za ki koyi da yayar ki ba?"

Ta sake kara sautin kukan ta ce, "Ai samun irin mijinta da yan'uwansa sai an tona a wannan lokacin, sannan kuma ni da ita akwai banbanci."

Takaicin ta ya kama Inna ta ce, "Banbanci kuwa a bayyane, ita ta yarda duk talaucinmu, mu ne iyayenta, za mu yi iko a kanta ba tare da ta ga gidadancinmu ba, sannan karatu kadan ta yi amma mai cike da ladabi da biyayya, in sha Allah Ubangiji ba zai kunyata ta ba."

Tana fadin hakan ta fita ta bar su da Baffa.

"Iyah!" Ya kira ta da muryar da bai saba mata irin ta ba, tunda shi kullum a cikin lallashi da tausasawa yake mata magana.

"Na riga da na zartar da maganar nan a gaban Mutari da iyayensa, ba zan koma na ce na fasa ba. Ko a fuska kika nunawa yaron nan tsarina bai miki ba, ki tabbatar kin nuna ban isa da ke ba, ba kuma zan sake yin iko akan ki ba."

Ya na rufe baki ya juya shi ma ya fice abinsa, sai ji ta yi kukan ya tsaya mata cak!

Amma wani irin ba'kin ciki take ji ya shake mata wuya da zuciya. Da 'kyar ta fita ta yi alwala ta yi sallar Maghrib da Isha wanda ba nutsuwa a cikinsu.

Da rarrafe ta isa kan shimfidarta, hawaye na bin fuskarta, ta ya ya za a mata irin wannan auren sai ka ce mutanen da? Ai ko shi Baffan da zai auri Innarsu, ya mata hidima, ita ma kuma da kayan dakinta aka kawo masa ita har yanzu gadonta na aure ne a dakin, duk kuwa da auren zumunci aka musu, shekaru kusan talatin. Amma sai ita a wannan lokacin za a mata irin wannan auren, kuka ya sake balle mata.😭

Tsawon lokaci tana kuka har kanta ya fara ciwo, a ranar dai ba ta yi wani cikakken barci ba, ba ta tuna matsalarta da MK ba sai da Asuba.

Tana idar da sallah ta ciro wayarta a caji ta lalubo lambar MK ta kira, har ta katse bai dauka ba, ta kira ya fi sau biyar amma bai amsa ba. ta ja wani dogon tsaki tana furta "Sai ka yi ta yi."

Ta kwanta ta yi shiru, amma sai ta kasa hakuri, ta sake kiran sa, nan ma bai dauka ba, ta yi ta kira har ta gaji, takaici ya sa ta yi jifa da wayar.

Har rana ta fito tana kwance ta ki fita, fishi sosai take yi, ga idanuwanta sun kunbura saboda tsabar kuka.

Inna kuwa ko ta kanta ba ta bi ba, ta yi dukkan ayyukanta, ta yi abin karin kumallo suka karya da Baffa amma ba ta nemi Iyah ba bare ta ba ta.

Sai da Baffa zai fita ne ya tsaya bakin kofar dakinta ya kira ta. Ta fito sanye da hijabi duk fuskar ta a kumbure, ta tsugunna ta gaishe shi, ya kalle ta cike da kulawa ya ce, "Iyata yau ban ji motsin ki ba ga shi har zan fita, kin san idan ban gan ki ba yini zan yi ba kuzari".

Ta sake yin kasa da kanta hawaye na cika mata ido, "maza fito ki yi wanka, ki sami abinci ki ci idan zan dawo zan taho miki da indomie har da Sadine na gwangwani, da ma kwanaki kin ce mini indominki ta 'kare, yau zan sayo miki ki ajiye a dakinki har da madara."

Cikin kuka ta ce, "Na gode"

Ya tafi yana jin kukan ta har cikin ransa, ya na raya yadda Sumayya ta zarta ta biyayya da gudun zuciya amma Iyah tafi shiga ransa matu'ka da gaske.

Ko da ta koma dakin sai ta sake dasa sabon kuka mai cike da kururuwa, yin sa take iya karfinta, fishin da MK ya dauka ya sake dagula mata lissafi.

Tun Inna na danne bacin ran ihun da Sa'adah ta cika mata kunne da shi, har ta kasa jurewa.

Don haka ta shiga 'daki ta samo wani danko mai kauri ta nada a hannunta, ta nufi dakinta, tana shiga kuwa ba bata lokaci ta shiga zabga matata ko ina, da iyakacin karfinta, da kyar Sa'adah ta kwace ta fice a guje, ta nufi hanyar zaure ta tsaya tana kuka sosai.

Ta dade kafin ta dawo gidan, tana rabe-rabe, Inna ta kalle ta rai a bace ta ce, " Idan kin san za ki ta sani a gaba kina mini kukan iyashege ki juya ki tafi duk inda za ki shiga, watau ni kika raina? Kin ga Baffanku ya fita shine za ki 'bude mini wannan ja'irin bakin naki da bai iya komai ba sai 'kulla karya da munafunci kina mini ihu. Wai har kin yi wayon da yafi nawa, ni za ki yiwa karyar Zainab za ki raka unguwa? Ashe da wannan shedanun kawayen naki masu yi wa Babba kallon raini kuka fita, har kin yi lalacewar da za ki shiga gaban motar namiji ya kawo ki har kofar gidanku, ki fito akan idon jama'a, oh ni Salamatu wacce irin yarinya nake tare da ita ne haka?"

Ta Fadi hakan tare da tafa hannu tana salati.

"Wai kuma don ki bata ni a gunsa shi ne zaki ce nasan zaki fita, to don uwarki daga yau kika kuskura kika ce mini za ki fita da sunan zuwa unguwa wallahi sai jikin ki ya fa'da miki. Na daina raga miki tunda ke rarrashi baya bi da ke, kafin nan kafin ki bar gidan nan sai na miki tabbuna ba ma tabo ba. Tunda nake da Baffanku bai taba ganin kasawa ta ba sai akan ki, jiya da daddare ba abin da bai fada mini ba, bayan an tabbatar masa a mota aka kawo ki."

Jikin Sa'adah ya yi sanyi kalau, ta yi shiru amma hawaye bai daina zubo mata ba, tana jin tsanar Khalil sosai a ranta duk shi ya janyo mata wannan tashin hankalin, da ya ajiye ta a hanya ai da ba wanda ya ganta, ga fushin Uncle MK, ga fishin Baffa duk da dai shi mai yawan yi mata afuwa ne. Amma yau har zane ta Inna ta yi, ba za ta iya tuna yaushe rabon da Inna ta dake ta irin haka ba.

A darare ta shigo ta shige dakinta, ta fito da shirin wanka, sai da ta fito ta shirya, sannan ta je ta tambayi abincinta, ba tare da ta kalle ta ba ta ce, "Ban yi dake ba tabbatacciya! Kina kwance na tashi na yi komai saboda zuciyarki ba imani balle tausayi, amma har ki iya cewa ina abincinki? Saboda ga baiwa kin ajiye, to ga tuwo can da kika raina sai ki hada wuta ki 'dumama, idan kuma kin fi nan sai ki zo ki dora abincin rana idan kin gama sai ki ci."

Tana kaiwa aya ta ja bakinta ta tsuke.

Cikin rawar murya ta ce, "Me zan dora?"

Kamar ba za ta kula ta ba sai kuma ta ce, " Dambu!"

Hawayen da ta ke matsewa ya balle tasa gefen dan'kwalinta ta goge, sannan ta ce, "To!"

Haka ta hau aikin sarrafa dambu tana goge hawayen da ya'ki yankewa ta san dan a musguna mata yasa aka 'kir'kiri yin abincin da zata jima bai kammala ba. Ba ta sami kanta a hannun Inna ba sai wajen karfe uku, saboda yadda ta'ki sa mata hannu, ada idan za su yi dambu kusan Inna ke jagorantar yi, kawai sai dai Sa'adah ta sa ido tana lura tare da gyara gyada ko zogale.

Amma na yau komai sakar mata ta yi, ta kuma kara yawansa a cewar ta za ta aika wa makwabta, ita dai Sa'a ba bakin musu saboda a tsorace take da ita don ba karamin duka ta mata ba.

Faranti guda ta cika da danbun ta debi ruwa a randa mai sanyi ta sami inuwar bishiyar dake tsakar gidan, ta fara ci hannu baka hannu kwarya tamkar ba Sa'adah mai cin abincin a gayance ba.😁

Inna na kallon ta a ranta ta ce, "Ja'ira yau kin gane yunwa ba kanwar uwa ba ce."

Sai da ta share abincin nan tas ta yi gyatsa gumi ya karyo mata, ta yi Hamdala. Ta jima a zaune a gun, sai da aka fara kiran sallar la'asar sannan ta cika bokiti da ruwa, ta jira Inna ta fito a bandakin sannan ta shiga wanka.

Sai da ta yi sallah sannan ta shirya, kana kallon ta kasan zuciyarta ba walwala, tana zaune waya a hannu tana ta kiran MK amma ya ki dauka, lamarin da ya sake dugunzuma damuwar da take ciki, a fili ta ce, "Me yasa nake son mutumin nan ne?" Ta sunkuyar da kai tana tunano adadin yadda take shiga damuwa saboda shi.

Haka ta ci gaba da kira ba kakkautawa har ta gaji. Sai kuma ta koma tura text din ban hakuri da maganganun soyayya masu taushi. Amma ko sau daya ba ta ga amsa ba duk kuwa da sun nuna mata sun yi delivered, (Watau sun je).

Wasa-wasa sai da aka shafe sati biyu ba ta ji daga MK ba idan kuma za ta yini tana kira ba zai dauka ba.

Abin ya yi matu'kar tayar mata da hankali tun tana boyewa har abin ya fara fin karfinta, ta zama wata iri, ko abinci ba kasafai take iya ci ba. Ga Inna ba sakar mata fuska take yi ba, abin ya hade mata biyu, ta fara ramewa a tsaye.

***

Bangaren Mk kuwa ba karamin zafi ya dauka da Sa'adah ba, kwana biyu ya yi a kwance yana fama da ciwon kai da wani irin zafi a cikin kirjinsa. Idan ya tuna yadda Sa'adah ta fito a gaban motar Khalil jikinta a dame sai ya ji tamkar ya shide, haushin ta yake ji ba ka'dan ba, gara ya gan ta da Alhaji Mamman akan wannan dan iskan yaron, so yake ya hakura da Sa'adah amma kunyar mahaifinta yake ji musamman yadda ya girmama lamarinsa.

Sannan ya san ko giyar wake yake sha bai isa ya tunkari iyayensa maza da maganar ya fasa auren ta ba, ya rasa inda zai tsoma ransa. Yana ganin yadda kiran ta yake shigowa wayarsa ba adadi. To me za ta ce masa? Ta je su karata da wanda ta zaba.

Kwanaki na ta shudewa, damuwar da Sa'adah ke ciki na sake karfafa, tsawon kwanaki ashirin ke nan MK bai dauki kiranta ba, balle kuma shi ya kira.

Ranar wata Laraba da daddare suna zaune da Inna a tsakar gida amma kowa na gefensa, Yan NEPA suka kawo wuta, daidai inda Sa'adah ke zaune hasken ya fi karfi, Inna ta zuba mata ido tana kallon yadda ta lalace ta birkice. Nan da nan tausayin ta ya kama ta, sai dai ba ta nuna mata ba, amma ta kudiri aniyar yi mata sassauci.

Washegari kuwa da walwala ta amsa gaisuwar Sa'adah, ta daina daure mata fuska, idan ta mata magana cikin dadin rai take amsa mata, sab'anin lokutan baya da hantara ce a tsakaninsu.

Afuwar da Inna ta yi mata yasa ta samu sau'kin halin da take ciki, amma har yanzu ba ta da kuzari da walwala, Inna da kanta ta ce mata, "Idan ban manta ba na kai wata ban ji Muutar ya zo ba."

Sunkuyar da kai kawai Sa'adah ta yi ta kasa cewa komai! Amma idanuwan ta sun kawo 'kwalla.

Ganin yanayinta ya tabbatar mata akwai matsala a tsakaninsu ta ce, "Hala kin sallame shi saboda ba zai miki lefe ba?"

Da sauri ta ce, "Haba Inna! Ni wallahi ban sake tayar da maganar ba."

Cikin takaici sosai Inna ta ce, "To labarin abin da kika aikata ya same shi."

Ganin hawaye ya kwace ma Sa'adah ya sa ta hadiye fa'dan da za ta fara yi mata, sai ta bige da fadin, "Kadan ke nan a cikin sakamakon da mai yin 'karya ya ke fuskanta."

A ranta kuma tana raya dole su yi magana da Baffa akan rashin zuwan MK shirun ya yi yawa.

Washegari Zainab ta kawo mata ziyara, suna zaune kan katifarta, "Sa'adah me yake damun ki haka?" Zainab ta fada cike da mamakin ramar da ta ga Sa'adah ta yi.

Bata boye mata halin da take ciki ba, ta zayyane mata komai.

Cikin takaici Zainab ta ce, "Ai indai kina biye su Safina sai sun kai ki sun baro, ka'dan ke nan."

Tana kuka ta ce, "Ni yanzu ki nemo mini mafita don Allah!"

"E ai yanzu da yake ta kwabe miki za ki neme ni, amma lokacin da kika bi su ai ban sani ba."

Waya ta mi'ka wa Sa'adah tana fadin, "Saka lambar Uncle Mukhtar din mu kira shi da layina." Jikinta na rawa ta karba ta hau jera zababbun lambobinsa, tana fatan Allah ya sa ya dauka tunda har layinta da bai san da shi ba ta sha 'kiran ba ya 'dagawa.

Cikin Sa'a kuwa ya dauka! Zainab ta gaishe shi, ya tambayi wacece?

Ta amsa da gabatar da kanta, sai ta shiga ba shi ha'kuri a madadin Sa'adah, ya yi shiru har ta gama.

Ya yi murmushi mai sauti sannan ya ce, "Ba dan ina ganin hankalinki ba da ba zan saurare ki ba. Ki yi hakuri, ki cire kanki a cikin wannan maganar, ba zan iya da halin yarinyar nan ba, duk yadda nake zaton ta ta wuce nan". Yana fadin haka ya katse wayarsa.

Bugun da zuciyarta take yi ya sake tsananta, a rikice ta ce "Zainab mai yake nufi? Ya fasa yi da ni ke nan?"

Cikin son ta kwantar mata da hankali ta ce, "Ba fasawa zai yi da ke ba In Sha Allah! Kawai ya yi fishi ne sosai, ai kema kin san ba ki kyauta masa ba."

Ta dade tana kwantar mata da hankali, kafin ta mata sallama ta tafi da al'kawarin za ta sake tuntunbar sa.

Kwanaki biyu da zuwan Zainab, Anty Sumayya ta yi waya Sa'adah ta je ta karbo mata sa'ko a karkasara gidan kawarta.

Akan dole Inna ta barta ta fita bayan ta sha jan kunne da nasiha iri-iri akan kar ta biya ko ina, har kunya ta kama Sa'adah ta na jin ita ta janyo wa kanta rashin yarda a idon iyayenta.

Tana karbo sakon ta juyo, duk da yadda Anty Walida ta yi nacin ta zauna ta karasa yi mata yinin, ita kuma ganin biyu da rabi ta yi yasa ta gaggauta fitowa dan ta zartar da kudirinta na son ganin Mk a yau.

Kai tsaye FGC Kano ta sauka, sai dai ba makarantar ta shiga ba, gangare can gefe ta tsaya inda suka ta'ba tsayawa da shi, ta san kullum ta nan ya ke bi. Cikin sa'a kuwa ba ta dade tana jira ba ta hango shi, yana doso inda take, a kafa yake tafiya. Ta ce, "Ko ina ya baro dan mashin 'din?"

Sanye ya ke cikin 'kananun kaya yana rataye da jakar da yake zuba takardun shi, ya mata kyau sosai duk da ta ga ya dan zube kadan.

Sai da ya wuce ta sannan ta bi bayansa, jin ana ta bin bayansa yasa shi jiyowa, ba zato idanunsu suka sarke, ya hade girar sama da ta kasa tamkar bai ta'ba dariya ba, ya juya ya ci gaba da tafiyarsa tamkar bai gan ta ba.

Sai lokacin ta yi magana "Uncle na yi kewar ka, idona sun yi kukan rashin ka!"

Ya ji ta sarai, bacin ransa ya dawo sabo, ya rasa wane matakin zai ajiye Sa'adah, duk inda ya ke ajiye ta, yau ya tabbatar masa ta kere gurin!har ta san ta bi saurayi gun aikinsa?

Ita kuma ganin bai kula ta ba har sun fara hango titi sai ta fara masa kukan da babu hawaye tana kuma fadin "Zuciyata ba za ta iya daukar fishinka ba, ka kalle ni ka ga yadda fishinka ya ramar da ni, ba na iya barci, ba na iya cin abinci, kamin afuwa, don Allah ba don halina ba!"

Ta fada cikin wani irin yanayi mai motsa ZUCIYA.

Ya juyo ya zuba mata ido tabbas ta rame, ta birkice amma hakan bai yi tasiri a zuciyarsa ba, musamman da ya tuno kallon rainin da Khalil ya yi masa, ya sake hango yadda ta fito a gaban motarsa, sai kawai ya juya ya ci gaba da tafiyarsa ba tare da ya ce mata uffan ba.

A kidime ta ru'ko hannun jakarsa murya na rawa ta ce, "Na san na yi ba daidai ba, na ba ka ha'kuri, ka yi hakuri mana!"

Bacin rai sosai a fuskarsa ya dube ta sannan ya ce, "Ke ba na son ballagazanci, a titi za ki ri'ke ni?"

Ba'kin ciki ya kama ta ta fara kukan gaske ta ce, "Ni ka kira da ballagaza?"

Kishi ya rufe mai ido sosai, ba wani ja-in-ja ya ce, "E, idan akwai sunan da ya fi haka muni ma ki hada da ballagazar, don kuwa sunayenki ne, dabi'un da kike yi irin nasu ne. Yanzu kuma kin nuna mini kin saba cu'danya sosai da maza, har kike ganin za ki iya cakuma ta a titi."

Ba'kin ciki ya turnuke ta, ba a taba yi mata tozarci a rayuwarta irin na yau ba, kuka sosai take yi wanda ya matu'kar taba shi, kawai waskewa ya yi. ba tare da ta sake fadin komai ba, ta yi gaba da sauri ba ta ko sanin inda take jefa kafarta saboda tsananin 'bacin rai.

Al'kalamin

Surayya Dee

✍✍✍

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

TALLAH.

Akwai ingantaccan maganin gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number..... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.....*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah.

47-48

A gigice ya ga ta nufi titi gadan-gadan tamkar zararriya, zuciyarsa ta buga, da azama ya bi ta ganin da gaske tsallakawa za ta yi ba tare da ta duba ba. A ki'dime ya fuzgo ta, ganin mota na shirin yin wasan-kura da ita, amsa-kuwwar motoci sun cika gun, har sai da mai motar ya tsaya ya fito ya dinga zazzaga mata sababi, yayin da ita ko kallo bai ishe ta ba illa fizgewa da ta yi daga ri'kon da MK ya yi mata, ta koma gefe tana hawayen ba'kin cikin maganganun da ya gasa mata.

Sai da ya ba wa mai motar hakuri ya tafi sannan ya tsayar mata da Adaidaita Sahu, juyin duniya ta ki hawa, har mai Adaidaitan ya ji haushi ya yi tafiyar sa.

Ya kalle ta ya ce, "Watau da ma zuwa kika yi ki sake tayar mini da hankali ko?"

Yana rufe baki ta ce "Kadai so hankalin naka ya tashi ne, ha'kuri na zo ba ka, ka ki ha'kura. Ka bi ni da kalaman muzanci, to ai sai ka yi tafiyarka tunda da ma ba kai ka kawo ni ba balle ka ce sai kasa na koma dole."

Ya kalle ta ya ga tana cikin fishi irin wanda bai taba ganin ta yi irinsa ba, sai ya sassauta ya ce,

"Na ji ba ni na kawo ki ba, amma kin ce gurina kika zo, idan kuwa haka ne to ba na son zuwan. Ki koma gida ni zan zo."

Kamar ta ce "Ba na son zuwan naka ni ma!" Sai ta daure ta kalle shi ta ce, "Nasan ba da gaske ka ke ba."

"Zan zo mana da gaske nake."

Ta yi shiru tana rantsuwa a ranta ba za ta yarda da maganganun da ya yi mata ba. Dolensa sai ya janye ko ya ga tashin hankalin da ya ke kirari.

Ya kalle ta ya ga ta turo bakin nan gaba, mamakin yadda ta ke son mayar da laifin da ta masa ya koma kansa ya ke yi.

"Kin yarda na tsayar miki da abin hawa?"

Shiru ta yi masa alamun ba ta yarda ba. Ya kalle ta ya ce, "Magana nake miki."

A gajarce ta ce "Ban yarda ba!Yawon ballagazan ci zan wuce."

Ji ya yi kamar ta wasta masa ruwan dalma a zuciyarsa, ya hassalo sosai ya nuna ta da yatsa ya ce, "Ni kike yi wa magana kamar kina yi da sa'anki? Saboda ba kya ganin girma da mutuncina?"

Ta yi mai shiru ta kasa cewa komai. Ya sake cewa "Ki dinga sanin abin da za ki na fada mini ba na son kau'din baki."

Duk yadda ya so ya tafi ya bar ta a gurin kasawa ya yi, ita kuma ta kafe akan ba za ta tafi ba, shi ya yi tafiyarsa ya 'kyale ta.

Da kyar da jubin goshi ta yarda ya tarar mata Adaidaita, bayan ya rantse zai zo gida ya same ta, sannan zai 'dauki kiran ta.

Yana tsaye yana kallon su har suka bar wajen. Wata ajiyar zuciya da bai san yana ri'ke da ita ba ta kwace, a fili ya ce "Wacce irin yar daru na kwaso wa kaina ne? Da motar nan ta taka ta, ina take son na sa raina? Me zan ce da iyayenmu idan aka gane muna tare ta sami wannan hadari?

Ya dade a tsaye yana mamakin irin son da yake wa Sa'adah. Ya dauka idan ya gan ta ba zai ji komai ba, ya dauka kaifin son ta ya dakushe, ashe ya nan daram. Musamman da ya ga mota na shirin take ta sai ya ji zai iya rasa ransa don ya tserar da ita, ko muzuran da ya mata na karfin hali ne kawai da son kwatar kansa a idonta.

Tana isa gida ana sallar La'asar, sai da suka yi sallah sannan ta ba wa Inna sakon da ta karbo, ta koma daki ta hau kiran MK.

Sai da ta kira har sau uku bai 'daga ba, shi kuma ya fito a Masallaci ke nan kiran ya shigo, bai daga ba sai da ya koma dakinsa ya kwanta sannan ya 'kira ta.

Har ta fara hasashen da ma zai iya rantsuwa akan 'karya? Sai kuma ta ga kiran sa ya shigo, da sauri ta dauka sai kuma ta yi shiru ta tura baki gaba tamkar yana ganin ta.

Shiru ya biyo baya tamkar ba kudi ke bin iska ba.

A shagwabe ta ce, "Na gode!"

Ya ce, "Godiyar me kike yi?"

"Ka cika al'kawari, don Allah ka yi ha'kuri wallahi na horu ba zan sake yi maka laifi ba."

Ta fa'da da rauni a muryarta.

Jikinsa ya mutu, wata irin kasala da ba ta da nasaba da gajiya ko barci ta lullube shi, murya a dakushe ya ce, "Kin bata mini rai, kin tayar mini da hankali, kin jefa ni cikin wasi-wasi mai yawa, kin janyo mini raini."

"Ka yi ha'kuri!" Ta fada da sauri.

Shiru ya yi ba tare da ya yi magana ba, saboda yadda ya ke fama da kansa, ji yake ina ma ya jita a jikinsa.

Murya ba amo sosai ya ce, "zan fada miki, ba na son yaron nan. Ina bakin cikin tarayyarki da shi, wannan ne karon karshe da zan miki afuwa a kansa, ba don girman son da nake miki da kunyar Baffa ba da na ha'kura da ke Sa'adatu. Saboda kina cutar da ni, da ni kika gani da Farida da ban san kalar tashin hankalin da za ki mini ba. Amma saboda yadda nake son ki, na ke gudun bacin ranki haka na rufe ido na rabu da ita da dukkan lamarinta. Ni kuma kin kasa tsayawa gare ni ni ka'dai."

Yanayin muryarsa da yadda ya ke maganar cike da rauni sai ita ma ya jefa ta cikin wani irin yanayin da duk mai lafiya ba zai iya kauce masa ba, tsikar jikinta har tashi take yi.

"Am sorry!" Ta fada a gajarce tana jin ina ma inama...

"Shike nan ya wuce amma kisa a ranki cewar yaune karon karshe da zan saurare ki na miki afuwa akan Khalil".

"Na gode my love!"

Mamaki ya kama shi, karon farko da ta kira shi da wani suna bayan Uncle.

Ya ce, "maimata abin da kika ce?"

Dariya ta yi "Thank you na ce!" Sai ya saki maganar ya ce, "Ba ni labari."

Haka suka sha hirarsu cike da Begen juna, dukkansu sun tabbatar sun yi missing din juna, sun kuma yarda farincikinsu na hannun junansu.

Washagari da yamma ya zo, ba Sa'adah kawai ba, hatta Inna sai da ta yi murnar zuwansa, hira suka yi cikin tattalin juna, har ya ba ta labarin irin gyaran da yake mata a gidan da za su zauna.

Tun daga wannan lokacin Sa'adah ta yanke hul'da da Khalil saboda ba karamin tashin hankali ya janyo mata ba.

Hankali ya kwanta sun shirya da MK amma ta 'kullaci kalmar ballagazancin da ya jefe ta da ita ba ka'dan ba, ta kuma ci alwashin maganar ba za ta bi iska ba, lokaci ta ke jira.

Haka kwanaki suka yi ta zuwa suna wucewa, har watan azumi ya kama al'ummar Musulmai kowa ya koma ga Allah ana fatan dacewa da Rahamar Ubangiji.

Zuwa wannan lokacin shirye-shirye ya yi nisa a bangaren MK, an kammala gyaran gida, gyaran da ya dawo da gidan tamkar sabo.

Mahmoud ne ya hado wa Sa'adah kayan shan ruwa da kayan sallah masu tsada har set biyar da takalmi da jaka set uku sai tarkacen kayan kwalliya da turaruka. Tare suka kawo mata, da za su tafi kuma ya sake ba da kudin 'dinki wanda ta 'ki karba sai da MK yasa ba ki sannan ta karba.

Yawan kayan da kuma tsadarsu ya dan rage mata damuwar rashin lefe musamman idan ta tuna tana da kayan wurin Alh Mamman a ajiye.

Ana yin sallah da sati 'daya iyaye da 'yan'uwan MK suka hada kudadensu, aka sayo dukkan abin da za a bukata, tun daga kan gado da kujeru masu kyau da aminci suka sayo aka shirya gida ya fito sosai, labulaye da carpet suka ajiye sai satin biki za a zo a saka.

MK da ya je ya ga irin kayan da aka zuba masa sai da ya yi hawayen farinciki, ya duba ya ga an 'kawata dakin Sa'adah da dan'kareren gadon da duk fariyarta ba za ta raina ba, ga kujerun ma masu kyau, ba irin gama gari ba, dayan dakin ne kawai aka malale shi da carpet aka bar shi empty, bai sha mamaki ba sai da ya shiga dakin dake tsakar gida wanda shi ne mallakinsa, an saka masa gado amma bai kai na dakin amarya ba, kowanne gado kuma da dimemiyar katifar Vitafoam a kai.

Ya zauna a bakin gadon yana goge idonsa, yana mai yin addu'a ga dukkan ahalinsa, sun masa zumunci ba ka'dan ba.

Ya zauna yana ganin TV da Fridge kawai ya rage wanda su kuma yayarsa Hafsatu ta ce ta aiko da su. Isowa ne ba su yi ba tunda a Lagos take.

Alhaji Isa shi ya sake komawa wurin Baffa ya ce idan ba damuwa suna son a yi auren a cikin sati biyu masu zuwa.

"Yadda ka ce ba ka bu'katar komai a gurinmu sai sadaki, mu ma muna ro'kon ka! Yarinyar kawai muke so don Allah!"

Suka rabu cikin walwala, tare da addu'ar albarkar Ubangiji a cikin auren.

Duk da Baffa ya ce ba zai mata kayan 'daki ba, kan dole ya karbi tsalelen gadon da mijin Sumayya ya aiko masa. Sumayya na zuwa ta nunawa Inna ku'din da za ta kashewa Iya, ita ma ta fito da nata ajiyar ta hada suka shiga kasuwa tare da Sa'adah, suka zabo kayan kicin na garari duk a 'ko'karinsu na kwantar mata da hankali, tunda sun san halinta na son kayan 'kawa.

Hatta kayan fitar biki masu kyau aka tanadar mata shike nan sai hankalinta ya kwanta. musamman da Sumayya ta ha'kur'kurtar da Baffa ya yarda za a kai mata gadonta 'kirar Dubai.

Kafin ranar 'daurin aure gidan amarya ya fito fes komai ya ji, Sumayya ta yaba 'kwarai da kokarin MK da iyayensa, saboda haka sai ta sa aka mayar da gadon dake dakin MK zuwa dakin dake cikin falon wanda babu komai a ciki, shi kuma aka saka masa hadadden gadon Dubai.

Kicin aka sake 'kawata shi da tsirarrun kayan alfarma, aka rufe gidan ana jiran isowar TV da Fridge da kuma amarya! don Mk tuni ya tare a cewarsa gadi yake yi.😁

05/06

Ranar aka daura auren Mukhtar Kabir Bichi da Sa'adatu Bashir Gogel, a Masallacin Sahaba dake Kundila, kamar yadda Baffa ya ce ba za a yi party ko ka'de-ka'de ba hakan ce ta kasance.

Amma kuma ya tsaya an yi abincin 'daurin aure da yini na fitar kunya, duk wanda ya halarcin auren Sa'adah mace ko namiji ya ci abinci mai rai da lafiya don kuwa Bijimin sa Baffa ya yanka, duk tanadin Baffa a shirya abincin fita kunya ya kare. A lokacin sarkar gold din dubu hamsin babba ce, ita ya siyawa amarya da shawarar Sumayya da take ta 'koda irin kokarin da MK da iyayensa suka yi. Sai kuma 'dinkunan da ya mata na kwalliyar amarci.

A Daren da aka daura aure suna zaune a gabansa ita da Sumayya da mahaifiyarsu, bayan ya yi addu'a ya ce, "Duk wani burina a yau ya cika Iyah, ina kyauta zaton na dan'ka ki a hannu na gari don Allah ki bi mijinki, nasan kinsan idan mijinki, ya yarda da ke to Ubangijinki ma ya yarda da ke, idan kika ri'ke wannan kadai za ki gane komai za ki yi a 'dakin mijinki ibada ne.

Ibada kuwa sai an daure domin za ka ci karo da abin da kake so da wanda ba ka so. Na ro'ki ki yi koyi da yar uwarki wurin boye sirrin aurenta, har yau din nan Sumayya ba ta taba fa'din ga laifin mijinta ba, mun sani ba fa don ba ya mata laifin ba ne, haka shi ma yana ri'ke da ita cikin ha'kuri da girmamawa. Ina sake miki nasiha ki zama mai ha'kuri, baki da'yan aure wallahi hakuri ne ya fi yawa, ina fatan ki yi ko yi da mahaifiyarki wurin ha'kuri da biyayyar aure!"

Ya janyo ledar dake gabansa ya fito da sallaya da kur'ani ya mi'ka mata, ta miko dukkan hannunta biyu da suka sha adon lalle ta kar'ba, yace "Ki rike ibada da kyau ita ce za ta jagorance ki duniya da lahira."

Ya kalli Sumayya yana fadin "Ina abin da nace ki ajiye?"

Da sauri ta mi'ka masa dama ta shigo da shi ya karba ya sake mika wa Sa'adah yana fadin, "Ki rike tsabta da kwalliya da ma ba na jin ki a wannan bangaren. Inda nake da shakku akan biyu ne. ki 'karanta buri Iyah kin dai san ni ubanki ba kowa ba ne, ki yi alfahari da abin da yake hannunki, ki daina sha'awar wanda suka fi ki ko kuma wanda ba tsarin tarbiyarku daya ba, a yanzu da za ki koma 'karkashin mijinki, ina hada ki da Allah kar ki dinga dora masa hidimar da ba zai iya ba, ko ba ra'ayinsa bane. Da ace za ki rabu da harkar kawaye to ina tabbatar miki za ki 'karantawa kan ki buri saboda ba kya hangensu. A karshen karshe na yafe miki dukkan kurakuran da kika mini, ina fatan Allah Ya lullube rayuwarki da albarkaSa, ya ba ki zuri'a mai albarka, ya kuma hore miki ha'kurin zaman aure."

Daki ya yi shiru sai shesshekar kukan Sa'adah, Baffa ya nemi Inna ta ce wani abu, ta girgiza kai tare da cewa, "Duk abin da zan fada na dade ina mata bita indai mai ji ce ai ta haddace su. Fatana Allah Ya albarka ci aurenta."

Cikin soyayya mai yawa Baffa ya kalli Sumayya ya ce, "Saura ke babbar yaya uwa ta biyu!" Ta yi murmushi cikin sanyin murya ta ce, "Komai kun fada Baffa, fatana a ce duk ta ji ku da kunnen basira, ta kuma ri'ke 'yan'uwansa da girma, musamman iyayensa. Ki rike su da mutuntawa komai za su miki kar ki nuna kin ji haushi ki yi hakuri, ki sake ninka kulawarki a kansu, duk kuma wanda ya je gidan, ki karbe shi da sakakkiyar fuska su ji tamkar a gidan yar'uwarsu mace su ke saboda sakewa da walwala."

Baffah ya nisa yace " idan Kika bi maganganun mu kin tsira! Idan kuwa kika je kika biyewa 'kawayen banza da son zuciya ki tabbatar ke 'kadai za ki dauki 'bacin ran da zai same ki, ki bi mijinki ko zaluntarki yake yi ki bishi da addu'a idan abin ya gagara, sai mu shiga, amma idan ke Kika bijire to fa kisani baki da wurin zama a gidannan".

Ya rufe zaman da doguwar addu'a ya kuma rike ta a hannunsa ya tafi kai ta 'dakinta da kansa a motar Alhaji Isa da ya zo daukar Amarya.

'Yan'uwan Baffa da na Inna da suka zo, sai mamakinsa suke yi da ya hana su zuwa kai amarya, ya tafi da kansa ya kai 'yarsa dakinta.

A lokacin kam ya zo da sabuwar dabi'ar da ta sha banban da al'ada, ashe shi yasa yasa aka kai su suka ga gidan amarya tun jiya?

SURAYYA DAHIRU.

✍✍

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR

TUKUICI GA

*AISHA IBRAHIM BAFARAWA*

(*BEAUTY*)

MK DA SA'ADAH NA GAISUWA

49-50.

GIDAN AMARYA

A gidan su Baffa suka tarar da su Baba Umaru da Baba Idi da kuma MK. Tunda Baffa ya fa'da musu a wurin 'daurin aure cewar shi zai kai amarya 'dakinta kar a turo mata, sai suka fasa komawa Bichi a yau, suka ce su za su karbi amarya da kansu.

Haka Baba Umaru ya tisa MK da jan kunne iri-iri akan ya ji tsoron Allah ya ri'ke matarsa cikin tausayi da adalci, komai za ta yi ya dauke kai ya fahimtar da ita cikin ruwan sanyi.

Baba Idi ya nisa ya ce, "Sannan zan fa'da maka gida naka ne, amma kayan ciki na matarka ne, kana dai ganin irin mutunci da karamcin da aka maka, to ina ro'konka! ka nuna kai ma ka san mutunci ta hanyar zama da yarinyar nan da kyautatawa, ba hankalinku 'daya ba, mata lamarinsu yana da gigitarwa.

Amma idan aka yi ha'kuri da su, aka musu afuwa sai a ji dadin zama da su, saboda masu rauni ne, kuma masu tausayi ne".

Alh Isa kuwa cewa ya yi, "Abin da zan fada muku ni ne uban Mukhtar, ni ne uban Sa'adatu, sannan ni ne alkalinku dukkanku 'daya kuke a gurina. Ba zan saurara wa duk wadda ba shi da gaskiya ba".

Ya kalli Sa'adah da take gurfane a lullu'be cikin lafaya, "Sa'adatu duk da ba na fatan matsala, amma duk abin da ya taso na rashin jin dadi, ni ne Babanki, ni za ki fadawa kar ki ji nauyi ko kunya, waya kawai za ki mini, ni kuma zan miki maganin ko mene ne, domin duk girman Mukhtar yaro ne karami a idonmu, na san kuma mun isa da shi".

Baffa dai bai ce komai ba, da'di ya cika zuciyarsa, Allah Ya kai Iyarsa cikin ahalin da suka san mutunci suke kuma rama shi da alheri.

Bai ce komai ba sai da suka mike, ya kalli Mukhtar ya ce, "Ban baka aure ba sai da na tabbatar kana da nagarta, ina kuma zaton kai din adali ne saboda ka siffantu da kyawawan dabi'u don haka ni ba na shakku a kanka. Sai dai kar ka bari jan kunnen da ake ta faman yi maka na ka kyautata mata, ya yi dalilin da za ka bari ta yi abin da ta ga dama, ka bude kunne ka ji ni sosai. Duk 'kawa ko makwabciyar da ka ga dabi'arta ba ta yi maka ba, ka shata wa matarka layin mu'amala da ita, idan ka bari ta fi karfinka to kai ne za ka sha wahalarta".

Su Baba umaru suka hada Baki wurin cewa, "Ba ma za ta bijire masa ba, ai barewa ba za ta yi gudu d'anta ya yi rarrafe ba, In sha Allah, irin halin gidansu na girma za ta yi ba *HALIN YAU* ba".

Aka rufe maganar da doguwar addu'ar zaman lafiya da neman tsari daga sharrin shaidan, da shaidanun mutane. Suka tafi MK ya bisu a baya, yana ta musu godiya tare da fadin duk abin da suka fada zai kiyaye, bai juyo ba sai da motarsu ta bace wa ganinsa. Sannan ya bi bayansu zuwa bakin titi ya karbo gasassun kajin da tun yamma Mahmoud ya yi masa booking, ya hado da yougurt din L & Z da kuma lemon 5alive, yana tafe yana ayyana bai taba ganin nisan bakin titi zuwa gidan nasa ba sai yau. yana isa ya rufe gidan.

Kamar a guje ya fada falon! ya tarar da ita zaune a inda suka bar ta, tana rufe ruf cikin lafaya.

Gefe daya ya ajiye ledojin hannunsa, ya isa kusa da ita ya tsaya, a zuciyarsa yake ta fadin Alhamdulillah! sannan ya sunkuya ya 'dago ta tare da fadin , "Assalamu alaiki! Barka da zuwa gidanki, ina miki murnar wannan rana mai cike da farinciki".

Ta yi shiru, ta kasa amsawa saboda yadda zuciyarta, take a cunkushe da alhinin barin gida.

Ya ri'ke hannun ta yana janta zuwa cikin 'dakin da shi ne mallakinta, a bakin gadon ya zaunar da ita tare da fadin, "Haka na ga ana yiwa amare." Yana warware mata laffayar zuwa kafadarta, fuskar ta masa kyau duk da ta kode saboda kukan da ta ke yi. Kusa da ita ya zauna sosai har jikinsu na gogayya da juna ya dan ri'ko ta ya ce, "Kukan na mene ne tamkar ba gidanki za a kawo ki ba, ke da kika yi sa'a a gari za ki zauna duk lokacin da kika so zuwa gida, zuwa za ki yi to menene abin kuka sai ka ce ba gidana kika dawo ba".

Tissue ya dauko a kan madubi ya shiga goge mata fuska, yana ta fadin maganganu masu taushi.

Ya kalli agogo ya ga tara saura,ya mi'ke ya dauko ledar kajin da ya bar su a falo, sai da ya shimfida musu abin zama sannan ya janyo ta ta sau'ko 'kasa, ya bude ledar

ya tura mata gabanta yana cewa, "Nasan tun safe ba komai a cikinki. Taimake ni ki ci"

Ya zabura ya nufi kicin ya samo 'yar roba ya wanke hannu sannan ya zubo ruwa a ciki ya dawo, da rarrashi da hikima ya sa ta cin kazar nan, har ta manta ita ba'kuwa ce, dama kuma azabar yunwa ce a cikinta. ya sake lallabawa ya tura mata yougurt, sai da ya ga ta nutsu sosai sannan ya kalle ta ya ce, "Ga toilet nan ki shiga ki yo brush ki dauro alwala"

Ya mike yana fa'din ni ma bari na yi alwalar.

'Kirjinta ya buga fargaba ta kama ta yau gata a daren farko da ta ke karantawa a cikin littafai ko ya ya nata daren zai kasance?

Har ya dawo tana zaune a inda take.

"Kin yi alwalar kuwa?"

Shiru ta masa ya tabbatar ba ta yi ba sai ya ce, 'Tashi mana!" Ya sa hannu ya 'dago ta, sai da ya raka ta har kofar bayin da ke cikin dakin sannan ya dawo yana tattare kayan da suka yi amfani da su, ya shimfi'da musu sallaya ya koma gefen gadon ya kishingi'da yana jin matsanancin bege na ratsa shi.

A bandakin ta tarar da sabon brush da makilin, sai da ta wanke bakin sannan ta 'dora alwalar sai kuma ta tsaya a bakin 'kofar ta kasa fita. Wata irin fargaba ce ke haniniya da ita.

MK da ya ga shirun ya yi yawa, sai ya tashi ya tura kofar ganin ta a tsaye, yasa shi yin turus, bai ce komai ba ya ru'ko hannunta yana fadin, "Ba na son ba'kon yanayin nan da nake gani tare da ke a yau".

Laffayar ya mi'ka mata ta fara kokarin na'de jikinta, ya kalle ta ya ce, "kin ga ba sai kin yi wannan na'din ba, kawai ninka ki yafa".

Ba ta musa ba saboda yadda bakinta da jikinta suka yi mata nauyi ainun.

Ya ja su, suka yi sallar da Annabi ya kwa'daitar da sabbin ma'aurata su yi. Bayan sun idar ya ri'ke goshin ya yi addu'a sosai, tana amsawa da amin a cikin zuciyarta. Suna shafa adduar ya mike ya fita! bai jima ba ya dawo bayan ya rufe 'kofar falon tare da kashe fitila da fanka, kasancewar farkon damina ne yanayin zafi ne.

Yana shiga ta kalle shi da gefen idonta saboda yadda kamshin sa ya sake cika dakin da hancinta, ta ga ya sauya kayan jikinsa zuwa farar jallabiya sabuwa 'kal. Hannusa ri'ke da wasu kayan, kai tsaye ya isa kusa da ita ya m'ikar da ita ya cire mayafin ya wurgar da shi, ya zame dan'kwalinta!dogon gashinta da ya sha gyara na musamman ya bayyana, ya kasa cigaba da dauriya ya fizgo ta jikinsa ya sa hannunsa biyu ya rungume ta sosai tamkar zai mayar da su halitta guda.

Ba ita ba, shi kansa jikinsa 'bari ya ke yi, 'kamshin man gashinta da na jikinta da kuma nasa kamshin suka hadu guri 'daya suka sake rikita shi, hannunsa sai kai komo ya ke yi a bayanta cikin wani irin shau'ki mai rikitarwa.

Ta yi luf a 'kirjinsa jikinta sai 'bari ya ke yana sake rikicewa da sa'kon da ya ke kar'ba.

A kunne ya ke rada mata "please hold me Sa'adah, sa hannu ki ri'ke ni don Allah!"

Cikin wata irin murya da ba ta san shi da ita ba yake ro'kon.

Kunya da tsoro suka sa ta kasa koda 'kwak'kwaran motsi balle ta iya masa abin da ya ke ro'ko.

Da 'kyar ta samu ta zame daga jikinsa ta koma bakin gado ta zauna kunyar duniya ta rufe ta.

Murya a da'kushe sosai yace, "Ga rigar barci tashi ki saka".

Kai ta sunkuyar 'kasa tana kallon 'yar guntuwar rigar da ba ta da maraba da abin tatar koko, ta ya ya za ta iya sanya wannan rigar, ko a ina ya samo ta?

Ganin ba ta da niyyan tashi ya matsa kusa da ita ya 'dora mata akan cinyarta tare da fadin, "Tashi ki saka don Allah"

Ta 'daga taga lalacewar riga ta wuce ma yadda ta ke tunani, da sauri ta ajiye ta tana fadin "Ni ba zan iya sawa ba, ba na son ta".

"Ni ina so! kin san tun yaushe na siya miki na ajiye? Kullum addu'a nake Allah ya kawo mini ranar da zan gan ki a cikin ta.

Ta shagwabe fuska ta 'daga rigar da sauri ta mayar ta ajiye, ita rigar ma kawai kunyata take yi, balle kuma a ce ta saka, kanta a kasa ta ce "Ka yi hakuri ni ba zan iya sawa ba".

Nan da nan ya ci laya, "Wallahi sai kin saka na gani".

Ya fada a dake! gabanta ya yanke ya fa'di ta shiga bubbuga 'kafa, tana 'kananun kukan da babu hawaye, hakan da ta yi ya sake 'kawata masa ita, ya sake matsawa kusa da ita sosai, ya yi 'kasa da muryarsa ya ce, "Rufe idon ki ni sai na sa miki da kaina".

"Ni dai ka yi hakuri ka bari".

"Amma kin ji na rantse, so kike tun yanzu ki fara 'ba ta mini rai, ki fara kwasar zunubi?"

Kai ta girgiza, ya ce, "To ki bar ni na yi abin da nake so, tun yaushe nake ha'kurin ki zama halaliya ta".

Ya fara zuge zip din rigarta ta ri'ke da sauri, tana fadin "Ka kashe fitila to".

"Idan na kashe fitila me zan gani?"

Ta yi shiru tana jin tamkar kasa ta tsage ta shige. Ta kasa kallon sa a raunane ta ce, "Ka juya to, ya yi murmushi ya ce, "To" Ya juya mata baya.

Kan dole ta sanya rigar amma ta kasa cire kayan ciki! Ta kuma lullube jikin da mayafi.

Jin ta daina kiciniyar sanyawa ya sa shi cewa "Na juyo?" Jin ta yi shiru ya sa ya juyo gabadaya, sai dai ganin ta a lullu'be kuma a takure ya sa shi fa'din "mene ne haka kuma?"

Ya isa ya mikar da ita tsaye ya fara janye mayafin, ita kuma ta 'kan'kame 'kirjinta da dukka hannun ta biyu. Ya juya ta bayanta ya ga yadda rigar ta kama ta, shape din surarta ya fito sosai. Da 'kadan ta rufe mazaunanta 'yar guntuwa ce sosai, mai kuma kama jiki, rashin kirkin rigar ya kai 'kurewa.

Tsayawa kawai ya yi yana kallon ta yana fadin "Ma Sha Allah kin yi mini fiye da yadda nake so".

Jin yana 'kokarin 'daga rigar sama sai ta yi maza ta saki 'kirjin ta ruko kasan hakan ya ba shi damar juyo wa ya kalli 'kirjin ta. bai ce komai ba kawai ya ci gaba da tasbihi, ya jawo ta ya rungume ta sosai fiye da rungumar farko.

A haka ya dangana su da gado, ya sa hannu ya kashe fitila, hasken bandaki ya ragewa dakin duhu, ya cire rigar da ragowan kayan ya wurgar.

Sannu-sannu ya bi da ita, duk wata ga'ba da 'kofa ta jikinta ba inda bai sa baki ya lashe ba, ya rikita mata jiki sosai! nishin da yake yi ya sake jefa ta cikin tsananin shauki da za'kuwa. A ranta kuma ayyana rashin 'kyankyami irin na MK take yi, inda ba ta yi zaton ana sa baki ba, shi yasa harshe yana lasa bai kuma tofar a 'kasa ba.

Sai da tafiya ta fara nisa ta gane al'amarin ba mai sauki ba ne, bai 'kyale ta ba sai da ya mayar da ita cikakkiyar mace.

Dukkansu sun galaibaita, saboda a tare suka bude junansu a leda. Sai da nutsuwa ta zo wa MK ya rungume ta tare da shafa kanta yana fadin maganganu masu nuna 'kololuwar soyayya da yabawar yadda ta kame kanta, kamar yadda shi ma ya kame. Wani irin son junansu ya cika zuciyarsu da gangar jikin su gaba'daya.

A tsakiyar Daren ya fita kicin ya dauko buta ya jona musu ruwa, shi ya fara shiga, kafin ya fito nata ya tafasa, ya kai mata ban'dakin ya taimaka mata ta sauko da ga gadon sai da ya ga ta shiga toilet din sannan ya ye zanin gadon saboda yadda suka bata shi, idan ya bushe jirwaye zai yi, ga kuma jinin budurci.

Ya shimfida wani, daga yadda yake aikin ka san a cikin farin ciki ya ke sosai.

Ita kuma Sa'adah tana can tana gasa kanta tana fadin ai a littafi daukar amarya ango yake yi, ya gasata ya mata wanka, sannan ya nade ta a towel, ya mayar da ita daki, ya shirya ta a kuma kwantar da ita kamar jaririya, shi komai bai iya ba.

Amma tana tuno yadda 'dazu ya sarrafa ta, ya jagwalgwalata son ransa, ya lashe ta tas, sai ta rufe ido da hannunta saboda yadda kunya ta kamata, ba ta taba karanta yadda ya mata din ba, salonsa daban ne.

Ta fito tana ra'be-ra'be, ya taro ta yana fa'din, "Sannu My Sa'adah! Allah ya miki albarka, da kansa ya shafa mata mai, da turare, suka kwanta ya dora ta akan cikinsa yana shafa jikinta a ranta fadin take shi baya gajiya ne da wannan shafar? Kafin barci ya dauke su, sai ji suka yi ana kiran sallah.

Mamaki ya kama MK yana tunanin ashe ba karamin lokaci suka shafe a tare ba, ba su kwanta ba sai da suka yi sallah. Zuwa masallaci ya gagari MK, ba zai iya tuna ranar da ya yi sallar Asuba ba a jam'i ba, sai yau da suka yi da amarya. 😁

Wayarsa ya kashe ya rungume amaryar sa bayan ya lullube su da duvert, barcin gajiya ya yi awon gaba da su.

Alkalamin

SURAYYA DAHRU

✍.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR

UZZIRI.

kwanaki biyu baza'a Sami posting ba, Ina cikin hidimar Biki ne, da zarar na Sami nutsuwa, zaku ji ni, na gode sosai da yabawar ku akan Rubutuna.

51-52.

Barci sosai suka yi sai wurin 12:25pm MK ya farka, idonsa ya sauka kan agogon dake makale a bango. Salati ya yi, bai ji mamakin yadda suka shafe lokaci suna barci ba, saboda sun ci bashinsa a jiya.

A hankali ya raba jikinsa da Sa'adah, ya zuba mata ido yana ganin yadda take numfashi a hankali gashin kanta ya barbaje ya zubo har kan fuskar ta.

Ba karamin kyau ta masa ba, duk kuwa da ba komai na alamun kwalliya, sai ya tsinci kansa da yi mata hotuna a hakan.

Da 'kyar ya yunkura ya shige toilet ya watsa ruwa don ya samu sau'kin nauyin da jikinsa ya masa musamman cinyoyinsa da yake jin su a daure suna masa ciwo. Ya fito daure da towel babba, bayan ya dauro alwala.

Ya shirya cikin kananun kaya da suka yi masa kyau, sannan ya hau bakin gadon ya fara shafa gashinta da ya tarwatse, yana kiran ta a hankali, kamar a mafarki ta ji shi. Sai dai kunyar sa ta hana ta bude ido bare ya gane ta farka, tana ayyana da wane ido za ta kalle shi da rana?

Ya san ta ji shi sarai, don haka ya shammace ta ya zame bargon da ta rufe jikin ta da shi, 'kirjinta ya bayyana, da sauri ta sa dukkan hannun ta, ta kare su, tare da fadin "Na shiga uku!" A shagwabe idonta kuma a rufe.

Dariya sosai MK ya yi tare da cewa, "Ashe ban gama cire kunyar gaba'daya ba?" Cikin tsokana ya hau gadon sosai, ya riko ta jikinsa yana fadin "second round ina kallon ki, kina kallo na, sai mu binne kunyar nan kawai".

A sukwane ta bude idonta ta ce "Uncle wallahi ban da lafiya, ka yi hakuri". Murmushi ya yi sannan ya ce "Kalle ni to".

Idonta a bude amma ta kasa dora su akan fuskarsa, da gaske kunyar sa take ji ba kadan ba.

Ganin hakan sai ya 'kyale ta, ya ce ta tashi ta shiga wanka, ya hada mata ruwan wankan. Ba ta yarda ta saki bargon ba, sai da ya ba ta tawul ta daura, nan ma ta kasa tashi sai da ya rike hannunta ya kai ta bakin kofa sannan ta shiga.

Kafin ta fito ya gyra gadon ya share dakin da falon har tsakar gidan kasancewar kwana aka yi ana kada iska, kura da ganyayyaki sun ba ta tsakar gidan. Yana gamawa ana kiran sallar azahar dan haka ya le'ka ya gan ta tana shafa mai, daga bakin kofar ya ce "Bari na je Masallaci idan na dawo sai mu karya ko?"

"Adawo lafiya." Ta ce ba tare da ta kalle shi ba, ya amsa yana jin dadin addu'arta, shi ma ya zama magidanci.

Ana idar da sallah ya juyo, a kicin ya yada zango risho kirar Butterfly ya kunna. Ya shiga fasa kwai yana soyawa bayan ya sa albasa sosai, da atturuhu, da maggie. Yana kammala soya musu ya kashe rishon tunda ya riga ya dafa shayi a kettle kafin ya fita ya juyo a tea flask.

A falo ya shirya komai ya leka ya gan ta kishingide a gefen gado da doguwar rigar shadda da aka mata shahararren dinki. Fuskarta ba kwalliya amma ta yi kyau sosai duk da ta yi fayau, ta dan fada kadan.

Kamshinta ya cika dakin, da sauri ya isa gareta yana fadin "Woow Amaryata kin kara yin kyau fiye da jiya." Ya sa hannu ya dago ta yana ci gaba da fadin "Anya yarinyar nan za ki dinga barina ina fita kuwa?" Kallon ki kawai, ya fi mini komai".

Dadi ya cika mata zuciya, tasirin kalamansa, suka bayyana akan fuskarta, saboda yadda take ta murmushi dimples dinta na lotsawa.

A haka suka isa falo yana cewa "Zo ki karya, ni kaina yunwa nake ji bare ke da nayi ta dabdala da ke"

Kunya ta kama ta, ta rufe idonta, kunya na burgeshi sosai bai yi zaton kunyarta ta kai haka ba, musamman yadda ya san ta da fitina.

Da kyar ya samu ta bude fuskarta, amma fa idonta na kasa tana kallon yadda ya baibaye falon da kayan shayi, dangin su madarab(peak), Ovaltine, sugar mai iyali (cube) da bread din Oasis Bakery, ga kuma soyayyen kwai.

Da kansa ya hada mata tea din da ya zama tamkar kunu saboda yadda ya ji kayan hadi ya tura mata gabanta yana cewa "Ki yi ha'kuri da iya wannan Amarya! Gobe In sha Allah, da wuri zan tashi na miki girki na musamman, yau mun makara ne".

Ita dai bata ce komai ba illa juya tea din da take ta faman yi ta kasa kaiwa bakinta.

Ya sake cewa "Akwai fa cake a fridge, ko na dauko miki?"

Kai ta girgiza ta ce, "A'a".

Kofi ya dauka ya hada nasa shayin, wanda ba shi da madara sai ganyen shayin (Beyond Comment) na asalin.

Sosai suka ci abinci saboda dukkan su yunwa suke ji ba kadan ba, duk da dai Iyah ta kasa sakewa sosai, sai dai shayinta kadai ya isa ya kosar da ita.

Ganin sun gama ya sa Sa'adah tattara kayan da suka bata, MK ya karba yana fadin

"Yi zamanki ki huta, ke bakuwa ce a gurina don haka ni zan tayin hidimar har sai kin zama yar gari a gidanki".

Murmushi ta yi, tana zaune ya kwashe komai yasa tissue ya goge mata hannu da baki, yana yi yana tsokanar ta, sai da ya fita zuwa kicin ita ma ta shiga toilet ta wanke hannun ta da bakinta sosai.

Ta fito tana karewa kayan furniture's din dakin ba karamin kyau suka mata ba, ko a ina ya samu kudin siyan wannan gadon?Haka nan tsaruwar falon ma ya burge ta, ta tabbatar ko iyayenta ma ba lallai su shirya mata gida haka ba.

Tana tsaye a falon tana jin buruntunsa a kicin da alamu wanke wanke yake yi, sai ta ji babu dadi yadda ta sakar masa yin komai, don haka sai ta saka takalminta da yake gefe wanda ta sako jiya, ta nufi kicin din ta tarar ya kammala, Frying Pan kadai ya rage, da sauri ta ce "Kawo na karasa, dama ka bari zan yi".

Ya juyo da dukkan hankalinsa gare ta ya zuba mata ido yana jin sabon son ta na huda zuciyarsa, idanuwansa da gangar jikinsa gaba'daya.

Ba ta san dalilin da ya sa ita ma ta zuba masa ido ta kasa daukewa ba, tsawon sakwanni suna kallon juna, Chemistry na aiki a jikin su. Ita ta fara janye fuskarta tana jin kunya na taso mata

Murya a dakushe ya ce "Ki koma ki yi hutawar ki, na gama yanzu zan zo".

Tana shiga falon NEPA suka dawo da wuta, ta kunna TV, a lokacin DVD ce tafi yawa, fim din sai Wata Rana ya bayyana akan gilashin TVn.

Ba ta kai ga zama ba, ya shigo falon, kai tsaye ya isa kusa da ita yasa hannuwa ya janyo ta zuwa jikinsa sosai, bugun zuciyarsu ya karu, har kowa yana jin yadda zuciyar dan'uwansa ke bugawa.

A hakan ya zauna a kujera, ya zaunar da ita kan cinyoyinsa, ya zame dan'kwalinta yana shinshinar ta tamkar maye, hannuwansa na ta kai komo a jikinta. Jikinta sai tsuma yake tare da wani irin shauki na ban mamaki.

Ya dinga kici-kicin ya zura hannunsa kasan rigarta amma ya kasa kasancewar doguwa ce kuma fitet. Karamin tsaki ya yi, yana rada mata "Ki daina samin doguwar riga irin wannan a yanzu".

Ba ta iya cewa komai ba, sosai yake ya mutsata. Ya yi nisa wurin tsotsar harshenta, ya ji wayarsa da ke aljihunsa tana ta kuwwa, da kyar ya hakura ya raba bakinsu ya fito da da wayar, ganin sunan Mahmoud ya sa shi sakin tsaki a fili sannan ya amsa tare da cewa

"Saboda Allah mene ne hakan?"

Mamaki ya kama Karfi ya ce "Yi ha'kuri leko ina kofar gidan ka karba wa Amarya sako" Daga haka ya katse wayar.

Kan dole ya fita yana bude gate din ya ga Mahmoud a cikin adaidaita sahu, ga kuma kaya ya sauke masa a bakin kofar gidan.

Ganin ya fito yasa Mahmoud ba wa mai adaidaita sahu umarnin ya ja su tafi ba tare da ya yi wa MK magana ba.

Da sauri MK ya bi su yana fadin "Karfi tsaya mana!" Amma fur ya hana direban tsayawa kan dole ya juyo yana mamakin yawan kayan da Mahmoud ya jibge masa.

Akwatina masu kyau guda biyu babba da karami, kwalin indomie guda biyu, kiret din kwai biyu, da leda mai dauke da kayan shayi. Gefe madaidaicin botiki ne dauke da soyayyar miyar kaji da katan din ruwa na SWAN da katan din coke da fanta. Daga jikin akwatin ya hango yar takarda da alamun soke ta aka yi, hannu yasa ya ciro ya fara dubaw *Abawa Amarya, miyar kuma In ji Umma*.

Murmushi ya yi ya san fushi ya yi, a ransa kuma jinjina yawan alherin Karfi yake yi.

Haka ya yi ta kinkima yana shiga da su cikin gidan, sai da ya kammala shigowa da su, sannan ya zauna yana cewa "Duka wannan sakon ki ne in ji Karfi".

Da walwala a fuskarta ta ce "waye hakan?"

"Mahmoud fa."

"Oh shi ne Karfin?"

Kai ya daga mata yana kokarin bude akwatin da ya fi girma, kaya ne tamkar na lefe, sai dai dogayen riguna da English wears sun fi yawa. Dayan akwatin kuma shake yake da kayan kwalliya da na gyaran gashi.

Sosai ta nuna farincikinta kan kayan tare da yi wa Mahmoud fatan alheri.

MK ya yi kasa da muryar sa soasai ya ce, "Mu je daki ki ji wata magana".

Nokewa ta yi tare da fadin, "Fada mini a nan".

"Maganar ba ta nan ba ce Sa'adah na!"

Ya tashi yana jan ta zuwa dakin, ganin da gaske yake yi, ya sa ta cewa "Amma dazun nan ka ce ni bakuwa ce, ba zan yi komai ba sai na zama yar gari?"

"E na fadi hakan, amma kuma ban ce har da wannan al'amarin ba".

Tabe fuska ta yi hadi da tura baki gaba ta ce "Ban warke ba, zafi zan ji."

"I promise you, ba za ki ji ba, I will be soft and gentle".

"Ni dai a'a uncle".

"Bangane a'a ba?"

Ya fada yana mata wani irin kallo. Kan dole ta mi'ka masa kai ya yi yadda ya ke so.

Bata fahimci komai a sai zafi da wata irin takura.

Bai samu kansa ba sai bayan La'asar, don haka a gurguje suka yi wanka, suka yi jam'i.

Kwalliya sosai Sa'adah ta sake yi duk da yadda take jin radadi a kasanta.

Kwanciya ta yi a dakin, tana ayyana gaskiya ba wani dadi a wannan lamarin, sai dai a barka da radadi da ciwon jiki. Romance dai, idan za a yini ana yi ba za ta kosa ba.

A karo na biyu ya sake shigowa dakin.

"Kin san dai barcin bayan La'asar ba kyau ko?"

Idonta a rufe ta ce "Ni ba barci zan yi ba".

"To fito falo, fita zan yi na dora ruwa akan risho idan ya tafasa ki wanke shinkafa ki zuba".

Shiru ta yi tamkar ba ta ji abin da ya ce ba, ya san ba ta gamsu da fitar da zai yi ba ne.

"Kin ji".

"Ni gaskiya ka kashe rishon".

"Ba za ki yi abin da na

saki ba ke nan?"

Cikin tura baki ta ce

"Ni tsoro nake ji kar barci ya dauke ni abincin ya kone".

"Ba fa dadewa zan yi ba, salad zan sayo kawai".

Da sauri ta ce "shike nan adawo lafiya, amma dai kana sayowa ka dawo gida."

"Mai za ki ba ni idan ina gidan?"

Kai tsaye ta ce, "Abin dadi mana."

Murmushi ya yi tare da fadin, "Kamar gaske, a haka kamar jaruma ana taba ki kadan sai raki".

Shiru ta yi tamkar ba ta ji shi ba. Ya juya yana fadin, "Bari ma na zuba shinkafar na san yanzu ruwan ya tafasa".

Biyo shi ta yi tana cewa, "Ka je kawai zan zuba, a dawo lafiya"

Bai wani jima ba ya dawo, da hanzari ta karbi ledar tana masa barka da dawowa, ya amsa cike da jin dadi.

Cikin kankanin lokaci ta yanka salad din ta wanke da gishiri, ta bar shi a kolanda, ta hau yanka cocomber da su tumatur.

Ba ta koma falon ba, sai da ta tace shinkafar, ta yi kasa da rishon ta mayar kan wutar don ta silala a hankali.

Tana shiga daki ta nufa, ganin hakan yasa MK da ke zaune a kujerar kusa da kofar daki ya fizgo ta ta fado masa.

"Kin ce na dawo da wuri na dawo din kuma sai ki shige ki bar ni, ko dai kari kike so?"

Zabura ta yi, ta zame tana cewa "Indai ba so kake ka mayar da ni chopping the rice □ ba, ya kamata ka daina wannan maganar haka nan".

Dariya sosai ta ba shi, ya dinga kyakyatawa, ita kuma ta shige daki tana cewa, "Dole ka yi dariya mana ka same ni kana yin yadda ka ga dama da ni, ba tausayawa".

"Oh haka kika ce? Za ki ga rashin tausayin kuwa".

Yanzu ma shi ya shiryo musu abinci, tana zaune tana kallon karamin tray din da ya zubo salad, mamakin yadda ya zauna ya yi garnishing din salad din da waken gwangwani da su cocomber da tumatur take yi, tamkar a restaurant.

A plate daya ya zuba musu abincin, suna ci suna yaba dadin miyar Umman Mahmoud.

Suna kammalawa Sa'adah ta kwashe kayan ta share gurin. Ya kalle ta ya ce

"Sannu da kokari, amma na ce miki sai kin fita daga bakunci kafin ki fara hidima".

Ta gefe ta kalle shi, ta juyar da idonta gefe sannan ta ce "Ka bar ni kawai na yi ayyukana tunda hidimar ba duka ka dauke mini ba".

Murmushi ya yi tare da cewa "Ashe ban yi gwaninta ba?"

Cikin kunkuni irin na shagwaba ta ce "Ba ka yi ba".

Karar wayarta ya katse damkar da ya yi niyyar kai mata, daki ta shige don a can wayar take. Da sauri ta amsa kiran "Anty Sumayya kin ce fa za ki zo mu yi sallama kafin ki wuce, ga shi har Maghriba ta kawo kai ban ganki ba".

"Kai Iyah! Da gaggawa kike, to muna kofar gidan, zo ki bude mana".

Katse wayar ta yi, ta

isa gaban madubi ta kalli kanta, riga da siket din atamfa ne jikinta, powder da turare ta sake shafawa sannan ta fito.

"Uncle, su Anty Sumayya ne suka zo"

Kafin ya yi wata magana har ta fice da sauri.

Bin ta ya yi da ido, yana jin wani irin abu a zuciyarsa akan me za ta fita a haka?

A hankali ya mike ya fita daga falon ya shige dakinsa da yake tsakar gidan.

Ba su jima da shigowa ba, ya fito, suka gaisa da Anty Sumayya da yaranta, ganin Sa'adah ba ta ba su ruwa ba yasa ya shiga kicin ya shirya ruwa da lemo a tray, da tumblers, ya doro cake din da yasa a fridge, yana jin farincikin ruwa da lemon da Mahmoud ya kawo musu na ratsa shi.

Da kansa ya dauka ya kai musu, Sumayya sai sannu take masa tare da fadin "Ga yara kuma sai ka dauko da kanka, sannu na gode".

Murmushi ya yi tare da cewa, "Ba komai Aunty".

Alwala ya yi, ya fito daga waje ya tsaya ya kira Abba ya danka masa sabbin kudi na dubu biyu,"Ku sayi sweet kai da kannenka".

Fir Abba kin karba ya yi, tare da cewa "An hana mu karbar kudi Uncle"

Dole sai Sa'adah ya kira ya ba ta, ya ce ta ba su. Ta kalle shi bayan Abba ya koma falon ta ce "Fita za ka yi ne?

"Masallaci zan je daga nan kuma zan je gida".

Bata rai ta yi sosai

"Ba dadewa za su yi ba Uncle, so kake na yi ta zama ni kadai? tunda dare ya yi kawai ka bari gobe ka je da wuri".

"To" Kawai ya ce ya daga labulen falo ya ce, "Anty Allah ya mayar da ku lafiya, mun gode sosai."

Ita ma ta amsa cike da mutuntawa.

Daki suka shige, suka bar yaran a falo suna kallo suna fama da cin cake. Jan kunne da nasiha iri-iri Sumayya ta sake yi wa Sa'adah.

Ta dauko wata leda a jakarta mai dauke da tambarin Welcare,ta mi'ka mata ta ce ki adana su sosai, likitan ya ce za ki iya shan wannan ba komai. Ganin da Sumayya ta yi Sa'adah ba ta bude ledar ba yasa ta ce "To ki bude mana na nuna miki yadda za ki sha".

Kin budewa ta yi, sai Sumayya ce ta bude ta fito da su, daya a cikin wata yar roba yake mai kyau an rubuta Women's Formula.

"Kinga wannan na robar Multivitamin ne 100 pieces ne kullum daya za ki sha"

Sai wannan ta nuna na kwalin shi ba kullum ba sai ranar da kika so. Ki kula da shi mai tsada ne sosai, daurewa na yi na siyo miki package dinsa, kafin ya kare dai na san za'a dade sosai".

Ba tare da ta kalli fuskar Sumayya ba ta ce "Na gane, na gode." Ta mayar da su ledar. ganyin wata takarda a ciki yasa ta janyo ashe recit din kudin ne, ganin yawan kudin da maganin suka lashe musamman na kwalin ya matu'kar ba wa Sa'adah mamaki.

Ta fito dana kwalin tana dudduba mene ne special a tare da shi da ya yi wannan darajar haka?

"Viagra"

Ta furta sunansa a fili, a kunyace ta sake cewa "Na gode sosai Anty".

Sumayya ta muskuta ta tsare Sa'adah da kallo mai tsanani sannan ta ce "Ina rokon ki Iyah kar ki jefa kanki a hallakar da MATAN YAU suka jefa kansu na shaye-shayen magunguna barkatai marasa fa'ida da inganci, da sunan mallakar miji. Kar ki yarda da wannan bankaurar wallahi ba a mallakar miji da wannan sai dai ki ta asarar kudaden ki, karshe ki hadu da ciwon da zai raba ki da mijin gaba'daya".

Cike da wauta Sa'adah ta ce "Fada mini abin da zan yi na mallake shi kamar yadda kika mallaki mijinki".

Dariya sosai Sumayya ta dinga yi har da kwanciya akan gado, lamarin da ya fusata Sa'adah, kawai sai ta fashe da kuka, da kyar Sumayya ta hadiye dariyar ta shiga rarrashinta.

"Yanzu mene ne abin kuka Iyah?"

"To akan me za ki mini dariya kamar mahaukaciya?".

"Tambayar ki ce ta ba ni dariya, amma nutsu ki ji mai zance miki. Mace tana kama mijinta da girki mai da'di, da kuma ba shi kulawa ta musamman a shimfida, da kuma tsaftar jiki da ta muhalli. Amma wadannan kadai, ba zai sa ta mallake shi ba, sai ta yi ha'kuri ta bi ra'ayin sa akan komai, ko da kuwa ita ba hakan take so ba, ya zama ba ta da ra'ayin kanta sai na mijinta, ta iya ladabi da biyayya, ta kiyaye

harshenta akansa. Ina tabbatar miki idan kika hada wadannan abubuwan sai kin mallake shi fiye da yadda kike so".

Tura baki gaba ta yi tana goge hawayen idonta, ta sake cewa "To idan ina son ya zama mijin ta ce fa?"

Mamaki da tsoro ya kama Sumayya, wai wannan yar mitsitsiyar yarinyar auren jiya, ita ce ke son ta mallake miji, bayan mallakar kuma ta mayar da shi mijin ta ce. Wane irin son zuciya ne ya shigo wa matan wannan zamanin haka?

Sumayya tsintar kanta ta yi da ri'ko hannun kanwarta ta kalle ta da tarin kauna sannan ta ce, "Abubuwan da na fada su ne za su miki jagora akan komai, sai kuma ki hada da addu'ar Allah ya zaunar da ku lafiya cikin aminci da tausayi. Amma karki yarda da kawayen da za su ba ki maganin mata ko a saki a hanyar zuwa wurin malamai wallahi ba za ki samu yadda kike so ba, ba komai a wannan hanyar sai bata da lalacewa".

Ta dan tsahirta kafin ta zarce da fadin "Ki ba shi dama ya zama sarki a gidansa, ke kuma ki zama baiwa kuma bafadiyarsa, duk abin da kika san yana so, ki masa tun kafin ya bu'kata haka nan ki guji abin da baya so kafin ya ankarar da ke, ina tabbatar miki idan kin yin hakan bayan mallakar da za ki masa zai ya zame miki mijin kan ta ce ma, matu'kar yana rayuwa kan tsarin ilimi da shari'a ne.

Ga turaren wuta nan Inna ta ce a kawo miki sai dazu suka iso, ni ma na diba na ga masu kyau ne, har da na tsugunno".

Ta mike tana fadin, "Kin ga an dade da idar da sallah bari mu tafi".

Da za su tafi rungume juna suka yi kuka kowacce ta ke yi tamkar ba za su sake haduwa ba. A dole suka rabu Sumayya na mata fatan zaman lafiya da zuri'a mai albarka.

Ba su jima da tafiya ba ta zuba gawayi a kasko ta zuba kalanzir tare da kyasta ashana, ta barshi a tsakar gida, ta share falon inda su Khalifa suka bata. Sannan ta shiga wanka, sai da ta yi sallar Isha, sannan ta duba ta ga wutar ta kama, ta dauko

ta zuba turaren. Kan ka ce kwabo gida ya cika da kamshi, sai kallon agogo take yi,har tara na shirin yi bai dawo ba.

Daidai lokacin ya dawo, waya ya kira, ta fita ta bude masa, kamar dazu ba mayafi a tare da ita.

Suna tafe yana fadin "idan za ki fito ki dinga saka hijab, ban son wani ya hango ki a haka".

Ta amsa da tom.

Tunda ga tsakar gida yake jin daddadan kamshi, suna shiga falon ya rikota yana cewa "Madalla da Antyn mu, irin wannan kamshi haka".

Ita dai ba ta ce komai ba, sai da suka zauna ta ce "Sannu da dawowa" Ya amsa mata cike da walwala.

"Shi ne ka tafi ka bar ni ni kadai har tsoro ya fara kamani".

Ta fada cike da shagwaba.

"Ai kuwa dai gara ki cire tsoro, kin san har sha dayan dare ina kaiwa a shago".

Murmushi ta yi kawai ba ta ce komai ba, amma a zuciyarta tana raya ba za ta yarda da wannan dogon zaman a waje ba, tana gida ita kadai.

Haka suka ci gaba da cin amarci ba kakkautawa cike da soyayya da kulawa, tun Sa'adah na jin zafi da tsoron haduwarsu har ta saba ta fara fahimtar dadi da nutsuwar dake cikin haduwar.

```Alkalamin

*Surayya Dee*.

``✍✍
```

[6/5, 14:08] +234 806 791 2288: □ *HALIN YAU*! □

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

Fatan alheri ga Amare

Hafsa Sani Abubakar

Halima Sani Abubakar

Ubangiji ya albarkaci auren ku, ya Baku zuri'a mai albarka.

BAYAN SATI SHIDA

Zuwa wannan lokacin, sabo da shakuwa mai karfi sun shiga tsakanin ma'auratan biyu, soyayya da aminci sun sami wajen zama a gidansu, kowa kokarin kyautatawa dan uwansa yake yi.

MK ya dauki soyayyar duniya ya dora akan Sa'adah da da hali kirjinsa zai bude ya cusa ta, saboda yadda ya ke jin ta a zuciyarsa, musamman yadda ba ta gajiya da bukatunsa. Duk da dai ya gane ita ma mabukaciyar ce ta gaske ga tsafta ga iya sarrafa girkin gargajiya, saboda ire-iren su aka fi yi a gidansu.

Babban abin da ya ke gigita shi a kanta, shagwaba da iya kwalliya, kullum sabuwa take zama a idonsa, kullum da sabon abin da zai gani a tare da ita, babban abin birgewa ta kama dukkan ahalinsa ta ri'ke da hannu biyu, ta zama yar gida a gidansu, akai-akai take kiran Hajiya Babba da Hajiyar Bichi tana gaishe su. Sun zo sau daya sun ga gida, da amarya.

Tana kokari sosai wurin yin abinci akai gidan su Mk mussaman masar Bauchi da miyar ganye, da kuma Dambu. Kasancewar mahaifiyar ta daga Bauchin take, sosai ta iya masar Bauchi.

Kullum yana gida, hatta FGC Kano ma ya daina zuwa, shago kuma sai Azahar yake fita, da zarar karfe biyar ta yi zai juyo ya bar su Abbas da kula da wurin, Mahmoud ya masa tsiya ya gaji.

Shi kansa Mahmoud din tunda ya je ya ci girkin amarya, dambun shinkafa ta yi musu da ferfesun naman rago, sai kunun aya bai sake yi wa MK tsiyar ya zama bita-zai-zai ba, musamman yadda kamshin turaren gafgaf da kajiji ya kama gidan gaba'daya, dole idan mutum ya yi katarin samun irin su Sa'adatu ya manne musu ya kasa fita ko ina.

A wannan tsukun ASUU ta janye yajin aikin da ta ke yi, a kuma lokacin aka tabbatar da MK da Mahmoud da sauran da suka yi sa'ar samun koyarwa a Jami'ar Bayero takarda shedar fara aiki.

Ranar da ya fara fita aikin dukkansu sun galaibaita, sati shida kullum suna manne da juna, ko fita ya yi Allah-Allah yake ya dawo. Don haka yanzu ma da zarar ya ga yana da tazarar lokaci, sai ya dawo gida ya ci abinci, ya yi abin da zai yi, sai kuma ya yi wanka ya koma, idan kuma ba shi da sauran darasi shike nan sai ya yi zamansa gurin amaryar sa.

Watannin su biyu da aure Sa'adah ta tsiri fushin da babu dalili, share shi take yi, ta daina hira da shi daga eh sai um um, ta rage walwala idan yana gidan, idan tana falo ya zauna, sai ta san yadda ta yi ta bar falon, haka nan daki.

Ba ta gudunsa, amma shi kadai zai yi kidansa yayi rawarsa, babu gudunmawa daga gare ta.

Wannan canjin ya matu'kar 'daga masa hankali ya yi tambayar duniya tace ba komai, kuma lafiyar ta 'kalau.

Rannan da daddare ya dawo da ga Masallaci, jikinsa a sanyaye ya zauna kusa da sallayar da ta ke sallah ya jira ta idar.

Tana ganinsa ta yi kamar ba ta gan shi ba ta fara kokarin tashi a gurin ya kira sunanta a kaurare.

"Sa'adah zauna magana za mu yi".

Ba ta 'ki ba, ta koma ta zauna amma fuskar nan a 'daure, sannan ta juyar da kanta gefe, ta ki kallon inda ya ke.

"Na tambaye ki mene ne yake faruwa kin ce mini ba komai amma kuma kin canja mini, kin tayar mini da hankali, wallahi da kinsan yadda nake ji a zuciyata da kin tausaya mini cikin kwanakin ukun nan.

Shiru ta yi, tamkar ba da ita yake ba, ya matsa ya riko hannunta, ta fizge tare da zura su cikin hijab, wata irin fargaba ta kama shi, bakinsa har rawa yake yi ya ce "Har abin ya kai mu ga haka, laifi na yi ke nan?"

Nan ma shiru ta sake yi.

"Don Allah Sa'adah me na yi miki? Ki fada mini, ba ni za ki duba ba, Allah na hada ki da shi".

Jikinta ya yi sanyi sosai, ta kasa cewa komai sai da ya sake rokon ta sannan ta bude baki ta ce, "Ni gaskiya zaman ne ba zan iya ci gaba da yi ba, na gaji".

Gabansa ya yanke ya fa'di.

Murya ba amo ya ce "Me na yi miki?"

Shiru ta yi, hankalinsa ya yi mugun tashi ya fara fa'din,

"Ban miki komai ba fa Sa'adah, don Allah idan wasa kike mini ki bari bana so".

Yana rufe baki ta ce "

"Wallahi ba wasa na ke yi ba, zaman ya isa haka nan".

Ya tsura mata ido tsawon lokaci ba kakkautawa yana nazarinta, ya lura da gaske take yi, bugun kirjinsa ya karu, gumi ya fara karyo masa, jikinsa na bari ya ri'ke kafadunta da karfi, ya ce

"Kar ki mini haka Sa'adah don Allah, ina sonki fiye da kaina, fada mini inda na gaza, me na ke yi wanda ba kya so?"

Ta yi shiru amma fuskar nan a daure tamkar hadari, hannunta ya ruko da karfi ya dora a kan kirjinsa ta ji yadda zuciyarsa take bugawa da sauri.

"Kin ji yadda zuciyata ta ke bugawa, tun daga ranar da kika canja mini Sa'adah har yanzu ban huta daga wannan bugun ba, ya sake matsarta sosai ya ce "Ko aikina ne ba kya so? Idan shi ne sai na je na ajiye musu".

"Ni ban ce ba, idan ba ka yi aiki ba 'kasa za ka ci?"

"Me yasa kika cire kanki, da gaske za ki iya rabuwa da ni?"

"E mana indai zan tsira da mutunci na."

Kansa ya kulle ainun ya kasa gane me take nufi.

"Ban gane idan za ki tsira da mutunci ba?"

Ta zumbura baki ta ce "Kai ba Bahaushe ba ne?"

Ransa ya fara 'baci, ya kalle ta cike da bacin rai ya ce "Kar ki fara Sa'adatu, kar ki fara mini rashin kunya ba zan 'dauka ba".

Ya mike ya fice da ga falon ya nufi dakinsa.

Zuciyarta sai rawa take yi, ita kanta jarumta take yi, ta kuma riga ta kudire sai ya janye waccan kalmar da ya jefe ta da ita, amma ta lura ransa ya baci sosai don ta fahimci indai ya ce mata Sa'adatu to ransa ya baci da ita ne.

Da kyar ta tashi ta yi wanka, ta shirya cikin guntuwar rigar barci cotton marar nauyi, ta zauna shan black tea, amma zuciyarta na tunanin ko MK ya yi barci, ko me yake yi, ko shima fishin zai dauka yau ba zai zo 'dakinta ba?

Ta dade a falo kafin ta kashe fitila da fanka ta shige daki ta kwanta, adduar barci ta karanta ta shafe jikinta, tana ta tunani, sai ta ji shigowarsa, dadi ya ratsa ta har da sakin ajiyar zuciya.

Yana tsaye ya kunna fitila idonsu ya hadu, nan da nan ta dauke idonta, ya kashe fitilar ya nufi gadon yana kwanciya ya janyo ta jikinsa ya saki ajiyar zuciya tare da fadin

"Ni ba zan iya fushi mai yawa da ke ba, bacin ran da kika sa ni dazu na yafe miki kin ji My Sa'adah! Ke ma ki yafe mini abin da na miki, ki kuma fada mini din kar na sake maimatawa a gaba".

Uffan ba ta ce ba, amma farinciki ke ratsa ta yadda yake ta rawar jiki da neman sulhu.

"Kin ji"

Bai jira amsarta ba

ya sake cewa " Don Allah me na yi haka har zuciyarki ta gaji da zaman mu tare, ban yi zaton akwai abin da zan yi ki daina sona ba".

Haka kawai ta ji zuciyarta ta karye, hawaye ya cika mata ido, cikin rawar murya ta ce "Ban daina sonka ba ai, kawai ha'kura zan yi don shi ne ya fi alheri tun ba ka juya mini baya ka fara wulakantani ba".

Jikinsa ya yi sanyi kalau, a sanyaye ya ce "Mafarki kika yi akan zan juya miki baya, yanzu a zaman da muka yi ba ki fahimci irin son da nake miki ba? Kin fi karfin ki wulakanta a hannuna."

Ta kasa cewa komai saboda tana bude baki kuka za ta yi.

Ya sake cewa "Na ji dadi da ba daina sona kika yi ba, ina hada ki da girman Allah ki fitar da ni daga duhu, me na yi miki?"

Kukan da ta ke matsewa ya subuce mata, hawaye har a kan kirjinsa, ya rasa abin da ya ke masa dadi, hankalinsa, in sun kai dubu to a tashe suke.

Haka ya dinga jijjigata yana shafa gadon bayanta tare da fadin sorry, tamkar mai mata bita.

Da kyar ya shawo kanta ta bude baki ta ce "Tun farko na so na hakura da aurenka saboda yadda kake nuna mini am nothing to you, sai dai na san Baffa ba zai fahimce ni ba, tunda sai da ya tambaye ni na ce ina sonka, iyayenka sun zo gunsa to ba ni da sauran dama, ban isa na ce na fasa ya saurare ni ba".

Ta sarara, ta ja hanci sannan ta dora da fadin, "Muna cikin wannan yanayin, sai na yi kuskuren shiga motar saurayi, kuskuren da ni kaina na yarda ban kyauta ba, ba irin ha'kurin da ban baka ba amma ka 'ki, karshe na sake yin wani kuskuren na dauki jiki na bi ka har inda kake, don ka gane yadda fushin ka ya hana ni zaman lafiya.

Sai ka bi ni da wulakanci kala-kala har ka iya ce mini Ballagaza akan idona!"

Kukanta ya dawo sabo, ta shiga yin sa har da rerawa tamkar a cikin nisha'di take, don kawai ta sake tayar masa da hankali, ai kuwa gogan ya kasa cewa komai tsabar yadda komai ya tsaya masa, yana tuno Baba Idi da ya ce lamarin mata yana da gigitarwa, tabbas ya yarda ga shi 'yar yarinya karama tana neman zautar da shi.

Cikin kukan ta ce "Tun lokacin na tabbatar barin ka shi ya fi alheri, tunda za ka iya jifa na da wannan mummunar kalmar a ranka, sai kuma na ga gara na nuna maka ni ba ballagaza ba ce, hakan kuma ba zai yiwu ba sai mun yi aure dole, zuwa yanzu na san ka gane in ma ni Ballagazan ce ko a kasin hakan".

Tsawon lokaci MK ya kasa bude baki ya yi magana. Ya yi shiru yana jin kukanta har cikin kwakwalwarsa.

Da kyar ya bude baki murya ba sauti ya ce, "Ba har zuciyata nake nufi wannan kalmar ba, subul da baka na yi".

Da sauri ta ce"Ai sai da na tambaye ka, ni ce ballagaza, ka ce e, idan akwai kalmomin da suka fita muni na hada da su domin na siffantu da hakan".

"Billahillazi Baby kishi ne ya rufe mini ido a lokacin, amma ba har zuciyata hakan nake nufi ba, na yarda na yi laifi ki yi ha'kuri na tabbatar ke din katangaggiya ce".

Zamewa ta yi a jikinsa ta koma karshen gado tana sake sabunta kukan da take yi tare da fadin, "Ni ba zan hakura ba, kai ne za ka yi ha'kuri kar ka wahalar da ni".

Mirginawa ya yi ya tarar da ita a karshen gadon, ya riko ta tana tirjewa, kukan gaske take yi, har da bubbuga kafa tamkar yar karamar yarinya.

Kwantar da murya ya yi sosai tare da cewa "Babyna tsaya ki ji, tsakaninki da Allah, tunda muka yi aure wacce kalar soyayya ce ba na yi miki?"

Cikin kukan ta ce "Ai don ka ga zargin da kake mini ba gaskiya ba ne, bayan haka kuma kana hutawa da ni".

Ya rasa ta inda zai bullo wa wannan yarinyar, ya nisa ya ce

"Zaman da muka yi na wata biyu har da doriya, ban yi wani abin da kika gamsu son ki nake yi da iyakacin gaskiyata ba? Ko a lokacin da kike ganin ba na tarairayarki, ai kona mini rai kike yi, na ce ba na son ganin ki da dan iskan yaron nan, amma ba ki ji ba, haka na yi ta ha'kuri ba don ina son ki ba za mu yi auren ne?"

Ya sake tausasa murya ya ci gaba da fadin, "Saboda Allah indai dama ba wani abu ne a ranki ba, mene ne na dawo da abin da ya wuce, ba haka kawai na fada miki maganar da kika kullace ni a ranki ba, ke kika janyo, ko ba ni da alaka da ke zan yi kishi yanayin da na gan ki, a matsayinki na mace mai daraja".

Ya yi shiru yana jin shesshekar kukanta, tana ta ajiyar zuciya tamkar wadda ya yini yana dukanta.

"Na roke ki, ki daina kukan nan haka, na yarda ban kyauta ba ki yi hakuri".

Ta yi shiru, kamar yadda ya roka din har da gyara kwanciya, da lulluba alamun barci za ta yi, tana sakin ajiyar zuciya, a ranta kuma tana fadin sai kuma rikicin gobe.

Ya so su kasance tare, amma saboda tsoron kar ta ci gaba da masa kuka yasa ya kyale ta, ba a jima ba ya ji saukar numfashinta alamun barci ya yi awon gaba da ita.

Ya saki gauron numfashi, ya haska fuskarta, da hasken wayarsa ya ga hawaye duk ya bushe a fuskar, kuma wani abin dariya ita da kanta ta boye fuskarta a jikinsa. Tsintar kansa ya yi da gyara mata kwanciyar yadda za ta ji dadin barcin.

Ya dawo Masallaci, ya tarar ta dira sabon kuka ga akwati a kan gado sai zuba kaya take yi tamkar mai shirin yin balaguron wata guda.

Zama ya yi gefen gadon yana kallon ikon Allah, da Asubar fari za ta fara masifa tamkar jiya ba ta yi ba, duk irin ha'kurin da ya ba ta ashe bakam ta masa. Yana kallon yadda ta gama shirya akwatin ya kasa cewa komai saboda gaba'daya He is speechless.

Wanka ya ga ta shiga yana zaune ta fito, ta shirya cikin riga da skirt na English wears, skirt (purple) iya guiwarta rigar kuma body hug (pink) an rubuta *BABY GIRL* ta kama ta ainun musamman daga kirji, ta gyara zaman ribon dinta a kitsonta na shuku, ta masa kyau ba kadan ba, har ya dinga raya don ta tayar masa da hankali ne yasa ta yin wannan shigar da Asubar nan tunda ta san yau ya kwana bai taba ta

ba. Ta shafe jikinta da turararuka kala-kala tun daga na jiki har na kaya, sannan ta dora bakar doguwar riga akan kayan ta yane fuskarta da dan mayafin rigar.

Ta dauko takalmi da jaka ta saka sannan ta ja akwatin ta nufi kofar barin dakin.

Wata irin fizga ya mata ta dawo da baya kamar za ta fadi sai kuma ta dire kan kafafunta. Kafin ta yi magana ya riga ta da cewa "Me kike shirin yi ne haka, ina ce tun jiya magana ta wuce?"

Hawaye yana zubar mata ta ce "Wallahi ba ta wuce ba don kuwa ni ba zan sake zama da kai ba".

Dariya ce ta subuce masa wadda babu nisha'di ya ce "Ok tunda haka ki ka zaba shike nan, sai na ga wadda zai raba ki da ni".

Ta juya za ta sake fita, wannan karon da karfin gaske ya janyo ta ya jefa ta gado tare da fadin "Wannan shi ne gangan, ba za ki fita ko ina ba, bai wani bata lokaci ba ya bita ya turmushe ya sakar mata dukkan nauyinsa.

Ta kasa koda kwakkwaran motsi, sai da ya tabbatar ta yi laushi sannan ya daga ta, sai kuka take masa mai sauti bai kula ba, sarrafa ta yake yi kawai, tun tana tirjewa har abin ya shiga jikinta ta yi lakwas ta sallama.

Tsawon lokaci kafin ya samu nutsuwa.

Sai da ya huta sannan ya tashi ya fita bayan ya zura jallabiyarsa, a shirye ya fito hannunsa ri'ke da mukallin mashin, tana kwance inda ya barta tana kallon sa, ta tura baki gaba ta dauke kai.

Murmushi ya yi ya ce "Kin ga kwana uku ke nan ina fita da yunwa amma yau a koshe zan fita, kullum haka zan dinga miki".

Harara ta watsa masa tare da cewa "Idan na zauna ba".

Murmushi ya yi tare da fadin "Ba inda za ki iya tafiya ki bar ni, wa zai iya da wannan fitinar ta ki ai sai ni din".

Ganin magana yake nema yasa ta daina tankawa.

"Zan tafi, ki tashi ki yi wanka ki karya, idan na dawo ban tarar da abinci ba, ki tabbatar ke ce abincin."

Ya fita yana fadin "Sai na dawo." A fili sharewa ta yi amma a zuciyarta addu'a take masa.

Yana barin tsakar gida ya janyo kofar ya rufe ta da kwado ya saka mukallin a dan jikin flowers, ya fitar da mashin dinsa, ya bar kofar gate din ba tare da ya rufe da jamlock ba.

Wanka ta sake yi, tana yi tana tsaki, haka kawai an mayar da mutum kamar agwagwa wanka dai wanka dai ba kakkautawa.

Ta mayar da kayan da ya cire mata bayan ta shafa mai, doguwar rigar ta ninke ta mayar durowa, sai da ta gyara gidan fes ta share ta goge ko ina. Ta kunna risho ta dora tukunya don dafa indomie, dogon Hijabi ta dauko ta saka, ta dauki kaskon turaren wuta, lekawa za ta yi ta samu yaron da zai samo mata garwashi a gidan Maman Nana, jan duniya kofa ta'ki budewa ga shi kuma ba da mukulli aka rufe ba, kan dole ta ha'kura bayan ta hango kwado ta yar karamar kofa, murmushi ta yi tana fadin

"Ya dauka da gaske tafiyar zan yi".

Tana karyawa ta yi wanke-wanke, ta dora abincin rana, farar macaroni ta dafa ta fito da miyar kifi daga fridge ta dumama ta bar ta akan rishon, ta juye macaronin a foodflask ta ajiye, ta tsinci kanta da son hada masa zobo, nan da nan ta dafa ta hada ta saka a fridge.

Sai da ta gyara kicin din sannan ta tafi ta kwanta, ba ta jima da kwanciyar ba, barci ya yi awon gaba da ita.

Bude ido ta yi ta gan shi tsaye a kanta alamun shi ya tashe ta, mi'ka ta yi ta sake juyawa don ta ci gaba da yin barcin.

"Ki tashi ki yi sallah biyu fa ta wuce".

Kan dole ta tashi don kuwa ba karamin jin dadin barcin ta yi ba, har ta idar yana kishingide a gefen gadon, ya kalle ta ya ce

"Kin yi abincin, ko kuwa ke ce abincin?"

"Don Allah ka barni na ji da abin da ya dame ni, ina dai rufe ni ka yi, ba ka tunanin faruwar gobara ko wani abu na ibtila'i, ina kulle ba?".

Cike da rashin damuwa ya ce "Na fi ki tattalin lafiyar ki, na riga da na yi riga-kafin komai. Ba ki amsa mini tambayar da na yi ba?"

Shiru ta yi ta kyale shi, ganin haka ya mike ya na cire rigar shaddar jikinsa, ya cire wandon, ya yi saura daga shi sai Boxer da singileti.

Inda take zaune ya nufa ya mikar da ita yana fadin "Taso".

Kwacewa ta yi ta fita falo a guje, tana fadin, "Wallahi ba za ka tsofar da ni ba, ga abincin can a kicin".

Yana dariya ya biyo ta ya zauna a kujera ya ce "Zubo mana"

"Ni na koshi".

"To ni zubo mini".

Ta fita tana kunkuni ai tun farko shi ne ya'ke zubo musu abinci, sai yau zai ce ita za ta zubo.

Haka ta shiryo masa abincin har da zobo, dadi ya kama shi sosai, ya dinga cin abincin hannu baka hannu kwarya, tabbacin tunda ya fita bai sa komai a cikinsa ba.

Yana kallon yadda ta zauna a falo ya san ta ki shiga daki ne don kar ya mata wani abu, abin da ba ta sani ba a falon ma ba abin da zai fasa.

"Sa'adah! Don Allah mu shirya haka nan, wallahi na gaji da fushinki, ki yi hakuri kin ji na janye wallahi ke kamila ce, mai kirki ce".

Ko kallon sa ba ta yi ba, bare ta amsa masa.

"Kin ga siyar mini da fushin to".

Ta zumbura baki sosai, ta sake yin shiru.

"Ki shirya gobe na kai ki, ki yini a wurin Inna, idan za mu dawo sai mu tsaya a Sahad store mu sayo iron din da ki ka ce na sayo miki"

Nan ma shiru ta yi.

"Kin ji"

"Ni wallahi albarka".

"Tom shike nan satin sama makaranta za ta tura mu Jami'ar Jos Seminar, ki shirya mu je, ki gaida Anti Sumayya".

Murmushi ta yi ta sunkuyar da kanta.

Shi ma murmushin ya yi tare da tambayar "Kin sayar?"

Kai ta daga tare da cewa "E amma fa har da fitar goben".

"Na sani ai, tunda mun shirya, mu je ki taya ni barci, kin san jiya ban yi wani cikakken barci ba, kuma na yi fitar sassafe."

Sai da ya fita ya kewayo sannan ya kwanta, ta bi shi tana masa tausa har ya yi barcin.

Shike nan rikici ya kare.

Ranar da suka tafi Jos ba su isa ba sai yamma likis, don haka a Hotel suka sauka, duk da Sa'adah so ta yi ta sauka a gidan Sumayya.

Washegari da safe da zai fita wurin aikin da ya kawo shi ya ce ta shirya ya raka ta, da yamma zai zo su dawo, nan da nan Sa'adah ta canja fuska, tana fadin "Ni dai ka bar ni na dinga kwana a can tunda dai kwana uku kawai za mu kara yi".

Kai tsaye ya ce "Ba zan miki karya ba, ba zan iya ba, zan dinga kai ki da safe, idan yamma ta yi, zuwa Maghrib zan dinga zuwa muna dawowa".

"Ni gaskiya kwana nake so na yi"

Ido ya zuba mata sosai, ba tare da ya ce mata uffan ba, ta sunkuyar da kai kasa, saboda yadda ta ke jin kallon na ratsata.

"Yini za ki yi"

Ya sake maimatawa a gajarce.

Bata rai ta yi sosai amma ba ta ajiye kayanta da ta dauka ba.

Ya kalle ta ya ga ta yi kicin-kicin da fuska, ga kuma kaya a hannun ta, shi ma ya daure tasa fiye da yadda ta yi.

"Ni ko kwana daya ka barni na yi".

Ransa a bace ya ce "Ke ki yi duka kwanakin ma, mu hadu a tasha ranar tafiya, idan kuma kwanakin ma sun miki kadan, ki yi ta zama har sai kin gaji".

Ajiye kayan ta yi, sannan ta bi shi suka tafi. Kowa sai kunci yake yi da dan uwansa.

Shatar taxi ya dauka suka nufi unguwar su Sumayya, ba mai cewa kowa uffan.

Da murna Sumayya ta karbe su, cikin kankanin lokaci aka cika gabansu da abin karyawa, a gurguje ya ci abincin ya tafi, ciki-ciki Sa'adah ta ce "Sai ka dawo" Ba tare da ta raka shi hanya ba.

"A hakan kike so ki mallaki mijin?" Sumayya ta tambayi Sa'adah.

"Tunda kuka zo fuskarki a daure, sai da ya tashi, kika ware, tun yanzu za ki koya masa bagarar da lamarinki? Tun yana tsoron ganin fushinki, har ya daina?"

"Da bakinsa ya ce mini zai zo Jos, na shirya zai kawo ni na gaishe ki, kuma yanzu ya ce ba a nan zan sauka ba, sai dai na dinga zuwa yini, akan mai zai hana ni kwana?"

"Akan ya damu da lamarinki mana, ke yanzu ba ki ga alherin da ya miki ba, idan kuwa haka za ki dinga masa zai daina kokarin kyautata miki. Me ya kai ki yin musu, har da fushi akan abin da ya zartar?"

Haka ta dinga mata nasiha cikin rarrashi, har Sa'adah ta ji ba ta kyauta ba.

A ranar Sumayya ta fahimci Iyah na da ciki, amma ganin ba ta san tana da shi ba, yasa ita ma ba ta mata maganar ba, kuma lafiyar ta kalau, ba wani tsirin abinci ko laulayi, kawai dai yawan kwanciya take yi.

Da kanta ta masa waya, da ta ga an yi Magariba bai zo ba, tana tambayar yaushe zai zo.

"Kin fasa kwanan ne?"

"Yinin da na yi, ba tare da kai ba, a daddafe na yi, sai yanzu na gane, ko kace na kwanan ma ashe ba zan iya ba."

Da'di ya kama shi ya ce "Har na dawo masaukinmu amma bari na zo".

Sosai suka huta, zuwan su Jos sai ya zama tamkar Honey Moon a gurinsu. Son juna ya karu a zukatansu.

Wani irin so da zazzafan kishin MK, ya cika zuciyar Sa'adah, zuwa yanzu ta tabbatar ya iya soyayya, irin wadda ma ba ta yi zaton akwai irin ta ba.

Alkalamin *SURAYYA DAHIRU*

✍✍.

[6/7, 11:54] Aminan Ibrahim: □ *HALIN YAU*! □

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•·•·

Ganin kullum ciwon gaba ya ke yi ba baya ba, yasa ya kaita asibiti, test aka ba su, tunda kan Taifod, malaria, da ciki (P.T).

Sakamakon na fitowa komai Negative, illa na cikin da ya kasance positive.

Maganin tsayar da amai da karin jini aka ba ta. Sai Panadol, tare da fadin sai a hankali za ta sami lafiya tunda jikinta na samun sauyin yanayi.

Sosai MK ya ji dadi, sai fadin Alhamdulillah yake yi har suka dawo gida.

Sannu kuwa har gajiya da amsawa take yi, motsi kadan zaicce sannu, tamkar mai nakuda.

Kwana biyu ta warware ta shiga harkokinta ba wata matsalar komai, lafiyayyen ciki ta samu komai ci take yi, ko sau nawa MK zai neme ta ba ta gajiya, wani lokacin ma ita take yin dalilin da za su hadun.

Mamakin yadda ta zama expert a wannan harkar take yi ba gajiya, har Allah-Allah take yi idan ya fita ya dawo, ko kuma dare ya yi.

Ta san mabukaciyace ita, amma ko kusa ba kamar yanzu ba. Tunda ta sami ciki, ba ta sake hadiyar Viagra, bare ta ce ko shi ne yake sababa mata yawan son sex.

Daga dukkan alama cikin ne ya zo mata da wannan salon, wadda take fatan kar ya zame mata dabi'a ta dindin, MK da'din hakan yake ji ba kadan ba, kullum a cikin fadin "Madalla da Babyn nan yake."

Cike da zumudi suke goyon cikin, wani irin kyau Sa'adah ta yi, fatarta ta sake yin laushi, ta goge ta yi tas, MK baya gajiya da kallon ta musamman yadda kirjinta ya cika dam, kugunta ya bude sosai.

Shi kansa MK ya murje farinsa ya karu sosai, kallon su kawai za a yi a san suna cikin kwanciyar hankali, da mutunta juna.

BAYAN WATA SHIDA

Zaune take a tsakar gida tana waya da Inna, "Inna har yau ba za ki zo kiga inda nake ba?".

Daga can bangaren ta amsa da cewa " To Baffanku ne ya hana ni, wai mai zan zo na yi miki".

"Cikin shagwaba ta ce "Na san da kin karfafa Inna da tuni kin zo, haka na sha jinya har na warke ba ki zo ba, da Anty Sumayya ce a garin nan take rashin lafiya da kin je kin ganta, amma ai ni ma Baffa ya zo ya ganni." Ta fada a sanyaye.

Dariya ta yi tana cewa "Iyah ashe dai har yanzu da saura, na dauka kin yi hankali sosai, musamman da na ga kina zaune lafiya da mijinki kuma kin tsare kanki ba kya yawo".

"To Inna yanzu na kai wata biyar ban zo gidan nan ba, tunda na ji fa'danku, ba na yawo na tsare kafata, ba sai ki dinga zagayowa kina gani na ba".

"E gaskiyar ki, to ki kwantar da hankalinki, ina tafe tunda ga Baffanku ma yana jin ki da kunnensa".

Da haka suka yi sallama ta kashe wayar, da kyar ta samu ta tashi saboda yadda cikin ya mata nauyi sosai tamkar ba cikin fari ba. Watansa bakwai, amma sai a yi zaton a watan nan za ta haihu, duk da cewar watansu takwas da aure.

A fili ta ce "Gara ki zo ki gan ni, ki ga yadda na zama".

Washegari kuwa bayan azahar sai ga Inna da yar rakiyarta Zainab Ma'aji.

Mamaki ya yi matu'kar kama Inna ko kadan ba ta san cikin har ya tsufa haka ba, ta san dai tana zargin ko da cikin tunda rabon da ta sa Iyah a idonta an kai wata biyar koma ya zarce hakan.

Ta zauna tana mamakin yadda ta aune ta zama babbar mace komai nata ya bude, da kyar take zama da tashi.

Kallon Zainab Inna ta yi ta ce 'Ashe kin kusa zama uwa amma ba labari?"

Dariya sosai Zainab ta yi tare da fadin "Inna Ina zan iya hirar haihuwarmu ta fari".

Yayin da Sa'adah ta sunkuyar da kai kasa alamun kunya.

Zainab ce ta shiga kicin ta hado ruwa da lemo ta kawowa Inna, ta sake komawa ta dauko tiren da ta gani an shirya kayan abinci a kai.

Hira suka yi, cikin walwala har Inna ta fahimci sauyin da Iyah ta yi, ta fara yin hankali.

Sai da suka zo tafiya, ta fashe da kuka, kamar wata sokuwa.

Cike da tarin kauna Inna ta sata a jikinta, tana fadin "Kukan na menene kuma Iyah? so kike ki tayar mini da hankali bayan cike nake da murnar ganin ki cikin nutsuwa da walwala, ko wani abin na damun ki ne?"

Cikin kukan ta ce "Ni so nake ki dinga zuwa".

Cikin rarrashi ta ce "Wani satin zan dawo, ai yanzu kam dole Baffanku ya bari na dinga zuwa akai akai".

Da haka ta lallaba ta suka rabu lafiya, ta raka su har gate bayan Inna ta shiga dakunan ta gani tare da sanya albarka.

Suna tafe Inna ta ce da Zainab "Ina murna Iyah ta yi hankali ashe dai da saura, indai ba so take na zama uwar zamani ba, ina ni ina zarya a gidanta?"

Dariya sosai Zainab ta dinga yi tana fadin "Mene ne a ciki Inna? Kin san Baffa ne ya hana mijinta barin ta zuwa gida, ke ba sai ki dinga zuwa ba".

"Ba ku da hankali"

Har gida Zainab ta raka Inna sannan ta tafi gidansu.

Allah- Allah Inna take yi Baffa ya dawo ta ba shi labarin Iyarsa ta kusa zama uwa.

Tunda su Inna suka tafi, ta debo kayansu da ya wanke jiya, ta zauna ta fara guga.

Ta kammala nasa tsab ta-ci karfin nata, ya dawo.

Ta fara kokarin tashi ta karbe shi, ya tsaya daga inda yake ya bude murya ya ce "Yi zamanki ki ji da kanki".

Ta koma ta zauna tare da cewa "Sannu da dawowa"

Bai amsa ba ya shiga kicin ya ajie ledar hannunsa, ya zubo abinci a plate, tare da cokula biyu.

Gefe kuma ya wanko guiba ya zubo a bowl.

Yana zama tun kafin ya yi magana ta sa hannu ta dauki gwaibar ta fara ci.

Ya kalleta ya ce

"Sau nawa zan ce miki ki daina gugar nan idan na sami dama zan yi?"

"To ina zaune haka ai bai fi motsa jiki ba, ni fa har wankin ma zan iya mana, kawai dai na bari ne saboda ka ce ba ka so.

Ya zuba musu abincin, yana fadin mun yi Ba'ki ne yau, ko kuma wani abin za mu yi da daddare?"

Tana murmushi ta ce "Yau babbar bakuwa muka yi baka nan"

Ya zuba mata ido cike da neman karin bayani.

"Inna yau dai Allah ya nufa ta zo"

Da sauri ya ce shine baki fada mini za ta zo ba?"

"Ni ma fa ban sani ba kawai ganin su na yi ita da Zainab".

"Ba ni labarin yadda ta kaya, kin saka hijabi kin boye cikin?"

Tana dariya ta ce "Ban saka ba, amma dai na ji kunya ba kadan ba, ita fa ba ta san ya girma haka ba".

Shi ma cikin dariyar ya ce "To me kika ba su da za su tafi?"

"Ban basu komai ba".

Ya rage fara'a ya ce "Kai Iyah don rowa?"

"To ai na ga farkon zuwa na na kai mata atamfa da sabulai, zuwan da na yi na karshe ma ka ba da kayayyaki na kai mata, yanzu ni kuma ba kudi ne da ni ba".

"Kudin da yake cikin durowa a dakina fa?" Ya tambayeta yana kallon ta.

"Uncle ai ban fada maka zan taba ba, sannan kuma cewa ka yi na sayayyar kayan Baby ne".

"Daga yau ban miki iyaka da komai nawa ba, akan su Hajiya da Inna, komai kika ba su ba zance don me ba?".

"Tom shike nan na gode zan gyara".

"Ina ta cin abinci baki sa hannu ba?".

"Ci abinka ni kunu zan sha, dazu Zainab ta taya ni muka yi".

"Kwana biyun nan ban san me yasa ba na son shinkafa ba".

Sai da ya kammala cin abincin ya tashi ya zubo mata kunun a katon mug, sannan ya jona gugar ya ci gaba da yi.

Suna zaune aka fara kiran Magariba, daidai lokacin kuma ya kammala musu gugar gabadaya.

Ya yi alwallah ya nufi Masallaci, ita ma ta tashi da kyar ta yi alwalar.

Kafin ya dawo ta shirya kayan su cikin durowa, ta tattare falon, ta kunna turaren tsinke na Touch Me.

Haka kwanaki suke ta shudewa har watan haihuwa ya kama, komai na Sa'adah ya sake canjawa, fuskarta, ta yi wani iri, hanci ya bude sosai, baki ya zama kato tamkar ba Sa'adah yar kwalisa ba.

Ita da kanta ba ta son ganin fuskarta a madubi, MK idan ya kalle ta dariya take bashi, amma ba ya iya dariyar a gabanta, tun kwanaki da ya kalle ta ya fashe da dariya, ita kuma ta saka masa kuka mai tayar da hankali, da kyar ya shawo kanta, shike nan bai kara ba, sai idan ya fita ko ya shiga dakinsa ya yi mai isarsa.

Ranar Alhamis da yamma ya isa gidansu, bayan sun gaisa da Hajiya Babba, ya tambaye ta yadda za a yi akan sayayyar kayan haihuwa.

Ta kalle shi da kulawa ta ce "Haihuwar ta matso ne?"

Ya ki tankawa.

Ta yi murmushi ta ce yanzu fa an daina wannan ala'adar, a yi sayayya amma wai sai ranar suna da a ba da kaya, kawai ku je ku sayo kayanku, ku ajiye Allah ya raba su lafiya".

A zuciyarsa kawai ya amsa, ya mata sallama ya yi dakin uwarsa!ya mata bayanin yadda suka yi da Hajiya Babba.

Ta ce "Shike nan a yi yadda ta ce din, ko ka hada su da Samira ta raka ta, tunda ku ba ku san mai aka fi bukata ba".

A gidan ya ci abinci kasancewar daga makaranta ya zarto, sannan ya musu sallama ya tafi.

Haka kuwa aka yi tare da Samira suka je kasuwar kayan jarirai ta asibitin Nassarawa suka zabo kayayyaki daidai misali, wadda za a fi bu'katar su.

Ganin kayayyakin nan ya karawa Sa'adah kaguwar ta haihu, da MK ya dawo ya ga yawan kayan da kyaunsu, shi ma ya ji dadi tare da yabawa Samira.

Dadi ya kama shi ganin da ya yi Sa'adah tana ta murnar kayan. Ya ce mai ya rage ba a saya ba?"

"Uncle komai an siya kawai rigunan ne unisex, sai anyi haihuwar za a sayi na mace ko na namiji, sai durowar Baby kawai".

"Tom shike nan su ma zan saya muku, ke ina naki kayan?"

Ta fara daddaga kayan gun tana neman ledar da kayan suke ciki, shi ne ya hangota ta fada tsakanin kujeru, da kyar ya janyo ta.

Ya bude yana ganin inner wears ne, sai pads, saboda ya tura Lagos Anty Hafsatu ta siyo mata lace da shadda.

Ya daga bireziyar da ta masa kyau sosai, har zai mayar, sai ya yi niyyar tsokanar ta, ya ce

"Anya wannan za ta miki kuwa?"

"Za ta mini mana ba ka ga an kara size din akan wadda na saba sawa ba?"

"To abin ne na ga kamar ba za ta rufe su ba".

"Kuma haka zan ta zama, ai Inna ta ce zan huce".

Ya guntse dariyarsa ya fita yana fadin, yanzu zafi ne da ke?"

Sai da ya dawo ya zauna ya ce, "Ki fito da kayan da zan kai miki dinkin".

Shiru ta yi masa tana ala'adarta ta zumbura baki.

Ya maze ya ce, "Da ke fa nake magana kin san na sha fada miki ba na son na miki magana ki yi kamar ba ki ji ba.

Ga mamakinsa sai ya ga hawaye na zuba a idonta, kafin ya tambayi ba'asi ya ji tana cewa, "Da alama idan na yi kiba daina sona za ka yi, kullum sai ka mini dariya, ina kallon ka kawai sharewa nake yi, don ma kai ka mayar da ni hakan din".

Ta kare tana kifa kai a hannun kujerar da ta ke zaune, tana masa kukan iyashege.

Maimakon ya ji ya damu sai kawai dariyar ta zo masa sosai, ya dinga kyakyatawa.

Lamarin da ya harzuka ta, ta tashi ta koma daki tana kuka sosai.

Sai ya yi shiru da ya hasaso yadda hanci da bakinta suka zama sai ya sake fashewa da dariyar, ya jima kafin ya samu dariyar ta tsaya masa.

Ya shiga mayar da kayan cikin ledoji ya kai su dayan dakin da ba kasafai suke amfani da shi ba, ya bude wardrobe ya zuba su ya rufe.

Dakin ya bi ta, ya samu tana ta goge fuskarta da tissue, kusa da ita ya zauna ya rungumo ta ta gefe, so take ta fizge amma ta kasa, ya fara magana a hankali.

"Me ya sa kike da saurin kuka ne Iyah? So kike Babyn mu ya zama mai kukan banza? Me yasa ba ki san wasa ba, ko buhu kika zama wallahi ba abin da zai ragu a son da nake miki, ba sha'awar ki nake yi ba, ba jikin ki nake so ba, ke nake so. Tsufa ko tawayar halittar ki ba za su canja soyayyar da nake miki ba, ki ri'ke wannan".

Sai ta lafe sosai a jikinsa tana sha'kar kamshinsa, ta sa hannu ta balle links din dake gaban rigar ta zura hannu tana shafo kirjinsa.

Cikin lokaci kalilan suka birkice, Sa'adah, ba karamin kidima MK take ba, nauyin cikinta baya tasiri a wannan fagen. Sosai kalamansa suka sata farinciki, shi yasa ita ma take mayar masa da tarin soyayyar da take masa a aikace ba ka jin komai sai numfarfashin MK.

Soasai suka sha shagalinsu, katon cikin su ba ya hana su komai, sai dai Mk ya san yadda yake yi ba tare da ya takura ta ba.

Yana tsaye gaban madubi, yana daura Agogon hannunsa, ita ma ta fito daga wanka daure da tawul, a bakin gado ta zauna tana ta numfarfashi, shi ya taimaka mata da shafa mai, pant da siket kawai tasa ta zura doguwar riga marar nauyi.

Ya dauke tawul din ya shanya a kofar bandakin. Ya dauke bireziyar da ba ta saka ba ya mayar inda take ajiye su.

Dake ya saba da tsokanarta ya kalle ta yace, "Iyah na lura idan kina koke-kokenki inviting dina kike yi ashe, daga yau na fahimta. I will be noted".

Hararar sa ta yi tare da cewa "Ka daina ce min Iyah, ba na so".

"Ni kuma ina so".

Duk wani abin da za a bukata lokacin haihuwa MK ya tanadar mata, hatta dinkunan da za ta saka ya karbo, ba abin da suke jira illa zuwam ranar haihuwa.

Ranar Talata da ta yi daidai da hudu ga watan Mayu 4/5, tun Asuba take faman murkususu, tun tana daurewa har ta gaza, a sukwane ya samo Adaidaita Sahu suka nufi asibitin Murtala, waya ya yi wa Hajiya Babba, ita ma a gaggauce ta bi su, sai da ta isa, sannan ya koma gida don dauko akwatin da suka shirya kayan zuwa asibiti, da kuma tabarma.

Karfe 1:45pm na rana Sa'adah ta haifo sankacecen yaro namiji mai cike da koshin lafiya, kukan da yake canyarawa ne ya tabbatar ma Hajiya Babba, Sa'adah ta sauka.

Ana zuwa albishir da karban kayan jariri, MK na isowa, ya tarar da labari mai dadi.

A Daren ranar aka sallame su, bayan an tabbatar da lafiyar uwa da jaririnta.

```Alkalamin Surayya Dee```

✍
```

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

57-58

Kafin wayewar garin labarin haihuwa ya isa kunnen Yan uwa da abokan arziki.

Umman fanshekara da ta kasance kanwa ga Baffa, Ya'yan Baffani su ke(cousins)! za ta zauna da Sa'adah kasanitacecewar mijin ta ya kwana biyu da rasuwa, kuma ba ita kadai bace tana da abokiyar zama.

Sosai Mk yake hidima da mai jego, komai akace ana bu'kata da rawar jiki zai kawo, har wadda ma ba a nema ba.

Umma sai yaba kirkin Mk da iyayensa ta ke yi, kullum suka zauna da Sa'adah sai tace "kin yi Sa'a Iyah, kin hadu da miji da ya gaji arziki d mutunci a wurin iyayensa, shi kam bai shure kyawawan dabi'un gidansu ba".

Murmushi kawai Sa'adah ta ke yi tana gasgata maganar Umma.

Ranar suna yaro ya ci sunan mahaifin Mukhtar, wato Muhd Kabir tun a ranar kuma Samira ta lankaya masa Jawad.

A zuciyar Sa'adah ba Jawad ta so ba, amma saboda kara ga kanwar Mk sai bata canja ba.

Sosai aka yi shagalin sunan Jawad abinci mai kyau aka yi a gidan su Mk, aka ciko manyan kuloli aka zo da su, jollof din shinkafa, bandashen Gurasa, da Alale. ga kuma dangin kayan sha irin su zobo, ginger, da kunun Aya masu dadi da sanyi. mai daukan hoto da video duk motsin Sa'adah sai dai ta ga hasken camera, tun safe kafin a cika suka sha hotuna da Mk cikin kwalliya ta burgewa.

Da azahar sai ga Halima da Safina sun zo kwatsam,sama sama suka gaisa da Zainab Ma'aji ta gabatar musu da abinci da kuma abin sha, yayin da Sa'adah keta rawar jiki akan su, suna ta yatsina, hatta abincin ma ko hannu ba su saka ba bare su ci.

Cike da murmushi Sa'adah tace "idon ku kenan, sai yau kuka tuna da Ni, ashe ma kunsan inda na ke! nema na ne baku yi ba?".

Halima da tafi Safina ginshira ta ce " Akan mai zamu neme ki, inace kin dauke mu kin watsar a shara, shiyasa muma muka manta da ke, kin ri'ke miji kin manta da kowa! zuwan ma yanzu da muka yi ba naki bane, na 'Dan mu ne ko kin fada mana kin haihu?"

Dariya sosai Sa'adah ta yi, tana fadin "shikenan yana godiya"

tare da cire nono a bakin sa, a kafada ta saba shi, sai da ya yi gyatsa sannan ta nade shi a shawul da ke canja masa riga aka yi, ta mi'ka ma Safina da tafi makwaftaka da ita.

Ido ta zuba tana yaba kyaun jaririn, ta ke ta ji sha'awar ta samu nata, ta jima tana ri'ke da shi, har sai da Halima tace " Ba za ki bani na ganshi bane?"

Sannan ta mi'ka mata tana fadin "Babyn ne so mashallah". Halima na zuba ido akansa taga kamannin Uncle Mukhtar sak a fuskar yaron.

A fili ta furta "Allah dai yasa kar ka kwaso mana halinsa".

Da sauri Sa'adah tace "Uncle din kike cewa kar ayi halinsa? ai kuwa zan fada masa".

Ta no'ke kafada, alamun ko ya ji Ina ruwanta.

Har kusan maghrib sannan suka tafi, suka ajiye mata leda mai dauke da rigunan yaro masu tsada guda uku da Pampers mai 48, ta musu godiya. Zainab tana daga falo tace ku gaida gida! da kyar ta basu ledar da ta ke rabawa mai dauke da sunan jaririn!cikin kuma memo ne mai hoton Jawad.

Kwana uku da suna dan kishiyar Umma ya rasu, daga ciwon ciki kawai sai mutuwa, dole ta tafi, ta taya yar uwarta zama da juyayi! mutuwar matashi akwai gigitarwa.

Kwanaki biyu a jere Inna ke zuwa da safe ta mata wanka da sauran hidima, sai ta mata wankan yamma sannan ta tafi.

Ganin zirga zirgar zata mata yawa kullum, yasa ta roki Baffa ya bari Sa'adah ta zo gida ko sati biyu ne, ta kula ta ita, ita kadai tasan me ta gani, da dukkan alama daki daya suke kwana da mijin ta, tunda Umma ta bar gidan.

Bai tsananta ba, ya amince amma da sharadin idan mijinta bai amince ba, baza'a matsa masa ba.

Tace "Ni ai da iyayensa zan yi magana, idan ka bani dama a daren nan zanje gunsu".

Bai hana ba, itakuma bata yi sanya ba, tana idar da magariba ta tafi gidansu Mk, a falo duk ta same su har Hajiyan Bichi, bata bata lokaci gurin fayyace bu'katar ta ba.

Dukkansu sun yi shiru!sai Hajiya Babba ce ta yi kundunbalar cewa "tunda har kika zo ba za'a hanaki ba, sai dai ki yi hakuri da kaina zan kawo miki ita, idan aka shirya".

Godiya sosai Inna ta yi ,har kofar gida suka rakota suna ta yiwa juna godiya.

Har ta isa gida tana mamaki! ko kishiyoyi nawa ne suka dace da kyakkawan zama irin na iyayen Mk? ko

Ana samun adalar uwargida irin Hajiya Babba, mai hade kan ahalin gida babu banbanci, ko kai sukar wani ga wani, da sauran gutsiritsoma irin na tsofaffin mata masu kitsa munafunci da sunan kishi? Ko

Ana samun amare masu kawaici da biyayya da sanin mutunci da alherin uwayen gida irin Hajiyan Bichi? sha'awar zamansu ya kamata tana jin inama, itama tana da abokiyar zama, ba yabon kai ba, da zata yi koyi da Hajiya Babba.

Da murna ta bawa Baffa labarin yadda suka yi, shi da kansa sai ya zaku Iyah ta dawo kusa da shi duk da dai bai furta ba.

Suna komawa gida, Hajiya Babba ta Kira Mk a waya, ta sanar da shi bu'katar mahaifiyar Sa'adah! ya yi shiru ya rasa mai zaice, jin shirunsa ya tabbatar mata da bai ji dadin maganarta ba, bashi kuma da niyyan amincewa.

Dan haka sai ta kwantar da murya cikin hikima tace " Da na yi karambanin amincewa, har naci alwashin da kaina zan kai musu ita, amma ba zai zama komai ba, idan banyi daidai ba, sai na koma na lashe amai na".

Cikin takaici iri iri yace "Ni bance ba, tunda kin amsa shikenan! amma dai sati daya za ta yi".

"Akan mai zaka 'kayyadewa iyayen ta kwanakin da zata yi a gaban su, ba ka ga mutunci irin nasu ba? neman alfarma suka zo yi gaban iyayenka, saboda girmama

hakkin aure. ba dan basa sonta, ko dan sun gaji da ita suka dauketa suka baka ba, yau kusan shekara guda. me zai sa ka shata musu layi dan su nemi su kula da lafiyar yarsu?"

Ya yi shiru yana jin maganar na shigarsa sosai, ya nisa yace "Shikenan Hajiya duk yadda kika yi dai-dai ne"

Dadi ya kamata! ta shiga jero masa addu'ar albarkar ubangiji a dukkan kasafin sa.

"Tunda ka yarda da hukuncin da nayi, duk da ba ka so! Ni kuma zan fada musu sati uku za ta yi maimakon wata guda".

Takaici ya sha'ke masa wuya, wai har sati uku, shi ya dauka anyi wuta ta yi sati biyu, to da fiye da wata ake nufi zata yi ko me?

Sa'adah na zaune a daki tana shayar da Jawad, shi yana falo yana musu guga, ya tattara kayan ya kulle ya kashe iron din saboda yadda jikinsa ya mutu da 'bacin rai.

'

Jiki a mace ya shiga 'dakin bai kalleta ba, ya wuce ya hau gado yana jin zazzabi na namen kama shi.

A gigice ta dinga tambayar sa lafiya kuwa, me ya same shi?

Jinsa shiru yasa ta shimfi'de Jawad! ta isa kusa da shi tana ta'ba jikinsa ta ji ko zazzabi ne yake san'darsa.

Ras ta ji jikinsa, sai rashin kuzari, ta shiga tambayar sa, ya kasa bu'de baki ya mata bayani, amma ganin zata masa kuka, ya fisgota jikinsa ya kankameta, yana sakin ajiyar zuciya.

Tsawon lokaci suna haka, cikin rashin kuzari yace "Tun yanzu na fara kewar ku"

Gabanta ya fadi ta kalleshi ido a bude "Tafiya zaka yi ka barmu?"

Sai kawai ta fara hawaye, ya kalleta yana jin sonta na sake daskarewa a zuciyarsa, shagwabarta, rauninta, soyayyarta na sake gigita shi.

Ya sake kankameta sosai yace " Kune dai za ku tafi ku barni, yanzun nan wayar da kika ji inayi!Hajiya Babba ce, wai na shirya miki tafiya gida, ki yi wankan acan".

Da'di ya cika 'kalbinta! ta ji tamkar ta tashi ta taka rawa, sai kuma ta ga yadda ya shiga damuwa akan tafiyar ta, idan har ta nuna murna! Tamkar ta baro bacin rai a tsakaninsu, dan haka sai ta hadiye dukkan murnar ta!

Ta tattaro dukkan damuwa ta yaba akan fuskarta da jikinta.

Cikin shagwabe fuska har da sake matso hawaye ta hau fadin

" Ni dai ba zan je ba, ai kaima kana kula da mu sosai".

Idan yace bai ji dadin kalamin ta ba yayi karya, ya shiga kissing dinta ba kakkautawa, ganin zai wuce iyaka, yasa ta katse shi, ta lura ya manta da halin da ta ke ciki na rashin tsarki.

Idonsa sunyi ja, sun kankance saboda fitina, ya zuba mata su,ya ce "Hajiya Babba da Innah ne suka zartar da hukuncin nan, hakuri zamu yi, mu yi yadda suke so".

Wani irin farin ciki ya sake kamata, amma a iya zuciyarta ya tsaya, tana jin zumudin sake zama da mahaifanta na taso mata.

Haka suka kwana yana jaddada mata irin kewarta da zai yi, tamkar wadda kasar za ta bari.

Kwanaki biyu a tsakani ta koma gida tare da dukkan abin da za'a bukata, Hajiya Babba ce kuma ta kaita kamar yadda ta yi al'kawari.

Sosai Inna ta ke kula da Sa'adah, wankan rumfu take mata ba tausayi, ga duren kunu, da tuwo, duk ranar da zata mata gardama kuwa cewa take yi " Na lura dakinki kike son komawa, zan 'kira Hajiya ta zo ta mayar da ke, tunda ina tattalinki, kina 'ki! idan kika kufu'de na ga yadda za kiyi rawar jiki akan mijin, ko shi ya yi rawar kai akan ki".

Shiru ta ke yi, kan dole kuma sai ta yi yadda Innar take so.

Jawad ya sami kyakkawan kulawa, kullum safe aka masa wanka ya sha nono, Inna take goya shi, haka zai yini a baya sai anyi azahar yake tashi, cikin 'kan'kanin lokaci ya bundume, kammaninsa da Mk suka bayyana 'karara.

A yini Mk na kiran Sa'adah kamar sau uku koma fiye, koyaushe cikin tambayar lafiyar su, ko yace Babana na kukan dare har yanzu, ko ya tambayi me take so, menene bata da shi, kar fa tace zata dinga 'dorawa Baffa nauyi.

Ire iren tambayar kenan a kullum, itakuma cewa take, komai akwai Uncle. Duka-duka ma yaushe muka zo ne?

Ranar da suka yi kwana biyar, ya je musu.

Ana idar da sallar la'asar ya Isa gidan, a zaure ya tsaya, yana faman kiran wayarta, tana ta ringing amma ba'a dauka ba, ya jingina da bango, yana ri'ke da wayar.

Baffah da yake faman jijjiga Jawad, saboda wankan da Inna ta ke yiwa Sa'adah, kullum ana idar da Sallar la'asar yake dawowa gidan dan ya ri'ke musu shi, su yi wankan, saboda riko da al'adar ba a barin jariri shi ka'dai.😁

Yau sai koke koke yake yi a dalilin cikinsa ya kumburaba a ankara ba, yana sa'be da shi a kafada ya doshi zauren, kwatsam yaga Mukhtar a tsaye.

Cike da girmamawa ya tsugunna ya gaida shi, Baffa sai fadin "ya ka tsaya anan? da ga yau ka dinga shiga kanka tsaye".

Baffah da kansa ya masa jagora har 'dakin Sa'adah yana cewa "wanka suke yi, zauna ka saurare su kadan".

Ya mika masa Jawad tare da fadin "dama so na ke na fita ana jirana za mu je dubiya asibitin Malam".

Cike da kunya ya karbe shi, yana masa godiya.

Baffah na shirin fita Inna ta fito duk ta hada zufa, ta kalle shi, ta ce "kwantar da abokin naka ka yi?"

"A a Babansa ne ya zo, yana gunsa, na shigo da shi, yana dakin Iyah ni fita zanyi, za mu je asibiti mu sake dubo Malam lado".

"Adawo lafiya, shikuma Allah ya bashi lafiya".

Ya fita, yana fadin "Ameen ameen".

Sai da ta sako hijabi sannan ta shiga suka gaisa da Mk, da yake ta fama da Jawad.

Ta karbe shi tana fa'din "Bari a masa wanka kar sanyin yamma ya sauka, ko idan ya ji ruwan dumi zai daina wannan koke koken".

Murmushi kawai ya yi, kansa a kasa, ya bata shi, a zuciyar sa tana jinjina kunyarsa, ko Idris din Sumayya bai kai shi kunya ba.

Yana zaune yana jin kukan wanka da Jawad ya ke tsalawa, jikinsa sai tsuma yake yi, yana jin tamkar ya leko yaronsa ko sabulu ne ya shigar masa ido, amma kawaici ya danne shi.

Ana cikin haka Sa'adah ta shigo da daurin kirji, ta yi mayafi da faffadan tawul.

Mamakin ganinsa a zaune ya daskarar da ita a tsaye.

Da azama tace " Uncle yaushe ka zo?"

"Tun dazu, dan Allah hanzarta ki dubo yaron nan , ki ji har shidewa ya ke yi?"

Ri'ke baki ta yi tare da cewa"oh oh wato Innah tace mini bani da kunya ko?"

"Haka yake da kukan wanka, da angama kuma ya yi ta barci, sai dare zai ishi Inna da kuka".

"Oh barinta ki ke da shi?"

Eh to, shi sai yace ba zai kwanta ba, sai dai a baya! itace kuma mai jure goyon, tace na kwanta na yi barci na huta".

"Amma kuwa dai ba ki da tausayi ko da ya ke, Auta ce ai".

Dariya suka yi a tare, ts shirya cikin doguwar rigar atamfa, irin dinkin masu shayarwa.

Ta zauna tana shafa mai tare da turare, ta yi cas, ta masa kyau, da gaske ta huce din, duk wani kumburi ya sace, fuskar nan da ta aune, duk ta sabe, ta dawo masa Sa'adatun nan mai burge masu kallon ta.

Yace "kin huce din fa Iyah, kin zama so mashallah".

Ta tura baki gaba, tace "ai so na yi na zauna kar na huce din, naga yadda zaka yi".

"Hmm ke dadina da ke misunderstanding dina kike yi sometimes".

"Iyah Iyah"

Ta mike da sauri tana amsawa ta fice gurin Innah da take 'Kiran.

" Zo ki dauke shi ki bashi ya sha, ashe cikinsa ne ya kumbura shiyasa kukan yau yafi na kullum, yanzu Ina bashi wannan maganin ya hau gyatsa, sai kuma ga tutu, dole sai canja masa Pampers din na yi"

Ta karbe shi tana fadin"Ayyah, sannu da kokari Innah".

Ta dawo dakin ta zauna ta fara shayar da shi, Mk da ya zuba musu ido yana jin duk wani bugun da zuciyar sa ke yi da kaunar su ta ke bugawa.

Sai da ya 'koshi, sannan ta mi'ka masa, ya karba yana mai masa kallon kurillah, yana ganin hoton fuskar sa, akan ta yaron.

Ya dago ya kalleta, ya yi kasa da murya sosai, sannan ya furta "Duk yadda kika yi ta makale min, ashe ba wani abin da kike tabukawa? dubi! ba wani abu, na ki a jikinsa".

Kunya ta kamata, ta kasa cewa komai sai ta buge da murmushi.

Haka suka sha hirarsu, ta na shan yoghurt din L&Z da ya taho mata da shi.

Kwana ashirin da haihuwar, Sumayya ta zo ganin Baby, tare da kayan uwa da jariri kala kala,sun zo juma'ah suka juya lahadi saboda makarantar Yara.

Ranar da ta cika sati uku ta koma dakinta, rawar jiki ba irin wadda Mk bai mata ba. Sun tabbatar sunyi missing juna, irin wadda ba su taba yi ba! haka suka cigaba da rainon dansu cikin tattali, da kulawa mai yawa.

Surayya Dahiru

✍✍✍

19/03.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

59-60

Irin kulawar da MK yake yi wa Sa'adah da danta, yasa take mamakin da ake cewa da zarar mace ta haihu sai namiji ya canja mata, ita kam ba ta ci karo da wannan matsalar ba, ta dinga tunanin ko don ta sami kyakkawan gyara ne a wurin Innarta da Sumayya, ko kuma dabi'ar wasu mazan ce haka?

Lafiya Lau suke zaune, har yanzu a cikin mararirinta yake tamkar amarya, hakan ba karamin faranta ranta ya ke ba.

Ya wadata su da komai daidai gwargwado, sannan da ya fahimci, ta fishi saurin fishi, sai ya ke kaffa-kaffa da abin da zai bakanta ranta, shi yasa zamansu lafiya, sai yan kananun sabani na yau da kullum da ba za a iya kauce masa ba. Kuma ba sa bari fishinsu ya wuce na yini daya.

Watan Jawad uku, Sa'adah ta kasa gane kanta, yau zazzabi, gobe mura, jibi jiri, kullum da abin da za ta tashi da shi.

Zazzabin hakori da rashin kuzarin Sa'adah, sai suka yi wa Jawad rubdugu, duk sun yi laushi.

Ganin yadda suke yamushewa ya sa MK ya kai su asibiti, gwajin farko ya nuna ciki ne a jikinta, na tsawon sati hudu.

Dankari! tun a asibitin take kuka, bakin ciki ya turnuke ta, da danyen goyo za ta sami wani cikin? kuka take yi sosai tana fadin sai dai a san yadda za'a yi, amma ita ba ta shirya sake haihuwa yanzu ba. Tun MK na rarrashin ta bari suje gida, har ya gaji ya kama bakinsa ya zuba mata ido.

Suna shiga gidan ko zama ba ta bari sun yi ba, ta ce

"To mun zo gidan fada mini yadda za'a yi".

Ya kalle ta da tausayawa ya ce "Zauna ki nutsu, ki huta sai mu yi maganar, ba inda zani yau, ina tare da ke".

Ba tavce komai ba, ta zauna tana huci, tana jin duniyar ta mata kunci.

Shi kuma ya shige cikin daki ya shimfide Jawad da ya yi barci.

Yana fitowa kicin ya wuce, ya zauna ya dafa musu indomie, ya juye a plate, ya kai gabanta ya ajiye, ya koma ya hado tea Sai da ya zauna sannan ya kalle ta ya ce, "Bismillah sauko mu ci."

Hawaye na bin fuskarta ta girgiza kai tare da fadin "Na koshi".

Ya kafe ta da ido, ya nisa ya ce "Me kika ci?"

Ta kasa ba shi amsa, tunda dai ba su karya ba, suka yi sammakon fita.

Ya sake kallon ta, sai goge hawaye take yi, har ransa shi ma bai so samuwar cikin nan a yanzu ba, amma tunda ya riga ya shiga, to ba zai ba ta kofar da za ta yi abin da take so ba.

"Idan har na gama cin abincin nan ba ki ci ba, fita zan yi, ba zan yi maganar da zamu yi a yau ba kuma".

Kan dole ta wanko hannu, ta fara ci, turawa kawai take yi, saboda gabadaya ba ta jin dadi, ga kuma bakin ciki da ya cika mata zuciya.

Sai da ya hada mata tea, ta sha, ya ba ta magani, ya dauke plate da cups din ya kai kicin ya dawo! ya zauna kusa da ita sosai.

Ya sassauta murya cikin lallashi ya ce, "Fada mini matsalar ki akan cikin nan, da kike ta wannan koke-koke da bacin rai".

Cikin kukan ta ce "Har sai na furta matsala, sannan za ka fahimci matsalolin da suka dabaibaye ni?"

"E fada mini mana wata'kila sai na fahimta a yanzu".

Ta goge fuskarta da ta yi kozai-kozai, sannan ta ce "Ba ka ga Jawad har yanzu jariri ba ne? sannan wannan cikin ba irin waccan ba ne, yau kusan sati uku ban da cikakkiyar lafiya".

Ta yi shiru tana jan hanci.

Sai da ya ji shirun ya yi yawa sai ya ce "shike nan matsalolin?"

"Ba shike nan ba, yanzu fa wannan lalacewar da Jawad ya fara yi, yana ta tsinkewa, cikin da yake sha ne, kuma bai isa yaye ba".

Da azama ya ce "Duk na fahimce ki Sa'adah, har zuciyata kuma tausayinku nake ji musamman Jawad, amma tunda Ubangiji ne ya ba mu ya za mu yi? Sai mu raini abin mu cikin farinciki da godiyar Allah".

Kukanta ya dan kara yawa ta ce "Yaye Jawad din za'a yi ke nan?"

"Wane irin yaye kuma ba dadin ji? Ai kin ji bayanin likita, ga magunguna nan ya rubuto muku, ba abin da zai same shi".

Maganganunsa suka haska mata sai ta haifi cikin nan dole, don haka ta dage ta dinga zunduma masa ihun kuka da ya yi sanadin tashin Jawad a gigice, shi ma ya cika dakin da kuka.

MK ya rasa wanda zai lallaba a cikinsu, dole ya wuce daki ya dauko yaron ya fara jijjiga shi.

Sai da ya yi shiru sannan ya kalli Sa'adah da take kuka irin na mutuwar Jahiliyya ya ce "Wane irin abu ne haka kike yi?"

Ba ta kula shi ba ta ci gaba da yin kukanta hannuwa aka.

Kan dole ya zauna kusa da ita yana cewa "Ki ga fa yadda kika sa Jawad kuka, don Allah ki yi hakuri, ke baki san baiwa ce Ubangiji ya yi mana ba?"

"Ni ba na so!" Ta fada da karfi.

"Shike nan na ji ba kya so, ni Ina so". Ya fada da alamun ya ji haushin maganarta.

"Karbe shi, ki ba shi ya sha".

Banda kuka ba abin da take yi, ko kallon sa, ba ta yi ba bare ta karbi yaron.

"Kin ji".

Ta kalle shi cikin ido ta ce "Na yaye shi".

Ganin yadda ta rikice neman tashin hankali take yi da gaske, ya ce "To ba shi ya sha yanzu, kafin a jima na siyo masa abin da zai dinga sha".

Nan ma a zafafe ta ce "Ba zan bayar ba".

Kyale ta ya yi, ya ajiye shi ya hado masa shayi mai dan dumi, ya dauko sabuwar feeder ya wanke ta da ruwan zafi, ya zuba shayin a ciki, sai ya zauna sannan ya dauke shi, ya fara ba shi, cikin ikon Allah ya shanye har da gyatsa.

Ya hada ruwa ya masa wanka, ya shirya shi tsaf, yana ta yi masa wasa, shi kuma yana ta dariya har barci ya sake awon gaba da shi, bai kwantar da shi a dakin Sa'adah ba, ya fita ya kai shi dakinsa don kar kukan uwarsa ya sake farkar da shi, ya rage masa karfin fanka sannan ya fita zuwa wurin Sa'adah, da har yanzu take yin kuka.

A kasan da take zaune, shi ma ya zauna ya ru'ko hannun ta, ya kira sunanta, ta ki amsawa, ya sake tausasa murya ya ce "Yi hakuri tashi muje na taimaka miki ki yi wanka, ki ji dadin jikin ki. Yi hakuri kin ji my sweetheart".

Da kyar ya shawo kanta ta yi wanka, bayan ta ce ba ta son taimakon nasa.

Mai kawai ta shafa ta zura doguwar riga cotton marar nauyi, ta kwanta, tana ta ajiyar zuciya ba jimawa barci ya wuce da ita.

Kwanaki uku ban da tashin hankali ba abin da Sa'adah take yi gaba'daya ta burkice, ban da kuka ba ta komai, ko wanka ba taki yi, bare aje ga hidimar gida, Jawad kuwa da tashin hankali take bashi nono sau biyu a rana duk kukan da zai yi kuwa.

MK ganin ba irin ha'kuri da rarrashi da bai yi mata ba, yasa ya zuba mata ido, shi yake yin komai na gidan har girki, ya ki yarda ya biye mata, ya tabbatar tana cikin halin da za a tausaya mata, duk da abin nata har da rashin mutunci, amma da zarar ya tuna abubuwanta na alheri sai ya mata uziri, babban abin da ya dame shi, rashin shayar da Jawad musamman da yake ana ba shi supplement na yara mai sa su kuzari da saurin girma, akai-akai yake jin yunwa, don ma yana shan madara da fricso cream.

Washegari da yamma ya dawo da ga wurin aiki tun daga waje yake jin kukan Jawad, a sukwane ya shigo cikin gidan, ya tarar da ita, tana zaune a falo tana ganin sa, amma ba ta dauke shi ba.

Bai taba jin haushin ta irin na yau ba, ya jima yana tsaye ya zuba mata ido, yana kallon ta, yana jin tamkar ya rufe ta da duka.

Kwafa ya yi, ya dauki yaron ya hada masa abincinsa, ya ba shi ruwa sannan ya kwantar da shi, yana ta shure-shuren 'kafa, tamkar ba shi ne mai kukan nan ba, da ma shi ba mai fitina ba ne, indai ka ji kukansa to dayan biyu ne, ko yunwa ko rashin lafiya, tunda ya yi kuka kafin su yi arbain shike nan ya daina kukan banza.

Wanka ya yi, ya fito ya zauna a falo, ya dube ta ya ce "Na gaji fa da abubuwan da kike mini, na yi iya hakurin da zan iya, na ga abin naki babu mutunci ko kadan".

Kai tsaye ta ce "Da ma ai so nake ka gajin, matu'kar kana son zaman lafiya, sai dai ka zabi daya cikin biyu, ko dai a yaye Jawad gaba'daya, ko a cire cikin nan".

Ransa ya yi matu'kar baci ya kalle ta ya ce "Ni ban san inda ake cire ciki ba, ke da kika sani sai ki je, ai don kin ga na damu da ke shivyasa kike mini wannan iyashegen, mafi yawa idan mace ta samu ciki da wuri irin haka, daga wurin mijin take fuskantar kalubale, amma ke don samun guri ni kike yiwa wulakanci".

Ya nisa sannan ya ce "Ba zan kai kararki ba, amma daga yau ba zan sake rarrashin ki akan wannan matsalar ba, idan kin ga dama ki bar cikin nan, idan kin ga hagu ki zubar a rariya, Jawad kuma In sha Allah yau an yaye shi, Ubangiji zai raya mini shi, ina ce idan mutuwa kika yi ma ba zai fasa rayuwa ba?"

Daga haka bai kara cewa komai ba, ya tashi ya shiga kicin ya hada cornflakes ya shige dakinsa, bai dawo falon ba, yana kudire ba zai sake dafa abinci ba.

Bai wani jima ba ya shigo, ya tashi Jawad ya canja masa riga, ya samo leda mai kyau ya zuba tarkacen da Jawad zai bu'kata, ya nade shi a shawul, ya saba shi a kafada ya fice, ba tare da ya kalli gefen da takep a zaune ba, bare ya yi mata sallama.

Kawai sai ta ji kuka ya zo mata, bakin cikinta daya yadda bai dafa musu abinci ba, kuma yunwa take ji, ta kalli agogo biyar da kwata 5:15pm, kan dole ta shiga kicin din ta hada tea ta dauko biscuit din super2 ta hau ci.

Gidan Samira da yake Dan'agundi ya tsaya ya ba wa yaro ya kai mata Jawad, sai da ya kira ta a waya ya tabbatar ta karbe shi, sannan ya tari Adaidaita ya wuce shagon askinsa, yana tafe yana tunani biyu, na yadda zai bullo wa Sa'adah, da na sayan motar da yake shirin yi.

Tana zaune har taran dare ba MK ba Jawad, hankalinta ya tashi, ga wata muguwar yunwa na addabar ta, ta rasa inda za ta tsoma ranta ta ji dadi, kewar Jawad ta addabe ta.

Sai goma saura ya dawo, a dakinsa ya ci burki, ya kwantar da Jawad da yake ta barci, tunda Samira ta masa wanka ya yi barci. Sai da ya gama komai tunda ga

wanka, har shafa'i da wutiri, ya nufi gurin Sa'adah, tana zaune a falo ta rasa me yake damunta.

Sallama ya yi bai jira amsawarta ba, ya shige daya dakin inda nan kayan Jawad suke, akwati babba ya dauko, ya hau zuba sabbin rigunansa da ba a kai ga bude su ba, sannan ya zuba na cikin drower kayansa, hatta bargonsa sai da ya saka cikin akwatin, da kyar ya zuge sannan, ya kashe fitilar, ya ja akwatin zuwa dakinsa, da ido ta bi shi, tana sake jin tashin hankali na kamata.

Dakin ta shiga, ta hau dubawa, ta tarar ba kayan Jawad sai tsirarru wadda suka fara yi masa kadan, sai dryar shanya.

Kuka ya kwace mata, tana raya duk bala'i, ba inda za'a kai mata yaronta.

Tana fitowa shi kuma ya shigo, ya zauna a kujera ya ce "Zo ki zauna, magana za mu yi."

Ba ta ki ba, ta zauna din, yana kallon yadda ta lalace tsabar fitinar da sanya a ranta.

"Gobe zan yi Asubanci zuwa Lagos, jirgin karfe shida zan shiga, kafin sallar Asuba Mahmoud zai zo ya kai ni Airport, zan kai Jawad wurin Anty Hafsa."

Kafin ya karasa ta fashe da kuka tamkar yarinya karama tana cewa " Billahillazi ban yarda ba, jaririn yaron za ka kai har Lagos?"

Dariya ta so subuce masa, ya cije yavce, "Ba yardaki na nema ba, fada miki na yi, saboda kina da hakkin ki sani".

"Idan na yarda Allah ya tsine mini, ai da ma na san yanzu ba ni da wani muhimmanci a gurinka".

Ficewa ya yi ya bar ta, ba tare da ya ba ta amsa ba, yana jin farinciki, da dukkan alamu shawarar Mahmoud za ta yi tasiri.

Kwanciya ya yi, bayan ya kashe fitila, addu'a ya fara yi, kawai ya ji ta shigo masa ba sallama.

Tasa hannu ta kunna fitilar dakin, suka kalli juna, na tsawon sakwanni, wani abu na taso musu a zuciya.

Shi ya fara dauke idanuwansa, murya ba amo ya ce, "Kin san dai ba na iya barci da haske a kaina ko? Yanzu kuma na gama fada miki Asubanci zan yi, don Allah ki bar ni na yi barci".

"Ka tashi mu yi magana".

"Ki adana maganar ki, idan Allah yasa na dawo lafiya, gobe irin wannan lokacin sai mu yi maganar".

"Wallahi yanzu za a yi ta". Ta fada cikin rawar murya hadi da kuka.

Ta zauna kusa da kafafuwansa, tana cewa " tsanar da ka mini har ta kai ka kaurace mini, sannan ka raba ni da yarona?".

"Ni ban kaurace miki ba, ba kuma zan raba ki da danki ba, kin taba jin inda aka raba uwa da danta? ko'ina na kai shi, ina tabbatar miki wataran da kansa zai neme ki. Ke kika ce idan ina son zaman lafiya sai dai a yaye shi, zaman lafiyar nake so".

"Wallahi ba zaman lafiya kake so ba Uncle, kawai so kake ka sake jefa ni cikin wani tashin hankalin, ai ba a nan kake kwana ba, sannan mene ne na kai wannan dan kilifin halittar har Lagos?"

"Kin ga Sa'adatu ni kwana a nan dakin ba ina nufin wani abin ba ne, kullum ni nake bin ki dakinki for more than a year, ke mai yasa yau ba za ki zo nan ba, ko kin zo na kore ki?"

Jikinta ya yi sanyi da jin kalmar Sa'adatu a bakinsa ta san fushi yake da ita.

A hankali ta furta, "So nake ka fasa tafiyarku Lagos".

"Ba zai yiwu ba, na riga da na fada mata gobe tasa a tare ni a Airport, kuma sai na koma nace na fasa zuwan?".

Ta fara kuka tana fadin, "Ba na son tashin hankali Uncle, na roke ka kar ka raba ni da yarona".

"Yau kusan sati ina fama da ke, ba irin ha'kuri da rarrashi da ban miki ba, amma kin runtse ido kina mini diban albarka, ko daukar yaron nan sai na miki wuta-wuta kike yi, dazu ga ki, ga shi, amma kika bar shi yana tsala kuka, zan zauna kullum a gida ne? Dole zan fita. Bayan haka kin daina yin komai a gidan nan tun daga kan shara, da girki, duk ban ce komai ba, ina yi, duk da haka ban tsira ba, duk maganar da ta zo bakin ki fada mini kike yi, har ki kalli idona ki sa mini sharadi idan ina son zaman lafiya sai na yi kaza".

Jikinta ya sake yin laushi, bai ba ta damar yin magana ba ya zarce da fadin, "Kin yi strike din wanka, da yi mini magana, akan cikin da ba ni kadai na samar da shi ba, ikon Allah ne. Kin san adadin matan da suke jika filon su duk dare a dalilin rashin haihuwa? Kin san adadin matan da suke fuskantar tashin hankali akan rashin haihuwa, ALLAH kadai Ya san adadin ba'kin cikin da irin wadaccan matan da suke cikin jarrabawar rashin haihuwa suke ciki, ke Allah ya ba ki, ba tare da kin sha wahala ba, ya sake kara miki, maimakon ki zama cikin bayi masu godiya, sai kika zama cikin masu butulci".

Zuciyarta ta yi sanyi, salama ta shige ta, ta fara fadin, "Astagafirillah!" A zuciya.

A fili kuma sai ta tsinci kanta da cewa "Ka yi hakuri".

Dadi ya lullube shi, amma bai nuna ba, ya ce "Ya wuce." A gajar ce.

Ya zuba mata ido yana ganin yadda idonta suka fada ciki, bayan rashin lafiya ya tabbatar har da yunwa ke sakadar ta.

Kafin ya yi magana ya ji tana cewa yunwa na ke ji.

Ya basar ya ce, "Babu kayan abinci ne a gidan?"

"Kwana biyun nan fa ba ni da lafiya, na san kuma idan ba na jin dadi kai ne kake dafa mana".

Ya hararetа kadan sannan ya furta, "To na daina yi tunda ba kya gode mini, ba kya ganin kokarina".

Ta yi kasa da kai, sai kuma ta mike ta shiga toilet din dakin, ta yi wanka sosai, tana ayyana yau kwananta uku ko hudu ba wanka, ta fito ta tafi dakinta, ta shirya cikin Riga da wando iya guiwa na barci, ta feshe jikinta da turararukanta masu tsuma zuciya, sannan ta koma dakinsa.

Inda ta tashi nan ta sake zama, ya dago ya kalle ta, yana jin tamkar ya rungume ta, fiye da sati bai ganta a nutse haka ba, kamshinta, sai ratsa shi yake yi.

Ya dan kalle ta kadan sannan ya ce "Ba za ki kashe fitilar ba, na ce miki barci nake son yi kada na makara".

Kafin ta yi magana Jawad ya farka, ya fara kukan neman abinci.

Da sauri MK ya dauke shi, sannan ya fara hada masa Madararsa da take kan side drower, tun dare ya ajiye komai na bu'katar Jawad kusa da shi, jego ya same shi a kwatsam😀

A kunyace ta matsa kusa da shi sosai, ta mi'ka dukkan hannu ta ce "Kawo shi".

Bai musa ba don kuwa, so yake ta ba shi nono, amma ya riga da ya kudire ba zai kuma rokon ta ta shayar da shi ba.

Ya mika mata, yana ci gaba da kokarin hada masa madara, rabin hankalinsa kuma na kan Sa'adah da I'm ya ga ta kwantar da Jawad a jikinta ta na kiciniyar shayar da shi.

Da'di ya kama shi, amma sai ya waske da cewa "Gaskiya da ba ki ba shi ba, tunda dai ya saba yinin yau bai sha ba, da an bar shi, tunda gobe ai ba sha zai yi ba".

Tura baki ta yi, sannan ta ce "Zan ba shi mana".

"Lagos din za ki bi shi, ki ba shi?"

Cikin shagwabe fuska da kuma hawaye ta ce "Na ba ka hakuri fa, ka ce ka ha'kura, ba sai a fasa tafiyar ba".

Ta yi shiru yana kallon ta, yana kuma kallon yadda Jawad ke ta faman shan nono ba kakkautawa.

Tsintar kansa ya yi da tambayar ta mai za ki ci?"

Kanta a kasa ta ce "Komai na samu zan ci, amma mai zafi"

Ya kalli waya ya ga shadayan dare, ya mike ya shiga kicin ya dade a tsaye yana tunanin mai zai mata mai sauki? Ya bude fridge ya ga akwai ragowan ferfesun naman kaza duk da ba shi da wani yawa, ya fito da shi, a tunaninsa ta cinye tunda yasan ta da son kaza, sannan ta ki yin girki.

Ya dumama ya juye a bowl, ya hada tea sannan ya dauko bread, duk ya shirya a kan tray, ya dauka ya kai mata dakin.

Har a lokacin kuma Jawad sha yake yi.

Kusa da ita MK ya zauna, ya ce "Kawo shi ki ci abincin kar ya huce, a hankali ta dago yaron da yake shirin yin barci, ta mi'ka masa, Jawad jin an raba shi da abincin sa, yasa kuka, sai dai da yake ya koshi, dan jijjiga shi kadan Babansa ya yi ya koma barcinsa, yayin da Sa'adah take ta cin abinci tamkar tana ci da wani.

Sai da gama ta gane jirin da ta yini da shi na yunwa ne.

"Uncle ba ka ba ni ruwa ba, ya sake zuba mata wata irin hararar kauna ya ce, "Kar ki sha ruwan, ke wannan abincin ma dana hado miki biyan ki na yi, kin shayar min da yaro na, saboda adalcina, ni ma na miki ya kamata".

Dariya ta kama ta sai ta bige da cewa, "Ke nan dai Jawad ya fi ni a gunka?" Ta fada cike da shagwaba.

Shiru ya mata, ga mamakinsa, sai ji ya yi ta kafa masa kuka, ya tashi ya zauna, ya kalle ta sosai ya ce "Kin koshi ba! Shi yasa za ki dora daga inda kika tsaya? To Allah ya baki sa'a".

Ta kara karfin kukanta tana fadin, "Ruwa zan sha, wayyo cikina".

Kan dole ya tashi ya dauki tray din gabanta, ya fice, ya dawo da ruwan ya dangwarar, yana fadin "Ki ci gaba da yi mini iyashege".

Haka ta dauki ruwan ta sha, sannan ta ce, "Thank you dear!"

Bai kulata ba, ya ce "Idan kin gama sai ki kashe mana fitilar".

Da rarrafe ta isa gefen gadon da yake kwance, a durkushen ta kamo hannuwansa ta ri'ke, cikin rauni ta ce, "Am sorry dear, na gane ban kyauta ba, ka yi mini afuwa, ka manta duk wani inconveniences da ya faru pls".

Bai ja ba , ya ce "Shike nan na yafe miki, amma ki dinga sanin abin da za ki dinga fada mini".

Da azama ta ce "In sha Allah, sannan don Allah ka hakura da kai Jawad Lagos, idan Allah ya kai mu na haihu sai ka kai shi, sannan ya kara girma".

"Wannan ne kuma ba zai yiwu ba, ba kula shi, kike yi ba, idan na fita kullum hankalina, ba a kwance yake ba, Allah-Allah nake na dawo na kula da shi, kin ga aikina yana bu'katar nutsuwata, don haka ki yi hakuri, idan ya isa shiga makaranta zan dauko shi, idan kuma ta nuna sha'awar ci gaba da rike shi, to zan bar mata".

Ta sake ri'ke hannun sa sosai, tana fadin, "Wallahi zan kula da shi fiye da yana jariri".

"Na ji zan bar shi amma bisa sharadi".

Da sauri ta ce, "Ina jin ka ko mene ne zan yi"

Ya kalle ta ya ga ta matsu ta ji sharadin.

Ya nisa ya ce "Ba za a yaye shi ba har sai na ce".

Da sauri ta ce, "Na yarda, har sai na haihu ma".

"Ni ba ruwana da haihuwa, ko kin haihu idan da yiyuwar ya ci gaba da sha, za ki dinga shayar da shi, idan lokacin sa ya yi, sai a cire shi! Idan kin amince da haka shike nan, idan bai miki ba, tabbas gobe zai bar gidan nan".

Kai tsaye ta ce "shike nan na amince".

Ya janyo ta, ya kwantar da ita a saman kirjinsa, yana shafa bayanta, yana fadin, "Allah Ya miki albarka Ya sauke ki lafiya."

Yana ta ba ta misalai masu dadi, ba akanta aka fara irin wannan ba, sannan matan so ne su ke yin kwane.

Rawahul Mk.

```Alkalamin

*Surayya Dahiru*

✍

*HALIN YAU*!
```

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

61-62.

Washegari da karsashi Sa'adah ta tashi, kafin karfe bakwai na safe, ta kammala soya dankalin turawa da sauce, gefe kuma ta dama kunun gyada da ake yi da danyar shinkafa.

Sai da ta share falon, sannan ta kai kayan abincin bayan ta shimfida ledar cin abinci.

Tana cikin share tsakar gidan ya fito yana sabe da Jawad, ya kalle ta, ya ce, "sannu da aiki." Ba tare da ta dago ba ta amsa da, "yauwa!"

Yana tsaye yana kallon ta har ta gama shararta ta kwashe, ta wanke hannuwanta, sannan suka rankaya zuwa falon, shi ya zuba musu, suka karya, Jawad na kwance yana ta shure-shure da furzar da yawu tabbacin yana cikin yanayin masu yin hakori.

Suna kammalawa, ya shiga wanka, ya fito a shirye cikin shudin (blue) jeans da fararar shirt, mai yarfin blue, sai tashin kamshinsa yake yi.

Har cikin dakinta ya bi ta ya tarar wanka ta yi wa Jawad, tun kafin a gama shirya shi ya yi barci.

Cike da farinciki ya mikar da ita tsaye, ya ja ta jikinsa, ya rungume, ya rasa kalmar da zai fada mata, kowacce kalma sai ya ga ta yi kadan ta wakilci yadda yake jin ta a rayuwarsa, a karshe dai cewa ya yi

"I really love you Sa'adah. Stay blessed!" Ya sake ta ya juya ya tafi ba tare da ya sake cewa komai ba.

Ta dade a tsaye, cikin sanyi jiki, kalaman ba karamin tasiri suka yi a zuciyarta ba, da kyar ta tattara kayan Jawad ta mayar da komai inda yake, ita ma ta yo nata wankan ta shirya, ta kwanta kusa da Jawad, suka sha barci, don sai kusan sha biyun rana suka farka, ta fara kokarin hada abincin rana.

Haka rayuwarsu ta ci gaba da gudana, ranar da tashi da karfin jiki, za ta yi komai, ranar da kuma jikin ba dadi zai yi abin da zai iya, kullum cikin tattalin ta yake, ba ya kaunar abin da zai tunzura ta, mai ha'kuri ne, amma a wannan yanayin da gimbiyar take ciki, ya sake ninka hakurinsa akan lamarinta kwarai da gaske yake tausayin ta.

Har cikin ya shiga wata shida ba wanda ya sani, saboda kwatakwata ta ki fita, duk son ta da ta fita unguwa musamman gidansu, ko gidan su MK, amma yanzu juyin duniya ya yi da ita, fur ta ki zuwa, sai dai ta gaishe su ta waya.

Tun Inna ba ta damuwa da rashin zuwanta har ta fara damuwa, idan lissafin ta daidai ne tunda ta koma gidanta sau daya ta je musu, sannan aka yi wattanni shida da zuwan.

Ranar nan suna waya ta ce, "Iyah wato yanzu Jawad da mijinki sun debe miki kewata ko?"

Da sauri ta ce, "Haba dai Inna! Kullum fa idan ban ji muryarki ba, kin san ba na jin dadi, har yaushe na same su! da za su dauke mini hankali?"

"To ai gani na yi muna gari daya, amma ki iya shafe rabin shekara ba ki zo kin gan mu, mun gan ki ba. Mijin ki duk bayan sati biyu zai zo ya gaishe mu, abin mamaki har ki iya ba shi Jawad ya kawo mana, amma ke shiru! Anya za ki yi imani kuwa?"

Jin haka ya sa Sa'adah ta fashe da kuka, tana fadin, "Ban da lafiya fa Inna duk zuwan da Uncle din yake yi bai taba fada muku ba?"

A gaggauce ta ce "Me yake damun ki?"

Kuka kawai take yi, da kyar ta ce "Ni dai idan na mutu ki yafe mini, ba da gangan na ki zuwa ba".

Sai ta katse wayar tana goge hawayen, a fili ta ce, "Na san gobe zan gan ki kin zo, kin ga abin da nake boyewa."

Hakan kuwa! Inna kwana ta yi tana zullumin wane ciwo ne ya addabi Iyah haka?

Karfe goma na safe ta isa gidan don ma Baffa ne ya hana ta fitowar sassafe, da tuni ta dade da zuwa.

Mamakin cikin da ta gani jikin Iyah ya zarta wanda ta yi a lokacin cikin Jawad, ta rasa mai za ta ce musamman da ta ga ya yi kwari, har yana shirin fitowa duniya.

Ganin irin kallon mamakin da Innar ta bi ta da shi, yasa ta kifa kai a hannun kujera ta fara sana'ar kuka.

Da tausayawa Inna tace, "Ni kin san akan koke-koken nan naki, muke batawa, mene ne kuma na kukan? Mene ne yake damun ki?"

Sanin bata da matsalar komai sai na cikin nan da ya mata shigar sauri yasa ta kasa cewa uffan.

"Idan na fahimce ki, halin da kike ciki yasa kika mayar da kanki mujiya a cikin jama'a, ke baki san baiwa ce Uabngiji ya miki ba, ai ba kowacce mace ke samun damar samun irin wannan haihuwar ba".

Ta ja numfashi ta ci gaba da cewa "jiyan nan aka mana tarihin Nana Fadima a Islamiyyar da na shiga, ashe Sayyadi Hassan da Sayyadi Husain ba tagwaye ba ne?

Duk zatona 'yan biyu ne, ashe daban-daban aka haife su amma Malamai sun yi ittikafin wata goma sha daya ne tsakanin su, ashe matar da tayi irin wannan haihuwar abin alfahari ne a gurinta, abin a mata barka ne, don kuwa albarkar diyar Ma'aiki ta samu".

Haka ta dinga rarrashin ta har ta sami nutsuwa.

Ta kara da cewa "Har addu'a nake miki kar ki yi irin haihuwa ta, ko irin ta uwar mijinki, kin ga dai shi ma su uku ne a dakinsu, da bakin ki kika ce mini sai da ya shekara goma aka haifi Ahmad kaninsa, ni kuwa tun a kanki aka rufe mini kofa, ki kwantar da hankalinki, idan Allah ya sauke ki lafiya, idan mijinki ya yarda zan daukar miki Jawad ke ki ji da jariri ko jaririya".

Sai Azahar ta tafi, har girki ta mata, sannan ta tafi ta bar Jawad na kukan zai bi ta ya gan ta da Hijabi.

Ba ta da'de da tafiya ba, Sa'adah ta dinga jin kwankwasa kofa, ta san ba Mk ba ne tunda da key a hannun sa budewa kawai yake yi shi yasa ba ta sa sakata.

Da Jawad a hannunta, ta fita ta bude kofar, ta yi turus ganin Halima da Safina a tsaye, cikin kwalliya ta burgewa sai kamshi suke yi.

Har suka shiga cikin gidan wani irin kallo suke mata, na uku saura kwata, suka zauna, ita kuma ta fice zuwa kicin ta zuba pure water mai sanyi, akan tray, ta kawo musu tana cewa "Sannun ku, daga ina kuke haka?"

Safina ce ta ce "Daga makaranta kin san sai yanzu aka fara daukar sababbin dalibai saboda dogon yajin aikin da ASUU ta yi".

Sa'adah ta ri'ke baki ta ce "Oh kuce da students nake tare, wane course kuke yi?"

Still Safina ce ta sake cewa dukkan mu Diploma in Public Administration muke yi, ba mu samu degree ba, saboda points din mu ba su kai ba, amma a satin nan zamu cike JAMB tunda an fara za mu sake trying".

"Ma Sha llah! Congrats, na muku murna, ni ma In sha Allah zan yi JAMB din, gara da na ji da wuri, amma ni Sociology ne zabina ko kuma English Language".

Sai lokacin Halima ta ajiye wayarta da take ta latsawa ta dube ta sannan ta ce "A ina za ki yi wannan karatun da kike fa'da?

Kai tsaye Sa'adah ta ce " B.U.K mana".

Dariya Halima ta yi irin ta iyashege sannan ta kalle ta, ta kalli cikin jikinta, ta sake mahar da kallon ta ga Jawad, ta ce, "Sai dai idan a gaban Uncle za ki yi karatun, tunda shi ma harshen Turanci ya karanta, yake kuma koyarwa".

"Ban gane ba?" Sa'adah ta tambaya da alamun karin bayani.

Ba kunya ba komai Halima ta kalli cikin idonta ta ce "Na ga ya mayar da ke akuya ne, ke kuma kin biye masa, don Allah dubi yadda kika zama just one year da aure".

Kalmar akuyar nan ta bugi Sa'adah, ta kasa hakuri ta ce, ni ce na zama akuya?"

"To mene ne banbancin ki da ita? Ki kalli kanki mana, 'da a hannu, 'da a ciki".

Idon Sa'adah ya cika da kwalla tabbas da gaskiyar Halima irin haihuwar akuya za ta yi.

Kafin ta yi magana, Safina ta tsoma baki ta ce "Ni fa tunda na zauna mamakin Gogel nake yi, ta saki jiki za ta mayar da kanta tamkar irin jakunan matan nan na kauye da ba su san komai ba sai dai su ci, su haihu duk shekara, duk iyashegen da namiji zai musu ba yadda za su yi saboda sun tara garke da shi, yo a wannan karnin wacce macen ce za ta yi irin wannan?"

Halima ta cafe da fa'din "Ba ki ga yadda ta susuce ba? tamkar ba Gogel fine girl din nan ba, duk ta tsofe, ta sakar masa jiki, shi ya tsotseta da daddare, dansa ya yini yana tsotsarta, duk kuma abin da zata ci sai anraba musu da unborn, in and out suke lasar ta, ba dole ta fita a hayyacinta ba".

"Sai ikon Allah, ke da karatu, sai ya gama tsofar da ke, kin daina burge shi, kiga ya dallo sabuwar yarinya, da ilimi ya gogar da ita, tunda kullum yana ganin yan mata sabbin 'kyan 'kyasa".

Hankali Sa'a ba karamin tashi ya yi ba, saboda yadda ta gasgata maganganunsu, mussaman da tasan kullum a cikin ganin tsala tsalan yan matan Jami'a ya ke.

A sanyaye tace "ya zanyi ne? ni kaina ban shirya haihuwa yanzu ba, sannan kuma shine yaki yarda! da nace sai dai a cire"

Dukkansu dariya suka sa mata, sai da suka tsagaita da dariyar! sannan suka ce, mai

yasa da kika yi arbain, ba ki je asibiti an dora ki akan maganin tsarin iyali ba?"

Kafin ta amsa, sun zarce da fadin " kar ki sake yin ganganci irin haka, idan kuma kin ki ji, ba Kya ki gani ba".

"Tuwo Inna ta yi mana zaku ci ko na dafa muku indomie?"

Shiru suka yi tamkar basu ji ba, sai can kuma Safina tace "Ni kam bana cin tuwo".

Halima bata dago ba, tace yi Indomie din kawai, amma plz kisa mana pepper sosai".

Haka ta dafa musu indomie da ta ji albasa da attaruhu, ta hada musu lemon Tang a jug ta fasa kankara ta jefa a ciki.

Sai da suka ci, suka gyatse, suka yi la'asar sannan suka tafi bayan sun jefa mata wasiwasi a zuciyar ta.

Daf da maghrib ya dawo gida, a gurguje yayi wanka ya tafi masallaci, sai da ya dawo, ya dauko musu abincin, suna ci, ya lura Sa'adah ba ta da walwala sosai, ya tambayi ko bata jin dadi ne! ta ce kalau take, ta isar da sakon gaisuwar Inna, da fara'a ya ce "Ina amsawa, ta biyo sawunki kenan? Ina fatan dai kin fa'da mata, bani da alhakin rashin ganin ki a gidansu?"

Kai tsaye ta ce "ko ban fada ba, ai tasan kaine, tunda ka mayar da Ni Akuya".

Maganar ta shige shi, amma sai ya ce ban gane na mayar da ke akuya ba?"

"Eh mana wata biyu da haihuwa ka sake dirka mini wani cikin, ai akuya ce mai hakan".

Ya kalleta soasai ya tabbatar wannan maganar ba daga zuciya da kwakwalwarta ta fito ba, ya kuma tabbatar ba a bakin mahaifiyarta ta ji ba.

Ya numfasa yace " Inna bata yi farincikin ganin ki da cikin ba kenan?"

"Hmm ita da take ta murna wai dama har addu'a take yi mana kar na gado rashin yawan haihuwar su ita da Hajiyar Bichi".

Ya sauke ajiyar zuciya, hankalinsa ya sake tashi, tabbas akwai wacce ta zo take kokarin birkita masa zaman lafiya a gidansa.

A zahiri sai ya murmusa ya ce " Ashe adduar Innace ta sauka akan mu, ba wai akuya na maida ki ba".

Ta tura baki gaba, tana jin ba zata sake yarda ta yi irin wannan gangancin ba a gaba.

A kicin ya ga tray din da aka ci indomie mai dauke da fork guda biyu.

duk yadda akayi wadannan bakin da ta yi ne, suka kitsa mata maganganu, tunda duk boren da ta masa a farko, ai tunanin ta bai bata irin wannan kalamin ba.

Bai sake shan mamaki ba, sai da suka kwanta, ya ji ta ce zasu yi magana, ya ce "Ina jinki".

"Uncle so nake yi nima na cike jamb foam".

Ya ji zuciyar sa ta buga, sai ya danne, cikin dabara dan ya fahimci inda ta dosa.

Ya ce " da kam ina da buri ki yi a wannan shekarar, kafin lokacin da komai zai kammala na samun admission kin yaye Jawad sai ki fara karatun ki, ba wata matsala".

"Yanzu kuma shikenan sai ba zan yi ba?"

Ta fa'da da gatsali.

"Ya sake dannar zuciyarsa ya ce " za ki yi mana, amma dai sai next year".

Ta tunzuro sosai ta ce "kenan sai nan da shekaru biyu kake nufi zan fara?"

Ba ja in ja ya ce " eh".

Jin haka ta fara sakin magaganu "Ni wallahi bazan yarda ba, kafin nan da shekaru biyu only God knows mai zaka mayar da Ni".

Ya yi shiru yana ta neman tsarin Allah ya kare zuciyar sa daga sharrin shaidan da fishi.

Jin ya mata shiru ba'kin cikin ta ya karu,ta fashe masa da kuka mai sauti, tana fadin son kansa ya yi yawa, duk 'kawayenta kowa na karatu sai ita kadaice mai zaman banza da kashe wando.

Rukota yayi zuwa jikinsa tana fizgewa, kan dole ya kwantar da ita, yasa hannun sa ya zagayeta.

Ya ce "Duk kawayen na ki fa'da mini me kamar Jawad? fa'da mini mai miji irin naki da yake tsananin son ki".

Ta yi shiru tana jan hanci, sai kuma ta ce "su ai ba'a tauye su ba, ba a rufe su a gida ana shirin tsofar da su ba".

Ya yi shiru, yana nazarin maganganunta, da ya tabbatar kitsa mata aka yi.

Ya sake fadin yanzu zaman aure ne ya zama abin kashe wando da tauyewa a gurinki? duk yadda Allah ya miki ni'ima, kin raina?"

" Kawai ni son kanka ne ya dame ni"

Mai na yi miki na son kai a zamantakewar mu?"

"Gasu nan kala kala, ka sani haihuwa dole, sannan ka rufe ni a gida, kai kuma kullum kana ganin yanmata, wataran sai inji zaka w amarce da mai degree".

"Su Halima sun zo too nan ko?"

Ya fada ba tare da yasan a fili ya fada ba.

"Ba su zo ba".

"Hmmmm! kawai ya fa'da ya fara lalubarta a kokarinsa na son ya kawar da bacin ran dake neman taso masa.

Ai kuwa ta buge hannun sa tana cewa " Dan Allah ka bari, kullum aikin kenan, ka fitine ni da daddare, danka ya tsotse ni da rana, ga kuma wadda yake cikima bai barni ba, so haba da wanne zan ji".

Ai kuwa hakurinsa ya 'kwace ya ce "Duk ma wadda suka zo suka miki famfo, ke kuma kika yarda ina tabbatar miki kidahuma suka mayar da ke, sannan maganar karatun da kike ganin sun tsere miki da shi, su a gidajen iyayen su aka basu damar su yi".

Maganar ta mata ciwo ainun a harzuke ta ce "wato ni iyayena basu bani dama ba kenan?"

"Eh" kawai yace ya tsuke bakin sa, ai kuwa ta kara 'karfin kukanta, tana ta yunkurin tashi amma ya danneta ya'ki bata dama.

Sosai suka yi rikici, saboda ya ki amincewa da ra'ayin ta, na ta yi jamb a wannan shekarar.

Sai dai kan dole ya ajiye nasa fishin, Yana fadin ta yarda da shi, bazai taba juya mata baya ba, ita kanta yake so ba wani abu na kyan surarta ko zurfin ilimi ba.

indai zata biyewa maganganun wasu, ba abin da zata ci ribarsa a rayuwar ta, ko karatun take yi, wasu sai sunce ta 'ki aure da sauran maganganun marasa Da'di.

Sannan ba abin da yake ruguza Jin dadin zamantakewar aure irin ka bawa wasu dama su shigo cikin matsalar gidanka.

Tun a daren suka shirya, ya saukar da ita, daga famfon su Halima.

Haka rayuwar ta cigaba da gungurawa da su,har Allah ya sauki Sa'adah lafiya, ta haifi kyakkawar yarinya mai kama da ita kwabo da kwabo, sai dai yarinyar da lalura ta zo, ko kuka bata yi ba.

Aka ri'ke su a asibiti, ko numfashi sai da oxygen take zuka, kwanata biyu tace ga garinku nan.

fadin irin tashin hankalin da Sa'adah ta shiga ma, bata lokaci ne, domin tunda ta dora ido akan yarinyar nan, sonta ya shigeta fiye da na Jawad.

Ashe mai gajeran kwana ce.

Kan dole ta ha'kura, ba kunya ta karbi Jawad a hannun Inna ta cigaba da shayar da shi ba tare da an ro'ke ta ba.

Mk ya dinga tarairayarta da lallashi, da nuna soyayya har ta warware ta cigaba da jegonta cikin salama.

Da yardarsa da amincewarsa suka je asibiti aka aunata, aka dora ta kan maganin tsarin iyali da ya dace da jininta, duk dan ta samu ta huta ta gyagije, shima ya samu hutawa da ita, da sau'kin gorin da ta ke masa na ya maida ta akuya😄.

SURAYYA DAHIRU.

✍✍

25/03.

 HALIN YAU!

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•·•

Dokar hakkin mallaka me lamba ta 68, ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake daidai da satar dukiya.

A guji taba ko sarrafa labarin nan ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

63/64.

Shekara daya a gaba.

Zuwa lokacin shekarun su uku da aure, a shekarar Allah ya yiwa Hajiya Babba rasuwa, a dalilin ciwon siga da ya kamata, ba'a gane da wuri ba, har ya taba kodarta, kwananta uku a asibiti ta rasu! mutuwar da ta gigita dukkan yan gidan su Mk dama wadda yasan Hajiya, barin Hajiyar Bichi da akayi zaman makoki ita tana gadon asibiti.

Kwarai suka shiga alhinin rashinta, sai dai ita mutuwa duk yadda zaka yi, ba zata dawo da mutumin data dauka ba, dole aka ha'kura aka bita da addu'a.

Mafarin dawowar Hajiyar Bichi Kano gaba'daya kenan, kullum ta Allah sai ta yi kukan rashin Hajiya, ko na ido, ko na zuci, karshe sai ta musu addu'a tare da mijinsu, tana fatan itama ta riske su cikin aminci.

Mutuwar Hajiya Babba yasa Hajiyar Bichi ta gane abubuwan da Hajiyar ta kare , mussaman na rashin tasowar fitina a tsakanin yaran, tunda ta kwanta dama, yaran gidan kansu ya fara rabuwa mussaman manyan yaransu mata na 'dakin Hajiya

Babba, da suke ganin dama kamar mallake musu uwa Hajiyar Bichi ta yi, kawai Samira a cikinsu bata biye musu to kuma itace karamar su.

Haka Hajiyar Bichi take ta ha'kuri da su tunda dai uwarsu ba abin da bata mata na alheri ba, duk yadda suke 'da'darewa da ita, yi take yi kamar bata gane manufar su ba, Abbas da Akil ne basa bata matsala, ko dan su maza ne?

Su Halima sun sami nasarar samun admission, dan haka ba sosai suke zuwa gidan Sa'adah ba, saboda sun koma new side.

Amma duk ranar da suka sami sararin zuwa gidanta sai Mk ya gane saboda yadda take daukan sabbin dabi'u.

Ranar wata litinin Safina da Halima sunje students affairs na cikin Jami'ar, gun a cike da dalibai kowa na yin abin da yake gabansa.

Suna daga can baya, kamar ance da Safina 'daga kai, sai ta hango Farida Torondi, da Uncle Mk na Sa'adah, da wata da bata ganeta ba.

A hanzarce ta zunguri Halima da hankalinta ke kan waya ta mata nuni da abin da ta gani.

"Munafiki dama ai nasan cin amanar Gogel yake yi, marar mutunci, ba dama aje gidansa ya dinga 'dacin rai da muzurai kenan, banda rashin gaskiya, menene na zargin mutane suna zuga maka matarka, ai dan yasan yana rashin gaskiya a waje ne".

Kafin su kammala, har su Farida sun gama sun fice tare da Mk.

Halima so take su wuce gidan Sa'adah, yayin da Safina tace ita ba zata iya zuwa ko'ina ba tare da taci abinci ba, dan haka suka zarce capteria.

Anan ma suka sake yin tozali da Mk da su Farida suna cin abinci suna hirar su cikin nisha'di.

Suka kewaye su, suka tafi can baya suka zauna, ta inda su Farida baza su gansu ba, yayin da sukuma idonsu na kan duk motsin su, suna daukarwa Sa'adah rahoto.

Halima fadi take "wannan mutumin mugune, ya rufe yar mutane ya hanata fahimtar komai. ashe shi yana nan yana sheke ayarsa"

Safina ta furzar da hucin takaici tace saboda Allah kiga ya hanata karatu, shima daf yake da ya kammala Masters dinsa, (Jami'ar ce ta dauki nauyin karatun nasa). Sannan yana tarayya da mai yin degree a fannin hada magunguna (pharmacy), above all daga rich family ta fito, oh Allah sarki! na tausayawa poor Sa'adah".

"Ka'dan kenan a sharrin namiji" inji Halima da take jin tamkar taje ta rufe su da duka.

Suna zaune suka ga su Mk sun mike, sun fita, a motarsa ya 'debi su, kuma Farida ce ta shiga gaban motar.

Ba'kin ciki ya kamasu da gaske suka ji, suna taya kawarsu kishi, Safina tace "takaici na daya, da bamu samu damar yiwa Gogel bidiyon su ba".

Halima ta amsa da cewa "wlh kuwa basirar yin hakan ba ta zo mana ba"

Daga capteria, basu zame ko ina ba, sai gidan Sa'adah, suka kwashe komai suka fa'da mata, a kokarinsu na tserar da ita daga cin amanar namiji, ita kuma bata gane duk mai zuwa ya fa'da maka abin da zai ruguza farin cikin ka, ba masoyi na hakika bane, mai sonka idan yaga abin da zai tayar maka da hankali! 'Boye maka yake yi mussaman a fannin auratayya tunda dai kowa yasan namiji is entitled to 4 wives, dan angan shi da budurwa matu'kar ba ba'dala suke yi ba Ina ruwan ki?

Kuka ta dinga yi, tana fa'da musu kwanaki biyun nan wulakanci ya ke tata mata, ya tsiri ya yi wanka da magariba ya she'ka kwalliya ya ce mata ya tafi shago, ba zai dawo ba sai after 11.

Suka hada baki wurin cewa "karya yake miki ba wani shago, wurin Farida yake zuwa, yau munga zahiri".

Safina da ta fi Halima kishi tace duk ranar da ya wuce goma na dare bai shigo ba, ki rufe gidanki, ya koma can su kwana tare, ai dan ya ganki sanyi kalau ne ya samu damar yin wani abin"

"Wallahi kisan me kike ciki akan makaranta, baya son ki dinga ganin mai yake yi, shiyasa yake ta miki yawo da hankali akan karatunki, oh mai za'a yi da irin su Mk".

Ita dai banda kuka ba abin da take yi, tana jin wani irin kullutu ya tokare mata wuya da zuciyar ta, ya sababa mata nauyin kirji, da kyar take zuko numfashi.

Haka suka tafi suka barta da kunan rai, suna jaddada mata tasan matakin dauka akan mijinta

Wawiyar kuma ta cika fam! tana jin yau ko yafi gyatumarsa kokari, ba zai yaudare ta da kalamansa na yaudara ba, ya maida ta wata nympho, da sun fara rigima sai yasan yadda ya yi suka kusanci juna shikenan sai ya kashe fa'dan, da zarar ya hau samanta bata sake tuna komai na bacin rai a tsakaninsu.

Ta ci kukanta ta 'koshi bayan tafiyar su, sai ta yi dabarar fara karatun kura'ani dan ta sami sau'kin 'kullutun dake neman fasa mata zuciya da makoshi.

A haka ya dawo ya tarar da ita, ta sami sau'kin bacin ran da ta ke ji.

Kusa da ita ya zauna yana sauraron kira'arta mai dadi, sai da ta kai Aya. sannan ta ajiye kura'anin ta mike tace "sannu da dawowa".

Ya amsa da "yauwa! Na gaji yau dinan sosai, na sha zirga zirga, ba tare da kalle shi ba, tace " wata'kila har wanka ya hau kanka".

Zuciyarsa daya ya ce "gaskiya kam idan na yi zanfi wartsake wa", ya kalli agogo ya ce bari na yi sauri na watsa ruwan kafin a kira sallah".

Ya mike ya yi dakinsa, ita kuma ta bishi da kallon tuhuma, da takaici mai yawa.

Da ya dawo bai nemi abinci ba, ta kara gasgata su Halima, ya taba jikin Jawad da yake kwance yana fama da zazzabin hakorin fi'ka, ya kalleta yace a kwance ya yini ne?"

Kai kawai ta daga masa, ya riga da ya saba da halinta na rashin bashi amsa da baki wani lokacin, dan haka bai damu ba.

Wani ikon Allah yau da wuri ya dawo, kamar yasan anshirya masa ya kwana a waje, haka suka kwana bai gane kan gimbiyar ba, ya daure, shima ya 'kyale ta.

Washagari suka tashi Jawad yana ta suma! ga wasu irin abu sun feso masa kamar borin jini, asibiti suka kai shi, aka bashi magaunguna bayan anmasa allurai, sunje siyan magani, suka tarar da Farida a pharmacy din, da azama ta zo gunsu ta karbi Jawad da yake hannun sa ta dudduba jikinsa tana fadin "Abban Jawad wannan ai 'kyanda ce(measles)".

Da kanta ta hado maganin da aka rubuta musu, har ta kara musu da wani sabulu da zai taimaka wurin baje fatar.

Lokacin da take yiwa Mk bayanin maganin da yadda za'ayi amfani da su, Allah kadai yasan yadda zuciyar Sa'adah ta ke tafasa, ko da Farida ta karaso fuskar Sa'adah a daure ta gaisa da ita, har Mk yaji kunyar yadda ta mata a gaban jama'a.

Ya mika kudin Farida ta ce "A a Uncle ka barshi, da dai na Gogel ne sai na barka ka biya! Amma ai Jawad 'dana ne nima", ta fa'da da sigar tsokana da wasa.

Ya yi godiya ta rakasu har mota, ya karbi Jawad a hannun ta, ya mika ma Sa'adah ta hakince a gaban mota, suka tafi.

Suna Isa gida bata jira ya gama daidaita parking ba, ta dauki ledar maganin da Jawad ta fice.

Tana kwantar da Jawad da yake ta barci tunda aka masa allura, ta samo biro, ta yiwa magaungunan nan shaida ta yadda ita kadai zata gane, ta daure ta ajiye su.

Ya shigo ya zauna, yana son yi mata magana amma ganin yadda ta 'daure fuska tamkar wadda ya zagi iyayenta, yasa ya mi'ke yana cewa " na tafi! Dan Allah kar kiyi wasa da bashi magani".

Ci kanka ba ta ce ba, ya gaji da tsayuwursa ya fita, yunwar da yake ji dole ya fita da abarsa, dan yasan tunda take wannan fishin ba yi zata yi ba, yasan ganin Farida ne ya sake tunzuro ta, tunda tun jiya take ta faman 'kunci, a ransa yana ayyana da jiya kuma ta ganshi yana taimaka wa kanwarta da ta samu admission zata karanta economics fa? Farida ba tasan komai a new side ba, tunda ita a old side take karatunta, shikuma sai ya rakasu a kokarinsa na kyautata mata kamar yadda take girmama shi a matsayin malamin ta.

Shi bai san har anzo anfesa mata ba.😊

Da yamma ya dawo, ya ya tarar da ita goye da Jawad, kayan da ya barta da su ya dawo ya same ta da su. kallo daya ya mata, ya gane bata ci komai ba, sannan bata yi wanka ba.

Ya rasa gane wannan masifar da ta 'dorawa ranta, da 'kyar ta bude baki ta ce "Sannu" ya amsa da yauwa ya isa bayanta yana duba Jawad da yake ta Nishi, shi dai ta masa wanka fes yake, sai dai jikinsa kamar wuta.

"Kin bashi maganin kuwa? na ga jikin, har yanzu bai sauka ba".

Ko kala ba ta ce ba, ya isa inda ledar maganin take ya bude ya ga ba wadda aka taba, bare a sha.

Ransa ya baci matu'ka da gaske, ya nunata da yatsa ya ce " Wai ke wacce irin yarinya ce marar mutunci?"

Ta yi 'kasa da kanta tamkar wadda ta saduda, yaci gaba da fadin "kin fara kaini bango Sa'adatu, kullum a cikin zullumi nake zaune da ke, masifar yau daban, ta gobe daban, haka ta jibi".

"Ai kaci moriyar ganga, sai ka kawo karshen zaman zullumi Mk" ta fada kanta tsaye.

A razane ya zuba mata ido, yana kallon ta, itama ta kafe shi da idon da suka cika da 'kwalla ba alamun tsoro ko shakka a cikinsu.

Ya kasa cewa komai, dan kuwa a yadda yake jin bacin rai zai iya na'da mata dukan tsiya, abin da baya fatan ya aikata kenan, dukan matar aurensa.

Ya mika hannun yana fadin "bani yaron, kai tsaye ta ce "idan kai ka haifar min, ba sai ka 'kwata ba".

Ya yi kanta yana fadin "Me kika sha ne? Bari na sauke miki iskancin da kike fama da shi".

Ga mamakinsa ko motsi ba ta yi ba, sa'banin da, idan ya mata irin haka take kwasa a guje ta 'buya.

Ya isa kusa da ita ya kama kafadunta ya girgiza da karfi har sai da Jawad ya motsa, ya ce " fada min me yake faruwa, me na miki har ya shafi wannan yaron da bai san komai ba?".

Tsaki ta ja, tare da fizgewa, ta koma gefe tana sake 'daure goyonta sosai.

" What! Ni Kika yiwa tsaki Sa'adatu? abin da kinfi kowa sanin na tsani a mini?"

Ai kuwa ta sake jan wani fiye da na farko, sannan tace " ka kashe ni! an maka tsaki Mukhtar".

Wani irin shock ya kama shi, a farko da tace Mk gatsal mamaki ta bashi, amma a yanzu da ta ambaci cikakken sunan sai ya gane ashe Mk din a mutunce ta fa'da.

" Allah ya tsare ni da kisan kai, duk bala'in da kike nufi na da shi, in sha Allah ba zai same ni ba".

"Tunda abin har ya kaimu ga haka, to shikenan! ki yi harkar ki na yi tawa, sauko shi na bashi maganin, sai ki mayar da shi".

"Baka ji mai nace tun farko ba? ka 'kwata' a shirye nake da mu karya yaron nan! idan har ni na tsugunna na haife shi wallahi ba zai sha wannan maganin ba".

"Ya zuba mata ido, yana jin haushin ta na samu gurin zama a zuciyarsa, ya ce "idan na siyo masa wasu zai Sha?"

"Idan na tabbatar da sahihancin su ba".

Ya dauki ledar maganin ya fita ba tare da ya sake cewa komai ba".

Bai wani jima ba, ya dawo da su, a wata ledar mai tambarin lamco pharmacy.

Ya mika mata, tare da cewa "gashi" ya juya ya fice.

Ta dudduba ta tarar da su dinne, illah ledar da ya canja, ta yi 'kwafa ta dankwarar da su.

Ana idar da Isha ya dawo, ya tarar da maganinsa akan kujera ita kuma ta shige 'daki ta rufe kofar, Jawad sai kuka yake yi.

Ya duba maganin ya tabbatar ba'a bashi ba, ya hau dukan kofar, amma banda kukan yaron ba ya jin komai.

Ya kirata ya fi sau hamsin amma tamkar bata gidan.

Ya hassalo sosai ya ce "wallahi idan yaron nan ya mutu, ke kika kashe shi, da hannuna zan mika ki wurin hukuma".

Sai lokacin ta ce "yi sauri kar 'kuda ya riga ka, wato ka maida ni bagidajiya, ka fita da magani kamar gaske, ka sake dawo min dashi, idona tar yake, bazan bashi ba".

A fili ya dinga fadin "Innalillahi wa Inna ilaihir raji'un".

Ya fice zuwa dakinsa, yana karfafawa kansa guiwar ya rabu da ita, ai ta fishi son yaron.

Karfe shadayan dare ya dinga jin kukan yaron, da farko ya yi biris, amma da ya dinga jin 'ka'karinsa baisan yadda akayi ba sai ganin kansa ya yi a jikin kofar dakin Sa'adah yana bugawa, yana cewa "ki dubi girman Allah ki bude min kofar nan, komai na yi miki, na yarda kimin komai, amma banda yaron nan, ki ji tausayinsa, ki ji tsoron hakkinsa".

Har ya gama bilayinsa bata tanka ba, tana jin ta shirya faruwar komai ciki har da rabuwarsu.

Cikin ikon Allah, sai Jawad ya sami barci adalilin ta bashi tea, ta bashi maganin zazzabin sa da yake da shi.

Da asuba kukan Jawad ya sake tayar da hankalin Mk, ya rasa inda zai tsoma ransa, a take ya kira Hajiyar Bichi a waya, bai fa'da mata komai ba, ya ce dai kwana suka yi Jawad bai yi barci ba.

Ba bata lokaci, ta taho,har da garin kunun ko zai dinga sha, tare suka shiga falon, ya dinga kiran Sa'adah amma ta 'ki budewa, sai da taji muryar Hajiya tana cewa"Sa'a, menene yake faruwa ne?"

Da sauri ta bude 'kofar, ta fito idonta, yayi luhu luhu, yayi ja tsabar kuka.

Ta mi'ka mata Jawad ta zauna a gefe tana kuka tamkar wadda aka yi wa mutuwa.

Hajiya ta kalleta, taga ta fita a hayyacinta, ta rame farat daya, ta maida kallonta ga Mk taga shima a firgice yake.

Tace ciwon Jawad ne ya susuta ku haka, ko kuwa wata matsalar ce?"

Ya dauko maganin ya mi'ka ma Hajiya ya ce "Dan Allah ki bashi maganin nan", ta karba, ai kuwa Sa'adah ta saka uban kuka tana cewa "Kar ki bashi Hajiya".

Hajiya ta rasa maganar wa zata dauka a tsakanin su, ta dubi Sa'adah tace "Yi shirunki bazan ba shi ba, fada min me ya faru?"

Ta kasa magana sai kukan da take yi mai dauke da shesshekar ajiyar zuciya.

Ganin hakan yasa Hajiya ta rufe Mk da fa'da, ta inda ta shiga, ba tanan take fita ba, tana jaddadawa laifinsa ne, tunda Sa'a ba me fitina bace.

Ya yi shiru ya dauki laifin da bai yi ba.

da lallashi, Hajiya ta samu Sa'adah ta fada mata dalilin da bata son maganin alhalin ba expired suka yi ba.

Da rawar murya ta ce " Budurwarsa ce ta siyi maganin, akan idona suka yi zance ta siya ta bayar".

Ta karasa cikin gunjin kuka.

Dariya abin ya bawa Hajiya, amma sai ta dake, ta dinga salati tana fadin "kice cin fuska ya miki? banga laifin ki ba, dole ki guji magani, ko nice haka zan yi".

Shi dai Mk ya zama tamkar gunki, yana kallon shari'ar son rai a wurin Hajiya.

Ba zato Hajiya ta ce yaje ya siyo wasu maganin.

Ya ce " Bafa su bane, tunda take wannan bala'in na zubar da su, na siyo masa wasu, amma ta "ki bashi"

Da rawar murya ta ce "Billahillazi, baka canjo wasu ba, duk abin da ya fito ta hannunta, na tsane shi, zan kuma gane".

Jin haka yasa Hajiya fadin "Bar Wannan gadddamar je ka siyo wasu a bashi ya dan sami sauki"

Bai q musa ba, ya mike, ya dauki ledar maganin, ya fita.

Sai da ya fita Hajiya ta dinga mata nasiha, tare da cewa "ki rage nuna masa kishinki a fili, sai ya samu dalilin da zai dinga musguna miki".

Ta kalleta tace "tunda da wuta jona ruwan zafi kuyi wanka".

Ta mike ta cika buta ta jona, mintina kalilan ta kashe kanta, ta juye, ta sake maida wani, kafin ta fito, Hajiya ta wanki Jawad a bandakin tsakar gida.

Ta dama musu kunu, ta juye a flask din shayi, ta zubawa Jawad a kofi, ta bashi, ya shanye tas har da kari, ta tabbatar shima har da yunwa ta sake gigita shi.

Sa'adah ta fito sanye da riga da zani na atamfa, dinkin ya zauna sosai, mussaman da bata cika daura zani ba.

Ta mikawa Hajiya kayansa, sai da ya koshi ta koge masa baki sannan ta saka masa kaya, dai dai lokacin kuma, Mk ya dawo dauke da magungunan, leda biyu, ya mikawa Hajiya, sai da Sa'adah taga na wurin Farida, ga kuma wadda ya sake siyowa, sannan ta saki ranta, a ransa fadi yake masifaffiya kawai.

Take Hajiya ta bude ta bashi, ta shafa masa na shafawa, barci ya dauke shi mai nauyi.

Sosai Hajiya ta musu fada, kuma duk na Mk yafi yawa, jan kunne 'daya, ta yiwa Sa'adah, kar ta sake saka Jawad a cikin fa'dansu, ta ki cin abinci, shi akan mai zata hana shi?

Ta cika kofi, da kunu ta mika wa Sa'adah tace "Shanye ki bani kofin".

Ta karba, ta fara sha, ya mata dadi sai kamshin kayan yaji yake yi.

Shi dai Mk yana kallon ikon Allah, anbawa Jawad, da Sa'a, shi ko oho.

Sai da Sa'adah ta shanye sannan Hajiya ta mike ta ce "zan tafi nasan ki da jin magana, na kashe wannan magana kar a kuma tada ta"

Da sauri ta amsa da "in sha Allah ta wuce".

"Na gode Miki Sa'a, Allah ya miki albarka".

Sa'adah ta amsa da "Ameen Allah ya kara girma" ta tashi tana mata rakiya hanyar waje.

Tare suka fita da Mk zai kaita, a hanya tana sake masa fa'dan, lallai ya kiyayi zungurar Sa'a, ta dora da cewa

"Kana ganin irin yadda take mutunta ni, tana haba haba da yan'uwanka, iyayenta mutanan kirki, lallai ba zamu shirya da kai ba, idan kace zaka wulakanta ta, mussaman ma akan wacce bata zo hannun ka ba".

Har ya kaita gida, kashedi take masa iri iri.

Da za ta sauka ya ce "kin basu kunu, amma Ni baki bani ba".

"Ina sane, kai Sa'a ce mai ba ka".

Murmushi ya yi, tare da cewa "Hajiya kar kisa na fara kishin yarinyar nan, naga tana neman zarta ni a gunki".

Ta yi murmushi tace " maza ka juya ka sake rarrashin ta, ka tsaya a hanya ka siya musu dan wani abin, kunu kadai bazai ri'ke ta ba, ta tara yunwa".

Haka kuwa, ya biyo ta titin Hausawa bawo road ya siyi wainar shinkafa da ake yi mai dadin gaske, a falo ya tarar da ita, tana zaune tana kallo.

Bata dago ta kalle shi ba, ta amsa sallamar sa, daga haka bata kara magana ba.

Ya tsaya ya ce "Ba ki mini sannu da zuwa ba fa".

Ba tare da ta kalleshi ba, ta ce "inace ka ce kowa ya yi harkarsa?"

"Na fa'da! amma dai Hajiya ta kashe maganar, ta ce kar a kuma tada ta".

 "Ita maganar maganin Jawad ta kashe".

Ya zauna, yana cewa "ga waina na siyo miki, tashi ki zubo mana".

Kanta a kasa ta ce" ci abinka".

Ya kai kicin ya adana, ya zubo wadda zai iya cinyewa, tare da kunu a kofi, yaso ya shiga dakinsa, sai kuma yafi zumudin zama kusa da ita.

Ya zauna yana fadin "dan Allah sauko ki taya ni ci".

"Ba zan sake cin abinci da kai ba, tunda muka yi aure, baka taba kaini restaurant munci abinci ba, amma ka dauki wacce kake so kun je! ba ruwana da sabgarka".

Ta fa'da hawaye na balle mata, ya yi shiru, yana jin sabon tashin hankali, ya rasa da bakin da zai kare kansa.

Ya yi shiru, ya kasa cin abinci, ko kaffara ba zai yi ba, su Safina ne suka kawo mata wannan labarin.

"Ki yi hakuri kin ji Sa'adan Uncle".

Kamar ya watsa mata garwashi, ta zunkudo ta ce " ta Ina ka zama kawuna?"

Kai ba 'kanin Baffa bane, bare na Inna, daga jiya ba zaka sake jin bakina ya kiraka da Uncle ba, ita dai da kuka hada dangi, sai tayi ta fa'da na bar mata"

"Ashe lokacin da kace min dole kayi kishin mace, idan ka ganta a gaban motar wani da ba Muharraminta ba, 'karya ka fada tsagwaronta? To ita mai kuka hada daka dauketa a gaban motarka?"

Kansa ya kulle, ya kalleta ya ce "Na yarda ban kyauta ba, ki yi hakuri, ki bani wata damar, ko banci albarkacin komai a gunki ba, naci albarka cin mahaifiyata da tazo ta baki ha'kuri, ta kashe maganar".

Jikinta ya yi sanyi, ta ce shikenan na ha'kura".

Da'di ya kama shi, ya matsar da kwanon abincin kusa da ita, ya ce to sauko muci".

Ta girgiza kai, "Na hakura, amma ba zanci da kai ba".

Ya tura mata, "to ci wannan, bari na zubo wani," ya mike ya fita da sauri.

Cikin sa'a ranar bashi da lakca sai 'karfe daya, dan haka, bai fita ko ina ba, yan tare da ita, yana ta kokarin wanke mata zuciya, shi da kansa ya tabbatar a duniya ba abin da yake so sama da Sa'adah da 'danta, idan aka cire Hajiya.

Sai dai duk nacinsa bata yarda da shi ba, kan dole ya 'kyale ta.

Kwana biyu tana mai yawo da hankali, kafin ta ha'kura ta sallama masa kanta, cikin rawar jiki yake komai, yana ayyana distance fa yana da amfani, domin ji yayi ta dawo masa sabuwa.

Yana samun kudi kuwa, ya dauke su ita da Jawad suka je restaurant din Royal Tropicana suka ci abinci, suka yi hotuna, irin wadda ake wankewa a take, take & wash, suka zarce country mall, ta zabi abin da take so.

A hanya ya ce "shikenan yanzu na dawo Uncle?"

"Hmm! magana ta wuce ka daina dawo mini da ita".

Ya shagwabe fuska ya ce " idan har da gaske ta wuce, then called me Uncle".

Ta fara dariya, tana cewa "ashe son girma ne da kai ban fahimta ba?"

Shima ya taya ta dariyar sannan yace "tsakanin ki da Allah! Idan nace Miki Sa'adatu ba kya jin wani iri? ke da kike kanwata nasan kina jin ba dadi, bare ni ki gatsa sunana gatsal"

"Amma ai tun ranar ban sake fada ba".

"Eh baki sake ba, sai dai kimin ta kurame, kiyi maganar ki ba tare da kin kama sunana ba".

"Nifa Wallahi na tsani, waccan sunan da kake kulafacin sai na cigaba da kiranka da shi".

"To shikenan zabo min wani, mai sweet, kika rufe ido kika cemin wai baki hada dangi da Ni ba ko?"

Ta ce "eh mana ai ba karya na fada ba".

"Ni Malamin ki, Ni Mijin ki,Ni Baban danki, duk wannan ha'din kin raina shi?".

Ta tura baki gaba, ta ce "shikenan, ka zabi sunan da zan fada maka a cikin wadannan,Malam, Miji, ko Uban 'da"

Dariya ta kwace masa sosai, cikin dariyar ya ce, "ke yanzu sai ki dinga cemin Uban 'da?"

Surayya Dahiru

✍✍✍

26/03.

 HALIN YAU!

Lafazi writers.

A guji taba wannan labarin ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba

Doka mai lamba ta 68 ta nuna cewa satar fasaha laifine da yake dai-dai da satar Dukiya.

GODIYA

Ina matu'kar godiya ga wadanda suka yi mini addu'o'in samun lafiya ga warwarewar lamura, tunda ga kan masu kira ta waya, da masu text, da masu yi mini ta dandalin WhatsApp, dukkanku na gode madallah, ubangiji ya fini yabawa.

65-66.

Ta yi murmushi ta ce " mai zai hana na fada maka idan kana so?"

Ya bugi sitiyari ya ce "my sweet Sa'adah, sometimes you are so funny".

Ta yi shiru ta kyale shi, ya sake cewa " ke yanzu ko inkiya da Jawad baza kimin ba, naga yanzu daga mace ta haihu take karawa Mijin ta matsayi ta hanyar yi masa alkunya da sunan yaronsu".

Ta tabe Baki, ta yi shiru, sai kuma ta kasa hadiye maganar.

"Akan mai zan maka alkunya da Jawad alhalin wadda ta fini cusa kai ta riga ni? Inace Farida Abban Jawad take kiranka? Kasan Ni kuwa har abada bazan bi ra'ayin ta ba, banda azarbabi, ba sai ta bari idan ta haifar maka nata sai ta yi komai ba, amma dan son sai ta nuna ita gwanace akan kayan da ba nata ba yasa ta ke yi mini katsalandan, ai na so ta yi kataborar ce min Iyah Basiru, wallahi da jikinta ya fa'da mata domin kuwa ba abin da zai hana na mata 'kamshin mutuwa".

Ganin za ta tunzuro da yawa sai ya share maganar da cewa "Na zabi miji, amma Zauj za ki dinga fad'a maimakon miji".

Yana rufe baki ta ce " duhun fata ta kadai, ya isa ka gane ni ba balarabiya bace, dan haka nafi kishin yarena".

"Amma duk musulmi dole ya dau larabci yarensa ne, domin yaren kura'ani ne, duk sallar duniya kuma a larabce muke yinta".

"Wannan daban" ta bashi amsa a takaice, daidai lokacin kuma suka iso gida.

A gidan ma maganar ya yi ta ja, inda ita tace Malam ta zaba, dan haka Malam zata dinga fada.

"Na fada miki ban son wani Malam, duk sunayen zamani, da na soyayya ki rasa mai zaki ce mini sai Malam sai kace tsoho ko wani Malamin zaure, duk yadda muke da ke darajata a iya ta Malami take a gurin ki?"

Tana dariya tace "kololuwar daraja kenan, Malaminka ai tamkar mahaifi ne, ana canja Miji, amma ba a canja mahaifi da Malami, domin ko ka guje shi, ya dai koyar da kai abin da baka sani ba, sannan ya koya maka tarbiya, a wurina Malam is a jewel.

Shikenan mafarin cemasa Malam tun yana ki, har ya fara amsawa, a lokacin da Jawad ya fara iya magana shima ya bi bakin uwarsa wurin kiransa da Malam.

Juyin duniya ya yi da Jawad kar yace masa Malam, amma da ya fara cewa Daddy, idan yaji Sa'adah tace Malam shikenan shima zaice Malam.

Sai ya fara cemata Daliba, ko abune sai ya bawa Jawad yace humm kaiwa Daliba, a kokarinsa na itama Jawad ya dinga kiranta haka😂

Amma sunan bai bita ba, sabanin shi da Malam ya zauna a bakinsa radam, ita kuwa Mami yake kiranta.

Tun lokacin Mk yake yiwa Sa'adah mitar yasan Jawad yafi sonta da shi, itakuma dariya yake bata idan yana wannan rikicin nasa.wataran tayi dariya, wataran tace haba Malami na. Sai ya yi murmushi yace

"A da nake Malamin ki".

Tace "har yau Malami na ne, tunda har yanzu karatu nake yi a gabanka".

"Wanne karatun kike yi yanzu?"

Tace " da ka koyar da Ni, ilimi da tarbiya, yanzu kuma kana koya mini karatun kyankyansar jarirai".

Tana fadin hakan ta gudu ta barshi, ya bita yana dariyar maganar ta karshe, wai kyankyansar jarirai? ya zauna kusa da ita yana cewa "ai kuwa dai kin yi gaskiya, Ni yanzu ma so nake mu zama mu hudu, ya kamata kije ki cire abinnan, mu fara sabon karatun kyankyansar jariran".

Tana dariya tace "ka rufa min asiri kai da kace sai na fara karatu, na yi nisa, da ka sake yi min ciki?".

Yana dariya yace "da bakin ki Kika fadi wannan maganar?"

Ta rufe ido tana Jin kunya na kamata.

Ya zauna kusa da ita yace "kisan dai kin yi jamb, kyau ne bata yi ba, nace ki cike F.C. E. Kin kasa fahimta ta, da yanzu za ki fara N.C.E, kinga yanzu dole ki sake zaman jiran wata shekarar, maimakon haka gara mu sami Baby, ai akwai masu karatun da goyo".

Shiru ta yi, itama tana son haihuwar yanzu, mussaman idan ta tuno fuskar baby girl dinta da ta rasu mai kama da ita, sai ta ji ta zaku da ta sake haihuwa, tasan da ta rayu, da ta nan tana tafiyarta ko ina.

" Ance mini idan Ina haihuwa rututu ba barina zaka yi na yi karatu ba?"

"Ni kuma nace za ki yi, har sai kince ya ishe ki, shin maganar wa za ki dauka, tawa ko ta su?".

"Shikenan zan cire, amma yanzu ka manta Jami'an lafiya na yajin aiki?"

" Na manta, idan su koma bakin aiki sai muje a cire ko?"

Ya fada cike da kulawa da rarrashi.

Su Halima na zuwa ta fada musu, Malam yace ko da goyo zata yi makaranta, karatu har sai ya isheta.

Safina ta kaikaice tace "wato ya ga kin yi kyau, kin bar Sa'ade kin dawo Sa'adah, shine zai sake dirka miki wani cikin? ke kuma har kin yarda da maganar sa?"

Suka kwashe da dariya, Halima tace "na rantse miki da Allah karya yake miki, barinki ne ba zai yi ba, kar ki sake ki cire abin nan sai kin tabbatar kin fara makaranta, tunda shi son haihuwar yake, sai ki yi amfani da hakan ki cimma burin ki".

Sa'adah ta yi shiru amma bata fahimci bitar Halima ba.

Tace "kamar ya ya na cimma burina?"

"Eh tunda so yake ki cika masa gida da Yara, sai ki kafe, ba za ki haihu ba, sai ya nemo miki admission, idan har da gaske zai barki, maki uku ne kacal ya hana points dinki su kai, da ya so, da tuni ya samo miki admission, lakcara ne fa, Yana da alfarma wallahi".

Safina tace "Ai ni bansan wadda ya iya rainin wayo irin Man din nan ba, mugun macijin sari ka noke ne, idan kika ga yadda yanmata suke sintiri a gurinsa, sai mamaki ya kamaki, farar fatarsa da tsayinsa ke rudar su".

Halima ta cafe da cewa "itama Gogel din ai abin da ya rudeta kenan, banda haka Ina da kamar Alh Mamman da bazan yi kukan rasa komai ba, Ina zan tsaya kula wannan mutumin, kinsan Allah Safina!

da Alh Mamman ta aura Ni kaina da tuni na jike da arziki, mu ture ta Alh Mamman, zata iya cewa ya mata tsufa, matashin saurayin nan da kasuwa ta daukaka ke shi chairman din Buji ventures, shima ya sota fa".

Safina tace "Ina ruwanta da tsufansa? Lokacin da Dadin mu ya auri mom Dina, ai kamar ita da Alh Mamman ne, gashi nan har yau suna tare, ta yi lub tana cin arziki, har muma muna cikinsa,kawai rashin rabo ne irin na Gogel, ga kuma rabon Jawad da kanwarsa a jikin Uncle"

"Ai kuwa rashin rabo ne na yarda da ke, Allah ya rabamu da rabon wahala".

Halima ta fada tana Jin takaicin rashin auran Alh Mamman.

Duk zuwansu basu da aikin komai sai kushe Mk, alhalin a gidan suke zuwa suci abinci mai rai da motsi, suna ci suna kushensa, barin ranar da babu wuta ko nama a abinci, sun dinga fadin mutum kamar Mk ya kasa kunnawa matarsa da dansa 'daya janareto su ji dadi, dole sai dare, daren ma sai ya fara nisa, Allah muna rokon ka tsari daga auren matsolon namiji.

Haka har lokaci ya sake ja, basu fasa zuwa ba, yanzu kuma sun dauki sarar shanye mata kayan tea ta hanyar yin Yar gullisuwa, ko sai sunci abinci, suce za su sha tea, ko cornflakes.

Suka sake cusa mata karya a ranta, bada komai take amfani ba, sai kaya masu tsadar gaske, yadda take tafiyar da tsarin rayuwar ta tamkar matar attajiri ba wai 'karamin lakcara ba.

Gayun ta ya 'karu, komai nata daukan ido ya ke, saboda sai zababbe, a lokacin Mk ba abin da yake so irin farin cikin ta, shi da kansa har mamakin yadda yake tsoron fishin ta yake yi, komai take so haka yake mata, kusan albashinsa da kyar yake rike su, saboda hidimnar Sa'adah, kowanne wata da Abin da zata ce, tana so, haka zai

yi mata jikinsa na rawa, mantawa yake yi da hidimar kansa, daga ya sallami Hajiya shikenan zai sa Sa'adah da Jawad a gabansa.

Amma duk da hakan Sa'adah bata fahimci matsanancin sonta da take yi bane, da kuma sa'a da tayi mai son kyautatawa iyali ne, sai ta fara wuce makadi da rawa, bata cika nazari kafin ta aiwatar da komai ba.

Suna cikin haka Jami'ar Bayero ta fara yanka fili manya tana rabawa Malaman makarantar, a hankali za'a dinga cira a albashinsu.

Mahmoud da sai a wannan shekarar ya yi aure, kai tsaye biyu ya karba, da nufin idan ya tashi ginawa ya yi gini mai yalwa.

Mk kuwa fargaban karban 'daya ma ya shiga, saboda a halin yanzu, badan shagon askin sa ba da sai ya hada da bashi a wata.

Mahmoud ya yi ya karbi biyu, Mk na bude bakinsa sai cewa ya yi daya zan iya karba, shima sai na yi shawara da Sa'adah, kar nazo ta 'kuntata.

Mahmoud ya yi galala yana kallonsa ya kasa hakuri yace " idan nace ka bari tafi karfinka kace ba haka ba, idan nace tsoron ta kake ji ka karyata Ni".

Murumushi Mk ya yi tare da caewa "kowanne namiji da yadda yake zaune da matarsa, kowacce mace da irin alherinta, da irin kuskuren ta, Ni sonta nake da dukkan alherin ta, da kuma kuskuren ta, bana jin tsoron ta, amma Ina jin tsoron fushin ta, dan haka duk abin da zan yi ,dan na samu zaman lafiya da ita zan yi".

Mahmoud ya tsinci bakinsa da fadin "Hakane".

Mussaman da ya tuno, yadda ta iya girki, da kwalliya, gidanta kullum a gyare, hatta Jawad kullum fes za ka ganshi, sannan tana da kyakkawar mu'amala da jama'a, dan

kuwa hatta amaryarsa yabon kirkinta da gayunta take yi! iya abin da ya sani na zahiri a kanta kenan, Ina kuma ga mu'amala ta sirri tsakanin ta da Mk, sai ya tsinci kansa da rashin ganin aibun yadda abokinsa ya yi deep a soyayyar ta, ya lalace a kanta, da yadda zai siya mata suturu na makudan kudade, shi ya siyi masu sau'kin kudi ya saka.

Bai karbi filin nan ba sai da ya shawarceta, tace "ka karbi biyun mana Malam".

"Idan na karbi biyu fa, hakan na nufin sai mun rage wasu abubuwan, tunda za a dinga yanke mini kudi ne".

"Tunda dai wataran gini zaka mini mai kyau, gashi kace idan filin biyun ne har garden zaka mini, ai sai a ha'kura da wasu abubuwan har Allah ya sa ka kammala biyansu"

Ya ji Dadi har ransa, da yadda ta fahimce shi,ya karbi filaye, Mahmoud na ta masa tsiyar Madam ta bashi go ahead kenan.

Shikenan sai suka canja daga rayuwar luxury zuwa tsaka tsaki, sai dai ba a dauki lokaci mai tsayi ba, abubuwa suka fara canjawa saboda yadda su Halima suke mata shaguben yadda Mk ya canja mata, suka dinga fadin ba wani fili da ya karba, yanmatan banza yake kashewa kudin, Raina ki ya yi, shiyasa ya shirya miki wannan karyar, itakuma tana gaskata su, ta kasa gane gadar zare suke yi mata.

Sannu a hankali sai suka fara kushe talabijin din falonta, alokacin plasma bata yawaita ba, sai irin ta falon wato LG slim tv.

Kullum Suka zo sai sunce wannan tv kamar ba gidan ma'aikacin gwamnati ba, kusan shekaru hudu amma ya kasa canja miki komai, tunda muke zuwa kullum abu daya muke gani.

Idan ta kawo musu pure water, sai sunce ruwan warin nama ko karnin kifi yake yi, suna fadin freezer da zai siya ta nama da kayan miyane yake ganin asara, gara yaje ya rabawa yanmata a waje.

Tun bata yarda, har maganganun suka shigeta, mussaman da ta ga falon amaryar Mahmoud, sai ta sake rikicewa, ba tare da ta yi nazarin kayan da suke rainawa, ita ba'a Mata kamar su ba.

Ta fara rikice masa, ya kasa gane kanta, ya zauna yana rarrashin ta, har ya samu tace ita tibin bango take so ya siya mata.

Ya rikota cikin kwantar da murya yace "ki yi hakuri zan siya, amma ba yanzu ba, kinsan dai yanzu ba cikakken kudi nake samu ba, amma da zarar naci karfin biyansu, zan siyo miki, ba sai na kammala biya gaba'daya ba, ya kara da fadin wacce kamfanin kike so?"

"Sumsung"

"To ki daina bata ranki akan maganar tv, mecece talabijin kuma?"

Ya lallaba ta da maganar tv. sai kuma wayar Black berry ta shigo, kullum su Halima hirar BB chart, Safina kam tuni ansiya mata, yayin da Halima take fatan saurayin ta ya siyo mata.

A ranar da saurayin Halima ya kawo mata wayar, suka je gidan Sa'adah suka nuna mata, Halima na fadin " kina ganin saurayi ma, da bana daga masa kafafuwa, ya fidda kudi ya siyo mini, bare ke da kullum yake hakar ki".

BB chart din nan ya matu'kar gigita Sa'adah mussaman da aka tabbatar mata, sai masu irin wayar ne suke yi.

Kullum mitar ya siya mata waya take, rannan da ya gaji, ya zaunar da ita yace "kinsan za ki dame ni mai yasa za ki sani karban filaye biyu? bani da kudin siya miki wayar da kike magana akanta, Ni kaina ban ri'ke ta ba".

Ai kuwa zamansu ya dawo wani iri, saboda ta kudire a ranta da gaske yanmatan banzan yake yiwa hidima, ita ya barta ko oho, mussaman da ya ki yarda ya kaita ta ga filayen nasa.

Ranar wata juma'ah sai ga shi da sabuwar plasma TV 32 inch, ga mamakinsa ba ta yi wani murna ba, lamarin da ya bata ransa sosai.

Haka ya daure, ya kira mai gyara ya hada mata har da satellite.

Kallonta kawai yake yi, a zatonsa siyan tv zaisa zamansu ya dawo normal, amma sai ya ga sabanin haka, saboda ta riga ta yi nisa a son Black berry, ta samu shedanun kawaye na mata famfo.

Haka suke ta gungurawa, yau fari gobe tsumma, mussaman da ya tsaya akan ra'ayinsa na ba zai siyi waya ta makudan kudade ba. haka jarrabawar jamb ta fito, a lokacin da F.C.E. ta fidda jerin daliban da suka sami gurbin karatu har da ita, inda zata karanta primary care education jiran lokacin fara daukan darasi take yi nan da yan wattanni. Hakan bai sa ta sauko ba, saboda ita B.U.K. take so, Safina sai cewa take "mijinki is very smart

Ya rantse ba zai kai ki makarantar da yake ba, dan kar agane yana da mata".

Yau da gobe akace ta fi karfin wasa, ya gaji da zaman rashin walwalarsu, ya kukuta ya siyo musu Android shi da ita, a lokacin bata jima da fitowa ba, dan haka itama mai tsada ce, ga mamakinsa ko Na gode ta gagareta fa'da wadda ko kadan ba halayyar ta bace, ko abu bai yi mata ba zata yi godiya ko a gajarce ne.

Amma wannan ajiyewa ta yi a inda ya bata ba tare da ta duba ba, ransa ya baci da ita, irin wadda bai taba ji ba.

Ganin idan ya cigaba da zama kusa da ita, komai na iya faruwa a tsakaninsu na rashin jin dadi, yasa ya mike ya fita zuwa shagon sa, bai dawo ba, sai shadaya da ashirin da bakwai 11:27pm.

Ya sake tarar da wani 'bacin rai fiye da na farko, wato rufe masa gida, bugu ka'dan ya yi, ya hakura dan kar makwabta su fahimci abin da ke faruwa, ya dinga kiran wayarta ba kakkautawa, tana shiga amma taki dauka, karshe ma sai ta kashe wayar gaba'daya.

Haka ya kwana a gate a cikin mota, ya yi kwanan zafi, da sauro, barcin kansa rabi rabi ne, wannan daren yana cikin jerin dare masu tsayi da ya fuskanta a rayuwar sa.

Duk juyin da zai yi, tunanin irin hukuncin da zai mata yake yi, ya gaji da wannan bala'in, zai nuna mata, neman zaman lafiya ba shine lasisin da zata dinga wulakanta shi ba.

Koda asuba kin bude masa ta yi, dan iskanci kuma ta kunna wayar amma taki 'dagawa. Ya Mata text yafi sau goma, har kurarin zai fadawa Baffa ya yi, amma ko gezau.

Har taran safiya, yana harabar gidan. Takaicin sa daya, ba ya ajiye kaya a mota. Mahmoud ya kira ya fada masa halin da yake ciki.

Da kyar Mahmoud ya shawo kanta ta bude masa, domin kuwa cewa ta yi, ya koma ya dauwama a gurin Farida.

Yana jin lokacin da ta zare sakata, amma ba'kin ciki ya hana shi tashi, ya jima yana addu'ar samun sau'kin zuciya kafin ya samu sassauci. ya shiga gidan kai tsaye dakinsa ya shiga, ya yi wanka, ya fito ya shiga kicin, ya hadawa kansa Abu mai sauki, ya koma dakinsa ya rufe, yini guda bai fita ba, domin ramuwar barcin da bai samu ya yi ba.

Itakuma tana zaune cikin shirin ko ta kwana, har sun yi waya da Halima ta fada mata abin da ta yi masa jiya, tace mata da kyau, gobe idan ya sake har gate din za ki rufe.

Sai azahar ya tashi, ya fito da shirin fita masallaci, Jawad ya biyo shi, ya ri'ke hannun sa, suka tafi bayan ya masa alwala, suna dawowa, Jawad ya dinga Jan hannunsa, Yana cewa" Mami falo". Ya daka masa tsawa ya shige dakinsa ya daga murya yace "je ka wurinta kai, domin ita da babu duk daya ne a gurina" Jawad ya fashe da kuka saboda tsawar da bai saba da ita ba.

Abin ya yiwa Sa'adah ciwo, a fili tace "Allah yasa yau ka sake yin dare, zaka san Ni da babu daya muke".

Tsawon kwanaki biyu, zaman nasu ya sake yin tsami, domin shima fishi ya dauka sosai, ya dauke sabuwar wayar da ta bar masa a gurin, sannan ya karbe wadda take amfani da ita.

Lamarin da yasa rikicin ya sake ta'azzara a tsakanin su.

Ta dayan bangaren kuma sai shirin tafiya Abuja yake yi, saboda za su yi wata jarrabawar scholarship da gwamnatin tarayya zata tura malaman jami'oi karo ilimi a kasashen Birtaniya, Canada da kuma Rasha.

Bai fada mata zai yi tafiya ba, har sai da ya kammala shirinsa, da zai tafi, ya tsaya daga bakin kofar falon yace " Zan yi tafiya, sai Allah ya dawo da Ni, ya bawa Jawad dubu uku yace "kai mata".

Mamaki yasa ta kasa bude baki ta yi magana, ya juya ya tafi, Jawad na kukan zai bishi.

A tunanin ta kwana daya zai yi ko biyu, amma sai da ya shafe kwanaki biyar ba shi ba alamun sa, a kwana na shida ne, idonta ya fara raina fata, mussaman da ta tabbatar da Mahmoud suka yi tafiyar, Amma shi ya dawo kwana biyu kawai ya yi.

Kuka ta dinga yi, tamkar shine mafita, ga rashin waya dake addabar ta, ga rashin sa.

Sai da yayi sati guda ya dawo, kallo daya ya mata yasan ta ji jiki, sakonsa ya daketa sosai, amma saboda Halinta na taurin rai, ko kallo bai isheta ba.

Washagari da ya fita, sai da ya kai 11pm kafin ya dawo, domin ya jarrabata ya gani. A bangaren ta tana son rufe masa gida amma ta kasa, kwanakin da ya yi baya gida, sune mafi tsauri a dukkan rayuwar ta, tunda suka yi aure bai ta'ba yin tafiyar da ya kwana ba tare da ita ba. tasan rufe masa gidan da ta yi ne, yasa yayi tafiya mai tsayi ba tare da ita ba, ba magana mai dadi, ko na zai yi missing dinta.

Ya dawo ya tarar da gida a bude, ya yi murmushi, yauma 'dakinsa ya zarce, wannan abin ya dameta, amma bata ji zata bashi ha'kuri ba, tunda ai ita ya zalunta.

Washagari yana shirin fita, ta fito ta tsaya a tsakar gida, sai da ya fito sannan tace " Ina son zanje gida".

Ba tare da ya kalleta ba, yace " Ba za ki je ba".

Ya sa kai zai fita, taja tsakin da yasa shi juyowa da sauri, kafin yayi magana tace "dama idan mutum na cin amanar matarsa, sai ya yi ta boyeta a cikin gida, mai za'a yi da auren likitan mata, da mai koyarwa a Jami'a, aiki ne na yan iskan maza, masu juyawa matansu baya idan sun sami biyan bu'katar su"

Ya zuba mata ido yana jin wani iri Abu mai kama da tsanar ta na son yiwa zuciyar sa dirar mikiya.

Ya nuna kansa da yatsansa, yace "Ni ki ka zaga?"

Idonsa ya kada ya yi jawur, ya rasa inda zaisa ransa ya sami sau'kin zafin da zuciyar sa ke yi.

Ya girgiza kai yace " Na gode, amma U will pay for it Sa'adatu".ya juya ya fice da sauri.

Ganin yanayinsa yasa ta jin nadama na dan shigarta mussaman yadda ya nuna kansa yana tambayar shi ta zaga? tasan bai taba zaton zata iya zaginsa ba, ita kuma ba'kin cikinsa ne yake neman kashe ta a tsaye, sannan ma a ina ta zage shi?

Fishi ya dauka sosai, sun kai sati a haka, abin ya fara fin 'karfin ta, rama take yi a tsaye, ko uffan baya cemata, Idan yana gida Jawad na manne da shi yana bashi labarin yaci abu kaza da iri kaza, ko yace su Anty Safina sun kawo masa abu kaza.

Hankalin ta bai tashi sosai ba, sai da yayi shopping, taga iya abin da ya zama dole ya siyo, wadda ya saba siya na kyautatawa duk bai siyo ba, duk wani tarkacen kayan kwa'dayi babu a siyayyar nan, hatta kayan miya da yake zuwa janguza ya lodo musu, wannan karan ko guda daya bai siyo ba.

Sannan a drower yake ajiye kudinsa baya mata iyaka, ya zara , ta zara, har su 'kare a haka, a wannan lokacin sai ya zauna ya yi 'kiyasin 200 zai isheta kullum da sunan kudin cefane, dan haka sai ya adana kudinsa yake bata wannan darin biyun, Jawad yake bawa ya kai mata.

A wannan lokacin da ya rikice mata, ya canja sosai, sai ta gane ashe dai da kirkinsa har yawa ya yi.

Ta fara neman hanyan sulhu, amma ta rasa yadda zata yi, yaki ya bata dama ko kadan, ko ta kai masa abinci baya ta'bawa haka take daukan abinta, ta fara daukan wanka da kwalliya, shikuma sai yake runtse idanuwansa daga kallonta.

Ta rasa mai kuma zata yi, sai ta dawo da gyara masa dakinsa, kullum idan ya fita, zata shiga ta gyara, gyara na mussaman, ranar da ta fara, da ya dawo ya gani, a ransa yace zaki san ba ke ka'dai kika iya neman masifa da tashin hankali ba.

Ganin ta debi kwanaki tana bin hanyoyin neman sulhu, amma ya yi biris da ita, sai ta canja salo.

Rannan da daddare ya dawo, ta kai masa abinci da tea din da ya zame masa ka'idar sha duk dare, tana ajiyewa yace " fita da su na gode".

Ta yi shiru tana kallon sa shikuma yana zaune, yana nazari a waya, amma yana jin kallon ta a jikinsa.

"Dan Allah Malam ka sha shayin nan na roke'ka".

Ya girgiza kai yace "Na koshi ne, ki ajiye zan sha da safe".

Da murna tace "Na gode".

Ta mayar kicin ta adana abincin a fridge, a gurguje ta yi wanka, ta bi dukkan jikinta ta shafa Arabians perfume masu kamshi sosai.

Ta dauko rigar barci ruwan madara, mai santsi ce kuma very transparent, ta gyara gashin kanta ta shafe shi da man gashi na Kuza. ta tsaya gaban madubi tana kallon kanta, tabbas ko ita ta burge kanta, ta tsinci bakinta da yin tasbihi da godiya gurin ubangiji,hakika an kyautata halittar ta.

Har taje falo kuma sai ta dawo, tana bin cinyoyinta da kallo, iyakacin Rigar rabin cinyarta ne, ko kusa da guiwata bata zo ba, bugu da kari, bata sa komai a kasan rigar ba.

Shaidan da zuciya suka fara wasan kura da hankalinta, suna kitsa mata idan taje a haka, ta yarda itace mai laifi, bayan duk irin yadda ya nuna mata ita da babu basu da maraba.

Ta tuna yadda ya shafe sama da sati biyu bai nemeta ba, shaidan ya sake tunzuro ta, yana jaddada mata irin zalamarsa akanta, idan ba wata ya samu a waje ba, yaushe zai iya jure tsawon kwanaki bai rabeta ba, tabbas mata yake bi na banza.

''

Ta koma ta kwanta a gadonta, tana Jin hawaye na bin fuskarta.

Sai juyi take yi, tana kallon yadda Jawad yake barcinsa cikin nutsuwa, tana jin inama itace shi, da bashi da wata matsala a duniyar sa, indai zai ci abinci, a masa wanka, a bashi sweet shikenan baisan komai na bacin Rai ba.

Ta kasa barci ta zabura ta sauko daga gadon, tana jin dolensa ya fada mata mai yake nufi da ita, ya kuntata mata, ya kuma fita fishi

Ta kunna fitilar dakin, ta fice ba tare da ta kashe ba, saboda Jawad .

A zaune ta same shi, yana marking din exams din 'dalibai.

Ya amsa sallamarta, hankalinsa na kan takardar da ke gabansa.

Ganin bai 'dago ba, yasa tace "Ina son magana da kai".

Yana cigaba da marking yace "Amma dai kinga aikin da ke gabana ko? Sai ki jira na kammala, ko ki tari lokacina na gaba".

 Hawaye ta ji na neman kwace mata, da ta tuna kafin su fara takun saka, baya iya yin aiki sosai matu'kar suna tare, ya fi kauri wurin tsokanarta, ta hanyar dumbulan kirjinta, ko ya biyeta su yi ta shiririta, tana bashi labarin ai tana yawan mafarki ta zama Hajiya, ta zama big madam, shikuma ya yi kudi, ya zama Alhaji, ya gina musu katon mansion.

sai yace Ina fatan dai ba kiga na 'kara aure ba? Wani lokacin tace bata gani ba cikin da'din Rai, wani lokacin tace abin da yake ransa ne, sai ta hau bori, shikuma ya lalace wurin rarrashin ta, a haka har su cinye lokaci mai yawa basu farga ba.

Amma a yau, gata a gabansa yana nuna mata bashi da lokacin saurarenta, aikin da yake yi ya fita muhimmanci kenan?.

Da gaske ita da Babu 'daya ne a gurinsa? sai kawai ta fashe masa da kuka irin wadda ta tabbatar yana gigita shi.

Surayya Dahiru

✍✍.

30/03.

 HALIN YAU!

NA

Surayya Dahiru.

Lafazee writers.

Doka mai lamba ta 68 ta nina cewa satar fasaha babban laifine da yake dai-dai da satar Dukiya.

A kiyayi ta'ba wannan labarin ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR

67-70.

Ya yi shiru yana jin kukan da take masa, yana ayyana rashin mutuncin ta kullum kara gaba yake yi. ransa ya baci iyaka, mussaman yadda ta ware murya tana masa kuka tamkar wadda ya ke mata dukan kawo wu'ka.

Ya kasa cewa komai, domin zuciyarsa sai fada masa take, ya daketa kawai, ko ya huce kadan cikin takaicin da take guma masa, itama kuma sai ta yi kukan mai dalili.

Tsawon lokaci tana kukanta, jikinta ya yi sanyi tubus, a dalilin halin ko in kula daya ya mata, da gaske dai Malam ya gaji da ita, hakan ya sake sa ta fashe da sabon kuka fiye da wadda take yi.

A harzuke ya nuna ta da yatsa yana cewa " tashi ki koma dakin ki, kici gaba da kukan a can. Idan kuma ba ki gama min tuya a gurin makwabta ba, sai ki kara himma har su shigo su ceceki."

Jin hakan yasa ta rage sautin kukanta, shikuma ya cigaba da aikinsa amma bashi da sukuni ko kadan, ya kuma yi al'kawarin ba zai ce ta daina kukan da take yi ba.

Aikuwa kusan raba dare ta yi, tana masa gunjin kukan da babu shagwaba, sai zallar bacin rai, irin kukan da me yinsa yake son a rarrashe shi, lura da hakan da yayi shikuma ya yi biris da ita, dan kuwa bai ga dalilin kukanta ba, shi ta musganawa, ta masa rashin kunya, bata bashi hakuri ba, shine take sa ran shi ya risina mata, lokaci ya yi da zai daina biyewa son zuciyar sa akan lamarin ta.

A inda take zaune barci ya sureta, sai sakin ajiyar take yi.

Sai da ya gama aikinsa, ya kammala komai, ya dauko Jawad ya kwantar da shi, ya dauko bargo ya lulluba mata, sannan ya kashe fitila ya kwanta bayan ya rungumo Jawad a jikinsa.

Da asuba ta tashi ta ganta lullube da bargo, ta ji dadi, sai dai rashin tashinta ta yi sallah ya dakushe waccan jin dadin, ta kalleshi har ya dawo daga masallaci, ta zuba masa idon da ya kumbura saboda kuka, murya a dashe tace "Malam abin har ya gagareka tashina na yi sallah?"

Ya yi mata shiru tamkar ba da shi take yi ba.

Takaicinsa ya sake kumeta, tace "Ma'aiki dai yace Allah ya jikan mijin da ya tashi cikin dare ya kuma tashi iyalinsa suka yi sallar nafila, to ina kuma ga wadda ya tashi, ya kuma tashi iyalinsa dan sallar Farillah? ka rasa wannan ladan, ba nice da asara ba".

Ya zuba mata ido yana kallon ta, Yana jin sabon tashin hankali na shigarsa, tabbas ta kerewa tunaninsa, an mata famfo fiye da duk yadda yake zato.

Haka ta gama sakin magaganu sannan ta fita zuwa dakinta, don yin sallah.

Kan Mk ya kulle, ya rasa mai zai mata, ya yi fushin, ya bagarar da ita, Amma duk a banza, wai ya zai mata ne? kawai sai ya tsinci kansa da daga hannunsa sama yana cewa "Allah kasan irin son da nake yiwa Sa'adah, Allah ka shirya min ita, ka bude kirjinta ta gane gaskiya, ta fahimci bani da nufin zaluntarta, ka zaunar da mu lafiya, Allah ka kara min ha'kurin zama da ita cikin adalci".

Ya kishingida yana tunano kafin shigowar su Halima cikin rayuwar aurensu, ko ya ya taga ya canja mata, ta dinga tambayar me ya same shi, ko itace ta masa laifi? Ta dinga bashi hakuri kenan, ko yace bata masa komai ba, kawai yanayi ne, ko baya jin dadi ne, duk da haka hankalin ta baya kwanciya sai ya dawo da walwalarsa, amma a yanzu kusan sati uku suna dauki ba dadi, amma kullum da abin da zata yi da zai sake bakanta masa Rai, karon farko da ya fara zargin Anya kuwa dama Sa'adah da gaske tana sonsa?

Ya dinga hasaso yadda yake gudun zuciyarta, har wasu da yawa suna ganin tsoronta yake ji, alhalin ba haka bane, kawai tsananin sonta da yake yi ne, yasa baya shiri da duk abin da zaisa ta koka, mussaman na rashin wani abu, zai ha'kura da dukkan bukatun kansa, matu'kar ita zata wadatu. Amma duk su Safina sun lalata mata tunani, sun jefa mata shubuha, wai yan mata ne da shi na banza! Tabbas suna neman raba shi da ita ne.

A fili ya furta " Allah kana ganin masu son shiga tsakanin aure, Allah ka min maganinsu".

Sai da ya isa makaranta! Ya na cikin motarsa ya ciro wayarsa, ya lalubo lambar Anty Sumayya, cike da girmamawa ya gaisheta, sai kuma ya yi shiru ya na jin nauyin zartar da kudiransa. Jin yanayinsa yasa ta tambayarsa ko akwai matsala ne?

Cikin jin nauyi ainun yace " So nake ki yiwa Sa'adah magana, mun dade cikin rashin nutsuwa, na yi iyakacin kokarina dan mu fahimci juna abin yaci tura, bana son na tayarwa da su Baffah hankali".

Hakuri Sumayya ta dinga bashi, tare da al'kawarin yanzun nan zata kirata.

Kai tsaye yace "ba waya a hannun ta".

Jikin Sumayya ya sake mutuwa, shiyasa kwana da kwanaki tana gwada layin Iyah baya shiga, ta damu kwarai da rashin jinta, sai da Inna tace mata, lafiya ce take buya, Ni kaina an kwana biyu bamu gaisa ba, da kuma wata matsalar ce ai da mun ji, tunda mijinta kusan kullum sai yazo unguwar, kowacce juma'ah kuma zai shigo ya gaishe ni, ya bar Jawad sai zai tafi ya zo ya dauke shi, na fahimci Iyah! indai naji ta shiru haka, to cikine da ita.

"Yanzu kana gida ne?"

Ya girgiza kansa tamkar tana ganinsa "Ina makaranta, sai da yamma zan koma".

Ai kuwa da yamma yan isa gida ba jimawa, Kiran Sumayya ya fado wayarsa, bai dauka ba, ya bawa Jawad wayar tare da cewa" sauri ka kai mata, Maman Gombe ce" dake tuni sun bar Jos tun shekaru biyu da suka wuce.

Da gudu kuwa Jawad ya fita sai dai kafin ya isa inda take ya danna ok, ya fara yiwa Sumayya surutu, ita kuma ta biye shi, duk da ba komai take fahimta a hirar tasa ba.

Fada sosai Sumayya ta yiwa Sa'adah, ta yi shiru tamkar tana jinta, sai da ta gama ta saka mata kuka tana fadin

"Yana zaune da yan'uwansa kalau, amma ni yana ba'kin ciki da hadin kan dake tsakanina da ke, Ina zaune da shi ne kawai, amma ba irin wulakancin da baya mini, ya fifita farin cikin yan matansa akaina, ya koyo wata dabiar da ba tasa ba, ko kukan jini zai ga inayi ba ruwansa, shine har ya kawo karata?".

Mamaki ya kama Sumayya tace "Ni kike fadawa wadannan maganganun? Eh na tabbatar Mijinki ba karamin ha'kuri yake da kaifin harshen ki ba, amma ki saurare ni da kyau, wlh idan baki canja ba, za ki jefa kanki a nadama mai yawa, wato ke har yanzu baza ki yi hankali ba? Kowacce mace da akwai inda take ha'kuri, ance miki auren wasa ne, ke naki ma wallahi ba matsala bace, kawai dorawa kanki kika yi, Ina ruwan ki da yanmatansa, ko aure yace zai kara Ina ruwan ki? Tun zuwan ku Jos na lura sai kin koya masa bagarar da lamarin ki".

"Dan ke mijinki ba mai hayaniya bane, ba mai kule kulen mata bane shiyasa kike ganin bani da matsala" Sa'adah ta fada a tunzure.

Cikin bacin rai sosai Sumayya ta ce "shikenan ki yi duk abin da kike so, ya dauka ina da wata kima a wurin ki! shiyasa yake ganin zan iya muku sulhu basai iyayen mu ba, amma tunda ban isa ba shikenan! Rayuwarki ce, kina da ikon yin duk yadda kika so, sai dai ki sani wadda bai ji bari ba, ba zai ki ganin hoho ba". daga haka ta kashe wayar ta, ta bar Sa'adah ri'ke da waya tana kunshekin kuka.

Jikinta ya yi sanyi, tana Jin Aunty Sumayya uwace ta wuce ta yi misayar yawu da ita! Dan haka sai ta sake kira, Sumayya ta daga tana cewa "menene?" Cikin kuka Sa'adah tace

"Na ji! kiyi ha'kuri".

Sumayya da bata da zafi, tace "yauwa Iyata, ni nasan indai a cikin Innarmu kika fito ba zaki 'ki jin abin da na fa'da miki ba, saboda kinsan nan duniya bani da kamar ki, mu kenan iyayen mu suka haifa, ki daina duk abubuwan da mijinki baya so, ki kara hakuri, idan ma ke yake zalunta ki yafe masa, ki yawaita addu'a sai kiga Ubangiji ya warware miki komai, fiye da yadda kike zato! Yanzu abin da nake so da ke, ki bashi ha'kuri, kar kuma a sake tada maganar koma wacce iri ce".

Sai da Sa'adah ta ja majina murya na rawa tace "Anty shine fa yake fishi da ni, yake ta share ni, ba abin da banyi dan mu shirya ba, ya ki bani fuska, kuma sai ya kawo karata?"

Cikin rarrashi Sumayya ta ce "bafa kararki ya kawo mini ba, nasan dai kuna zaune kalau ba zai barki ba waya ba, nice dai na tambaye shi Kuna lafiya kuwa, yace na

miki magana baya son ya shigo da Baffa cikin matsalar, iya haka ya fada min wallahi".

"To Anti na ji fa'danki, amma shima ki fa'da masa idan ina kuka, ya daina cemin na dame shi da kukan banza, ko na iyashege, ya bar komai ya rarrashe ni".

Sumayya ta 'kunshe dariyarta tace "Zan fada masa, amma ki bashi ha'kuri first, nasan kafin ki yi tuba sai tura ta kai bango, kullum ina fada miki hakan sifface ta girman kai.

"Anty sanin da, kika mini, wlh na bashi hakuri, ta hanyoyi da dama, ai ba sai na fada da baki ba, shi da kansa yasan na bashi hakuri, kawai dai ya runtse idanuwansa ne".

"To yanzu ki fada da bakin ki yasan Ina da mutunci a gurinki, idan na fada miki zaki ji! Idan kuma kin ki, shikenan, kin wula'kanta Ni, kin wula'kanta kanki".

Da haka Sumayya ta risinar da Sa'adah, sun dade suna magana har sai da kudin wayoyin ya kare tas, sannan suka ha'kura.

Da kanta ta kai masa wayar, duk da Jawad na cewa ta bashi ya kaiwa Malam! ta bashi wayar ta zauna gefen gadon Sannan tace " Malam ka yi hakuri dan Allah".

Idonsa a rufe, bai bude su ba yace "Ni dama barcin da kike hanani yi da daddare ne, bana so, hakuri na zai iya :kwacewa, idan zaki yi kukan ki ban hana ki ba, amma pls stay away from me, na riga na gane ban da mutunci ko ka'dan a gurinki, zaki iya zagina kan ki tsaye, zaki iya fada min duk maganar da ta zo bakin ki, na zuba miki ido ki yi duk abin da kika ga dama, amma ki jira sakamakon zagin da kika min, na rantse miki! ba zai tafi a banza ba".

Ya karasa da rawar murya saboda 'bacin rai.

Hankali Sa'adah ya yi mugun tashi, mussaman yadda ya yi maganar da dukkan zuciyarsa, ta zuba masa ido tana ganin yadda yake numfarfashi tamkar wadda ya yi gudun fanfalaki, dan tsananin bacin rai.

Ta zame ta durkusa a jikin gadon ta ru'ko hannunsa "ka yi hakuri, ba zan sake ba".

Ya bude ido da suka yi jah yace "wallahi za ki sake, ba dai kin bada kofar da wasu suka shigo cikin rayuwar aurenmu ba? ba kin fi gaskata maganganunsu, sama da nawa ba, nace ban son su zo min gida, kin nuna ban isa ba, saboda kina jin isar gidan na ki ne, na sha jan kunnen ki akan kaifin harshen ki, amma kullum sake koyon dabarun ba'kaken magana kike yi, ki rubuta ki ajiye wañnan *HALIN YAU* din da suke cusa miki, kina dauka babu nazari bare tsinkaye, ba inda zai kai ki sai nadama, na fara gajiya da halin ki, hakuri na ya fara kaiwa geji gaskiya, Menene bana miki da kike wulakanta ni haka?"

Jikin Sa'adah ya yi wani irin nauyi, zufa sai karyo mata take yi ta ko Ina, ta kasa bude baki ta yi magana, dan hatta harshen ya mata nauyi ainun, hawaye kuma tamkar an bude famfo, Jawad da yake tsaye yana kallon su, ya karaso ya fara goge mata hawayen, Yana cewa "biskit za ki ci? ko Malam ne ya doke ki?"

Ta kasa magana kamar yadda hawayen ya ki yankewa,ya zuba musu ido yana ganin yadda Jawad ke goge mata hawayen,yana kuma fa'din ta yi shiru, zai goyeta a kekensa, wani irin abu mai kama da tausayi ya tsirga masa yana ayyana karfin soyayyar da ke tsakanin uwa da 'da.

Murya a dashe Mk yace "ki ci gaba da kukan, so kike ya 'kullace ni, ya zaci kamar Ina gallaza miki ne, idan girma ya cimmmani ya'ki jin 'kaina"

Da sauri ta dago manyan idanuwanta ta zuba masa, a fili akan idonsa tace " Malam plz ba kai bane, ka dawo wancan Malamin nawa! mai yawan yi min afuwa, mai tausasa mini".

Ya mayar da idonsa ya rufe yace "shikenan ya wuce, dauki "danki ku tafi gurinki barci zan yi".

"Ka yafe mini?"

"Nace ya wuce" ya fada a gajarce.

Taja hannun Jawad! amma yaron ya coge alamun ba zai bita ba, ta tsaya tana kallon sa ya hau gadon ya kwanta jikin Babansa, Mk ya rungume shi yana ji a ransa shima fa Jawad na sonsa sosai😀Mk manya.

Kwana biyu, Sa'adah ta sauko, tana komai yadda ya kamata, ta bangaren Mk shima yana iyakar kokarinsa na bai sake yin wata maganar ba, zai ci abincinta, idan ta masa magana, yana amsawa kadaran kadahan, kawai a shimfida ne ba ya kulata, ta gama shure shurenta, ya yi biris, duk da shima fama yake da shan lemon tsami.

Tana zaune tana tunanin mai zata masa ya ta'ba ta, hawaye na siraro mata, saboda yadda abin ya dagula mata lissafi, mussaman yadda ta san shi da rashin ha'kuri a wannan harkar, idan ta hasaso ko a waje yake samu sai ta ji tamkar ta sume, ta sake ramewa ta yi zuruzuru, kamar ance kunna radio, aikuwa nan ta ji sanarwa a gobe litinin hukumar zartarwa ta kwalejin tarayya ta kano (F.C.E.) zata rufe yin registration.dan haka duk dalibin da bai yi ba ya hanzarta kafin a rufe.

Ta yi shiru, ta tabbatar Malam yasan ranar da aka bude dan farawa, dan kuwa yana da aboki da yake aiki a gurin, duk da ba lakcara bane.(Non academic staff)ne.wani sashi na zuciyar ta yace kika sani ko ya biya miki ne? Da haka ta samu sukuni kadan.

A ranar bai dawo da wuri ba, dan haka ta danne komai ta barshi ya gama komai cikin nutsuwa, sai da suka kwanta ta bijiro da maganar da ta ji a radio.

Tsawon lokaci ya mata shiru, zuciyarta ta sosu da wulakancin nan da ya tsira, ashe haka yake jin rashin dadi idan ya mata magana ta share? ta daure tace "kana tare da ni kuwa?".

"Ina jin ki, na sani, har na biya miki, yasa hannun ya ja drowar gefen gadon ya fiddo da teller ya nuna mata, farin ciki ya mamayeta, kafin ta yi magana sai taji yana maganar da ta kasa gane manufarsa.

"Na gama miki komai illah wurin da yake bu'katar signed dinki!amma a yanzu na fasa, matu'kar da aurena akan ki! wallahi ba za kije makarantar nan ba".

Cikin rudu tace "Ban gane ba fa?"

Ya tashi ya kunna fitila, sannan ya zauna! ya zuba mata ido yace

"Ina nufin idan har sai da yardata zaki yi karatu, to baza kiyi ba, idan kuma ya zama dole sai kin yi, sai dai kije a matsayin single amma ba matata ba".

Hawaye ya balle mata, ta ru'ko hannuwansa cikin rawar murya tace

"Na roke ka kar min haka! dan Allah kar bari na gasgata masu fadin ba zaka taba barina na yi ilimi ba".

Ido cikin ido yace "gara ki gasgata su Sa'adatu, ada kam na kudiri aniyar ilimi sai kince ya isheki! amma Billahillazi yanzu na fasa, ba ki fara karatun ba, kina iya zagina, bare kuma na baki damar da kullum sai kin fita, kin yi cudanya da mutane daban daban, tunda na gane kawaye zasu iya rinjayar ki, zasu iya canja miki dabi'a, zasu iya ruguza mana kyakkawan zaman mu, daga lokacin na gane barinki karatu mai zurfi ha'dari ne, ilimin sakandiren da kika samu, yasa kina jin kina da yanci, Ina kuma ga kin shiga babbar makaranta, ki zauna ki yi rainon Jawad kawai, tunda nace ki cire loop din nan, amma sun zuga ki, kar ki bari ki tara yara mu tsufar da ke, to ki zauna ki tabbata da kuruciya".

Kuka take yi, tana bashi ha'kuri, yace "na gama maganata, zabi na gareki, dan kuwa wallahi ba za kije ki koyo mini karatun raini da rashin da'a ba, a haka kina iya zagina,nan gaba kuma sai dai na ji mari."

Kuka take yi tun daga kasan zuciyar ta, a duk tsayin rayuwarta a duniya a ranar ta fara sanin Ashe kuka ma kala kala ne, duk wadda tayi a baya na nisha'di da shagwaba ne, na yau ne take yin na zunzuruntun bacin rai.

Ya kalleta yace "Ba abin damuwa bane Wannan fa, domin na riga da na baki damar ki, dan hakama nake ta dan jah baya, dan mu dan saba da rashin tarayyarmu, Ina tabbatar miki idan kin zabi makaranta akan aure! Wallahi zan dauki nauyin karatunki, kuma zan wanke ki a gun su Baffa, zan dauki laifin rabuwarmu Ni ka'dai."

Murya na rawa tsabar kuka tace, "Dan girman Allah yaushe na zage ka?"

"Kina nufin na miki sharri ba ki zage ni ba?"

Ta sake ru'ko hannuwansa da kyau tana harhado kalmomi tace " Ni bance haka ba Malam! amma dan Allah ka yi hakuri, na canja Wallahi, ba zan sake ba"

"A ranar da kika zage ni dama na tabbatar miki u will pay for it! zaki yi karatu da yardata ka'dai, idan na gamsu kin canja din da gaske, idan na tabbatar ba mahalukin da zai canja ni a zuciyar ki".

Ya zare hannuwansa daga nata ya mike, itama ta mike ta tsugunna ta ru'ko kafafuwansa, tana fadin "Malam bazan iya barinka ba, dan Allah, ba dan halina ba, ka janye wannan kudirin ina son karatun amma da yardar ka nake so".

Yace "idan kuwa kina son karatu da izinina, wallahi ba bana ba, to be frank Sa'adatu! ban san time din ba, har sai na gamsu ba third party a tsakanin mu, sai na gamsu na wuce zagi da diban albarka ta kowacce fuska daga gareki".

Ta sake shi! sanin halinsa idan ya rantse shikenan ya gama magana, ta ha'kura tana jin bakin ciki tamkar ta mutu! ta huta. Kuka ba irin wadda ba tayi ba, Mk da kansa mamakin kansa ya ringa ji, bai taba zaton zai iya mata haka ba, sai dai wata'kila yadda take gasa masa duk maganar da ta zo bakinta yasa ya iya jarumta haka.

Sa'adah tana ji, tana gani, ya hanata makaranta, duk ta zama wani iri, zaman nasu dai gashi nan, ta koma shiru, ba walwala sosai, kullum cikin kunci take amma bakinta dif, sai kuma yanayin data koma ya dame shi, fata yake su koma kamar da, rayuwar farin ciki, amma abin na neman cin tura, a zahiri dai suna zaune lafiya amma kuma babu nisha'di a cikin zaman.

Saboda su Halima da suke fadin "dama ai sun san pooling dinta yake yi, ba wata makarantar da zai barta, duk dan'iskan namiji zai yi iya yinsa ya kulle matarsa a gida saboda sun San Annabi baya tuntuben harshe, duk abin da ka yi da matar wani, sai anyi da taka.

Wattanni kusan biyu zamansu ba armashi, bata masa komai na laifi, amma kuma ta dadare ranta, suna cikin haka, aka fara babban zabe na kasa, kowa yasan Malaman jami'oi ne baturen zabe, Dan haka wata guda aka dauka ana yiwa su Mk horo na mussaman kan yadda zasu kare muradan yan kasa, kar su yarda ayi amfani da su, ayi wa dimokaradiya kafar ungulu, Malaman addini suka dinga musu wa'azi na suji tsoron Allah su yi gaskiya a cikin aikin da za su yi, karshe suka rufe bayanin da cewa duk wadda aka bashi kudi dan ya yi magudi, to ya karbe kudin ya adana, sannan ya yi adalci, ma'ana ya fadi sakamako na gaskiya.

A yanzu da suke shiga shekaru biyar da aure shi da kansa ya tabbatar tsoron ta yake yi, idan akwai abin da ya tsana to ta share shi, ko ta tsiri fushi, ko ya fita sai ya dawo, yasan yadda ya yi ya shawo kanta, yayin da ita kuma take jin kanta a sama komai take so sai ta same shi, SUMAYYA kanta mamakin yadda Sa'adah ta dawo take yi, kullum cikin tsadaddun sutura take , hatta salooon din da Sa'adah take zuwa one in town ne, kullum suka yi waya sai ta mata nasiha ta saukaka buri, ta rage dorawa mijinta hidimar da bai kai ya yi ba.

Itakuwa sai tace da ba zai iya ba, ai da bai yi ba, ya hanani karatu ai kuwa dole yamin yadda nake so, tunda idan ban ci ba ma, na waje ne zasu ci, har Sumayya ta gaji ta zuba mata ido tana mata addu'a.

Rannan da yamma Zainab Ma'aji ta ziyarce ta, kasancewar ana daukan lokaci kafin su hadu a dalilin Zainab din tana karatu ne a Jami'ar jahar kaduna(K.a s.u). ba kowanne hutun ma take zuwa Kano ba, sai take barin hoste ta tafi gidan kanwar mahaifiyarta ta yi hutunta indai ba mai tsayi bane.

Mamamki ta tsaya yi ganin yadda Sa'adah ta koma, ta goge sosai, fatarta ta yi fresh tabbacin tana samun tsadadden mai, tasan Sa'adah Yar gaye ce, amma ko kusa ba kamar yanzu ba, da ta ke samun dukkan wants dinta.

Sauyi sosai ta gani tunda ga jikinta, da abubawan more rayuwa na gidan, da cima ta mussaman, ga wata irin ginshira da ta gani a tare da ita.

A sanyaye Zainab tace "Kin zama wata Hajiya ko big madam zance? lallai Uncle a gaishe shi, ina Jawad? hatta maganar Sa'adah ta canja sai anfitar mata da wani salo na daban. lamarin da Zainab ta dinga dariya tana fadin ko za ki yiwa kowa wannan iyashegen ban da ni.

Suka yi dariya gaba daya sannan suka shiga hira, a gidan Mk ya tarar da ita, ta gaishe shi da girmamawa, shikuma ya dinga mata barka da zuwa cikin karamci, a dan dawowarsa da ya yi , Zainab ta fahimci abubuwa biyu, Uncle Mk ya gama lalacewa akan soyayyar kawarta, yayin da ita kuma Sa'adah take amfani da hakan take yin duk abin da take so.

Zainab ta tsinci kanta da adduar ALLAH yasa su Halima ba su jefa ta cikin HALIN YAU na bin malaman tsubbbu, domin ta tabbatar tun shekarun baya da Halima bata gama sanin kanta ba, take zuwa gidan malamai, ko aiken uwarta ko na kanta.

Har ta bar gidan tana jinjina wa Mk tana fatan Allah ya bata miji mai kwatankwacin halayyar sa.

Manyan kudade Mk ya samu a zaben da aka gudanar, saboda karamar hukumar da aka kai shi, itace mafi yawan jama'a, ganin gwamnati mai ci zata sha kaye, sai ta hargitsa zaben wannan yankin, tare da kiran Mk har gidan gwamnati a sirrince, aka tura makudan kudade a asusunsa akan ya canja alkulluman zaben, ya karbe kudin kamar yadda aka sanar da su.

bai canja alkulluman ba, amma sai sakamakon ya zama inconclusive, ma'ana bai kammala ba.

Kwana biyu yana jin farin ciki, yana ayyana indai kayan 'kawa sune muradin Sa'adah zai mata su, zai kashe mata ko nawa ne dan zamansu ya dawo tamkar shekaru biyun farko na aurensu.

Ba zato, ta ganshi da deep freezer, hankalinsa ya kwanta da ya ga Sa'adah ta yi murna, rabon da ya ga murmushinta sosai irin haka tun kafin su fara yar tsama.

Tare suka fita, suka yi siyayya mai uban yawa da tsada, hatta Sa'adah da kanta sai da ta girgiza da irin manyan laces da atamfofi super, da kuma shadda getzner da Mk ya dinga dibar mata. matu'kar tace abu ya mata kyau zaice ta dauka.

Barin takalma kirar itali da dogayen riguna rantsatsu, hatta turaren Escada da yasan tana so amma baya iya siyansa saboda tsadarsa, a wannan lokaci guda biyu ya siya mata, bayan kayan kwalliya na garari, suka zarce bakin asibitin Nasarawa, suka yiwa Jawad siyayyar hadaddun kaya masu yawa, hatta dan gidan Mahmoud da ya kasance jariri(Dady) sai da suka masa siyayya sosai.

A hanyar su ta komawa ya bata labarin inda ya samo kudi, ya kara da cewa

"Ina son na kewaye mana filinmu, a kuma fara ginin zuwa inda zai samu, a hankali kuma sai na dinga yi, har na kallama".

Ya kalleta ya ga farin cikin ta ya kasa boyewa yace "ki nutsu ki fada mini irin tsarin da kike so a miki a ginin, nasan dai kina son garden?"

Da azama tace "Da swimming pool, sannan upstairs nake so, irin wadda kafar benen zata kasance a tafken falo, a mini dining area, sannan kicin ya zama a cikin falon yake a fili, Ina fatan ka gane irin wadda nake nufi?"

Cike da shauki yace "Na gane duk da bai gama zuwa mana ba, nasan kema a finan finan ketare kike ganin kicin din, ba damuwa za'a miki irinsa Ummu Jawad my dear".

Ta rufe ido tana jin duk wani kunci na zuciyarta ya wanke mata tas. Shikuma yana ta barin jiki wirin sake sata walwala.

Tafiya ya shirya musu zuwa Abuja, duk a kokarinsa na son dawo da amincin dake tsakanin su.

Gidan Mahmoud da yake Goron Dutse, aka kai Jawad saboda makaranta, kuma yafi kusa.

Ranar Alhamis suka tafi, sun Isa lafiya, karfe uku suna madaidaicin Hotel din da ya kama musu daki.

Sallah suka yi, sai cin abinci ya biyo baya, wadda a hanya suka tsaya ya siyo, sai da suka koshi, suka yi wanka dan warware gajiya, sannan suka dora da sallar la'asar.

Barcine ya gwada musu fin karfi, Mk ne yafara yi, Sa'adah ta zuba masa ido tana kallon kyakkawar fuskarsa, da yadda yake sauke numfashi a hankali cikin nutsuwa, wani irin shauki na mamayarta, tana jin sonsa na bin duk wata kafa ta jikinta. A haka itama barci ya wuce da ita ba zato.

Sai daf da maghrib suka farka, suna mamakin lokacin da suka shafe suna barci.

A gurguje, Mk ya dora alwallah ya fita neman massalaci, ai kuwa cikin sa'a bai yi tafiya mai yawa ba, ya samu.

Kafin ya dawo Sa'adah ta ninke shimfidar gadon, ta dauko bedsheet din da ta zo da shi ta shimfida, ta sake dauko burner ta jona ta zuba turaren wuta, nan da nan daki ya dauki daddadan kamshi.

Ganin lokaci ya tafi bai dawo ba ta gane sai ya sallaci isha lafin ya shigo.

Ya dawo ya sameta cikin kwalliya sosai, ga sanyi ac da kamshin turarenta da kuma na turaren wuta ya cakude, dakin ya zama na mussaman.

Da sauri ya yi wurgi da ledojin hannunsa wadda gasasshiyar kazace, sai kuma ruwa da yogurt masu sanyi. ya isa kusa da ita yasa hannun ya rungumeta tsantsan yana ta shin shinarta, ita kuma ta lafe a jikinsa tana jinta in a new world.

Sun jima a hakan, kafin ya saketa, ya zauna a kasan kafet, idonsa ya kada, leda ta bude ta dauko plate da ta juye musu kazar, suna ci ta gabatar masa da shayi a dan karamin flask ga kuma cup da spoon a ciki, ya kalleta da murmushi yace "shiri kika yi haka?" Murmushi ta yi kawai.

Suna kammalawa Sa'adah ta yo brush, ta hadawa Mk ruwan wanka. Kafin ya fito ta shirya cikin sabbin nighties masu daukan hankali. Ya fito daure da faffadan tawul, ya tarar da jallabiya da gajeran wando akan gado, ga kuma body spray dinsa na Malizia.

Turaren kawai ya fesa ya dauke kayan ya dorasu kan side drower.

Ya zauna sanyi dakin na ratsa shi, yana ayyana suna komawa zai sanya musu Ac.

Tana tsaye tace "ba zaka sanya kayan ba?" Ido ya kanne tare da fadin "Ban bukatar su a yanzu".

Kunya ta kamata, ta waske da fadin "Mai ba zaka shafa ba shima?"

Maimakon ya amsa mata sai ware ya dukkan hannuwansa biyu alamun ta zo gare shi, ta tsaya tana kallon sa, ta kasa motsawa, yace "plz Dear come to me".

Cikin kunya ta isa gare shi, ya zaunar da ita kan cinyoyinsa ya rungume ta tamkar zai hade su.

Ta lafe a kirjinsa tamkar wadda zai shayar da ita, ya sunkuyar da fuskarsa daf da tata, numfashin su ya dinga haduwa, tsinin hancinsa akan nata, jikinsu ya dauki wani irin tsimi.

Ya raba hancinsu, amma fuskokinsu a hade. Cikin wata murya da Sa'adah bata sanshi da shi ba yace "Ina sonki, ina son na rayu da ke! Dan Allah stay with me".

Jikin Sa'adah ya yi la'asar, da murya marar amo tace "kana ganin zan iya barinka ne Malam?"

"Matu'kar kina tare da su Halima, kina basu damar da suke cusa miki ra'ayinsu Ina tabbatar miki zasu raba ni da ke" ya fada cikin rawar murya.

Kafin ta yi magana ya zarce da fadin "Ina miki son da zan sadaukar miki da komai, idan nace komai, ina nufin har rayuwa ta amma ke baki fahimci hakan ba"

Ya sake ri'keta sosai, cikin wata murya irin ta karaya da lamari yace "Bana son kaifin harshe Sa'a, bana miki akan me zaki dinga mini? zan ro'ke ki! dan Allah fada mini inda na kuskure miki da ban cancanci ki zauna da ni lafiya da kyautatawa ba?"

Ta yi shiru tana jin hawaye na cika mata idanuwa, haka kawai take jin tamkar wani abu na tashin hankali zai biyo baya.

Jin shirunta sai ya zarce da fadin "ki bude baki, ki mini magana, ki fada min inda na gaza sai na gyara tunda ubangiji ya dora mini sonki da son zama da ke".

Ta girgiza kai muryar ta na rawa tace "Ba ka gaza ba Malam".

Ya nisa yace "Am not good in bed?".

Kunya ta kamata, ta cusa fuskar ta a kirjinsa, yace "magana muke yi ta gaskiya".

Ta dinga dan dukan kirjinsa tana cewa "Ai kasan dai kure ni ka ke yi anan ma."

"Idan kuwa hakane, to mai ya kawo Kika canja, mai yasa kike bijire mini?"

"Ka yi hakuri zan canja".

Yaushe zaki canja din?".

Ta tura mai Baki gaba cikin shagwaba tace "Na canja fah".

Da'di ya kamashi ya dinga kai mata kisses ta ko ina tamkar mayunwacin zaki.hannuwansa suna ta kai komo a jikinta.

Da kyar ya sarara mata, dukkansu sai numfashi suke mayarwa, daga inda yake ya mika hannu ya janyo ledar yogurt ya bude ya fara bata a baki, Yana cewa "ke Amaryace yau! irin Amaryar da ta kerewa mata hudu"

Da'di ya kamata, ta sha iyakar shanta, ya shanye ragowan da ta bari daga nan ya sa harshe yana lashe mata baki, ya janyo harshenta Yana sucking irin deep din nan, daga haka suka fada zazzafar soyayya mai dimautarwa.

Haduwar ta zama so ma sha Allah, saboda hadin kai da Sa'adah ta bayar, sabanin kwanakin baya da take zame mishi very doll.

Surayya Dahiru

✍✍

07/04.

 HALIN YAU!

NA

SURAYYA DAHIRU.

lafazee writers.

A guji taba Wañnan labarin ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.

Doka mi lamba ta 68 ta yi nuna cewa satar fasaha Babban laifine da yake dai-dai da satar Dukiya.

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR

Tukuici ga

HAJIYA RABI SANI

Bisa yaddda kike son rubutun Halin Yau, Na gode, Allah ya shirya zuri'a

SA'ADAH NA GAISUWA.

71-74.

Wannan dare ya shiga cikin dararen da ba zai shafe a zukatan su ba, saboda sun jiyar da junansu farin ciki na ban mamaki. Sosai Mk ya bawa Sa'adah soyayya da kulawa mai yawa, kullum suna tare ba inda yake zuwa idan ba masallaci ba, itama kuma bata komai sai gyaran daki, wannan hutun ya sabunta soyayyar su, ya kara musu shakuwa, ya kuma goge dukkan tsattsar dake zukatan su, aminci da Nishadi ya cika 'kalbinsu.

Kwanaki biyar suka yi amma fahimtar da suka samu a cikinsu ya zarta na wattanni biyar.

Ana gobe za su dawo da daddare, suna kwance ya rungumeta sosai tamkar zai maida su halitta 'daya, hatta bugun zuciyar su suna ji, sai dai bugun da zuciyar Mk yake yi ta zarce ka'ida.

A hankali Sa'adah ta ce "Malam baka da lafiya ne?"

Murya a dakushe ya ce "me kika gani?"

"Bugawar da zuciyarka take yi yanzu ya sha ban ban".

Cike da rauni ya ce "fargaba nake yi Sa'adah! bana son mu koma Kano ki canja mini, na fi son wannan rayuwar da muke yi, mai cike da nutsuwa da girmamawa".

"Nace komai ya wuce fa, sannan ai na baka ha'kuri, mai yasa ba ka gamsu ba?"

Kai tsaye ya ce "ki mini al'kawarin yanke kawancenku da su Halima, Ina rokon ki, ki rabu dasu, sannan ki mini al'kawarin baza ki dinga 'daga mini hankali ba, komai kike so a hankali zan miki kin ji? Ni dai fatana mu zauna lafiya".

Haka kawai ta ji hawaye na zubar mata karon farko da ta ji tausayinsa ya cika mata zuciya, sai take jin tamkar mutuwa ce zata sure wani a cikinsu.

Jin 'dumin hawayenta na zuba akan kirjinsa, yasa nasa hawayen da tun dazu yake kokawa da su, suka kwace masa! kwatsam Sa'adah sai jin saukar hawayensa ta yi akan goshinta, karon farko da ta ga ko jin hawayensa a cikin shekaru biyar da ta yi tare da shi, hatta mutuwar Hajiya Babba da ta masa mugun bugu, ita dai bata ga hawayensa ba.

Kuka sosai Sa'adah ta saka tana cewa "Malam me kake yi haka, me na yi haka? me yasa kake zullumi har haka akaina? Kai baka ganin laifin kanka sai nawa ka'dai?"

Da rawar murya ya ce " Nan duniya ba wadda zai cusa mini ra'ayi akan ki na yarda, saboda na fishi sanin ki, hakanan son da nake miki ba za bani kuzarin da zan cutar da ke ba".

"Nima ba a cusa mini ra'ayi akan ka ba".

Murmushi mai sauti ya yi wadda baya dau'ke da nishadi ko ka'dan.

Ya ce "shikenan fatana dai ki kulle kofofin da kika bude wasu suke shigowa cikin matsalar mu, wadda Ni da ke kawai ta shafa".

"To Malam ya maganar makaranta ta?"

"Da gaske za ki yi, amma sai kin dawo mini Sa'adah ta, kinsan tun farko bana shiri da Gogel badan komai ba, sai dan rudeness dinta, shine yanzu zaki dawo mini a Gogel din?"

Ta 'dan dara kadan! kafin ta yi magana, ya rigata da cewa "Ban so na fada miki yanzu ba, amma bari ki ji, kinsan naje Abuja na yi jarrabawar scholarship, idan na Sami nasara, zan yi PhD dina tsawon shekaru hudu a kasar England, so nake idan na tafi, naga da yiwuwar ku bini ke da Jawad sai ku bini, sai kiyi karatun ki acan, amma ba al'kawarin hakan na yi ba, Ina fatan dai hakan ya kasance, muna komawa zaku yi passport, na riga na yi nawa, idan hakan bai samu ba sai kiyi anan, kafin na dawo kinci karfin karatun ki".

"Allah ya zaba mafi alheri"

Inji Sa'adah.

"Ameen ameen" MK ya amsa mata.

Da haka ya shiga lasarta cikin wani salo mai gigitarwa, tsawon lokaci yana sarrafata kafin su fada duniyar masoya mai nauyin bayyyanawa.

Karo na biyu da Sa'adah ta gasgata ana kwana ido biyu, a ranar basu runtsa ba, dan kuwa a kunnen su aka fara kiran sallar asuba, wanka Mk ya fito ya ganta kwance tamkar matacciya barci na kai mata caffa

"Daurewa za ki yi, ki yi wanka ki yi sallah, sai ki yi barcinki".

Da kyar ta tashi tana Jin dukkan gabb'anta sun mata nauyi wadda ba komai bane ya sababa hakan ba illah sububurdar da ta sha a hannun Mk hatta farcenta nauyinsu take ji, ya fice masallaci yana jaddada "kar fa ki koma".

Ta yunkura ta nufi toilet din tamkar mai koyon tafiya, da ruwan mai zafi ta yi wankan, ta jima zaune cikin ruwan saboda yadda take jinta a bude, tana ayyana me yasa shi baya kaita toilet ya gasa mata jiki, ai yasan yau bai mata da sauki ba.

A daddafe ta yi sallah, akan sallayar ta kudundune tana ta fama da kanta tare da fatan ta sami barci ko ta dawo daidai.

Koda ya dawo ya iske ta a kasa, murmushi ya yi sannan yace "ga ta da kwadayi ga kuma lalaci".

Ya dauke ta cak ya dora a gado, ya cire jallabiyarsa, sannan ya kwanta ya lullube su da bargo, a tsarinsa so ya yi su tafi daidai wannan lokacin, rashin barcin da bai yi ba, yasa ba zai iya tuki cikin nutsuwa ba, dan haka ya kwanta yana raya ko da la'asar zasu iya tafiya kaduna, su kwana acan, jibi da safe sai su wuce Kano, a lokacin hanyar Abuja zuwa kaduna cike take da aminci da tsaro, Allah mun tuba, Allah ka dawo mana da aminci da tsaro a yankin arewa da Nigeria gaba'daya.

Lafiya Lau suka dawo kano, a gidan su Mk suka fara tsayawa suka ci abinci, Hajiya sai Ina ka saka ta ke yi da su, mussaman ta dinga murnar yadda ta ga Sa'adah ta yi kiba ta yi kyau alamun ba ta da matsala.

A lokacin Sa'adah ta ga freezer Hajiya irin ta su ce, da alamun tare ya siyo musu, sai cinikin kankara da pure water take yi kuwa.

Ta gabatar musu da abinci wadda shinkafa da wake ne, da miya sai salad, yayin da Sa'a tace da mai da yaji take sha'awar ci, da hanzari Hajiya tace duk Ina da su, ta fice cikin sauri tana ayyana Allah ya sa ciki ne da ita.

Ta dawo ta ajiye mata tana cewa " jiya Mahmoud ya kawo mini Jawad, ku shiryawa darunsa dan yace ba ruwansa sa da ku, tunda kuka gudu kuka barshi shi ka'dai.

Suka zube mata doya da dankalin turawa da tuffa, sannan suka tafi, ga mamakin Sa'adah sai ta ga ya sauka kan titi ya fada layin unguwar su, farin cikinta ya kasa boyuwa ta ce "Na gode Malam ".

Tare suka shiga gidan suka gaisa da su Baffa da yake yana gida yana fama da mura, sun dan jima tare da Baffa sannan ya fice dan dubo shagonsa.

Hira sosai Sa'adah suka sha a lokacin kuma ta ga gyaran da aka yiwa gidan nasu.

Baffa ya kalleta yace "Iyah Dan Allah ki dinga yiwa mijinki biyayya, ki kyautata masa, ki zauna da kowa nasa bisa karamci, ki ga yadda Gidan nan ya dawo duk aikinsa ne, Ni kam ba abin da zaki mini ki sanya ni farin ciki irin ki zauna da mijinki lafiya da kyautatawa, mazajenku suna wanke mini takaicin rashin haihuwar Namiji, ba abin da zance musu sai dai Àllah ya yiwa nemansu albarka ya shirya musu zuri'a".

Inna ta amsa masa da "Ameen ameen".

Suna cikin haka almajirai suka shigo da doya da dankali.

Mk da Sa'adah sun sha albarka da nema musu tsarin shaidan da makiya.

Da zata tafi Baffa ya ce "kice da mijinki ranar juma'ah ya taho mini da Jawad na kwana biyu ban ganshi ba, kewarsa da ta surutunsa ne suka sukurkutani ba mura ba".

Dariyar jin dadi ta yi tare da cewa "Zan fada masa kuwa Baffa".

Ranar wata alhamis ta ce ya kaita asibiti ta cire abin tsarin iyalin da ke jikinta, da kansa ya ce ta bari suga ko tafiyar za ta yiwu, sai ta cire a can.

Sosai suke zaman lafiya, saboda Sa'adah ta daina zungurar rigima, shi kuma yana kaf kaf da farin cikin ta. A haka har suka kwashi wattanni biyar.

Rannann ya dauketa suka je filinsa da ake ta aiki, ya dinga nuna mata yadda fasalin ginin zai kasance, amma bata fahimci komai ba.

Sai da suka dawo ya dako littafin zanen gidan ya nuna mata, ta yi muranr ganin katafaren gidan da zai zama mallakinsu, sai dai ta kalubalanci ta yaya kafar bene zata zama biyu?.

"Ke kika ce kafar bene a falo kike so?

wannan kuma ta baya ne sai kin shiga corridor sai ki ga kafar benen, idan Ina sama, kina da bakin ki, zan fita ta bayan, ko kuma idan Ina tare da bakina baki da matsalar komai, bari a gama, na tabbatar zai burge ki.

Ta tura baki gaba ta ce"Na ga sama ma katon falo ne ga dakunan barci tamkar na 'kasa sannan har da kicin, ko dai na Amarya ne?"

Ta fada tana matso 'kwalla, ya wurgar da littafin, ya ru'ko ta jikinsa ya ce, "Ke ce uwargida kuma amarya ta, da gaske nake kin cike mini gurbin mata hudu, ki daina wasiwasi akan maganata, ko an kaddara mini zan 'kara aure ina tabbatar miki, ba zan hada ki da kowa a gidan ba, daga ke sai yaranki ki yi yadda kike so".

"Ban cike gurbin mata hudun ba kenan?"

"Oh Sa'adah! kin zarta mata hudu ma, kawai ban son na miki al'kawarin da za'a jarrabe ni da rashin cikawa ne, kinsan bamu muke tsarawa kanmu rayuwa ba, idan haka ne kuwa bai kamata mu yi katsalandan akan goben mu ba, Ina tabbatar miki a burina ke kadai kin isheni rayuwa, sannan har yau ban taba jin son wata a zuciyata da ya kai matsayin da zan aurota ba".

Ta lafe a kirjinsa tana jin dadin yadda ya ke rawar jiki idan za ta botsare masa.

Kudin da Mk ya samu sun yi albarka kwarai da gaske, ya fadada shagon askin sa, ya sake budewa Ahamad wani shagon, hatta gidan da suke ciki ya sha gyara na mussaman, ya sakewa falonsu kujeru da sauran abubuwan more rayuwa da ya dace da ra'ayin gimbiya Sa'adah.ya kuma biya kudin aikin Hajj.

Sa'a kam ba a maganar yadda take lasar kudi har gold ya sai mata, waya ce dai bai siyi wacce take so ba, amma ya bata waccan da ta raina da kuma ainihin tata da ya karbe.

Baba Isa da su Baba umaru duk Sun Sami tagomashin inconclusive, duk da dai dama akai akai yana waiwaryasu da abin da zai iya na Alheri da neman albarkar su.

Shigowar what'sapp ya taimaka wurin tabarbarewar tarbiya, a farkon shigowar sa ya rudi mutane da yawa mussaman Mata dan hatta abinci sai andauka an dora a WhatsApp, gida mai kyau kuwa kullum cikin tallansa ake yi. Ya zama ba sirri, mussaman idan mace tana cikin wadata ta hanyar status take bayyana matsayin ta, hakan ya sake jefa Sa'adah cikin buri sosai kullum cikin kara son kayan garari ta ke .

Sannu a hankali aka fara bude groups daban daban ciki har da na tsofaffin dalibai, babbar mastalar group din su Sa'adah hade yake da mazan set dinsu tunda makaranta tasu hadaka ce da maza.

A haka Khalil ya samu numban ta, suke gaisawa lokaci zuwa lokaci, duk da baya nan yana Egpt yana karantar sociology.

Ta hanyar what's app ya mallaki hotunanta dana Jawad, idan ta yi status zai yi saving, ba a karan kanta ta ke tura masa ba.

Haka Kuma taron tsofaffin dalibai (reunion) sai ya zama ruwan dare, ko Ina taron tsofaffin dalibai ba 'kak'kautawa.

A wannan lokacin FGC Kano ta shirya nata tunda ga kan daliban farko har zuwa daliban da suka kammala a shekarar taron.

Taron ya kai taro, mafiya yawa daliban ma'aikatane ko manyan Yan kasuwa' har tsoffin Malaman duk sun halarta, dan haka Mk ma ya je, manyan mata masu aji, wadda suka yi wanka da ilimi da gogewar rayuwa duk sun kewaye harabar makaranta.

Sai farin ciki ake yi, mafiya yawa kuma cikin shiga ta alfarma suke, Sa'adah na cikin jerin da basu da makusa tun daga kan suturarta har zuwa fatar jikinta, kawai na'kasun ta 'daya ba a motar kanta ta je gurin ba, bata ji muzanci ba, sai da Mk yace mata zai tafi idan sun kammala ta wuce gidan Inna zai 'dauketa acan.

Kusan 'Yan set dinsu kowa da mota ta je har 'yanmatan cikinsu, Halima a motar Safina suka je, motar da Sa'adah taga Farida a ciki ta matu'kar tsaya mata a rai.

Hira ake ta yi, ana zuga wadda rayuwar su ta yi nasara ta hanyar kambaba lamarinsu, wasu kuma ana yi musu gadar zare, daga gefen su Sa'adatu, wasu matan ke hirar da ta ja hankalinsu, duk da seniors din sune sosai, 'daya cikin matan ta ce

"Ni da aure kuma mun yi hannun Riga, ba komai a cikinsa sai jidali, da hawan jini, baka da ikon yin komai na ra'din kanka, sai ka jira namiji, sannan baka da 'yanci ko kadan a aure".

'Dayar wadda da alamun ra'ayin su daya da wadda ta kammala bayani itama ta cafe da cewa "ai kuwa dai lubna da gaskiyar ki, dare, asuba, tsakar rana kowanne lokaci miji saka'dar ka yake yi tamkar jaka, amma da za ka bijiro da bu'katar ka, ba za'a maka ba, ko za'a maka din kuwa sai ka gama wulakanta".

Lubna tace da Asiya "Ashe kin gane karatun! dan haka tsakanin mu da namiji a hadu ayi ar'kallah kowa ya kama gabansa, yanzu kiga da ka ke cin gashin kanka cikin kankanin lokaci ka mallaki abubuwa masu daraja, wadda macen aure sai ta shekara fiye da ashirin ba ta mallake su ba".

Wata cikin su, tana bude Baki ta ce "Amma kuma matan aure sun muku zarra da mutunci da kuma 'kima, macen aure tana tsufa tana sake daraja, adalilin gatan da musulunci ya mata".

Dukkan su suka sa mata dariya, suna ganin wautarta, Lubna ta ce "kai ku rabu da Hajara kunsan tunda ta gama wannan makarantar ba ta sake shiga aji da nufin zurfafa ilimin ta ba, kenan kanta a duhu yake bata san komai ba, tana cikin jerin matan da maza suka rufe a gidaje suke gallaza musu, suka kuma hana su fahimtar cigaban da duniya ta samu"

Su Halima da suke jin tattaunawar suka kwashe da dariya suna fadin "ai yanzu duk wadda ta zauna namiji na mata mulkin kama karya mata ta rako duniya, a wannan karnin da ilimi shine komai yaushe zaka yarda a barka da jahilci, barin ma idan mijin naka mai ilimi ne? Da zarar muguntar namiji ta motsa sai dai ki ji ya amarce da mai ilimi, ko kiga yana jin kunyar ya saka ka a al'amuransa".

Jikin Sa'adah ya yi sanyi ganin itama cikin rukuninsu ita kadai ce mai sakandiren, haka akayi ta kutsiri tsoma, ba a gama da wannan maganar ba, a saketa a kamo wata, da za su tafi, a motar Safina suka dunguma har kofar gidansu suka kaita, a hanya suka yi hirar Humaira Suraj da a yanzu take aure a sokoto, dama can ne garinsu aiki ne kawai ya kawo mahaifin ta Kano.

Tun wannan lokacin Sa'adah ta fara canjawa, ita da kanta tasan ba abin da ta nema ta rasa illah motar kanta ba wai ta Mijin ta ba, amma zuciyar ta sai tsalle take mata tana ganin kamar ita ta wuce komai sai ta jira iznin miji kafin ta zartar, tana bu'katar ta zama yantacciyar mace mai yin komai babu 'dar balle fargaba.

Kullum a WhatsApp su Halima na sake kuranta kyakkawar siffarta, har suna cewa ba wadda zai ganta yace ita ta haifi Jawad, ko su da suke 'Yan mata basu fita komai ba.

Suna cikin wannan zaman na ba yabo, ba fallasa, Su Halima suka zo mata da kaya cike da katuwar leda, kana ganin ledar kasan tafiyayyace, sai da aka bude kaya, suka ga kayan Jawad ya kai set biyar, sai agogo na English gold, da kuma waya blackberry bold 4, da tarin alawowi da biscuit duk tsaraba ne inji Khalil abawa Jawad waya da agogo kuma nata ne.

A kidime Sa'adah ta ce "Na shiga uku Safina idan Malam ya gani fa, da me zan kare kaina? Gaskiya bazan karba ba tsoro nake ji.

Harara Suka galla mata, Halima tace "to kuma barinsa zaki yi ya gane daga inda suka fito, sai an kwana biyu kice Anty Sumayya ce ta aiko muku, waya kuma ki boye abarki sai ba ya gida, ko idan zaki je taron fitar kunya, na gaji da ganin ki da karamar android shiyasa na fa'da masa baki da wayar shiga taro".

Safina ta dora da cewa "Da yake ya damu da farin cikin ki kasa da awa ashirin da hudu da fa'da masa ya siyo, ya bayar akawo miki, gaskiya Gogel kin tafka asarar masoya, na tabbatar ko yanzu da kika zama uwa, Khalil zai aure ki a matsayinsa

na saurayi".

Suka hada baki wurin cewa "duk da ke 'din ma kinfi 'yanmata da yawa nagarta".

Tun lokacin hankalin Sa'adah yafi karkata kan wayar nan, kullum Mk ya fita za ta fito da wayar ta, ta yi komai, mussaman take da layi na daban a ciki, amma da layinta ta bude komai.

Tun Mk na tambayar ba'asin canjinta har ya gaji, yana ganin ya kyaleta ya huta shima, dan taga yana damuwa ne shiyasa take masa wulakanci, dan haka ya rungumi sabuwar rayuwar da ta bude musu, hatta a shimfida ta canja, ba wai gudunsa take yi ba, kawai zama take yi tamkar gunki, sai dai ya yi kidansa ya yi rawarsa shi ka'dai.

Haka nan abu kadan Jawad zai yi ta rufe shi da duka tamkar wadda take dukan babba.

Wadannan dabi'u suna matu'kar ciwa Mk tuwo a 'kwarya mussaman dukan yaron da ta tsira, ko abu ne ya hadasu sai ta huce akan 'dansa.

Rannan suna kwance sun gama mu'amalar da ba gishiri a cikinta balle Maggie, ran Mk a bace yake sosai, ya rasa mai zai mata kuma, ya riga ya kai gejin rarrashinta, ya gane gaba'daya kwakwalwar kifi ne da ita.

Ya yi gyaran murya ya ce "tsakanin ki da Allah ki fada min me kike nufi da ni, rokon ki nake yi, yanzu na tabbatar ba kya sona Sa'adatu".

Yana rufe baki ta ce "Kaine dai baka sona, komai zan yi a laifi na ke, 'dazu ba ka ga irin 'barnar da Jawad ya mini ba, dan na dake shi, ka hayayya'ko mini, salon kasa ya raina Ni".

"Amma tun ba yau ba ki ke wannan fizgewar, yaushe rabon da ki saurare ni cikin da'din rai, kullum da bacin rai kike yarda da ni, ko kin yarda kai tsaye to sai dai ki zame mini tamkar gawa, anya kuwa dama kina sona? anya kina jin tsoron hakki na akan ki, amma na yafe miki, na kuma dauki laifin ko menene ki yi hakuri ki yafe mini".

Ta tura baki ta ce"Tun yaushe nake ce maka zan dubo mahaifiyar Halima da ta yi hatsarin mota, duk yan ajin mu sun je banda ni".

Murya ba amo ya ce " Hana ki dubo uwar Halima yasa ki ka na'de kafar wandon yin min wula'kanci haka?"

Ta yi shiru ta kasa cewa komai saboda ta ga ya hassalo sosai, ya furzar da iskar bacin rai ya ce "Shikenan ko da wani laifin bayan wannan?"

Kamar shasha ta ce "yauwa ni fa yanzu nake son motar nan, na ga kai kuma kana nufin kamar sai anja lokaci, kawai ka dakatar da ginin ka siya mini".

Ya kalleta ido cikin ido ya ce "yin hakan shine sharadin samun zaman lafiya a tsakanin mu?"

Ta kasa amsawa tsawon lokaci, dan haka ya ce "Ba wadda zan miki ko 'daya, idan ya so zaman namu yafi haka muni".

Ta tashi ta fita tana 'kun'kuni, akan sai ta je, ta gaji da 'yadda ya maidata bagidajiya marar yanci, kansa ya sara yana jin ba'kin cikin ta na neman kassara shi.

Haka har kwanaki uku suna zaman doya da manja, Rannan cikin dare ta ji hannunsa na lalubarta, ta zabura kuwa ta bige hannun, tare da fadin "Bana so".

Bai saurare ta ba ya damko ta, ya fara kokarin gwada mata 'karfi saboda ya gaji da rarrashinta.

Ganin da gaske zai cimmata alhalin ta riga ta kudiri aniyar ba za ta saurare shi ba.

Dan haka ta fashe da kuka ta ce " raping dina za ka yi? na fahimci bani da mutunci a gurinka indai ba bu'katarka ce ta ciyoka ba, na daina ganin aibun 'yantattatun mata wadda suka juyawa aure baya, saboda sun san ba komai a cikinsa sai ba'kin ciki da takura da kuma 'bacin rai".

Jikin Mk ya mutu yana rike da ita, da ta lura, tashin hankalin da ke zane baro baro a fuskarsa ba zai bari ya ci gaba da rarrashinta a YAU kamar yadda ya Saba ba.

"Matan da suke zaman kansu, duk abin da suke so, aguje suke samu, amma matan aure sune agaba wurin samun hawan jini saboda tsabar bakin cikin da mazajensu suke 'kulla musu".

'Kololuwar tashin hankali Mk ya shiga, ji yayi jiri ya kwashe shi dan ma a zaune yake, ya tafi luu ya buge 'keyarsa da fuskar gado.

Da kyar ya dauki hannunsa ya ri'ke kansa da yake tsananin sarawa, da karfi ya dinga ambaton" innalillahi wa Inna ilaihir raji'un".

Ya dade yana nanata kalmar, har ya dan sami nutsuwa kadan, ya mike ya saka rigarsa da wando, ya ware murya sosai ya ce "Ni ki ka fadawa wannan maganar? Ashe kuwa har yau baki gane ni ba, zan nuna miki ba a bariki muke ba, ba kuma auren bariki na ke yi ba, ki ri'ke dukkan abin da ki ke tun'kaho da shi bana so, ki ji'ka ki shanye abin ki, amma ki sani yau da Gobe zasu biyar da ke indai kina sha'kar numfashi".

A daren ya dauke dukkan abin da yake nasa ne a cikin dakin Sa'adah, sai Agogon hannunsa da yake cikin wadirof dinta ya manta bai dauka ba. har ya kwanta ya tuna bai dauko tawul dinsa ba, ya koma ya dauko, kafin ya fita ya tsaya ya kalleta tana zaune duk jikinta ya saki da alamun ba tasan girman munin maganar data furta ba, sai bayan ta fada.

A kausashe ya ce "Na tsane ki, na tsani na bude ido na ganki, ba dai kin fi sha'awar rayuwar 'kazanta akan ta sunnar Ma'aiki ba? kin raina duk kokari na, kin raina ni'imar da kike ciki, Na rantse miki! ba dan kunyar Baffa ba, da a yau na mayar da ke 'yantacciyar macen da kike fata, ni kaina NADAMAR auren ki na ke yi, amma na gode Allah da nake ganin sakamakon son zuciyata a duniyar nan, ba sai naje lahiraa ba,'kiri 'kiri na nunawa mai sona da gaskiya HALIN YAU, na butulci".

Ya juya ya fita ya barta cikin rashin sukuni mai yawa.

Tun daga ranar ya bala'in dauke mata wuta, idan ya fita tun safe, sai dare ya fara turawa zai dawo, sannan matu'kar yana gida to kuwa kofar dakinsa a gar'kame ta ke hatta Jawad ba kasafai yake ganinsa ba, kullum cikin tambayar Sa'adah Ina Malam ya tafi?".

Wannan ne karon farko da ya yi fishi ba waiwaye, hatta fuskarta baya son gani a yanzu, sabanin da da ganinta shine cikon farin cikinsa, har yau fama yake da ciwon da bakaken maganganun suka sababa masa a zuciya yake yi.

Ana haka mijin Sumayyah ya yo waya akan bata da lafiya sosai, haihuwa ne ta zo mata da tangar'da anmata C's an fito da yaro amma kuma bata da lafiya.

A ranar Baffa ya sanar da Mk, akan gobe za su yi asubanci zuwa Gombe shi da Inna, idan ba damuwa ko zasu tafi da Iyah ta gano jikin yar'uwarta.

Bai yi nauyin baki ko kunya ba, ya ce "Zan zo na kai ku Baffah amma ita daga baya zata je".

Godiya sosai Baffa ya masa tare da fadin "ko bata je bama ai kai kaje , ka wakilceta".

Haka akayi tafiyar Sa'adah ko labari bata ji ba, a ranar Baffa suka juyo da Mk, da kuma Hajiyar Bichi da ke ta bisu, suka bar Inna dan ta kula da Sumayya, kafin Umma fanshekara ta je sai Innan ta dawo.

Ganin da innah ta yi har washagari Iyah bata 'kira ta yi jajen mai jiki ba, sai hankalin Inna ya tashi tana tunanin ko itama ba ta da lafiya ne?

Tana Shirin 'kiranta, sai ta 'kira suka gaisa, mamaki ya sake kama Inna ganin ba alamun ta samu labarin halin da 'yar'uwarta take ciki, dan haka sai tace "mijinki bai fada miki Ina Gombe ba?"

"Wallahi bai fada mini ba, wani abin ne ya faru?" ta tambaya a kidime.

A sanyaye Inna ta ce "yayar taki aka yiwa tiyata ga yaro nan lafiya lau, sai itace bata Jin dadi, amma dai da sauki".

Cikin muryar kuka ta ce" shine ba ki fada mini ba Inna?".

"Mijinki ne fa ya kawo mu, jiyan suka juyo da Baffanku, Kinga ai bana yi zaton ba ki ji ba, duk yadda akayi ba zaman lafiya kuke yi ba Iyah, tunda da bakinsa yace baza ki zo ba, sai muka dauka ko kema ba Kya jin dadi ne ya rufe mana, har da Hajiyar Bichi muka zo, duk jiyan suka juyo".

Kuka kawai Sa'adah ta ke yi, irin kuka na rashin madafa, sosai kukan ya ta'ba Inna, tashin hankalin ta ya 'karu ga na Sumayya da ta ke kwance bata san wadda ke kanta ba, ga na Iyah da ba tasan ha'ki'ka in matsalar ta ba.

A sukwane ta kira Baffa tace lalle akwai matsala tsakanin Iyah da Mijinta, cikin rashin daukan maganar da muhimmanci ya ce "Mijin ta bai kawo 'kararta ba, ita ba ta ce ga laifinsa ba, sai kawai naje na hau bincinkarsu, tunda sun iya 'boye sirrinsu, sai a bisu da addu'ar Allah ya daidaita su".

"Ka shiga maganar nan, da alamun fa abin babba ne, hatta zuwan nan da ya yi Gombe bata sani ba, kar a zuba musu ido fa".

"To" ya ce mata a gajarce ya katse wayarsa! yana cewa lamarin mata yana da ban mamaki, kawai dan kina so a tursashi ya barta taje inda baya so taje sai kice naje na shiga tsakanin su, duk tsawon lokacin da suke tare waya ya san yadda suke zaune?

Haka kwanaki suka yi ta shudewa a cikin Wannan hali tsakanin Mk da Sa'adah, kullum 'kara nesanta kansa yake da ita, zuwa yanzu da suka cika sati biyu cikin wannan halin, wadda ko a mafarki bata yi zaton zai iya shareta har haka ba, domin tun ranar da ta yi wannan katobarar bai sake bin takanta ba, asalima ta lura bai son ganinta ne har zuciyar sa, tana ganin idan ya dawo a gaggauce yake shigewa dakinsa ya rufe kofa, hakanan idan zai fita a hanzarce ya ke ficewa, duk yadda bai son ya ji kukan Jawad amma a yanzu duk kukan da zai masa ba ya tsayawa ya bi ta kansa.

Ta shiga damuwa da tsoro irin wadda bata taba shiga ba, tsoron ta 'daya idan iyayenta suka ji mai ya jawo wannan tashin hankalin, wanne irin kallo zasu yi mata,?

Ta 'kudiri aniyar yau zata bashi, ha'kuri ta kuma nemi ya barta taje ta gaida Aunty Sumayya.

Haka akayi, taran dare ta yi wanka, ta shirya cikin kwalliya ta burgewa, tana jin dirin motarsa da kiciniyar bude gate, ta fita a hanzarce ta shiga kicin mai ma'kwabta ka da 'dakinsa ta tsaya.

Ai kuwa ya shigo da sauri, ganinsa rungume da kayan wankinsa da ya kai wanki, jikinta ya sake yin sanyi, komai zata yi masa, idan zai kai wanki zai shiga har 'dakinta ya hada kayanta akan nasa ya kai musu wankin amma banda Wannan karon.

Kafin ta yi yunkurin shiga dakin nasa sai ta ga ya fito ya fita da alamun ya yi mantuwane, dan haka sai ta yi wuf ta shige 'dakin, yana shigowa kuwa ya rufe 'dakin bayan mukulli har da sakata ya sanya.

Yana shigowa ya ganta lafe jikin wadirof, ga mamakinsa sai yaji kwalliyar da ta yi, bai ji komai na burgewa akanta ba, hakanan kamshin ta da ya cika masa hanci bai yi tasiri a jikinsa ba, kyakkawar fuskarta da ke sanya shi nisha'di, a yau ba'kanta masa rai ta yi, hakanan surarta da ke jefa shi cikin shauki, a yau takaici ya ji ya maye gurbi.

'Bacin ransa ya dawo sabo fil tamkar yanzu take gasa masa maganganun da suka zame masa tamkar 'digar dalma a zuciya, suka yi awon gaba da kaso mai yawa na matsananciyar soyayyar da yake mata.

Baice mata komai ba, ya shiga rage kayan jikinsa, ya shige wanka, tana tsaye ya fito ya shirya, ya tada sallar shafa'i da wutiri.

Sai da ya idar ya zauna bakin gado ya kalleta, ya ga duk ta takura, ta susuce, ta lalace, idonta ya fada alamun dai tare suke 'dan'danar 'bacin rai.

Kafin ya yi magana ta rigashi! Ta tsugunna ta ri'ke gadon ta ce "Dan Allah Malam ka yi ha'kuri, ban taba jin nadama irin wadda nake ciki ba".

"Ba ki mini komai ba, abin da ke zuciyarki ki ka amayar, sai dai ina so ki sani wallahi ba ki fara nadama ba, ina tabbatar miki za ki shiga NADAMAR da ta zarce wadda kike ciki, da kinsan yadda na tsani ganin ki da hakan ka'dai ya isa ya saki nadama, da kinsan yadda kika wanke kanki a zuciyata da kin gane asarar da kika yi ba ka'dan bace".

Kuka ya goce mata, ta rarrafo da nufin ri'ke shi, ya zabura ya mike tsaye cikin bacin rai ya ce "idan kika yi kuskuren sa hannun ki a jikina, na rantse miki sai na miki abin da za ki gamsu ba ki da sauran 'kima a gurina. domin duka zan miki irin yadda ake na'dawa 'yantattatun matan bariki idan angama cin moriyar su".

Kukan ya tsaya mata! da gaske ta yi kuskure, irin kuskuren da ake yi sau daya amma sai an nemi hanyoyi gyara dari bai gyaru yadda ake so ba. daga jiyo magana a bakin shedanun mata ta ara ta yafa, har ta zo ta fa'dawa mijin aurenta wadda da gaske samun irinsa zai yi wahala.

Ta zauna 'dabas tsakanin gado da wadirof ta dinga kuka, mai cin rai, na tsantsar nadama.

Daga inda yake ya ce "Ta shi ki bar mini 'daki ban bukatar ki a cikinsa".

Ta kasa koda kwakwkwaran motsi. tace "ka yi hakuri ba dan ni ba, ka dubi girman Allah ka yi hakuri".

Jikinsa ya yi sanyi yace "Na ji, amma dai tashi ki fita, ina bukatar ka'daici ne, duk sadda nake da bu'katar ki a dakin I will let you know".

"To ka daina rufe 'dakin, na yarda duk sadda na zo ka kore ni, amma ka daina rufewa".

Ya zuba mata ido yana jin takaicinta na sake kama shi, amma da yake so yake ta fita ya shaki iska marar takura sai yace mata to a takaice.

Ganin ya amsa mata sai ta tashi ta bude 'kofar ta fita tana fadin " ka yi hakuri, ka yi barci mai cike da walwala".

Ya bita ya rufe kofar, ya dawo ya karanto adduar barci ya kwanta.

Washagari da sassafe ta shirya masa abincin karyawa ta zauna zaman jiran ya bu'de 'kofar, ai kuwa yana budewa ya ganta da tiren abinci, a bakin kofar dakin, yasa kai zai wuce ta ce, " Ina kwana?"

Ya amsa a gajarce, "ga abinci na gama". ya girgiza kai ya ce

"ki daina wahalar da kanki wurin yin abinci saboda Ni, na riga da na 'yanta ki daga dukkan yi mini hidima kowacce iri ce".

"Cikin rawar murya ta ce "kace fa ka yi hakuri?"

"Da ban yi hakuri ba, da baki ganni akan 'kafufuna ba, da ina can akan gadon asibiti saboda ba'kin cikin ki, da ban yi ha'kuri ba, da ban tsaya ina miki magana ba".

Ta goge hawaye ta ce "ka kara hakuri dan Allah nasan na yi ba dai dai ba".

Ya girgiza kai ba tare da ya ce komai ba, ya fara tafiya, da azama tace " Malam! Umman fanshekara gobe zata tafi Gombe, dan Allah ka bar ni mu tafi tare, ni sai na dawo ko jibi ne".

Ya juyo a zabure tamkar wadda ta fadi mugun abu ya nunata da yatsa ya ce" dama nasan duk wannan saukar da kan da kika yi, kina da bu'kata ne, ba kya tashi mutunta ni, ko kwantar mini da kai sai kin ganni da kudi, ko kina son na barki kije wani guri".

Cikin kuka sosai ta ce "Haka ka dauke Ni?"

"Kin wuce hakama ke kam, saboda ke ciki ce mai manta kyautar jiya, mai manta alheri, da kina da hankali, da baki cemin za ki tafi yawo Gombe ba, kawai tafiya za ki yi kanki tsaye".

Ta zuba masa ido ta ce "dubo Anty Sumayya ne yawo?"

A kausashe ya ce "ke kika san Sumayya, ni mai na hada da ita! ko dole nace?"

Tashin hankali 'baro 'baro ya bayyana a jikinta gaba'daya, lalle da gaske Mk ya shiryawa tashin hankali iri iri, wai Anty Sumayya ce yake fadin sunan ta gatsal, duk da ya girmeta da shekaru biyu amma Anty yake cemata, sannan kuma har yana cewa mai ya ha'da da ita?.

Ta kalleshi baki na rawa ta ce "Dan Allah Malam ka yafe mini, mu zauna lafiya ba zan iya kar'ban wannan tashin hankalin daga gareka ba, na rantse maka ba zan kuma maka laifi ba, zaman lafiya zamu yi, fiye da yadda ka ke so".

Ya yi murmushi ya ce "na la'anci zaman lafiyar da ki ke so mu yi Sa'ade, zuciyarki bata da alheri, kwakwalwarki ba ta da tsinkaye, harshenki yafi na maciji dafi, ba sauran zaman lafiya tsakanin mu, idan har kika zauna lafiya da ni ban yafe miki ba".

"Zuwa Gombe, ko yanzu kina iya tafiya, sai dai idan ina da hakki akan ki, ba za ki ga alheri a yayin tafiyar da dawowar ba in sha Allah".

Ya ja dogon tsaki yana fadin shashar yarinya da bata san mutunci da kyautatawa ba".

Ya sake jan dogon tsaki ya fice, ya barta tana kukan ita yake yi wa baki da mugun fata?.

SURAYYA DAHIRU

✍✍

18/04

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

•.•

SADAUKAWA GA

SADIK ABUBAKAR.

75_77

Hannu ta 'dora aka ta dinga kuka,tana fadin "Hasbunallahi wa ni'imal wakil".

Har akayi azahar tana zaune inda take, ba abin da tasa a bakinta, duk da ga tiren abincin nan a gabanta, ba idonta kawai ba, hatta fuskar ta kumbura ta aune sosai saboda kuka, ta fada ta yi zuru zuru, ta dinga lissafin adadin rikicinsu, aduk fa'dan da zasu yi ita take janyowa, ta sake tuno adadin alherinsa hatta iyayenta bai huta da yi musu alheri ba, tun kafin ma ya aureta.

Ta sake tuna duk laifin da take ganin ya mata cikin biyu ne, ko dai kawai zuciyarta ta raya mata ya Mata kaza a matsayin musgunawa, sai wadda 'kawayenta zasu ce ya yi a makaranta, ko ya mayar da ita Bagidajiya, alhalin ita tasan yadda yake girmamata yake girmama dukkan ra'ayin ta, amma sai tunanin ta ya bace ta biye musu.

Ta tuna yadda yake tsananin son su zauna lafiya, su rayu cikin walwala da mutuntata juna, sai gashi yau da bakinsa yana la'antar zaman lafiya, yana fa'din bai yafe mata ba, idan ta zauna lafiya da shi.

Idan ta yi wadannan tunaninka sai ta rushe da kuka, tana yi tana cewa "wallahi da gaske na gane gaskiya".

'Kiran sallah ya sa ta tashi, ta yi alwallah ta yi sallah, ruwan Lipton kawai ta sha.

Tana zaune har dare! sallah ke tayar da ita, gefe kuma tana tunanin Jawad, da ya nan da ya debe mata kewa, yau kwanansa uku a gidan Samira, tunda suna hutu.

Akan idonta ya dawo, kusan a guje ta sha gabansa tana kuka, tana cewa "Dan Allah ka yi ha'kuri, ya girgiza da ganin yadda fuskarta ta koma a yini 'daya kacal, ta so bashi tausayi amma da ya tuna haka take idan tana son abu, da zarar ta samu muradinta kuma za ta sake kirkiro wata matsalar.

Ya dubeta ya ce "Ba ki fara kuka ba, sai burina na raba Safina da gararanba a titi ya cika"

Ta kalleshi a razane, bai damu ba ya ce "babban burina ta zame mini amarya, na tabbatar zan sami nutsuwa da ita, ki adana hawayenki zuwa wannan lokacin".

A gurin ta yi fa'duwar yan bori tana kuka tamkar yarinya har da tirza 'kafa irin yadda Jawad ya ke yi.

tsaki ya mata yana fadin "Ba kuka ba ko bubburwa za ki yi bai dame ni ba". Ya shige ya rufe kofarsa.

Washagari daga sallar asuba bai dawo gidan ba, hankalin ta ya tashi ba ka'dan ba, ta kalli agogo ta ga har karfe uku ta tabbatar yana shago tunda yau lahadi.

Abin duniya ya taru, ya mata yawa, idan ta tuna kalamunsa wai son Safina ya ke yi, sai taji tamkar ta shide, ta tuno yanayin halittar su daya, ko a makaranta ana yawan fadin dirin jikin su shigen iri daya ne, da gaske za ta iya daukan hankalinsa kenan?

Hawaye ya sake goce mata, karon farko da ta fara jin tsanar Safina a ranta, tana raya ba zata kuma ganin dariyarta ba, bare ta ga fuskar zama a gidanta

Maganar ta mata ciwo fiye da zaton mai zato.

Tana zaune ta ji wayarta ta hau kuwwa, da hanzari ta dauka, ganin Hajiyar Bichi ce, tun daga muryarta Hajiyar ta gane ba ta cikin sukuni.

"A kwance kike ne Sa'a? na ji muryarki ba walwala".

Duk yadda ta ke danne kukan sai da ya subuce mata, hankalin Hajiya ya tashi ta dinga tambayar ta dalili amma ta kasa yin magana, sai kukan kawai.

Dai dai lokacin kuma Mk na zaune dakin Hajiya yana cin alalan gwangwani da ya ji lafiyayyen manja da yaji.

Ta kashe wayarta ta zubawa Mk ido, tana jin takaicinsa na kamata, a kausashe tace "mai ya hada ka da Sa'a?"

A nutse ya ajiye cokalin hannunsa, ya kalleta yace "Me tace na yi mata?"

Ranta ya sake baci ta ce " Na tambaye ka, ka amsa mini da tambaya! Na lura da kai, ka mayar da ni shashar uwa, duk sadda ka sami matsala da matarka sai ka tattaro ka dawo da kwanon abincinka wurina saboda ka zubar mini da mutunci a idon yarinya, amma zan gyara".

Ya yi sukuri dan yasan gaskiya ta fada, yana yin hakan. A raunane yace "Hajiya ni fa ba abin da ya ha'damu, kinsan kuma yadda nake son 'dan'danon girkinki, dan na yi aure shikenan sai bazan ci ba?".

Ido kawai ta kafe shi da shi, tun yana murmushi har ya fara shafa 'keyarsa, yana jin kallon na shiga jikinsa, yana tuna lokutan baya na 'kuruciya, idan Hajiya ta musu irin wannan kallon take suke shiga hankalin su, saboda yadda ya 'kunshi abubuwa da yawa ba sai ta yi magana ba .

"Tashi ka kaini gidan, na ji ba'asin kukan da take ta faman yi, wa ya sani ma ko dukan ta ka yi".

"Haba Hajiya! Kinsan dai ban samu tarbiyar dukan mace ba, ita kukan banza ne da ita, duk sadda zuciyarta ta raya mata, kuka take yi, da dalili ko babu".

"Mahaukaciya ce ai".

Jin amsar Hajiya yasa shi yin shiru ya lura ranta a bace yake da shi, ya mi'ke ya dauki waya da mukallin motarsa da ke gefensa ya kalleta ya ce "Allah ya huci zuciyar ki Hajiya, ina jiran ki a mota".

Kozai kozai suka tarar da ita, cikin kwanaki uku kacal gaba'daya ta lalace, karon farko da Hajiya ta ganta kaca kaca, kullum fes zata tarar da ita, haka muhallinta.

Hajiya ta ka'du kwarai da yadda ta ganta, da sauri ta isa kusa da ita, ta ri'ke ta, ita kuma ganin ta sami mai rarrashinta yasa ta kwantar da kanta a jikin Hajiyan ta dinga rera kukan tamkar mai wa'ka.

Mamaki ya kama Mk! ya coge a bakin kofa yana kallon kukan shagwaba da iskanci a wurin Sa'adah, ta masa laifi, ta kai 'kararsa.

Ya na'de hannunsa a 'kirjinsa, yana sauraren 'korafin da ta ke rattabawa Hajiya! "kuskure na masa cikin rashin sani, na yarda na yi laifi, na bashi hakuri tamkar harsena zai tsinke ya ki ha'kura, yanzu kuma sai ya fara soyayya da kawata dan ya ci mini fuska ya kuma janyo mini raini"

Cikin kuka sosai take bayanin.

Hajiya ta rasa mai za tace! ta fahimci Sa'a ba 'karamin kishi ne da ita ba, kishin nata kuma ya zarce ka'ida, amma da ta lura har da 'kuruciya a kanta, sannan dabi'a ce ta matan YAU sawa miji ido da kuma 'dorawa kai zazzafan kishi tamkar wadda aka musu busharar an janye ayar da ta bawa maza damar auren abin da ya musu da'di, daga mata biyu, uku ko hudu.

A hankali ta ce "akan yana da budurwa ki ka maida kanki haka, Ina ruwan ki? ki daina sa ido ko bibiyarsa, ba ruwan ki da abin da yake yi matu'kar bai tauye miki hakkin ki ba, idan kuma ya na 'ketare dokokin shari'a wannan kuma tsakaninsa da ubangijinsa ne".

Kan Sa'adah na 'kasa tana ta kuka, kukan kuma shi yake tayar da hankalin Hajiya.

"Wai wannan kukan na menene haka Sa'a? Kin ga kuwa yadda fuskar ki duk ta aune?"

Murya a dakushe ta amsa da cewa "ki ce ya daina mini fishi, sannan idan na dafa abincin ya dinga ci".

Kafin Hajiya ta yi magana, Mk ya yi fit yace "Ni yaro ne da za ki dinga control 'dina? Na 'ki na ci abincin na ki"

"Kin ji da kunnen ki ban isa da shi ba, dan haka ki share hawayen ki, komai da ki kasan hak'kinsa ne ki masa kar ki gaji, ubangiji ne yace ki masa biyayya, idan ya zalunce ki, ba zai barshi ba".

Ta mike tana gyara zaman Hijabin ta, ta sake cewa "Ki yi hakuri, kar ki biye masa, kinsan idan tururuwa ta so lalacewa fuffuka take yi, Allah ya miki albarka kin ji! Ki tashi ki yi wanka ki ji da'din jikin ki".

Ta juya ta fita ba tare da tabi ta kan Mk ba, da ya bita a baya yana cewa "Hajiya! ko kula shi bata yi ba ta yi ba, a waje juyin duniya akan ta shiga motarsa ya kaita, kamar yadda ya kawota, ta 'ki bude baki ta masa magana bare ta amince, haka ya dinga bin ta har titi, ta tari adaidaita sahu tana shiga, shima ya yi wuf ya fa'da, har suka isa Na'ibawa ba abin da ya ke yi sai tunanin mai zai yiwa Sa'adah ya huce.

Ba zai iya tuna lokacin da Hajiya ta masa irin wannan fishin ba.

Suna isa ta sau'ko ta wuce gida, ya tsaya ya biya kudin, sannan ya bita cikin gidan

Yana isa ya tarar da ita zaune a tsakar gidan, bata shiga dakinta ba tabbacin ba zata saurare shi ba.

Ya tsugunna, ya dinga bata ha'kuri, ya dade yana fama, kafin ta ce "Nunawa ka yi fa ban isa na zartar da abu a kanka ba, ganin na isa ne yasa ta ce na yi maka magana, kai kuma ka bata amsa da ta ke nufin ban isa ba, dan haka duk ranar da Sa'a ta fara ganina ba 'kima kar ka ga laifin ta".

Ya yi shiru yana ayyana wai su mata haka suke ne? manya da yaransu sun iya kacaccala magana, su juya ta, komin gaskiyar ka sai sun nuna su ka zalinta ko ka ketawa haddi?

Kan dole ya ce "Ki yi hakuri Hajiya Dan Allah! sannan ina tabbatar miki da ikon Allah ba macen da zan zauna da ita alhalin bata ganin girman ki".

"Fatana ki huce, ki yafe mini bacin ran da na sanya ki".

Fuska ba walwala ta ce "idan har kana so na huce, hankalina ya kwanta, to ka zauna lafiya da matarka, na lura itace bata da gaskiya, amma abin da zaka lura ko a lahira wani na cin albarkacin wani, ka manta komai ta yi maka, ka mata afuwa, ba hankalinku daya ba".

Ya nisa ya ce "Allah Hajiya ban so ki ka shigar mata ba, so nake kawai ta

banbance tsakanin zaman lafiya da kuma zaman tashin hankali, ta fitine ni wallahi".

"Kaine Babba hakuri za ka yi! sonka take yi, shiyasa ta ke kishin ka, tunda ka fahimci matsalolinta sai ka kiyaye abin da zai tunzura ta, har hankali ya shigeta, wata rana ko ance ta yi wani abin ba zata yi ba".

"Shikenan na ha'kura saboda ke, amma wallahi ki dinga mata fa'da Hajiya! tana sake yin mini yadda ta ga dama ne saboda kina bin bayanta, kwalbar ha'kuri na ta kusa fashewa akan lamarinta".

"Kai kuma haka za ka yi? mahaifinka mai ha'kuri ne akan sabgogin mata, kafin muga fishinsa mukan

'dade, duk yadda zan bata masa rai kuwa da zarar nace yi hakuri to maganar ta kare".

Shiru ya yi! A ransa kuma sai cewa yake yi ba za ki gane mai yarinyar nan take mini ba ne, inda a iya kishin ne ai da sauki.

A fili kuma ya ce "shikenan Hajiya ta ci albarkacin ki magana ta kwanta".

" So nake ta mutu murus, ba wai ta kwanta ba".

Ya yi dairya ya ce "ki mata fa'da, idan ta kwantar da hankalinta, magana ta wuce, amma idan tana tayar min da hankali ai dole laifin baya ya dinga tasowa, yana zama sabo".

"Zan ja kunnenta sosai, amma ka ri'ke a ranka na kashe wannan matsalar, kaima ka kashe ta a ranka, sannan kar ka kuma zuwa cin abinci gurina idan kun yi fa'da, bana so! bana so".

Ya amsa da "to sannan ya mata sallama ya tafi, yau har zaure ta taka shi tana cewa "ka zarce gida kai tsaye ka nuna mata na isa da kai."

Ya amsa da fadin "To In sha Allah".

Madallah da uwar miji irin Hajiyar Bichi, masu maida surukansu tamkar ya'yan su, suke musu adalci irin wadda ko wacce uwa take so ayiwa 'yarta.

Gidan kuwa ya zarce, ya sameta a inda suka barta har lokacin kuma kukan ta ke yi, sai dai alamun sun nuna ta yi wankan duk da ba kwalliya ta yi ba.

Ya tsaya a bakin 'kofar falon ya zuba mata ido yana jin takaicinta na kama shi sosai.

A kausashe ya ce "Rashin mutuncin ki kullum 'kara tunbatsa take yi, ki mini cin mutunci, ki raina arzikina ki nuna mini bariki ya fi aurena, sannan ki zame ki kai 'karata, saboda kin koyi munafunci?"

Ta kasa magana sai kukanta da ya 'karu.

Shi kuwa ya zarce da fadin "Tunda kin zama macijiya ki sare ni, ki koma ki baibaye uwata da kalolin alherinki na makirci da tuggu, to Ina tabbatar miki nima daga yanzu kome kika mini sai na fadawa Baffa, su dinga raba 'bacin ran tare da Hajiya".

Ya ja tsaki ya shige dakinsa.

Ta jima tana zaune cikin rashin sanin abin yi, sannan ta tashi ta bi bayansa, cikin sa'a bai rufe 'dakin ba, yana zaune a bakin gado iskar fanka na kada shi.

Akan gadon ta zauna kafadunsu na gogaiya da juna, ta ri'ko hannunsa tare da jingina kanta a kafadarsa murya ba amo tace"Am sorry Malam! Wallahi zuciyata ba za ta iya 'daukan fishinka irin haka ba, ka yafe mini' ka manta dan girman Allah".

Ta karasa cikin kuka na sosai.

"A hankali yace "Na ha'kura, amma mantawa sai a hankali, idan kin kiyaye, kin kuma rufe 'kofofin da zan dinga tunawa din! ki sani ba dan Hajiya ba, da ban san ranar da zan miki afuwa ba, saboda kin riga kin shayar da ni mamaki da ba'kin ciki mai yawa".

"Na yarda na yi ba dai dai ba, dan Allah kar ka yanke mini kauna, ka sake bani dama".

Ita da kanta ta yi dalilin da sai da suka hadu a lokacin, tun Mk na basarwa, har ya kasa cigaba da jarumtar ya ru'ko ta suka sami nutsuwa, haka nan sai da haduwar ta yi awon gaba da kaso hamsin na bacin ran da ke zuciyarsa.

Tun a wannan rikicin Sa'adah ta fahimci ta rasa damammaki a gurin Mk, ya matu'kar rage rawar jiki akanta, ya daina tattauna halin da yake ciki da ita, haka nan baya zama ya shiririce mata da hirarrki kamar da, za su yi hirar amma a gajarce, sannan mafi yawan hirar sai dai ita ta kawo.

Haka suke wannan zama har Jawad ya dawo daga gidan Samira, so take ya barta ta je Gombe amma tsoron tambayar ta ke yi, har mamakin kanta take yi, yadda take tsoron su yi rikici yanzu.

Washagari alhamis da safe ta tura Jawad ya tambayo musu za su je su gaida Maman Gombe da ganin Baby boy, tunda sai satin sama hutun su zai 'kare.

Jawad bai jima da zuwa ba, ta ji Mk na 'kwalla mata 'kira, gabanta ya fadi sosai da hanzari ta shiga dakin tana cewa" Na'am".

Kallonta kawai ya yi, ta gane ba zai barta ba, ta tsugunna tana sauraronsa.

Sa'a an 'kara kwas na respect 😁

"Kin aiko Jawad za ku Gombe, inace dama ban hana ki ba tun farko?"

Ta yi sukuri tana jin fargaba na kamata, da 'kyar ta bude baki ta ce " ai kace ba zan ga alheri ba".

"To yanzu na ce ki ga alherin! Aje lafiya, adawo lafiya shikenan?"

Ta kalle shi ta ga yana daddana waya hankali kwance.

"To kwana nawa zamu yi?"

"Sai kin gaji da zama sannan ki dawo".

Ya fada hankalinsa na kan wayarsa.

Hawaye ya cika idonta tana jin tamkar ta sume.

Murya na rawa ta ce "Malam yanzu fa ban yi maka komai ba, Allah shine shaidata, na yadda na ke gudun na 'bata maka, amma kai kwata kwata ka yanke mini kauna, ka ki ka yafe mini, kana zaune da ni akan tilas.."

Kuka ya kwace mata sosai, cikin ko in kula ya ce "kin so yin kuka ne, kince za ki je Gombe, nace adawo lafiya, har da abin arzikin ki yi iya adadin kwanakin da kike so, shikenan kuma sai ki bare mini baki, to fada mini me kike so na ce miki?".

Ta dago da manyan idanuwanta da suka yi ja ta zuba masa akan fuskar sa, tsawon lokaci idanuwansu a sarke, chemistry na aiki akansu, a sanyaye Mk ya janye fuskar sa gefe daya, yana kokawa da abin da ya taso masa.

A hankali ta furta "so nake ka ce kwana kaza za ku yi".

"To sati hudu ya yi miki?"

Da mamaki ta kalle shi ta ce"ai zuwa wannan lokacin su Jawad sun '

dade da komawa school".

Kai tsaye ya ce "Ba da shi za ki tafi ba ai, ke 'kadai za ki yi tafiyar ki, ki je ki yi abin da ki ka ga dama".

Jikinta ya yi sanyi ta tabbatar ba barinta zai yi ba, sai kawai ta mike ta ce "Na gode".

Ta fita zuwa kicin, ta hau aikin abincin rana, ta na yi tana kuka, bata ta'ba sanin Mk na da ri'ko ba sai a wannan karon.

Haka tana ji tana gani har Inna ta dawo ba ta je ta gano su ba.

Ko zuwa ta yiwa gidansu dan ta yiwa Inna barka da dawowa, da 'kyar ya barta, shima sai da la'asr lis da zai tafi shago ya tafi da ita, kafin su Isa magariba ta yi, amma dan son ya musguna mata bata fi awa daya ba ya mata waya shi zai tafi, idan kuma bata gama ba, ta taho idan ta kammala, alhalin yana kaiwa fiye da goman dare.

Haka ta fito ta bishi yana ta cin magani, har suka iso ko uffan ba suce ba, wannan sabuwar rayuwar ta yiwa Sa'adah tsauri matu'ka da gaske mussaman da bata saba ba, ya riga ya sabar mata da wasa da raha, uwa uba kullum shine cikin rarrashinta da son ganin murmushi a fuskarta, shiyasa yanzu sauyin ya zo mata da tashin hankali.

Hatta Inna sai da ta yi 'kwalla da taga irin ramar da ta yi, sai dai fa'da sosai ta mata tana fadin tasan itace duk ta jànyowa kanta komai take ciki.

Cikin kuka ta ce "Ni damuwata 'daya yadda Anty zata ga rashin kirkin banje na gaishe ta ba".

Da sauri Inna ta ce "ba zata ga laifinki ba ai tasan aure ki ke yi, ba zaman kanki ba, kar ki damu ta warware sosai, Ba ki ga Anis ba ya yi 'bul'bul da shi, ki bi mijinki a hankali kin ji".

Haka suke rayuwar yau fari gobe tsumma, shi kansa Mk so yake ya manta komai amma maganganunta sun dasa masa wani irin ciwo a zuciyarsa, sun yi karfin da suka sababa masa hawan jinin da yake shan magani kullu yaumin, idan ya tuna sadda ta ke fada masa matan bariki na da daraja fiye da matan aure sai ya ji tamkar ya sume.

Ranan asabar da safe suna karyawa da wainar shinkafa da miyar ganye da ta ji tantakwashi, sammako ta yi ta shirya masa tare da kunun farar shinkafa da danyar gyada, tasan yana son wadannan abincin, sai da ta yi wanka ta ci kwalliya sosai sannan ta gabatar musu.

Suka kammala ta kwashe komai, ta zauna kusa da shi sosai, a ladabce ta ce "Malam ina son na je asibiti".

Ya kalleta ya ce,"me za ki yi?

Ta sunkuyar da kanta 'kasa ta ce " abin nan zan cire ".

Ya zuba mata ido yana jin tausayinta na neman kama shi, yasan so take ta yi abin da zai sa shi farin ciki, dan haka sai ya sassauta ya ce "Inace tun a Abuja na ce ki bari mu gani tukun, ko abin da nake fata zai kasance, idan ki ka haihu kun zama ku uku lissafi zai canja".

Ta dago idonta cike taf da hawaye ta kalle shi " Na dauka ka fasa tafiyar da ni, tunda yanzu ka canja mini akan komai".

Ta fa'da hawaye yana zubo mata. take ya ji sonta ya dawo daga suman da ya yi, Ashe son ba raguwa ya yi ba, comma ya shiga.

Ya bude mata dukkan hannuwansa biyu, a yau bata tsaya jan aji ba, da sauri ta fada masa, yasa dukkan hannuwansa ya rungumeta tsantsan ita kuma tana kuka kasa kasa.

Baice komai ba, illah shafar bayanta yana jin sau'kin 'daurin da kirjinsa ya yi akanta.

Tun daga ranar ya canja, ya daina 'daure fuska, sannan ya bu'de mata kofar nisha'di a tsakanin su, sab'anin satikan da suka shude da ya rufe ta rif.

Saukowar Mk ya sa ta fara murmurewa, tashin hankalin da ta shiga yasa ta manta da wayar ta Bb, sai yanzu da ta sami nutsuwa take fitowa da ita, idan ya fita.

* Tsautsayi*

Ranar da ta zama 'bakar Rana ga rayuwar ma'auratan guda biyu, wadda tarihin rayuwar su ba zai cika ba, sai an sako ranar.

Asabar ce cikin watan Augusta da safe bayan sun kammala karyawa cikin walwala, ya shirya ya mata sallama, zai je ta'aziya Baban Abokinsu ya rasu daga nan zai zarce gidan su ba zai dawo ba sai yamma, ta masa addu'ar dawowa lafiya,ya tafi tare da Jawad. Kafin ya fita ta nemi iznin za ta je kitso, bai hana ba, ya amince mata.

Sai da ta gama komai na gyaran gida, ta yi wanka, ta tsaya jikin wardrobe tana nazarin rigar da zata sanya.

Wata daguwar riga ta janyo data jima bata sa ta ba, garin janyowar ta hado da ledar kayan da su Halima suka kawo mata na tsarabar khalil, wadda ta manta da su, ta leka ta ga rigunan Jawad ne da agogon ta, sai kwalin wayar Blackberry, ta jefa kan gado akan sai ta dawo zata san yadda zata yi ta nunawa Mk rigunan, dan ta fara sakawa Jawad tunda tsadaddu ne.

Ta dauko wayar daga inda take boyewa, ta jona a caji, ta shirya ta rufe gidan ta fita, zuwa bayan layinsu inda take kitson.

Mk da ya fito daga gidan rasuwar gidan Mahmoud suka zarce adalilin motar Mahmoud din ta lalace, dan haka ya kai shi, ai kuwa Jawad ya ce anan zai zauna wurin Dady.

Anan ya 'bata lokaci, ganin hadari ya hadu sai ya yanke hukuncin komawa gida ya huta bayan la'asar sai ya je wurin Hajiya.

Ya isa gidan, da mukallin hannun sa ya bude gidan, ya shiga, dakinsa ya kwanta sai ya tuna yana son dauko Agogon sa dake dakin Sa'adah da bai dauko ba, kullum sai ya fita yake tunawa.

Ya mike ya doshi dakinta, ya duba ya dauko Agogon, har ya kai bakin kofa sai ledar kan gadon ta ja hankalinsa, mussaman da ta kasance ta waje ce, dan haka sai ya koma ya dauko ya bude, ganin kaya ne, ya zazzage su akan gadon, kayan Jawad basu dauki hankalinsa kamar tsadadden agogo da kuma kwalin wayar ba.

Zuciyarsa ta dinga bugawa, wani irin tsoro, da razani suka shige shi, shaidan ya kawowa zuciyar sa caffa! kawai sai ya dinga tuno sadda take cewa matan bariki na mallakar duk abin da suke so cikin gaggawa.

Innalillahi wa ilaihir raji'un kawai ya ke ambata, ya kalli socket ya hango wayar da bai san da ita ba, ya karasa gurin ya dauko, yana dubawa, ganin Blackberry ce kuma babbar sai hankalinsa ya sake tashi, ya kasa budewa saboda ta sa mata password.

Da yake data a kunnen ta ke

Ya dinga ganin sakonni na shigowa ba jinkiri.

Ya dinga jin jiri na katantanwa da shi, bai taba jin tashin hankali irin na yau ba,me Sa'adah take yi haka? A ranar ya gane duk yadda yake daukarta ta wuce nan.

Kusan mintina talatin yana zaune a dakin nata, cikin tashin hankali iri iri.

Daidai lokacin ta shigo gidan a sukwane, tunda ta ga motarsa a waje ta shigo a hanzarce, zuciya na 'bari, ba ta yi zaton zai dawo ba, wacce irin 'kaddara tasa ta bar kayan nan da waya a fili?

Kai tsaye 'dakinsa ta shiga dan ganin wanne kallo zai mata?

Har 'bandaki baya nan, bugun zuciyar ta ya karu, cikin shahada ta nufi ta nufi falon , bata ganshi ba, fargabar ta ta 'karu ta tabbatar ya ga wayar nan.

'Karfin hali ta lalubo ta dora a fuskarta duk kuwa da zuciya da gangar jikinta sun 'ki karban wannan 'karfin halin.

Da sallama a bakinta ta shiga dakin, yanayin da ta iske shi, sai da ya ka'da mata 'ya'yan hanji.

Bai 'dago ya kalleta ba, amma ya amsa sallamarta da murya marar amo.

Ta aro jarumtar 'boye kaduwar da take ciki, ta matsa kusa da shi tana cewa "Ba ka jin dadi ne, da kace sai yamma za ka dawo, a Ina ka baro Jawad?"

Ya dago yana kallon ta, yana jin wata irin tsanar ta na neman Samun muhalli a zuciyar sa.

Bai amsa mata ba, ya zuba mata ido yana jin tamkar ya tashi ya yi ta dukanta. marar gaskiya akace ko a ruwa gumi ya ke yi, ta dinga jin 'barin jiki irin na fargaba, ta yi sukuri tamkar ace 'kyat ta fece da gudu.

Ya mi'ke ya isa inda take tsaye yace " A Ina kika samo wadannan kayayyaki masu daraja?"

Cikin rawar murya tace "Anty Sumayya ta aiko mana, dama na fito da su idan ka dawo, ka gani"

Ya zuba mata ido yana kallon yadda ta ke shirya zancen da babu azanci a cikinsa, ledar kayan ta nuna daga Egypt kayan suke, sannan a cikin kwalin wayar akwai risit din siyan wayar a ciki mai dauke da sunanta a takaice(S.B). Kwanan watan ya nuna ta kai wattanni biyu a hannun ta.

Ya ce "Sumayya yaushe ta je Egypt ban sani ba? Ta hannun wa sa'kon ya same ki?"

Ta muzanta kwarai da gaske, ta kasa bude baki ta yi magana.

Ya dauko wayar yana cewa "Wannan wayar da ta lashe manyan ku'da'de Sumayya ta aiko miki? Ko kuma saurayin ki, ki ka fa'dawa mijinki ya gaza?"

Ya mi'ka mata ya ce "Bu'de mini! tashin hankalin ta ya ninku, Baki na rawa ta ce "kar ka yi aiki da zato, wayar Halima ce ba tawa ba".

Idonsa ya canja zuwa jah, jijiyoyin kansa suka bayyana ru'du ru'du, makoshinsa ya bushe, zuciyarsa ta cushe da tsananin bacin rai, hankalin sa ya kai 'kololuwa wurin tashi.

"A zafafe sosai ya ce " wacce maganar zan kama, wayar Halimace ko Sumayya ce ta kawo miki?

ki bude min wayar nan tun kafin na tozarta ki, domin sai na dauke ki munje gaban Halima, Ina rantse miki da ubangiji agaban Baffa za'a yi komai".

Ta fara kuka tana cewa "Ajiya ta kawo mini itama ba tata bace, dan Allah ka yi hakuri, gaskiya na fada maka".

Karon farko da hakurinsa ya kwace ya dauke ta wani irin mari mai katse ji da gani na wucin gadi! ya ce "Da aurena Sa'adatu, da aurena akan ki? Idan wayar Halima ce to wannan Agogon da kayan na uwar waye?"

Tsananin zafin marin yasa habo ya goce mata, duk da hakan bata damu ba, asalima kukan tsayawa ya yi cak duk da hakan furucinsa ya fi firgita ta sama da marin

A gigice ta ce " gaskiya na fada maka, ka yarda da Ni"

Ta riga ta kudiri aniyar komai zai mata ba zata bude ba, domin a jiya ma sun yi chart da Khalil, duk da ba wani dirty abubuwa suka tattauna ba, amma akwai maganganun da ba zata so Mk ya gani ba, mussaman hotunan sa da ya turo mata, ita kuma ta tura masa na Jawad.

Hankalin Mk ya kai ma'kura wurin tashi ya matsa kusa da ita sosai yace "ki bude min wayar nan idan ba so kike ki wulakanta kanki ba".

ta karba, amma ilahirin jikinta rawa yake yi na tsananin tsoro da firgici.

Fiye da mintina goma tana ri'ke da waya amma ta 'ki budeta, lamarin da ya sanya Mk ya ce ta fita suje gidan su Halima, ya tasa ta a gaba har tsakar gida, anan ta coge akan ita ba zata je gidansu wata Halima ba.

Ya nuna ta da yatsa ya ce "Billahillazi sai kin je, daukota zamu yi, muje gaban Baffa shine al'kalin wannan jahilcin na ki".

Ta rasa inda zata tsoma ranta, ta tabbatar Halima kai tsaye za ta ce ba wayarta bace tunda ba ta 'ki ta kashe auren Mk ba dama.

Ya koma 'daki dauko mukallin mota, tashin hankali yasa ya kasa ganin inda ya ajiye, yana cikin dube dube kawai sai jin 'karar fashewar abu ya ji da karfin gaske.

Ya fito da sauri, ya ga wayar ta rotsa, ta fashe sosai, ta wargaje yadda ba zata tashi ko ta moru ba.

Bai san sadda ya isa gareta ba, ya sha'keta sosai, sai da ya lura tana dab da sumewa ya wancakalar da ita, ya hau dukanta da hannuwansa.

Ganin yana dukan amma ba abin da yake ji na sauki sai ma 'karin tafasar zuciya, ya kyaleta ya zauna a kasa dabas ya dinga ambaton innalillahi wa ilaihir raji'un, hawaye bakin ciki na tsere akan fuskar sa.

Ta dago da 'kyar ta ga yadda ya ke zubar d hawayea! a fili bai damu da aga yana kukan ba, duk wata dauriyarsa sa ta kwace a YAU.

Hankalin ta ya sake ri'banya tashi, ta dinga kuka tana fadin " Ka yafe mini, wallahi ba wayata bace".

A tunzure ya antayo ashar irin wadda bata taba jinta ba, ya maka mata, tare da cewa "Idan ki ka kuma bude baki da nufin yi min, magana ko bani ha'kuri Billahillazi sai na miki abin da baza ki manta ba".

Wayarsa ya ciro aljihu, da kyar ya iya lalubo sunan Fahad Auwal!

Dalibinsa ne tun a FGC yana cikin samarin Sa'a duk da dai bata ta'ba kulashi ba, sannan yanzu ma dalibinsa ne a B.U.K.

Da girmamawa ya gaida Mk.

Cikin rashin sukuni Mk yace "Fahad cikin class mate din ku na FGC akwai mai karatu a Egypt kuwa?"

Dan Jim Fahad ya yi sannan yace"Khalil Ibrahim ne kawai a Egypt".

Ko godiya Mk bai tsaya yi ba, ya katse wayar.

A fili ya ce "ban da tabbas, amma idan har yanzu kuna tare na tabbatar kun tabbata wakilan manyan shedanu a doron 'kasa".

Ta 'kara karfin kukanta ta ce "Mala.. ya katseta ta hanyar jifanta da takalminsa da hagu. Tare da cewa "ki mini shiru, dama ai na fada miki ba zan sake yi miki uzziri akan shedanun yaron nan da baisan kimar da darajar aure ba".

Ya jima yana ambaton addu'ar we yayewar ba'kin ciki, *"YA HAYYU, YA QAYYUM BI RAHMATIKA ASTAGIS*.

Ya 'dan sami nutsuwa ka'dan ya kalleta ya ce " kin yi wankan ko ba ki yi ba?"

Da'di ya kamata mussaman da ta tuna da asuba ya gama mitar hakurinsa ya 'kare, wannan karon period dinta takes too long. ta yi dariya ta ce bai 'karu ba kawai matsuwar da ka yi ne, amma dai nasan ba tantama I will be ready today.

Tunaninta nemanta zai yi tunda dabi'arsa ce ya kusanceta a lokacin da ya ga shaidan zai dagula zaman lafiyar su.

Da hanzari ta ce "Na yi".

Ya zuba mata ido sosai yana so ya ji ko akwai sauran gurbi a zuciyarsa da zai sake yi mata uzziri, sai ya ji babu saura, yana jin idan bai rabu da ita ba, tabbas ba'kin cikinta ne zai zama ajalinsa.

Dan haka muryar sa cike da rauni, hawaye na zirarowa ya ce "*Na sake ki, saki daya Sa'adatu*! Na ba ki dama ki zama yantacciyar da ki ke fata".

Ta 'kwala uban ihu mai gigitarwa.

30/04.

 HALIN YAU!

NA

SURAYYA DAHIRU.

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

Doka mai lamba ta 68 ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake dai satar Dukiya.

*A guji taba wannan labarin ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.*

Godiya ga makaranta

Ina matu'kar Jin dadin yabawar ku kan rubutuna, Hakika da kune Halin Yau ya je inda ban yi zaton zai je ba. na gode muku dukkan makaranta littafin HALIN YAU da fatan ana lura da sakon da nake nufin isarwa, ana watsi da shiriritar da yake ciiki, Ubangiji ya bamu damina Mai albarka.

Bari na sada zumunta da ku masoyan Sa'adah

Hajiya Rabi Sani

Aisha(cisse)

Tababa ta Malam

Asma'u Umar Ingawa

Samira Annuri.

Khadija Sadiq

Safara'u Niger.

Zainab Abdallahi

Aishatu maina

Khadija Bishir(Dijengala enterprises).

Masoyan da yawa mu tara a shafin gaba.

* SADAUKARWA GA*

SADIK ABUBAKAR.

Kuka ta ke yi tamkar ranta zai fita, ta rarrafa ta ri'ke kafarsa ta dama.

Cewa ta ke yi " Kar ka mini haka Malam, laifina bai kai ka 'dau wannan hukuncin ba, dan Allah ina sonka, ina son zama da kai".

A hanzarce ya fincike kafarsa, ya nunata da yatsa amma ya kasa bude baki ya mata magana saboda yadda yake jin wani irin sanyi na ratsa shi duk kuwa da yanayin garin a daure yake da zafi, saboda hadarin da ya hadu amma ruwa bai sauko ba.

Da 'kyar ya mike, ya shiga dakinta, ya dauko mukallin motar wadda yana tsakar dakin a yashe, rashin nutsuwa ya hana shi ya gani.

Ya fito, ya tsaya yana kallon yadda take kuka mai tsananin ciwo, irin kukan nan da ba ya sa a ji sau'kin tashin hankalin da aka tsinci kai a ciki.

A hankali ya ce "Tashi muje na kai ki gida".

"Dan Allah Malam ka yi hakuri Ni bazan tafi ba".

Fuskar nan a daure tamkar hadari ya ce " Ba za'bi na baki ba, ki tashi na kai ki cikin mutunci, tun ba ki tafi dutse a hannun riga ba".

Hawaye face face a fuskarta, Ta ce "iddah zan yi a dakina kamar yadda shari'a ta tanadar, ka girmama shari'a.

A kufule ya ce "wallahi ba anan gidan ba, ki je, ki yi a gidanku duk wata zan aiko miki abin da zai ishe ki! Na 'ki na girmama shari'ar, ke iyakokin ubangiji nawa ki ka take saboda son zuciyar ki, yanzu ne ki kasan ka'idojin shari'ar?"

Ta yi 'kasa da kanta dan kaucewa kallon tsanar da yake mata.

"Tashi muje" ya fada a kausashe.

Ta 'ki koda motsin kirki, sai shesshekar kukanta kawai, wadda ta ke yinsa har cikin 'bargonta.

A hasale sosai ya ce " Sa'adatu taurin kai a yau ba zai amfane ki da komai ba, bazan dauke ki da karfi ba, amma ki sani idan har ba ki tashi na mayar da ke cikin mutunci kamar yadda aka bani ke cikin mutunci ba, komai zai iya faruwa a tsakanin mu, na tsani na bude ido na ganki".

Nan ma ko uffan ba ta ce ba, sannan kuma ta 'ki tashin.

Ai kuwa ya ce "shikenan! Komai ya faru ki kuka da kanki, ya shiga 'dakinsa, mintina biyu ya sake fitowa ya dubeta tana kuka tamkar Baffah da Innah sun mutu rana 'daya, amma ko tausayi ba ta bashi ba.

A kausashe ya ce "Zan fita yanzu! kuma wurin Baffan zani na fada masa yau na mayar da ke 'yantacciya, amma ki sani Billahillazi idan har na fita ni ka'dai na haramtawa kaina ke, idan haka ta faru, shari'ar ta ce ba dalilin ki zauna kimin idda a gida ko?".

Tamkar tab'ab'biya ya ga ta mike ta fita waje a guje, ya bi bayanta dan ya lura tamkar ta zauce ne.

Ba ta tsaya a harabar gate din su ba, waje ta fita kai tsaye, ta yi kicibus da wani tsoho sosai, zai wuce, a gabansa ta zube cikin fitar hayyaci tace "ka taimake ni Baba"!

Dai dai lokacin Mk ya fito ya tarar da su a hakan.

Da sauri ta dinga cewa "ga shi nan Baba, bashi ha'kuri saki na ya yi, fa'da masa Allah ba ya son saki, yana kuma tare da masu hakuri"

Kallonta kawai za ka yi ka gane sakin nan ya susuta ta, ya gigita ta sosai.

Tausayinta ya cika zuciyar dattijon, ya kalli Mk ya ga shima a gigicen yake kwarai da gaske.

Duk da hakan sai yace "zo kusa da ni 'dana, Mk bai 'ki ba, hakan nan ya matsa kusa da shi ya tsugunna, a tausashe yace "ka yi hakuri ka ji! da gaske Allah na tare da masu ha'kuri, ba a biye sha'anin mata, yanzun nan za su rufe ido su yi abin da za su shekara suna nadama".

Mk dai baice masa komai ba, bai ji kuma zai janye sakin nan ba, tabbas sai ta je ta banbance tsakanin zaman gidan miji da rayuwar da take hari wannene 'yanci?

A hankali tsohon ya kuma fa'din "na tabbatar ko iya haka ka barta ta gane bakin Rijiya ba wurin wasan makaho bane".

Murya ba sauti Mk ya ce "Baba kar ka sa na yi abin da zan zalunci kaina, ina ro'kon ka, ka yi ha'kuri, al'kawari 'daya zan maka, matu'kar zuciyata ta huce da lamarin yarinyar nan, to kana cikin wadda zata ci darajar su na yafe mata, amma a yanzu idan ka tirsasani na mayar da ita, auren namu zai iya lalacewa gaba'daya, ka yi ha'kuri ka fahimce Ni".

Kafin Dattijon ya yi magana Sa'adah ta zabura ta sake kwasa a guje ta shige gidan.

Tausayinta ya cika zuciyar wannan tsohon, ya riko Mk sosai ya ce " Na fahimce ka 'dana, ba kuma zan maka dole ba, mai 'daki shi yasan inda yake masa yoyo! Amma ina son ka ri'ke a ranka cewar yarinyar nan tana sonka sannan uwar ya'yan ka ce, dan haka kar ka yi amfani da zato wurin hukunta ta, ka boye laifin ta, Allah ya muku albarka gaba'daya, ya kuma huci zuciyarka".

Da ga haka ya saki Mk ya juya, ya tafi, ga mamakin Mk sai ya ga cikin sakwanni mutumin nan har ya yi tafiyar da ya bacewa ganin sa, ya dinga wasiwasi anya kuwa wannan mutum ne? a tsufansa ba zai iya irin wannan sauri haka tamkar walkiya ba, ya shiga gida yana ayyana ko dai aljanine cikin aljanun Sa'adah.😂

A bakin motar ya tarar da ita, tana tsaye hawaye ya ki tsaya mata.

Ya bude gate din, sannan ya karasa ya bude motar suka shiga, sai da ya rufe gidan sannan suka tafi.

Ta by pass hanyar 'Dorayi ya bi dan haka hanyar ba yawan motoci, sun zo daidai Wailari ya ga ta fara wata irin jijjiga tana cewa "Laifina bai kai wannan hukuncin ba, kar kasheni da raina, Baffa ba zai bar Ni na zauna masa a gida ba, ina ka ke son na tafi?" Sai kawai ya ga ta sume.

Kan dole ya gangara gefen titi ya bude ruwan roba na Highland da ke gaban motar mai dan sanyi, daga gidan Mahmoud ya taho da shi, ya watsa mata, ajiyar zuciya ta saki tare da rushewa da kuka sosai har muryar ta fara dashewa, fadi take yi "Ka ji tausayina mu koma gidanmu, Jawad zai yi kukan rashi na, komai ka ce na yi bazan kuskure ba, na yarda ka 'Kara aure, ka sake 'karawa, ka sake 'karawa, ya fi mini sau'ki da na rasa ka".

Idan ya ce jikinsa bai yi sanyi ba, ya yi 'karya, idan yace maganganun ta basu yi yunkurin karya masa zuciya ba ya yi munafunci.

Ya zuba mata ido yana kallon yadda tashin hankalin awa daya rak ya susuta ta, yaci gaba da kallonta yana so ya samu dalili gamsasshe da zai mata afuwa, amma da zuciyarsa ta hararo masa cewa "Hai'ntarsa take yi shiyasa ta 'ki bari ya ga ta'addacin da ta ke yi da aurensa akanta, sai ya ji zuciyar sa tana zafi tamkar ana gasa burodi.

Ya zuba mata ido ya ce"Sa'adatu kowanne bawa da irin kaddararsa, Allah ya sani na iya bakin kokarina na mu zauna lafiya, kuma shine shaida akan son da nake miki, matu'kar gaskiya zan fada miki, zuciyata ba za ta nutsu da ke a yanzu ba!

Al'kawarin da zan miki daya ne, ba wadda zai ji mai ya ha'damu, Ina tabbatar miki zan dauki laifin a idon kowa, kema kuma kar ki fa'dawa kowa ko da Baffa ne kuwa".

Ya yanko tissue yana goge'kwallar da ta cika masa idanuwa.

Ta zama very speach less, bugun zuciyar ta ya karu, wani irin zazzabi mai zafi ya fara kokarin kai mata caffa. ta koma ta kwanta a jikin kujerar tana jin duk wani tashin hankalin duniya yau ita aka ha'dawa shi.

Tsawon lokaci suna haka, shiru ya ratsa, sai fama suke da radadi a zukatan su.

Cikin 'karfin hali ya tayar da motar ya hau titi, karon farko da Sa'adah ta yi fatan inama su yi hatsarin da zai zama ajalinta, ta huta da azabar ciwon da ke damun zuciyar ta.

Bai tsaya ba, sai a kofar gidan su, gabanta ya yanke ya fadi, ta tuno maganganun Baffa a ranar da zai kaita dakin aurenta.

Ta kalle shi ta ce "Baffa korata zai yi, kar ka barni anan, mu tafi gidanmu Malam, na yi al'kawarin ba zan sake ri'ke kowacce irin waya ba".

Ta ru'ko hannunsa ta sake fa'din " Na amince ka yi amarya ka tafi da ita karatun da za ka tafi, Ni ka barni zan jiraka, fatana kar ka barni".

Magana ta ke yi ba kuka, sai tsananin bacin rai da tashin hankali.

Ya kalleta sosai "a karon farko da ya ganta cikin NADAMAR gaskiya, sai dai nadama marar amfani ta ke yi domin ta riga ta yi a 'kurarren lokaci.

Baice komai ba, ya bude motar ya fita, haka ta bude itama ta fita sanin akan titi suke, a zaure ya tsaya ya ciro wayarsa ya 'Kira layin Baffah, ya sanar masa ya zo yana zaure.

Cikin rashin sa'a ya ce "dazun nan na tafi Gogel, sai jibi kuwa zan dawo, ko akwai matsala ne?"

Kai tsaye Mk ya ce "akwai Baffa Amma zan zo na sameka anan din"

"Ba sai ka zo ba Mutari, in sha Allah zan juyo a yau ba sai gobe ba".

Ya yi godiya, sannan suka kashe wayar.

Sa'adah na rakube a jigin bango, ta matso ta tsugunna guiwa biyu ta ce " Rashin samun sa alamun ubangiji bai son rabuwarmu ne, Dan Nabiyur Rahamati ka dauke ni mu koma gida".

Ya kalleta sosai ya furzar da iskar bacin rai ya ce "wa ya siya miki Wannan Agogon da kuma waya?"

Hawaye ya balle mata, ta rasa mai za ta ce.

Ganin ta yi shiru ya sa shi cewa tashi ki shiga gidan zan je shago na jira dawowarsa.

Ya fita da sauri, ya yin da ita kuma ta durkushe a 'kasa tana kuka sosai.

Ta jima tana kukan da 'kyar ta tashi ta shiga gidan ta tarar da mahaifiyarta tana zaune tana Jin radio.

Tana layi ta 'karasa kan tabarma sabon kuka na kaico iri iri na sake ku'buce mata.

Tambayar duniya ba wadda Inna bata mata ba amma ta 'ki tankawa, lamarin da ya dagula hankalin ta.

Kan dole ta 'kira wayar Baffah ta sanar da shi ga Iyah ta zo tana ta kuka, kuma ta ce mijinta ne ya kawota da kansa.

Ya amsa mata da gashi nan ya juyo.

Ta ajiye wayar cikin sanyin jiki ta kalli yadda ta ke kuka jikinta har 'bari yake yi, ga wata irin rama ta yi, har ba'ki ta ga ta sake yi mata sosai.

A hankali ta;ce "kin tasa ni a gaba kina irin wannan kukan mai tayar da hankali, amma kin 'ki bu'de baki ki fa'da min mai ya same ki, ba Kya jin tsoron ciwo ya kada ni, kinsan fargaba da zullumin da nake ciki?"

****

Mk na zaune a shago, amma jinsa yake tamkar a cikin rijiya saboda tsananin yadda ya takura ga wani irin matsanancin kishi ya matse kofofin numfashinsa, ya sababa masa azabben ciwon kai mai tsananin. Yawun bakinsa ya kafe sai daci yake ji har makoshinsa! ya ciro wayarsa ya kira Mahmoud ya sanar da shi, yana cikin matsala ya zo gidan Hajiyan Bichi ya same shi.

Ya fito kai tsaye ya tari mai acaba(A lokacin ba a hana ba) ya kai shi gidansu, dan bashi da sukunin da zai iya tu'ki, domin al'amarin na nisa damuwar sa na 'kara girmama, wani abu ne mai tsananin ciwo ya tokare a 'kahon zuciyarsa mai azabtarwa.

Yana isa kai tsaye can cikin dakin Hajiya ya shige ya wuce ta a falo tana yanka kankana.

Mamaki ya kamata, ba zata iya tuna yaushe rabon da ya shigo ya ganta a falo amma ya zarce uwar daki ba.

Ta yi jim, tana sauraronsa ganin fitowarsa, amma abin mamaki mintina fiye da goma sun shude bai fito ba, dan haka sai ta mike ta bi bayansa dan jin ba'asin wannan sabuwar dabi'a.

Yanayin da ta tarar da shi ya tabbatar mata akwai matsala, da azama ta isa gareshi tana cewa lafiyar ka kuwa?

A hankali ya ce"kaina tamkar zai fashe Hajiya"

Da jimami ta ce "Ai da Abbas ko Akil ka kira wani ya raka ka asibiti, a kwanta da ciwo ne ba a sha magani ba?"

Dai dai lokacin Mahmoud ya iso suka gaisa da Hajiya da ta fito falo tana masa iso.

"Shiga! yau zuwa ya yi ya mini sake sake a gado da sunan ciwon kai".

Mahmoud na dariya ya mike yana cewa " Hajiya ai gara ya kwanta ya more da zarar kunga mun yi aure shikenan sai ku dora mana dukkan girma alhalin matu'kar kuna raye mu yara ne 'kananu".

Ya shige cikin dakin.

Kallon Aminin nasa ya yi ya tabbatar yana cikin tashin hankali babba. Yasan karfin zuciyar Mk duk abin da ya bayyana a jikinsa tabbas ya yi tsamari ne.

Da gaggawa ya shiga ya zauna a gefen gadon, ya na fadin "me ya ke faruwa ne?"

Cikin rawar murya Mk ya dinga yunkurin magana amma ya kasa yi, ga mamakin Mahmoud sai ganin kwalla na gangarowa ta gefen idon Mk.

Take hankalin Mahmoud ya yi tashin gauron zabi, murya kasa kasa cike da tsantsar aminci da kulawa, ya ru'ko hannuwansa ya ce "Yi hakuri Mukhtar! Fada mini damuwarka in sha Allah I will stand for you".

Da rawar murya Mk ya dinga ambaton Sa'adah, Sa'adah".

A hanzarce Mahmoud ya ce" me ya same ta, me ta yi?"

Da 'kyar ya bude baki ya ce "mun rabu, na saketa Mahmoud"! ya karasa da murya mai cike da tashin hankali.

Wani irin zabura Mahmoud ya yi ya mike yana cewa"How comes, akan me? subhanllah!"

Shiru ya ratsa dakin! kowa tunani, na katantanwa da shi.

A kasan makoshi Mk ya ce " ka

fa'dawa Hajiya, tashin hankali na yadda zan fa'da mata, da yadda za ta karbi lamarin".

Mahmoud ya zuba masa ido, yana kallon irin yadda Aminin nasa ke zu'ko numfashi da 'kyar tamkar mai fama da cutar asma.

A hankali ya koma ya zauna yana jin tashin hankali shima na ziyaryartar sa.

Tausayin Mk ya ratsa shi ya sake ru'ko hannuwansa a karo na biyu ya sassauta murya ya ce," Ina fatan sakin sunna ka yi, ina fatan mu gyara wannan matsalar kafin su Hajiya su ji, yanzu ina ita Sa'adah ta ke?"

Cike da rashin kuzari ainun ya ce "Na kaita gidansu, saki daya na yi mata, abin da nake so ka fahimta, da abin zai gyaru da ko kai ba zan raba 'bacin ran da kai ba".

A hankali Mahmoud ya muskuta ya ce "Kar ka yi haka, ka yi hakuri mana, da wanne irin ido za ka kalli dattijon arziki irin Baffah?"

Wannan karon Mk ne ya tamke hannun Mahmoud ya zarce da cewa "shine babban tashin hankali na, fiye ma da yadda nake jin fargabar da Hajiya za ta shiga, amma kuma bana jin zan iya cigaba da zaman mu tare, iya adadin zaman da 'kaddara ta hukunta za mu yi kenan, ka fa'dawa Hajiya sai muje ka raka ni wurin Baffah, duk da bana jin dadin jikina".

Ya fada a sanyaye cike da yankewar Buri.

"Mukhtar Nima ba zan iya fa'da mata ba, da wanne baki zan fadi wannan 'bakin labarin?"

"Cike da rauni ya ce " daurewa za ka yi Mahmoud".

Shiru ta ratsa dakin a karo na biyu, nazari soasai Mahmoud ya ke, yana tunanin wacce irin 'kaddara ce mai zafi ta raba Mk da Matar da ya shaida yafi sonta akan kansa?

Yana son jin menene ummul aba'isin wannan matsalar, amma kuma tunda Mk bai bu'da masa ba, shikuma ya yi al'kawarin ba zai tambayi komai ba, zai kuma yi dukkan mai yiyuwa dan ya sulhunta tsakanin su.

A dabarance Mahmoud ya 'daga murya ya ce "Sam bazan iya fadawa Hajiya wannan tashin hankalin ba, kai da ka yi, kaine mai fa'da ba Ni ba".

Ai kuwa wannan kalamin na Mahmoud ya janyo hankali Hajiya, da azama ta fa'da 'dakin tana fadin " menene ba za ka iya fada mini ba Mahmoud! wanne tashin hankalin ya rakito?"

Dukkansu suka yi shiru aka rasa mai bakin magana, ta zauna da'bas a 'kasa tana salati, da fatan ba wani rashin gaskiya Mk ya aikata ba.

Ganin irin damuwar da ta shiga yasa Mahmoud yin 'kundunbalar fadin "Hajiya ki yafe mu, ina ba'kin cikin sanar da ke yau Allah ya 'karar da zamansa da Sa'adatu".

Salati mai 'karfi Hajiya ta rafka, tana cewa "Kar ka jinginawa Allah'karar zamansu, jingina masa, dama ya da'de yana fatan rabuwar, ganin ya kasa samun damar shine yanzu ya murde zaman da 'karfin tsiya."

"Oh ni Rabi'atu ina ganin tasku, da wanne 'bakin ciki zan ji? da wadda yan'uwanka suke guma mini, ko da naka? Alhaji da Hajiya Babba sun mutu sun barni da ku, kuna neman kashe ni da ba'kin ciki".

Ta fara hawaye, tana gogewa da hannun zaninta .

Da ga Mk har Mahmoud sun yi laushi tubus da jin kukan Hajiya, hankalin su kuma ya sake tashi matu'ka, da rawar murya Mk ya ce "Na roke ki, ki daina zubar da hawayen nan dafi ne a rayuwa ta, da kinsan azabar da nake 'dan'dana na tabbatar da sai kin sassauta mini, ki yi hakuri Hajiya ba yadda zan yi ne, abin ne ya fi karfina, ki mana addua ki kuma yafe mini".

"Yanzu ina Sa'a din ta ke?"

Mahmoud ya ce "tana gidansu, yanzu ma komawa zamu yi dan bamu sami Baffan ba".

Hajiya ta sake sa salati tana tafa hannu, tare da cewa "yanzu idon ku, idon tsohon nan ku iya fa'da masa kun mayar masa da 'ya Bazawara? kaico na taya ku jin kunya".

"Yanzu ku tashi ku kaini gurin Alh Isa".

Sai da Mahmoud ya taimakawa Mk sannan ya mike.

Fada sosai Mk ya sha a gurin Alh Isa, sai daga karshe ya sassauta ya ce " Ka yi kyan kai da ka yi saki 'daya tal, fatana ka janye ka mayar da matarka, kowa hakuri ya ke yi da abokin zamansa ,ta ci darajar mahaifinta".

Kan Mk na kasa baice komai ba sai da Baban ya kammala sannan cikin ladabi ya ce "A mini afuwa Baba, a yi hakuri, a sani cikin addu'a ina cikin ru'dani mai yawa, ina rantsuwa da ubangiji ina cikin ru'danin da nake jin inama ajalina ya riske ni a yau saboda tsananin asarar da nake jin na tafka, ba yadda zan yi ne, abin ne ya fi 'karfina"

Dukkansu jikinsu ya yi sanyi mussaman yadda yake maganar cikin rawar murya tamkar ba Mukhtar ba, namiji mai karfin zuciya.

"Allah ya daidaita ya kawo mafita " cewar Alh Isa da ya rasa mai zaice, dan ya lura Mukhtar na cikin rashin nutsuwa da firgici, ya tabbatar kuma yana da gaskiya, sannan mai 'daki shi yasan inda yake masa yoyo.

Dukkansu suka amsa da "Ameen, ya yin da Hajiya ba haka ta so ba, so ta yi ya wula'kanta mata shi, ya kuma tirsasa masa ya mayar da matarsa ko ba ya so.

Har da Alh Isa suka 'dunguma zuwa gidan su Sa'a, Hajiya ce kawai ta ce ba zata je ba, bata san da idon da za ta kalle su ba.

A tsakar gidan Baffa ya jagorancin zaman, Alh Isa ne ya yi karfin halin bayyana mutuwar auren wadda ya matu'kar dukan zuciyar iyayen na Sa'adah, juyin duniya ba wadda ba'a yi musu ba, amma sun 'ki bayyana menene dalilin da ya haifar da wannan tashin hankalin, kukan da Sa'a ke yi tamkar za ta shi'de ya sake 'daga hankalinsu.

A hankali Mk ya ce "Baffa Ina rokon ka, kar yanke mini kauna, ka yafe mini, kaddarar muce ta zo da hakan, har wayewar garin YAU bamu san zamu tsinci

kanmu a cikin wannan mawuyacin HALIN da muke ciki ba, ina kuma fatan itama ka yafe mata, ba laifinta bane Baffah".

Gurin ya yi tsit sai shshshekar kukanta kawai ake ji, Mahmoud ya kamu da ciwon tausayin masoyan biyu, mussaman Sa'a kallo daya za ka mata kasan tana cikin tsaka mai wuya.

Baffa ya nisa ya ce "Ba aurenta ne ya hadamu ba Mutari, ba kuma zai zama dalilin rabuwarmu ba, nasan halin girma irin naka, tsiyar a gunta take, yanzu kuma zata gane tsiyar har wasali gareta, domin na tabbatar laifin nata ne, ba zata 'ki zaman aure ta yi tunanin zata zauna a gabana ba".

Ga mamakin Mk sai ya ji kalaman Baffa sun sake girgiza masa zuciya.

Da sauri ya mi'ke ya koma kusa da shi ya ce "Baffa Dan Allah dan Annabi ka yi ha'kuri, idan ka yi haka bazan yafewa kaina ba, ka yiwa Allah ka barta ta ji da tashin hankalin da na jefata, ba laifin ta bane, nawa ne, Ni za ka hukunta ba ita ba".

Ido kawai Baffah ya zubawa Mk da yake gurfane a gabansa yana rokonsa idansa jawur, ga wata irin rama da ya yi ta farat daya.

A ransa fadi yake Iyah kin tafka asara, kubucewar miji irin Mutari abin ki shimfi'da tabarma azo a miki jaje ne.

Ya tabbatar laifin na Iyah ne, amma ya 'boye laifinta, ya kuma tsaya kai da fata wurin nema mata sassauci da aminci a gurinsu.

Baffa ya dafa kan Mk ya ce " Madallah da mutanan kirki irin ka, madallah da mutane masu irin dabi'ar ka, madallah da zuciya mai adalci irin ta ka! Saboda kai zan bar Iyah ta zauna a gidan nan, ban taba jin takaicin rashin ya'ya da yawa ba sai yau, da ace Ina da wata 'yar! da wallahi taron nan bazai watse ba sai na musanya maka da ita".

Kwalla ta 'kwacewa Mk ya na jin kunya da tausayin Baffa na sake masa rubdugu, wacce irin kauna ya ke masa haka, anya bai yi rashin kirki da ya kasa yin ha'kuri da 'yarsa ba?"

Ba zato suka ji Mk na cewa "Baffa me yasa ba zaka ba ni umarni na mayar da ita ba, sai ka yi fatan ka bani yar'uwarta idan hakan ya yiyu ka haramta mini ita gaba'daya fa?".

Ba ki 'daya jikinsu ya dan yi karfi saboda kalaman Mk, wadda suke bushara da zai iya daidaitawa da matarsa, yanzu ko anjima.

Inna ta ce "Tunda baka da wata da za ka bashi, ai sai ka mayar masa da wadda ka ke da itan".

Cikin kuka sosai Sa'adah ta ce " Na gode Innah".

Surayya Dee

✍

 HALIN YAU!

NA

SURAYYA DAHIRU.

•·•

LAFAZI WRITERS ASSOCIATION ® ✍

_____

```{Kyakkyawan lafazi a cikin rubutu yana ɗamfare da bin ƙa'idar Adabin Hausa.```

```Lafazi gidan karamci da mutuntaka, Harshenmu abin alfaharinmu.}``` ✏✏✏

_____(✪)_____

https://mobile.facebook.com/Lafazi-Writers-Association-104448621878916/

Doka mai lamba ta 68 ta nuna cewa satar fasaha babban laifi ne da yake dai da satar Dukiya.

*A guji taba wannan labarin ba tare da izinin mai Hakkin mallaka ba.*

Gaisuwa da fatan alheri ga wadannan groups din

LAFAZEE FANS

DANDALIN MUM KHADY

HAFSAT SODANGI fans

DAGA DAJI 1&2 fans

PAID GROUP na BINTA ABBALE

DANDALIN SADA ZUMUNTA NA ANNURI.

JIDDA REAL FANS

FADILA LAMIDO FANS

SADNAF NOVELS GROUP

TASKAR AISHA MICHIKA

_*Dama sauran wadanda ban ambato ba, mu hadu a shafin gaba, Kuna da yawa Allah ya bar kauna_*.

MK, SA'A DA FARIDA NA GAISUWA

SADAUKARWA GA

SADIK ABUBAKAR.

79_80.

"Ba zan ba ka umarnin da na san kunya da nauyi ne zaisa ka yi shi ba.

Ba ni na maka umarni ka auri Iyah ba, ku ka hada kanku, ka aureta bisa ra'din kanka, ka zauna da ita cikin shekaru bakwai, Ni da mahaifiyarta shaida ne akan kyakkawan rikon da ka mata, haka nan, ka na girmama mu da dukkan zuciyarka, kana jin nauyi na tun kafin na baka aurenta, idan har za ka iya sakin Iyah, to ni kuwa bazan yi son zuciya ba, na tabbatar abin ne ya fi 'karfin ka".

Ya nisa ya cigaba da cewa

"Zan so kwarai ace na mutu na barta a hannun ka, domin Ina da yakinin ba za ta wulakanta ba, amma ya na iya da HALIN 'dan YAU mai yin aiki da son zuciya, daga baya kuma ya jinginawa tsautsayi da 'kaddara".

Alh Isa ya muskuta ya ce "Tun kafin mu zo nan, na umarceka da ka janye, ka mini gardama, amma yanzu kana cewa ya baka umarni ka mayar da ita, Ni baka jin nauyi na Mukhtar?"

Kunya iri iri ta sake rufarwa tashin hankalin da Mk ya ke ciki, a sanyaye ya ce " A a Baba bayan nauyin ka da nake ji, wallahi kallon uban da ya isa ya zartar da hukunci akai na na ke maka! Abin da yasa ban amsa ba, ina jin tsoron kada na mayar da ita a yanzu auren ya lalace gaba daya, saboda zuciyoyin mu cike suke da bacin rai mai ya.."

Cikin dimaucewa Sa'adah ta

katse shi da cewa "Ni zuciyata ba komai sai salama da nadamaar *HALIN* da nake ciki, na yi al'kawari zan jure duk wani kalar fishinka, ba zan yi abun da za mu kai ga lalata auren mu ba".

Tausayinta ya ratsa su dukkan su, gurin ya dauki shiru, sai fama suke da tausayin su, kowa ya lura laifin Sa'adah ne, amma Mk ya kafe laifin sa ne, su gafarce shi, haka aka tashi ana addu'ar, Allah ya daidaita su.

Bayan tafiyar su Mk, kukan Sa'adah ya karu, sosai ta ke rusa kuka, yayin da iyayen ta suke fadin ba ki ma fara kuka ba, domin sai nan gaba za ki gane asarar da ki ka yi ba 'yar 'karama bace.

Zazzabi mai zafi ya rufe ta, hakoronta suka dinga karo da juna, jikinta sai rawa yake tamkar mazari.

Da farko shareta suka yi, sai da suka ga abin na sake 'kamari sannan Inna ta kai mata 'dauki, tana sa hannu a jikinta ta ji zafi zau.

Har dare tana cikin wannan yanayin, kan dole Baffa ya 'kira wani jami'in lafiya, mai chemist a unguwar ya zo ya bata taimakon gaggawa.

Haka al'amarin ya kasance da Mk, bayan sunje sun sauke Baba Isa, yace da Mahmoud gidan Hajiyar Bichi zai maida shi, suna shiga falon nata ya yanke jiki ya fadi, alma'arin da ya matu'kar tayar da hankalin su, 'Karfi ya fita a gigice, ya yi sa'a ya tarar da Abbas na gida, ya 'Kira shi suka ciccibi Mk zuwa wani asibiti mai zaman kansa mafi kusa, dole aka kwantar da shi sakamakon jininsa da ya yi mugun hawa, baya ga haka yana cikin damuwa da ya ke bukatar hutu..

Abbas ne ya zauna da shi, sauran yan'uwansu kullum suna zarya a asibitin, haka nan Mahmoud kullum sau biyu yake zuwa duba shi.

Har zuwa wannan lokacin Jawad na gidan 'Karfi bai san me yake faruwa ba, takanas Mahmoudya je ya debo masa uniform da kayansa kullum da safe zai kai shi, idan anta shi kuwa mai aikin matar ke hawa adaidaita ta dauko shi, idan ya tambayi Mamin shi ko Malam sai ace sun yi tafiya ne, bai damu ba, tun tafiyarsu Abuja ya saba zama gidan Mahmoud Karfi.

Kwanansa uku aka sallame shi, tare da gargadin ya rage damuwa, ya kuma kula da shan maganinsa.

Haka ya tattare dakin Hajiya, tun tana ki, har ta ha'kura ta barshi, kan dole ta koma kwana a babban falon su, da suke zama ayi dab dabla lokacin Hajiya Babba.

Kwanansa biyu a dakinta yana warware wa, a cikon na uku ne ganin ya dan sami sauki har ya ci abinci, yasa ta bijiro da maganar Sa'adah.

"Matu'kar kana son mu shirya to ka dawo da matarka, rashinta ne duk ya susuta ka haka, idan kuwa ka 'ki jin maganata kar kuma takowa inda na ke, ko gaisuwar ka bana so".

Hankalin sa ya tashi, ya fara 'ko'karin fahimtar da ita da hujjoji, amma fur ta hau dokin na 'ki.

Ganin da gaske ta ke yi, shikuma a yanzu wani irin tsoro da firgicin zama da Sa'adah ne ya ke kama shi, bai ta'ba tunanin za ta yi abin da ta yi ba, mussaman yadda ya ke wadata da komai, uwa uba kuma yadda ya ke tarairayarta da gudun zuciyar ta, idan har hakan bai sa ta kiyaye masa amana ba, bai ga kuma me zai mata ba.

Kansa har zafi yake wurin tunanin, me yasa ta yin hakan? Ya tabbatar shi baya ha'intar ta akan me ita zata ha"ince shi?

Wani irin tsimin bacin rai ya taso masa, mai hade da kishin da ya haddasa tsanar Sa'adah, ya kasa bu'de baki ya yi magana kawai ya kife kansa akan guiwowinyasa ya fashe mata da kuka tamkar yana cikin shekarun 'kuruciya.

Wannan kukan ya matu'kar ta'ba zuciyar Hajiya, ta shiga ru'dani da wasiwasi akan lamarin Sa'adatu, kan dole, ta ha'kur'kurtar da zuciyar ta, ta ce ta janye takunkumin dolen da ta yi masa.

Amma a zuciyarta sai hasashen wanne irin abu ta yi mai muni haka?.

Sati guda da faruwar wannan lamarin, amma har lokacin Sa'adah na kwance ba lafiya., saboda ta 'kuntata zuciyar ta, ta 'ki cin abinci, kullum cikin kuka ta ke, ta yi wata irin rama mai tayar da hankali, kuka ta yi shi irin wadda ba ta yi tunanin akwai mahalu'kin da ya yi irinsa ba, ko ya ya ta ayyana Mk ya saketa, shikenan sun rabu? sai dai Inna ta jiyo ta 'barke da kuka tana fadin na tafka asara, na yi nadama.

Sannu a hankali zance ya shiga kunnuwan dangi, kowa ya ji mutuwar auren sai ya shiga alhini saboda yadda aka shaida soyayyar da Mk ya ke yiwa Sa'adah, mussaman Auntyn Lagos, Maman Gombe da Samira, hankalinsu ba karamin tashi ya yi ba, da kuka Antin Lagos ta 'kira Hajiya tana tambayarta gaskiyar magana, cike da tausayi Hajiya ta tabbatar mata sun rabu tabbas.

Da rawar murya take fadin "Hajiya ki matsa masa ya dawo da ita, na tabbatar duk inda ya ke, ba ya cikin nutsuwa, yana sonta".

"Hmmm kawai ki musu addu'a amma lamarin na su akwai tashin hankali." Inji Hajiya .

Wata guda Mk ya 'dan wartsake, ya koma harkokinsa da 'karfin zuciya irin ta namiji, sai dai abin na nan ma'kale a zuciyar sa yana jin har ya koma ga mahallicinsa ba zai manta ba, idan ya tuna dalilan da zai hana Sa'adah ta bashi wayar nan sai ya ji bugun zuciyar sa ya karu, wani lokacin har jiri ke dibansa.

Ga Sa'a kuwa wannan watan ta cinye shi ne a kwance tana 'dan'danar azabar ciwon so da nadama, tunda gyatumarsu ta kawo ta duniya bata taba fuskantar tashin hankali irin wadda ta ke ciki ba, fata take mutuwa ta dauketa ta huta da wannan zugin da zuciyar ta take mata, inama ta bashi wayar nan ya gani?

Wata'kila da ba zai zafafa lamarin har haka ba, tun shekaranjiya da ya aiko mata wasu cikin kayanta shake cikin akwati babba, yini ta yi a ranar tana kuka, ba abin da ta ke fata irin ta ji ko da Muryar Mk, amma abin ya faskara, ga tunanin Jawad rabon da ta ganshi tun ranar da suka rabu da Babansa, ta yi dalilin da suke rayuwa a wuri daban daban, wannan kadai ya isheta ladabtarwa.

Cikin wannan 'kangin ta sake cinye wani watan har da 'karin kwanaki goma, zullumi ya ishi Sa'a, saboda kwanakin iddarta na gab da kammala, duk wadda ya ganta yanzu, muddin ya santa a wattannin baya, sai ya tausaya mata, gashi dai ba ta rasa komai ba, amma ta rasa kwanciyar hankali, satin ta biyu a gidan Mk ya aiko da kayan abinci kala kala wadda za su kwashe rabin shekara suna ci, sai kuma ya mata siyayyar komai na bukatunta tun daga kan kayan shayi har sabulai, da tarkacen abubuwan da zata bu'kata, amma ko taba su ba ta yi ba, hakanan abinci sai Inna ta tausaya mata, ta zauna kusa da ita, ta matsa mata sannan za ta yafita .

A lokacin Sa'adah ta fahimci ba abin da yafi nutsuwar zuciya da'di, addu'a ta ke sosai akan ta sami sau'kin tashin hankalin da take ciki, idan ta ji yo su Baffah na hira har da raha shi da Inna sai ta tambayi kanta yaushe za ta fara dariya ne ita?.

Yanayin da ta ke ciki ya fi kama da na mai takabar da mutuwar managarcin miji ya zo mata kwatsam.

Daidai wannan lokacin Sumayya ta iso Kano dan jajantawa yar'uwarta halin da tsinci kanta a ciki.

Halin da tarar da Iyah a ciki ya bala'in girgiza ta.

Cike da tausayawa tace " Na sha fada miki halin da kika jefa kanki ba inda zai kai sai nadama, gashi tun ba a je ko ina ba, kina fuskantar Halin Yau! duk wadannan kawayen na ki da kika mayar allon kwaikwayon ki YAU suna Ina?"

Karon farko da Sa'adah ta fara jin sassauci domin sai a ranar ta Sami wadda ya mata fa'da, iyayen ta sun zuba mata ido, ba wadda ya buda baki ya mata fa'da, sun mata dungu suna gasa ta da idanuwan su kawai, hatta Baffah da ta tabbatar ba abin da yake so a duniya irin ta, wannan karon ta na hango ko oho da yake yi da lamuranta.

Ta ri'ke hannun Sumayya ta na wani irin kuka, tana fadin "kin fada mini, ba irin gaskiyar da ba ki fada mini ba, sai dai an riga an kadddara mini yanka kazar wahala, dole kuwa sai na figeta tas, Mukhtar mutumin kirki ne, laifin duk nawa ne, sai dai nima kadddara ce da bazan iya kauce mata ba, ki taimake ni Aunti! ki bashi ha'kuri, Tunda Baffa ya barni da kaina".

Ta shide tsabar kuka! Hankalin Sumayya ya ru'banya tashi, amma hakan ta daure, ta tausasa murya ta ce " ki daina irin wannan kukan, idan har kin yi amanna kaddara ce ta hau kan ki, to ki yi hakuri ki bita da istigifari, yawan kuka da 'kauracewa abinci da takurawa zuciya ba abin da zai haifar miki sai ciwon da zai kayar da ke, ina tabbatar miki duk wadda zai shiga damuwa a dalilin rashin lafiyar ki, ke ce dai mai jin jiki?"

"Na gode sosai Anty dan Allah ki 'kira shi, ko zai ga girmanki".

Sumayya ta nisa ta ce "Bana jin girmana zai sa ya janye kudirinsa tunda har bai janye saboda Baffah ba".

Hawaye ya kwaranyowa Sa'adah ta ce " Baffa ba ya son na koma ne, a gaban mu Mukhtar ya ce ya bashi umarnin ya mayar da ni, amma 'kememe Baffa ya 'ki, ya barni na ji da dabarata".

Sumayya ta yi shiru, tana jin tausayin 'kanwarta na sake kamata, ba ta gane muhimmancin mijinta ba sai da ya kubuce mata, ta tuna wani lokaci da ya shude tana mata fadan ta bi mijinta su zauna lafiya.

Ta nisa ta sake tuno amsar da Sa'adah ta bata a waccan lokacin, "Anty ki ta cemin na bishi, na masa biyayya ko da yana cutar da ni, akan me zan yi irin wannan rayuwar auren alhalin ko yau Mukhtar ya barni Ina da yakinin zan samu wadda ya fi shi."

Ta dago ta kalle ta, yau Mukhtar ya barta, da ya tashi barin nata ba shi kadai ya tafi ba, sai da ya yi awon gaba da dukkan nutsuwa da walwalarta, bugu da 'kari hatta kyaun da ya sa take ta'kamar zata samu wadda ya fi shi, ya tsiyaye tas, ta kai duba ga kirjinta , ta ga sun yamushe a cikin riga, mamaki ya kama Sumayya bata taba sanin nonon Iyah zai iya zubewa haka ba, domin ko da take shayarwa a tsaye kuma a cike suke, irin wadda suke ma'kale ne a kirjin mace, amma tashin hankalin da take ciki suma ya tabasu, hakanan gashin kanta sai saukewa yake yi, ga uwar rama sai ido gwara gwara tamkar idon agolan Banufe.

Ta ke Sumayya ta dinga neman tsari da shiga tashin hankali kwatankwacin irin wadda Iyah ke fuskanta, ta kuma nemawa yar'uwarta samun sassauci da mafita.

A hankali ta ce "zan 'kira shi, sai zuwa dare tunda yanzu yana gurin aiki, fatana dai ki kwantar da hankalin ki, ki karbi kaddarar ki da hannu biyu, yanzu a ina Jawad ya ke?"

" Ni ma ban sani ba" Sa'adah ta fada a sanyaye.

A daren ranar kuwa Sumayya ta 'kira layin Mk, da girmamawa ya amsa wayarta, suka gaisa, ta fara da tambayar Jawad, ya amsa da yana nan lafiya Lau, shima ya tambayi nata iyalan, da 'kyar Sumayya ta iya masa maganar Iyah, ga mamakinta

sai taji ba alamun zafafawa, ya ce "Anty ku bimu da addu'a da ga ni har Sa'adatu abin ya zo mana a ba zata, muna bu'katar mu nutsu, zuwa gaba muga me ubangiji zai zartar mana, har yau ina sonta, Ina fatan mu sake zama, sai dai muna bu'katar hutu da nutsuwa, idan dukkan mu mun fahimci manufar auren, zamu dawo mu sake zama abu guda, amma for now, ya kamata mu bar komai a hannun mai juya al'amuransa ya mana zabi".

Sumayya ta amsa da "Hakane" tare da yi masa godiyar amsa 'kiranta da ya yi, ta rufe maganar da ro'kon ya kawo mata Jawad yaranta suna ta tambayar shi. Ya amsa da gobe juma'ah zai kawo shi ya yi week end tare da su".

Ta ajiye wayar, tana kallon Sa'adah da ta yi mata 'kuri tana son jin abin da ya ce.

Kasancewar Sumayya na cikin jerin mutanan da basa yiwa 'karya kwaskwarima dan su da'dawa wani, kai tsaye ta ce "Iyah ki barwa Allah zabi kin ji, idan zaman ku bai 'kare ba, za ki koma dakin ki, idan kuwa iya adadin da aka deba muku za ku yi kenan, ina tabbatar miki ba za ki koma ba, hakan kuma ba shine 'karshen farin ciki ba".

Kuka sosai Sa'adah ta yi a wannan daren, kafin ta tashi ta 'doro alwallah ta fara sallar nafila, idan ta na addua a fili take fadin " Allah ka rufa min asiri, ka mayar da ni 'dakina, Allah na tuba".

Sumayya kawai kallon ta take tana sake jin tsoron ubangiji na kamata, yau Iyah ke wannan haukan akan Mk, Ashe duk wani kau'di da ginshirar da take yi shine kanta ya dawa?

Ko yau Mk ya mayar da ita, ta yi amanna ya karya duk wata fuffukar da take ji da ita, za kuma ta nutsu ta daina fitinarsa, tun lokacin da ta haihu amma ya iya hana ta zuwa ta dubo ta, ta tabbatar Sa'adah ta fara kai shi bango ne, ta kuma koya masa rashin kirki.

Washagari kuwa ya kawo Jawad har kofar gidan Baffa da 'yar karamar jakar kayansa da kuma ledar biskit da alawowi ga su Ayman.

Da gudu ya shiga cikin gidan! Mk na tsaye yana jin rashin dadi, yana son ya shiga ya gaida Inna, amma kunya ya ke ji, hakanan ya ke ganin rashin kyauta wa idan har bai shigan ba, saboda ya saba duk sadda ya kawo shi zai shiga su gaisa sannan ya tafi, haka idan zai dauke shi.

Har ya juya sai kuma ya dawo ya shiga, ya dade a tsaye a zauren, yana tuna moments dinsa da Sa'adah a cikinsa.

Dukkansu suna tsakar gidan Suka ga Jawad ya shigo a guje, suka rungume juna da Ayman 'din Sumayya, duk da Ayman din ya bashi shekaru biyu, amma abota suke yi sosai.

Inna ta tashi ta dauko hijabin ta da ke rataye a bakin 'kofa ta saka tana tambayar Jawad wa ya kawoka?

Yace "Malam ne", ba ta zauna ba ta dauko tabarma ta shimfida a inda ta saba shimfida masa, tana ayyana

tasan zai shigo, aikuwa kafin ta dago ta ji sallamarsa.

Ganin Sumayya lullube ta ke da mayafi, Sa'adah ce kawai a zaune ba mayafi daga ita sai doguwar rigar atamfa wadda wuyan ya mata yawa tsabar rama, kanta ba dankwali asalima tsifa take yi, ga tulin gashinta a gefen ta wadda ya ke zuba tamkar wutar daji.

Inna ta amsa masa tare da bashi iznin shigowa, Sa'adah da tun jin sallamarsa ta daskare a zaune, ta rasa me za ta yi duk kuwa da yadda Jawad ya saki Ayman ya zo ya haye cinyarta yana taba wuyanta, alamun ramar da ta yi shima ta bashi mamaki.

A hakan Mk ya shigo, idonsa ya fada cikin na Sa'adah, gabansu ya buga a tare da azama ya dauke idanuwan sa, ya isa ga tabarmar da yasan dan shi aka shimfida, a ransa ya dinga godewa ubangiji da 'kaddare shi ya shigo, da ya kunyata Inna.

Suka gaisa cike da kunya da girmamawa tamkar komai bai faru ba, haka suka gaisa da Sumayya.

Da Sa'a ta gaishe shi ya amsa mata ba yabo ba fallasa, amma yanayin da ya ganta ya matu'kar bashi mamaki da tausayi, mussaman da ya ga Jawad ya lafe a jikinta.

Ba ta ji kunyar Inna ba,

bare Sumayya, ta ajiye Jawad ta mike ta dauki hijab ta bi Mk hanyar waje, a zaure suka tsaya, ya zuba mata ido, bai ji so ko tausayin yadda ta lalace ba, domin tare suke shan bakin cikin, kawai dai shi Namiji ne, namiji kuwa da juriya aka san shi.

Ya daure ya ce "har yau ba ki fara cin abinci bane? kin ga irin ramar da ki ka yi kuwa?"

Hawaye ya 'balle mata ta ce " Ka yi hakuri , na 'kira Jawad ka tafi da mu, ka mayar da ni gidanka, ba sai ka kulani ba, zama tare da kai 'karkashin inuwar aure ya gamsar da Ni".

Ya yi murmushin da babu nisha'di ko kadan yace " ba kya yawan addu'a, ki nemi zabin Allah a tsakanin mu, ba son rai ba, sau da yawa mukan so abu 'kololuwar so, sai abin ya zama sharri ne a garemu, hakan nan muna 'kin abu iyakacin 'ki, sai ya zama alheri a garemu".

"Kar ka kwatanta ni da sharri Malam, ina hadaka da girman Allah ka yi hakuri ka yafe mini".

Ta tsugunna guiwa biyu a 'kasa

Ta cigaba da cewa "saura 'kiris na kammala idda, ka taimake ni, ka ji 'kaina."

Daidai lokacin Baffa ya shigo zauren ya kewaye su ya wuce ba tare da yace uffan ba.

Jikin Mk ya yi mugun sanyi, bai so Baffa ya gansu a haka ba, ya dubeta ya ce " ki koyi karban rayuwa a yadda ta zo miki, ki kuma daina wasa da damar da rayuwar za ta baki, na so ki, iyakacin so, amma menene amfanin son da babu kwanciyar hankali ko aminci a cikinsa?"

Da haka ya juya da sauri yana fadin "ki yi murna kin zama 'yantacciyar macen da ki ke fata".

Ta jima tana kukan zuci da na fili, sannan ta shiga gidan, ba ta tsaya a tsakar gidan ba ta shige daki ta kwanta tana cigaba da rizgar kukan da ba ya amfana mata komai.

Ganin wulgawar Jawad ya dan rage mata kewa, ga Sumayya da take tausarta.

Ranar lahadi suna zaune, Sumayya na mata kitso bayan Ahamad 'kanin Mk ya zo ya tafi da Jawad, kawai suka ga ana ta shigo da kaya, kallon su kawai Sa'adah ta yi ta fahimci kayan ta ne Mk ya Aiko musu, tunda ya ga an'ki zuwa a debo.

Abin mamaki sai ba ta ji kuka ya zo mata ba, ko dan ta yi kukan har ta gaji ne?

Tsakar gidan sai da ya cika da kaya, domin duka gadajen nan uku ya Aiko mata haka nan kujerun falo da tv plasma hatta freezer da bai 'dade da siya ba, ya ha'da ankawo mata.

Ga wasu bakko guda uku sha'ke da kaya, Sumayya ta bude biyu duka kayan Sa'adah ne, ya yin da 'dayar labulaye ne da zannuwan gado a wanke a goge, sai lokacin 'kwallah ta zowa Sa'a, wato ya da'de yana shirya mata kaya, tunda ga labulayen da suke dakunanta ma ya cire su anwanke su. Haka akwatunanta duka kayanta ne a ciki, ba kayan da ba' a wanke an goge ba, a cikin fishi ma Mk ya iya alheri, ta ayyana a ranta.

Gwala gwalan ta ne kawai ba ta gani ba, indai ba a tsakiyar kayan ya 'boye su ba. Ilai kuwa cikin katon akwatin ta ya saka mat su a tsakanin kaya.

Dukkansu jikin su ya yi sanyi da ganin kayan, hatta Baffa da yake nuna mata bai damu ba, ganin wannan kayan ya tayar da hankalinsa, balle Inna da take ta faman goge hawaye a fuskarta.

Ganin hakan Sumayya ta roki Baffan su, za ta tafi da Sa'adah Gombe, ta kwana biyu, idan ta 'dan warware sai ta dawo.

Ya kalli Sumayya, a sanyaye ya ce "kin manta ba ta kammala iddarta ba? har yanzu a matsayin matar Mutari ta ke, bani da ikon da zan turata wani guri alhalin ba hakki na bane yin hakan".

"Baffa dan Allah ka bari mu tafi, mutumin nan, ba mayar da ita zai yi ba, gaba'daya ya fita a kaina wallahi".

Murmushi ya yi ya ce " Ban sanki da son zuciya ba, Sumayya! Kar son 'kanwar ki ya mayar da ke mai son kai, kinsan me ta shuka masa ne? Ruwa ba ya tsami banza, har yau ya 'ki fadan me ta yi masa, maimakon haka sai ya 'dorawa kansa laifi, Ina rantse miki da Allah! Iyah ce ta yi wani abu marar 'dadi, ko shekaranjiya na ganta durkushe a gabansa, Ni na fara tsoro da wasiwasi akan lamarin ta, Allah dai ya sa ba wani mugun abu ta yi ba"

Sumayya ta kasa magana, tausayin Iyah na ratsa ta.

Ko da shiga dakin a zaune ta sameta, ta tsurawa gefe 'daya ido, idonta a soye, sai da Sumayya ta kirata sau uku sannan ta amsa a firgice.

"Ki fa rage dogon tunani Iyah Ina jiye miki ciwon farat 'daya.

Ta dago ta dubi 'yar'uwarta ta ce "Dama na mutu Aunti".

Da sauri Sumayya ta ajiye Anis ta 'karasa kusa da ita ta rungumeta ta ce " idan ki ka mutu, ki barni da wa Iyah? ke ka'dai gare ni bayan Innah, ko da na haifi mace ba zata cike min gurbin ki ba, bare ban haifa ba, me yasa ba za ki duba wadda farin cikinsu na 'damfare da ke ba? Yanzu Mukhtar din da ba ki san shi ba sai da kika mallaki hankalin ki ne, zai sa ki yi fatan mutuwa ki bar Baffah, ki bar Inna, ki bar Jawad, ki bar Ni?"

Sai lokacin kuka mai ciwo ya gocewa Sa'a.

Sumayya ta cigaba da cewa ki fauwalawa Allah lamarin ki, ina tabbatar miki zai kawo miki mafita, ki ha'kura da Mukhtar yadda ya ha'kura da ke, ba sai da shi za ki rayu ba, ba sai da shi za ki yi farin ciki ba, ki dube mu, ruwa da iska ba zamu canja ki ba, shi kuwa ko gobe kina iya jin ya auri madadin ki, ya shayar da ita soyayya irin ko ma ta zarta wadda ya miki, fatana dai ki 'dauki darasi, kar ki sake maimata irin kuskuren da ki ka yi idan kin samu wata damar".

Ganin maganganun na shigar Sa'adah sosai, Sumayya ta zarce da fadin "gaba'daya aure ha'kuri ne da kawar da kai, duk macen duniya da ki ka ga ta tsufa a 'dakinta ta shiga 'kalubale kala kala, amma idan aka yi ha'kuri aka danne sai a cimmma babban matsayi, ki cire buri, da son 'kyale 'kyale ki rabu da 'kawayen banza na tabbatar wadannan abubuwan sun taka muhimmiyar rawa wurin mutuwar aurenki".

Sosai ta ke kuka a 'kirjin Sumayya karon farko tun bayan rabuwar su da ta samu ake rarrashinta cikin tausayawa.

Haka suka shafa lokaci mai yawa Sumayya na lallashinta, tare da 'karfafa guiwarta.

Kwanaki goma Sumayya za ta yi tare da yaranta, adalilin Yaran suna hutun zangon karatu na uku, sannan kuma mijinta na cikin tawagar da aka zaba zuwa New York din 'kasar Amurka akan sanin dabarun inganta bankunan 'kasashen Africa.

Zaman Sumayya ya taimaka wa Sa'a sosai, tare suke cin abinci, sannan sai da ta sa Inna ta sauko da ga fushin da take yi da ita, Baffa kuwa cewa ta yi tasan duk dauriya yake yi, amma ai shi da Iyah sai Allah.

Ya yi dariya ya ce "wato ta tabbata kema zargina kike akan na fi sonta, kamar yadda itama ta ke 'kalubalantar gyatumarku ta fi son ki".

Sumayya ta yi dariya ta ce "Ni bana kalubalantar ka Baffa, ai ita 'karama ce, sannan sunan iyakar ka ce".

"Allah ya miki Albarka Sumayya, yau kusan shekaru sha bakwai da auren ki, ba ki taba janyo mini bacin rai ko jin kunya ba, ina fatan ki dore da hakan, ina matu'kar jin dadi, Ina alfahari da kasancewa ta uba a gare ki, Àllah ya miki shirya miki zuri'a, ya faranta miki, ya buda miki kofofin alheri".

Cikin kukan farin ciki ta ke fadin "Ameen Baffa!ni ma Ina alfaharin da ka kasance uba mai kare mutunci da martabar yaransa a gidajen aurensu madallah da uba irin Baffah na".

Sa'adah da ke 'daki tamkar mujiya ta ji wani 'kullutun ba'kin ciki ya mamayeta tun farko dama tana kishin taga iyayen ta suna nunawa Sumayya soyayya sama da ita, duk da Inna ta fi wannan abin dan ta cusa mata takaici, amma Baffah kowa yasan itace 'Yar gaban goshinsa, amma wai yau ita ya ke yiwa zambo, yana nunawa Sumayya ce mutum, yana ta 'kwararo mata addu'a ita ka'dai.

Hawaye na zuba 'kasa 'kasa ta ce "Ni da na yi shekaru bakwai aka sako ni, sai a kore ni ko a tsine mini na bi titi ina tsince tsince".

Da sauri ta tura hular kanta a baki tana cewa " Astagafirillah Ubangiji ba da Baffah na ke ba da kaina na ke, Allah na tuba, ka yafe min, ka mini albarka, ka saukaka mini lamarina, ka mayar da ni 'dakina".

SURAYYA DAHIRU

✍